🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾

💰💸 DOLLARS 💸💰

🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾

Story & written by
mommyn fareesa

Happy sallah to All Muslim Allah ya maimaita mana ya k'arbi ibadunmu👏🥹

*GODIYA*
Alhmdllh Ala kully halin" godiya ta musammun ga Allah S W A daya nunamun na fara wannan littafi lafiya"yah Allah yadda na fara lafiya Allah kabani Aron rai da lafiya na gama lfy....

*GARGAD'I*
wannan littafin k'irk'irarran labarine banyi shi dan wata kodan waniba idan yayi daidai da rayuwarshi Arashine"Aguji sauyashi ta kowace siga sbd hakkin mallakata ne....

dedicate to All members of my groups🥰Ina yinku over guys💃💃

BISSIMILLAHIR RAHAMANIR RAHEEM

Page 1&2

KANO STATE ! ..........misalin k'arfe hud'u da mintina goma sha d'aya na yammacin yinin yau Friday"garin yayi lullumi da d'an duhu had'e da iska me tsananin dad'in gaske, sbd hadarin dake a lullub'e sararin samaniya…....Adaidai lokacin kuma wasu zuk'a zuk'an had'ad'd'un motoci guda 4 na kece raini suka doso cikin Anguwar kabuga Ajere"duk wanda ya kallesu saiya k'ara kallonsu sbd yadda sukayi matuk'ar yin kyau"hakan yatabbar ma da y'an Anguwar both yadawo...kai tsaye bakin get d'in wani katafaren gida na Alfarma Anguwa guda suka tsaya"wanda daga bakin get d'in gidan daga sama An rubuta *BUGAJA'S HOUSE* da manyan harrufan bak'i"securities ne kusan 24 ke tsaye daga bakin get zuwa cikin get d'in gidan da kuma gefen dogon ginin daya k'awata tsarin gidan...horn kawai Aketa dannawa babu k'ak'k'atawa"yayinda wasu y'an jarida maza ukku mata biyu ke tsaye daga gefe, da Alama wani suke son gani.....motar dake daga tsakkiya fara me tinded itace y'an jaridar suka nufa"saidai tun kafin suyi mgn driver d'in motar yayi ciki ta hanyar danna hancin motar cikin gidan"yayinda sauran motocin dake bayansu guda biyu suka bi bayansu"hakan ya tabbarma da y'an jaridar cewar wanda suka so su gani suyi mgn dashi bazai yuyu su ganshi ba"kimanin shud'ewar mintina 3 motocin suka gama yin parking"kafin gaba d'aya motoci guda ukkun body quards suka fito daga ciki suka zagaye farar motar aka bud'e back sit....saida aka d'auki kusan second 5

kafin Anutse Aka zuro wasu dogayen k'afafuwa masu sanye da takalmi *chukka boot* Atake wani irin sanyayyan k'amshin turaruka yacika wajen"Ida fitowa yayi yana sanye da jeans blue da t shirt red colour ,wacce ta fito da k'iran shape d'in jikinsa irinna k'arfaffan namiji meji da mazan taka,ya Aza hula pasincap wacce ta rufe goshinsa da gashin kansa me sulb'i da taushi"yayinda idanuwansa ke b'oye da eye glass bak'i"sosai kayan sukayi matuk'ar dacewa da lallausar farar fatar jikinsa mai matuk'ar shek'i da d'aukar idon mai kallo" ga wani mayataccen k'amshinsa mai saka zuciyar mai shak'a raunana da nutsuwa"red lips nasa Atsuke suke"dogon hancinsa da zagayayyen k'asumbarsa kawai Ake iya gani"yayinda hannunsa guda ke rik'e da phones nasa guda biyu "yayinda gudan hannun ke rik'e da k'aramar waya k'are Agefen kunnansa"mgn yakeyi k'asa k'asa bama'a iya jin me yake cewa"sai dai A hankali yake maganar tamkar baya so! *dollars bugaje* kenan! matashin saurayi me jini Ajika"dan k'walisar guy d'in nan maiji da lokaci da giyar kuɗi , kyakykyawa mai girman kai da jan aji wa manyan matan dake nuna zallar kaunarsu garesa..."kamar yadda wasu ke fad'a"ita kanta tafiyar tasa Abin kallo ce sbd yadda yake yinta cikin nutsuwa kuma baza'a ce da sauri koda lak'ai kaita yake yintaba"tunda yafito daga cikin motar ya shak'i iska ya fesar, drictly ya nufi sashen su daddy bayan yayima body quards nasa Alamar baya buk'atar su"wayarsa ya janye daga gefen kunnansa ya cigaba da tafiyarsa yana tunanin meyasa suruj keson yatsaya y'an jarida suyi fira dashi?"bayan duk wani Alkhairi da zaiyiwa wani ko wata yana yine dan Allah badan wasu su saniba"shi Aganinsa yin abu sbd mutane su sani su yaba maka *Riya ce*.....yana wannan tunanin ma'aikatan sashen su daddy dake daga bakin k'ofar shiga parlourn suka fara gaidashi kamar zasuyi masa sujjada "ya tab'e baki ya wuce ciki"Ahankali yaturo k'ofar parlourn ya shigo da sallama sau guda iya lab'b'ansa "bayan *Malika* dake zaune ta tsare k'ofar da Ido sbd tana jiran shigowarsa da mutanan dake cikin parlourn zasu d'auka beyi sallama ba ya shigo sbd yayi k'asa da murya...."kallo d'aya yamata ya d'auke kansa yana ya mutsa fuska"dukda ita bata samu damar kallon idanuwansa ba saidai kyakykyawar fuskarsa kawai data k'wallah cikin second 2 ta janye idanuwanta sbd gudun kar ya gane tana kallonsa"taci gayunta cikin sabuwar Atamfa super jaba "wacce aka mata wani watsatstsan d'inki na doguwar riga gownt"sai fari da Ido takeyi tana murmushi "yayinda *dollars* ya d'auke kansa bema san tana yiba"kabeer da naseem da mahaifiyarsu Hjy jamilah suna zaune kan kujerun da suka k'awata parlourn"Naseem nata kallonsa yana murmushi wanda shekarunsa ba zasu wuce 17yrs ba ya mik'e tsaye yana fad'in oyoyo *yaya Muslim* ! dama nasan yau zaka dawo shiyasa ban fita ba"yak'are maganar yana tsayawa gefensa cikin nuna murnan ganinsa"shi kuwa fuska yad'an saki yakama hannunsa suka zauna gefen kujera yayinda Malika keta masa sannu da zuwa cikin kashe murya "Hjy jamila kuwa murmushi ne me tattare da ma'anoni masu yawa kwance saman fuskarta"tunda suka zauna Naseem ke gaidashi da tambayarsa yaya yabaro k'asar America?"kafad'arsa kawai yadafa kafin yasaki murmushi me d'an fad'i"cikin muryarsa me kauri da dad'in Amo yace"mommy Ina wuni?"lafiya qlau ya hanya?"naga wannan sarkin maganar ya janye hankalinka ne"Alhamdulillah! kawai yafad'a Atak'aice"sai lokacin yaya kabeer ya gaidashi"ya Amsa cikin rashin kula ya mik'e tsaye "yaya food is ready! cewar Malika tana washe baki"saida dollars ya d'auki kusan second 5 kafin yace "okay sannan yacika hannun Naseem da nufin ya wuce side d'in daddy"Naseem yayi karaf yace"yaya yaushe zaka kaini wajen Anty muslima ?"niban san gidansuba kuma bata zuwa nan gidan.....wani makirin murmushi dollars yasaki Akaro na farko sbd yana lura da irin hararar da Hjy jamila ke wurgoma Naseem "tamkar bazaiyi

mgn ba  sai kuma Anutse yace"*very soon zata dawo nan gidan harta d'auki Abinda ta jima da Ajiyewa* daga haka yayi gaba yabar musu daddad'an k'amshin turarensa "yayinda Hjy jamila da Malika da yaya kabeer ke kallon kallo sbd sun kasa gane ma'anar kalaman dollars"wani irin gwabron numfashi mommy ta saki tana bin Naseem da mugun kallo tace"bak'in muna fuki ban hanaka zancen shegiyar yarinyar nan ba?"ki barshi mommy na masa shegen duka magulmacin banza"cewar yaya kabeer"haba mommy ! Na rasa laifin me Anty Muslimsa ta muku keda su Anty Malika da bakwa sonta??"bayan kuma itama y'ar gidan nan ce daddy ne mahaifinta....kallon da Malika ta jefesa dashi yasaka yayi shiru yana gunguni yafita"yaya kabeer yaja tsaki ya mik'e tsaye shima yabar parlourn"mommy ta kalli Malika tana fad'in kin tabbatar kin zuba maganin cikin komai da kika tanadar masa?"Eh mommy na zuba"to shikenan boka yace muddin yaci Aikin gama yagama"so nakeyi da safe na yiwa Alh mgn yamasa zancen zai had'aku Aure kinsan da sauri zai Amince duk wannan girman kan nashi zai ajiyesa "ya zama mu Hjy najah ta haifama shi "indai bashida wannan sunan da darajan ga mutane da kallo be isheniba" balle har naso ya Auri y'ar cikinah"muslima kuma na riga na rabata da Alh yana jin zafinta Aransa baya kulawa da ita "shiyasa kikaga kamar bashine ya haifetaba"wlh mommy na tsani shegiyar yarinyar nan nan ko sunanta naji an fad'a sai naji fad'uwar gaba"nifa rabona dana ganta 2yrs kenan" hmmm! idan Ana sallah ba'a mgn yarinya ,in bacin tsoron hukuma dana kasheta da hannu nah"tun tana cikin uwarta naso na zubar da cikin y'ar banza Amma Allah yasa rayayyace"nide mommy burinah yanzun shine naga na mallaki yaya Muslim Amatsayin mijinah"idan hakan yafaru saina zuba ruwa k'asa nasha"wasufa da yawa gani sukeyi kamar ba d'an gidanmu bane k'arya nake musu"ni  yanzun na mallaki yaya Muslim za'a ga Abu wlh"ta k'are maganar tana juya idanuwanta had'e da lumshewa "tana jin kamar ta jawo ranar tazo"itadai Hjy jamilah na zaune tana  Aikin kallonta , had'e dayin murmushi sbd itama tana hasaso irin yadda  zata k'ara fantama idan ta zama surukar *dollars bugaje*.....

Daddy da Abba suna zaune a parlourn daddy suna firansu irinta d'an uwa da d'an uwa"Ahaka dollars yashigo da sallama cikin nutsuwar data zamo dabi'arsa"duk irin matsayinsa da d'unbin dukiyar daya tara  be hanashi girmama K'annan mahaifin nasa ba"wanda  Ayanzun sune iyayen shi "cikin murnar ganinsa suka Amsa sallamarsa "wanda rabonsu dashi duka sati d'aya kacal kenan"duk week end Agida Nigeria yakeyinta"sbd sauran ranakun baya k'asar yana zuwa k'asashen waje yana duba kamfanin nikansa nacan.....my friend sannu da isowa"cewar daddy yana murmushi bayan sun Amsa sallamarsa"Abba na murmushi yabashi hannu had'e da fad'in babanah ya hanya?"Alhamdulillah Abbah da fatan na sameku lafiya?" yak'are maganar yana zama kan carpet"duk suka Amsa da lafiya qlau"babanah meyasa baka son fira da y'an jaridah ne wai?"banaso wasu na kiranka dame girman kai.....shiru yayi na kusan second 10 tamkar bazaice komai ba"sai kuma ya kai hannu bisa kansa "Ahankali yayi baya da pasincap d'insa "nutsatstsiyar fuskarsa mai cike da kwarjini da cikar haiba da zati ta bayyana"uhmm Abba d'an jarida shegen mutum ne"tsayawa na saurarensu Aganina bashida Amfani"iya Abinda nasani komai zanyi inayine dan Allah ba dole sai kowa yasani ba"wannan gaskiya ne babanah Amma idan lokacin daya kamata ka saurarensun yayi ka saurara kajiko? "dollars na k'ok'arin mgn babbar wayarsa tayi ringing "kobai dubaba yasan Abbie ne sbd  irin ringing d'in daya saka masane.... d'an murmushi yasaki yana kallon wayar yace"daddy Abbie ne ! dama banje wajen suba shida Eyyah nan nafara zuwa"to shikenan my friend maza kaje wajen takwaranka "dato ya Amsa ya mik'e tsaye cikin nutsuwa yafita"suka bishi da kallo Abba yace"yaya zaman suraj da

muslim da kabeer bbu Aure yana damuna?"especially ma muslim" da shine babban kuma kaga irin yadda Allah ya d'aukakashi yaka mata Ace yanada iyali "hakane gaskiya nima Abin nadamuna Amma mubarsu su duka tsakaninsu da Abbie ne"tunda yayi shiru be musu zancen ba Akwai Abinda yake nufi"balle kuma kasan ba'a shiga tsakanin Abbie da my friend"hakane yaya Allah yazab'a Mafi Alkhairi"sai kuma dama inaso na maka mgn kan muslima.... Atake daddy ya had'e rai yana duba time ya mik'e tsaye had'e da cewa kasan 5:00 pm inada meeting a office "dama dalilin k'in fitar tawa shine zaman jiran shigowar Muslim d'in"to Alhamdulillah na gansa ya iso lfy.daga haka yayi shiru yana gyara malun malun d'insa "tsabar mamaki Abba kasa mgn yayi saidai kawai yabiyosa suka fito tare"tunani yakeyi Aransa meyasa duk sadda za'a yi zancen muslima daddy bayaso ko bazai tankaba kamar ba y'arsa d'aya Haifa ba"in bacin da Muslim ke tsaye wajen d'aukar nauyinta da karatunta dafa har yanzun bazasu son wani Abu Akan taba "sai kuma Abbie dake k'ok'arin kulawa da ita shima......dollars na fitowa kai tsaye side nasa ya wuce sbd mutum ne shi mai masifaffiyar tsabta "dukda garin yayi sanyi da dad'i Amma yafi buk'atar yayi wanka kafin yaje wajen kakannin nasa ya gansu "sati guda kawai da yayi batare dasuba shine kawai yasan yadda yaji"ba k'aramin kewarsu yayiba"da trolleys d'insa guda biyu yayi cin karo had'e da wani body quard nashi da Alama shine yakawo troleys d'in "yana ganinsa jikinsa har kirma yake yace"y'allab....da hannu ya masa Alamar yaje kawai"kafin yazaro key daga cikin Aljihun wondonsa yabud'e k'ofar parlournsa yasaka trolleys d'in ciki"wani irin sanyayyan k'amshi na turarukan wuta dana irin  turarensa yadaki hancinsa"yabi ko Ina da kallo very need"ya lumshe fararen kyawawan idanuwansa yana koma bud'ewa"yana jin tsananin k'aunar *Eyyah*  Azuciyarsa,sbd yasan itace ta gyara masa "duk sati idan zai dawo Nigeria haka take gyara masa sbd farin cikin sa"dan tasan besan masu Aiki na shiga sashensa"kuma gashi da k'yank'yami"numfashi ya sauke yana nufar upstairs yatura k'ofar katafaren bed room d'insa"wanda tsarin ginin d'akin baccin nasa irin na k'asar turai ne"gaba d'aya bango guda glass ne yana iya hango wanda ke waje Amma shi ba'a iya ganinsa"Ajiye trolleys d'in yayi gaban ward rope yafara k'ok'arin rage kayan jikinsa....Kimanin shud'ewar mintina 37 dollars yafito cikin wani zazzafan wankan dayafi na d'azun "Shi mutum ne da ko yaya yasaka sutura ko badan kwalliya ba saita nuna kanta a jikinsa, koda bamai muhimmanci bace da rashin tsada"rufe part d'in nasa yayi ya wuce b'angaren kakannin nasa"yana a hanya jefi jefi yana Amsa waya"Ahaka ya shigo had'ad'd'en parlourn Hjy Eyyah"wanda koda yaushe ke a tsabtace"dattijuwar Arzik'i dakeda shekara 72 Aduniya"tana zaune kan carpet tana Azkhar d'in yamma"kayan marmari cikin plate na'a gabanta Ajiye"tana d'an ci tana kuma kallon TV "wuf d'aya idan ka kalleta zakayi zaton bazata wuce 65 yrs ba sbd hutu da jin dad'in rayuwa yab'oye shekarunta"tunda taji sallamar d'an gidan nata"fuskarta ta fad'ad'a da fara'a tana Amsawa had'e da cewa babban mutum ka koma inda ka fito"wato shine sai yanzun katuna damu ko?"shidai beyi mgn illah murmushinsa me ban sha'awa dayake saki"ya zauna gefenta yadafa kafad'arta suka gaisa "kafin yazame jikinsa ya Aza kansa saman cinyoyinta"muslim baka girma ko?"k'in tankata yayi"kaga Abinciccikan dana Ajiye maka duk suna nan harda mutuniyar taka(fura)"ta k'are maganar tana shafa suman kansa"saida yad'an b'ata fuska kafin yace "nifa naci Abinci cikin jirgi sai Anjima k'ilan zanci"shikenan harda naman duk sai Anjiman?"uhmm"ya fad'a yana duba Agogon fatar dake d'aure Adamtsan hannunsa "eyyah zanje gidan umma nadubata(mahaifiyarsa)" Amma fisabilillahi Muslim haka mukayi dakai?"tunfa wancan satin nace kaje kadubo muslima kwana 2 mun dena jin motsinta kace Abari sai wannan satin"kabar zuwa

wajen umman naka saida dare ko safe mana......shiru yayi tamkar badashi iyah ke mgn ba"dole waima shine zaije yadubota?"shifa gaskiya ana takurashi,gashi yana jin haushin yarinyar sbd y'ar rainin wayo ce ko gaidashi batason yi sai kakarta ta mata mgn"shi kuma baya d'aukar raini" ko namiji d'an uwansa be isa yatakashiba balle mace,macenma kuma k'aramar yarinya"wacce ya yaraina da.....wai kana jina maganarce ta gagara ka Amsamin ishashshe?"tamkar zaiyi kuka yad'ago kansa yad'an kalli Iyah fuska bbu walwala yace "zanjefa eyyah"hmm ! muslim yaka mata kaduba zancen nan gaba d'aya na rasa meyasa daddynka baya son zancen muslima tuni batun yanzun ba"nayima Alh zancen sai yace karna damu"kaje dan Allah kadubota ni yanzun tunda ta zama budurwa naji ban Aminta da zamanta wajen Hjy hajaraba....shidai dollars sauraronta kawai yakeyi yana kuma danna waya"hakan kuma yayi daidai da shigowar yaya suruj"mutumin kana nan kenen?"uhmm kawai dollars yafad'a yana janye kansa daga kan cinyar eyyah "fuska bbu walwala yatashi tsaye yana kallon suraj yace"muje"Ina kenan?"tab'e baki yayi yak'i tankasa yanufi k'ofa "eyyah ta girgiza kanta tasan sarai beson zuwa sbd beson tayi fushi shiyasa zaije"batasan lokacin da murmushi yasub'uce mata ba"gaba d'aya tasan muslim beson b'acin ranta itada Abbie"baya tsallake umarninsu "shiyasa kaf cikin jikokinta babu wanda yakai matsayin da Muslim ke dashi Awajensu"

wai Abokinah lafiya Ina zakaje ne?"cewar suraj yana isowa gefen dollars dake k'ok'arin Amsar key hannun driver ya cillahwa suraj batare daya furta komai ba "wai meyasa dollars baka son fita da body quards naka sai dole?"saida yad'an tab'e baki had'e da d'age kafad'a kafin yace babu Atak'aice yana bud'e gefen me zaman banza yashiga ya zauna "shima suraj d'in shigowa yayi yabama motar wuta had'e da cewa Ina muka nufa"da k'yar dollars yace" hotoro" d'an murmushi suraj yasaki sarai ya fahimci eyyah ta turashi yadubo muslima shiyasa yaketa d'acin rai "yasan halin Dollars idan y'an jin kansa suka motsa yafi miskilin mutum wuyar sha'ani"yasan shiba miskili bane sbd sarai yana mgn Amma da wanda yaga dama"saidai da yawan mutane na masa kallon me girman kai....kana bani mamaki wani lokacin"musammun idan natuna Abaya yadda kake kulawa da muslima"Amma yanzun na fahimci bakwa shiri da ita"da Anyi zancenta saika had'e rai "kodai kaima Hjy jamilah ta shiga tsakaninku ne?kamar yadda ta shiga tsakanin muslima da daddy....look Suraj! Kasan dai na tsani irin wa'annan maganganun"mutum ko Aljan be isa yamun Abinda Allah be munba"sannan kadena mun zancen marar kunyar yarinyar nan"yafad'a yana yatsina fuska ya d'auki earpiece ya lakafa a kunne"suraj ya girgiza kansa had'e da cewa kaji dashi"na fahimci yau wata sabuwar masifa kakeji ko?.....to bani nakashe zomon ba! banza dollars yamasa ya maida kallonsa Awaje sbd ganin Anfara yayyafi da buji"saiya lumshe Ido ya jingina bayansa Ajikin kujerar fuskarsa kadaran kadahan"sbd yana son irin wannan yanayin na damuna"sarai yana jin yadda suraj ke masa fira Amma yamasa banza....

******************

Anutse cikin kamun kai had'e da jan aji take tafiyarta, tana doso cikin layin Anguwar tasu "yarinya ce black beauty da bazata wuce 20 yrs ba"tana sanye da dubai abaya light puple "wacce tayi mata matuk'ar kyau ta haska fatarta"wanda sai mai kallo ya nutsu ya kalleta sannan zai gane irin baiwar sihirtaccen kyau datake dashi"ita ba doguwa ba kuma gajeraba"bazamu kirata me k'iba ko ramammiyaba"fuskarta babu make up a kwab'e take sbd kasancewar ta shagwab'ab'biya "daga gidansu k'awarta jidda take takai mata ziyara sunyi kuma fad'a da ita

sbd yayan jiddan yace yana sonta"tana cikin wannan tafiyar iskan hadari yataso aka fara yayyafi "kamar Ance ta juya ta hango wasu samari su 3 da k'ananun kaya Ajikinsu suna biyota"gabanta yafad'i sbd ta fahimci irin y'an shaye shayen nan ne"saita juya taci gaba da tafiya Amma Atsorace take sbd ganin layin bbu kowa dan yayyafin yafara k'arfi"koma juyowa tayi a karo na biyu  taga sun kusa cimmata suna nunata da yatsa, hakan yasa ta baza Aguje "Atake suka mara mata baya suma.....✍️

Uhmmm wannan shine somun tab'i! littafin dollars da zafinsa ya sauka sai mun nutsa cikin gundarin labarin zakusan Ainahin dame yake tafe?

Hanzarta biyan naki halal d'in tanan 👇
wannan book d'in nakudine
Regular grp 500
Vip grp 1000
Special grp 2k wato 3pages in a day

zaku biya kud'in ku ta wannan acc number👉2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK
Kituro shaidar biyanki what's app number d'ina  08100084251 500 kawai ake turo Kati idan bakida acc amma sauran payment d'in ta acc ne

banason transfer d'in Kati ko vtu photo d'in katin MTN zaki d'auka saiki turo  dan Allah banda kira❌

Y'an nijar kutuntub'i wannan n👉 +227 88 01 90 50

Regular 500f
Vip 1000f
Special grp 2000f

Dan girman Allah da darajan iyayenki karkimun mgn idan baki shirya ba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: 🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾

💰💸 DOLLARS 💸💰

🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾

Story & written by
mommyn fareesa

Dedicate to zainab hamisu wada Ina yinki over tawan 🥰🥰

Free page 3&4

..........Cikin tsananin tsoro da tashin hankali take gudu had'e da waiwayon su ,gashi Anata yayyafi bbu Alamar kowa a layin"duk gidajen dake layin kowane get A rufe yake"nishi kawai da hak'i takeyi sbd tafara gajiya da yin gudun "tana k'ok'arin shan kwanar wacce daga ita sai layin gidansu taku san cin karo da wani mashin....da hanzari ta kauce tana sakin k'aramar k'ara tayi tsaye tana maida numfashi had'e da tsurama  mamallakin mashin d'in firgitattun lulu eyes d'inta dake tattare da tsoro da rikicewa"saida taji gabanta yafad'i da suka had'a Ido dashi"sbd yaja ya tsaya ruwan na sauka Ajikinsa da hular kwano saman kansa"sai kayan ball  dake Ajikinsa...kallonta kawai yakeyi bece komai ba"saidai tana d'auke idanuwanta mutanan na isowa suka kwashe da dariya suna binsu da wani irin shegen kallo "Arikice *muslima* tafara girgiza kanta tana matsawa baya cikin zazzak'ar muryarta me sanyi da d'an kauri tace"dan Allah kataimakeni ! ban sansuba sun biyoni....ke ! dama najima Ina ganinki bakin titi kina wucewa kuma kin mun"wannan lusarin be isa ya hana faruwar komai ba"cewar babbansu yana lashe leb'e had'e da binta da mayen kallo"Ahankali yazare hular kwanon dake saman kansa yayi wurgi da ita yadiro daga saman mashin d'in"yayinda muslima ke tsaye daga gefe tana raba Ido duk ta jik'e da ruwa"sauran mazan biyu sunyi matuk'ar jin shakkar *Aliyu* dake nufo gaban ogan nasu"hakan yasa suka ja baya"wata wawar cakuma Aliyu yamasa fuskarsa bbu rahama yafara bashi zafafan puncher's had'e da fad'in ka d'auka ban sanka bane?"kun saba yin tsageranci cikin Anguwa sbd ana k'yaleku ko?"yak'are maganar yana ingizashi da k'arfi sbd ganin zai fiddo wuk'a daga cikin rigarsa"jikinsa nata warin wee wee ,da Alama saima da sukayi shaye shaye suka biyota"yana ingizashi ya ware Aguje "wani irin numfashi muslima ta sauke"sai kuma tafara k'ok'arin juyawa ta  tafi sbd ta rasa meye zatace masa?" ita dai ko sunansa bata sani ba"ta fahimci Anan Anguwar yake Amma farkon layin"wannan ganinta dashi na ukku ne"duk time d'in da zata wuce tana lura dashi yanata kallonta.....Ina zakije ne ?"muryarsa me taushi ta dawo da ita tunaninta"batare data kallesaba tace"gida zanje nagode sosai "inane gidan naku?"yafad'a yana d'aukar hular kwanon sa yanufi gefen mashin"meye ruwanka da sanin gidanmu?"ta fad'a tana ja baya "murmushi yayi sbd tabashi dariya ya lura matsiwaciyace ga kuma tsoro datake dashi"sbd ya fahimci idan k'ilan yace shima biyota zayayi guduwa zatayi"Ahankali yace inada ruwa da sanin gidanku"muje na rakaki "kinga ana ruwa kar kiyi zazzab'i ko?"shiru tayi tak'i mgn tayi gaba"shi kuma yabiyota yana jan mashin d'in"har lokacin ruwa Akeyi saidai bada k'arfi ba"har suka iso bakin get d'in gidansu babu wanda yayi mgn cikinsu"saida ta tura k'ofar get d'in sannan ta juyo suka had'a Ido dashi"da sauri ta d'auke kanta "murya Atausashe yace"sunana *Aliyu Ahmed* Anan Anguwar nake banjima da dawowa ba daga wajen gama karatu nah ba"Ina yawan ganinki Anan layin idan ba damuwa inaso muzama Abokai"tana k'ok'arin mgn sukaji

horn"juyowa muslima tayi.....dam! k'irjinta yabuga da k'arfi sbd ganin motar kamar ta dollars ce "dukda yana jimawa kafin yazo gidan, kuma bada mota guda yake zuwaba Amma ranta yabata shine cikin wannan motar "sosai taji haushi da b'acin rai "sbd ita bata wani son yana zuwa yayita wani shan k'amshi da rainin wayo shiyasa ita babu ruwanta dashi"musammun data fahimci da k'yar yake Amsa gaisuwarta"wani lokacin kuma k'ememe zaiyi yak'i Amsa gaisuwar tata ya basar kawai....kinyi shiru?"shima Aliyun haushi taji yabata"saita wani turo baki tace"nide sai Anjima "pls samun contact naki mana"yak'are maganar yana mik'a mata k'aramar wayarsa "Adaidai lokacin kuma motarsu dollars ta shige cikin get d'in gidan"tunda suka shigo layin ya lura da muslima dake tsaye da wani saiya d'auke kai kamarma be lura ba"suraj ma yaso yayi mgn Amma ganin yadda dollars ya had'e rai yasaka be tankaba"saidai kuma bayan sunyi parking sun fito sai yaga yana sakin wani shed'anin murmushin daya fito masa da baiwar kyawun halittar sa,yana shafa lallausan b'akin gashin kansa irin na buzayen usuli"suraj ya girgiza kansa sbd yasan tabbas wata tsiyar dollars zai shiryawa muslima"dan dama idan zai shirya wata muguntar haka yakeyin irin wannan murmushin...shine Agaba suraj natake masa baya suka wuce cikin parlourn da sallama Anutse "Hjy na kwance kan 3 seeter tana tunanin Ina muslima ta tsaya har shidda saura ga yayyafi Anfara?"tanaso ta kirata Amma bata iya gane number nata"gashi *sadam* duk yau bezo gidan ba"motsin turo k'ofar da sallamarsu yasaka ta tashi zaune "Atake ta saki murmushi tana fad'in *yusuf* ne yau  Agidan namu"kansa ak'asa yace"nine Hjy barka da hutawa"yak'are maganar suna zama kan kujera suka gaisa"kafin Hjy tace"*halimatun* bata nan taje gaisuwar juma'a gidansu k'awarta hauwa'u"gashi har Anfara ruwa batama dawo ba"shiru kawai dollars yayi Aransa yace"tana gidansu k'awa ko tana can tsaye da saurayi suna mgn....be gama wannan tunanin ba yaji sautin muryarta me kama da busar sarewa tayi sallama ta shigo "ko kallon gefen datake beyiba saima yamaida hankalinsa kan waya ya d'aure fuskarsa"wai sai yanzun kika dawo?"cewar Hjy ,Eh Hjy ruwa Aka fara danaga yak'i tsayawa saina taho kawai"yaya suraj sannu da zuwa Ina wuni?"murmushi na sub'ucewa suraj ya Amsa sbd yasan sbd tabama dollars haushi shiyasa bata nuna tasan da zamansa a parlourn ba balle harta sakosa cikin gaisuwar"shi har mamakin rashin shirinsu yakeyi"lafiya qlau muslima ya karatu?"Alhamdulillah mun gama sai jiran saka mako"wai bakiga abo.....Hjy dama daddy yaturomu mu tafi da ita can wajensa zatayi ko sati biyu sbd wasu daga cikin dangi basu sontaba"yak'are maganar yana wurgoma muslima wata uwar harara "sbd ganin tasaki baki afurgice tana kallonsa da sauraronsa"saidai yana hararar ta ta murgud'a masa d'an bakinta "ta maida kallonta wajen Hjy sbd taji wace irin Amsa zata bama dollars"yayinda shi kuma uban gayyar ya jefi suraj da kallon gargad'i yana gimtse fuska......to shikenan bbu damuwa saita had'a kayanta ta biku ko?"nide Hjy dan Allah Abarshi gobe sat day zanje kawai....ta fad'a cikin shagwab'a "mik'ewa tsaye dollars yayi fuskarsa bbu Annuri ko kad'an cikin gadara da d'auke kai yace"muna waye mintina biyar na baki ki samemu Acan"Hjy zamu wuce sai Anjima "bejira cewar taba yasakai yafice da hanzari"yana jin zuciyarsa na zafi"dole yasaita yarinyar nan tunda wuri sbd ya lura raini yafara shiga tsakaninsu"zata kuma gane kuranta idan shi sa'an wasanta ne.......yana fitowa yanufi mota yanajin suraj na masa mgn yak'i tankasa yabud'e motar yashiga mazaunin driver "kai zaka yi driving d'in kenan?"cewar suruj bayan ya shigo cikin  motar"banza dollars yamasa yana duba wristwatch d'insa yanata jan tsaki"can ya hango Muslima na nufosu jaye da troley tanata sharb'an kuka "directly gefen dayake zaune ta nufo sbd k'ofar Abud'e take"shi kuwa yana ganinta yakoma had'e rai.......murya araunane take

furta dan Allah yaya muslim kayi hak'uri ni wlh bana son zuwa can, kowa baya sona saisu eyyah kawai kuma su yaya kab.....shout up! zaki wuce ki shiga mota muje ko saina tattakaki"Ina kika baro ita rashin kunyar taki?"na d'auka Ai ban isaba ki rok'eni"kamar yadda ban Isa ki gaisheniba"Amma dan Allah bakai bane baka Amsa.....bazaki wuce kishi ba?"yakatseta da k'arfi"yana tsareta da mayatattun idanuwansa,Aguje ta bud'e k'ofar ta shigo"shidai suraj naji na gani Amma be tanka musu ba"saidai dama yasan tabbas murmushin dayaga dollars yayi ya tabbatar wani Abu marar dad'i zai yiwa muslima "saidai yasha Alwashin zai masa mgn ya hak'ura bayan sati 1 yamaida ita wajen kakarta yasan halin Hjy jamila ba kyau ne da itaba"sannan ga daddy ya tsani yarinyar zaman k'unci kawai zatayi Agidan....da mugun gudu dollars yaja motar suka nufi gida"motar tayi tsit muslima nata sharb'an kuka....mitww! wlh kokimun shiru ko kuwa idan muka Isa gidan kukan da zakiyi sai yafi wannan "tsit tayi sbd tasan zai iya yimata mugunta tunda yatsaneta shima....

Alh yusuf bugaje dattijon Arzik'i me nagartattun halaye"Wanda keda ilimin Addini matuk'a"Asalinsa d'an k'auyen bugaje ne dake jihar katsina state"duk kowa nasa nacan"kasuwancin siyar da fata yakawosa garin kano"har ya had'u da halimatu sukayi Aure suka zauna Anan cikin garin kano yana kasuwancinsa"duk bayan d'an lokaci yakan je bugaje yaga iyayen sa"haihuwarsu ta farko suka sami d'a namiji suka saka masa suna Isma'il,daga shi sai sulaiman,sai habibu sannan Autarsu habiba "sun taso cikin so da k'aunar juna had'e da had'in kai"da farko irin sana'ar Abbie sukeyi ta siyar da fata daga baya da suka gama karatu kowa yahad'a da Aikin gwabnati da kuma kasuwanci"cikin ikon Allah Isma'il dayake duk yafisu kyau yataso da farin jinin mata"yanada 25 yrs ya Auri naja'atu jinin buzaye kyakykyawar gaske y'ar masu dashi"suna zuba wata iriyar soyayya kamar zasu cinye juna "watansu goma naja'atu ta haifi santalelen d'anta me kama da mahaifinsa harma yafishi kyau"sai kuma ya d'akko farin fatarta"Aikuwa tsabar murna Isma'il yasaka ma d'ansa suna *yusuf* saidai Ana masa Akunya da muslim"muslim yataso cikin gata da kulawa "musammun wajen daddynsa sulaiman dake nuna masa k'auna"Muslim nada 3 yrs Alh Isma'il yagina gida me shashe 3 ,shi guda iyayensa guda"sai kuma sulaiman guda"sbd yafahimci k'anin nasa nason Aure"yayinda shi kuma Habib be fara zancen Aure ba"ga lokacin Alh Isma'il nata samun bud'i sbd hud'd'ar kasuwancin ta man fetur da sirikinsa yasakasa Akai"wato mahaifin naja'atu.....babu b'ata lokaci akasha hidimar Auren sulaiman da Amaryasa jamilah"shima cikin ikon Allah yana yin Auren hanyoyin samunsa suka ninka nada"saidai naja'atu na fuskantar matsala da Jamila sbd tana nuna mata tsantsar hassada sbd mijinta yafi nata"kuma tafita komai na kayan d'aki"gashi da muslim yaje sashen zata koreshi saidai idan sulaiman (daddy) yana nan bata koransa "Alokacin kuma muslim yana wajen eyyah tun bayan yaye data karb'esa bata maidoshiba yaci gaba da zamansa saidai kawai idan yayi muradi yazo yayi wasanshi yakoma wajen eyyah"hakan yasa yataso cikin wayo da ingantacciyar tarbiya"yayi wata iriyar shak'uwa da Abbie da eyyah.....muslim nada shekara hud'u cif Alh Isma'il yayi Accident yarasu"hankalin iyayensa dana matarsa Hjy najah yatashi matuk'a"bayan naja'atu ta gama takaba ta koma gidansu"taso ta tafi da muslim Amma daddy ya hana"saima cewa yayi shi zai Amsheshi lokacin kuma jamilah ta haifi kabeer yanada y'an watanni"ruk'on muslim yadawo wajensu daddy saidai Agaban idon daddy kamar Hjy jamilah zata goyashi Amma bayan idonsa sai zagi hantara, dacin zarafi"hakan yasa muslim ke mugun shakkarta "tun eyyah da Abbie basu lura har suka fara lura sbd ganin muslim koda yaushe yana

cikin damuwa ,ga rama yanata zabgawa"hakan yasa eyyah ta maida hankalinta wajen lura da komai kasancewar dama can jamilah bata mataba tafi son najah"wata rana daddy baya gari ta rufe muslim da duka ya gudo sashensu eyyah yanata kuka duk ta fashe masa jiki da waya"Aikuwa ran eyyah yab'aci taso tazo ta sameta Abbie ya hana "hakan yasa tace muslim bazai koma sashenba"lokacin da daddy yadawo yasami labari bece mata komai ba"tayi mamakin jin shirun nasa"saidai wata biyu da faruwar hakan aka d'aura Auren Habib (Abba) da matarsa Aysha (ummi)" sai habiba da mijinta taheer,saidai kuma bayan an d'aura nasu kuma aka d'aura na daddy da Amaryar sa hafsat"kyakykyawar budurwa d'anya sharaf tanada 17 yrs ya Aureta "tsabar furgitan da jamilah tayi harda su suma tayi"tabi ta d'aga hankali"bayan Auren hafsat ta janye hankalin daddy"saidai matsalar data fara fuskanta data sami ciki zai zube ga daddy yarage kulawa da ita"har matar Habib ta haifi d'anta ramadan , Amma hafsat bata haihuba"Abin mamaki Allah yasakawa hafsat k'aunar muslim "tana jansa ajiki da bashi kulawa sbd tana tausayinsa ,hakan ba k'aramin ciwo yakewa jamila Araiba"saida hafsat tayi shekara 8 Agidan sannan ta haifi y'arta halimatu me sunan eyyah (muslima)"wacce ita da kanta tasaka mata muslima"Alokacin muslim ya girma yanada 17yrs dan yayima SSCE"lokacin kuma har ummi ta haifi zainab,ita kuma jamilah ta haifi Malika"tunda muslima tayi wayo tafara gane muslim "dayake kiran mamanta da Anty"baya son kukan yarinyar yana zama yayita rainonta baya damuwa da zai b'ata lokaci"shidai daddy saidai yayi murmushi ya kallesu idan yana mata wasa"hakan na kona ran Hjy jamila sbd ita baya d'aukar Malika "hasalima daga gaisuwa babu Abinda ke had'asu dashi"sannu Ahankali muslima na girma shak'uwarsu na karuwa da yayanta Muslim"gefe guda kuma hafsat ta kasa gane kan daddy yana mata wulak'anci saiya fita yakirata ta waya yabata hak'uri"idan yadawo kallo bata isheshiba"ko ita ke girki d'akin Hjy jamilah yake kwana"har muslim dake yaro yafara fahimta Aikuwa yasanarwa Abba "Antynsa na fuskartar matsala"shi kuma Abba yasanarwa Abbie, Atake yakira hafsat yamatsa mata da tambayoyi "da farko ta b'oye saidai kuka yaci k'arfinta tasanar musu shekaranta guda rabon daya kwanta da ita"kuma ita ta yafe masa sbd tana ganin kamar ba yin kansa bane"ba k'aramin b'aci ran Abbie yayiba"yakirashi yamasa tas"sannan yatashi tsaye wajen Addu'a da yimasa nasiha sai Abin yayi sauk'i"bayan an yaye muslima hafsat ta fara laulayi wanda shine Ajalinta ta rasu"hankalin daddy yatashi saidai Hjy jamilah kamar ta zuba ruwa k'asa tasha"dangin hafsat suka Amshe muslima "ranar da aka tafi da ita kasa gane kan muslim eyyah tayi"sbd ko kifta ldo yayi tasan meyake nufi tunda ita ta raineshi"tun bayan komawar muslima wajen kakarta ta mance shak'uwarsu da muslim"yayinda Hjy naja tuni tayi Aurenta tanata haihuwarta Acan "Anan kuma mommy ta haifi Naseem"sai ummi ta haifi faruq da siyama"gaba d'aya Muslim komawa yayi shiru shiru hakan yasa daddy yaturashi ingila yayi karatu"lokacin daya dawo Nigeria yanada 28yrs"lokacin kuma Naseem shine k'arami Acikin kaf zuri'ar gidan dan ba'a haifi siyama ba"tun yaron na ganinsa yana zuwa wajensa yana sharesa hardai yad'an fara sake masa fuska"sbd shi bbu ruwansa da Hjy jamila da yaranta sbd ta nuna masa tsana da k'iyayya kuma ta azabtar dashi Abaya"saidai kuma gashi Allah ya had'a jininsu da Naseem"yaron da bayajin komai yamasa kyautar 500k wai yayi shopping "kasancewar ya had'a digree nasa kan kasuwanci yana dawowa daddy ya damk'a masa dukiyarsa ta gado yafara kasuwanci"cikin shakera goma muslim ya mallaki dukiyar data wuce tunanin me tunani"yayi had'in gwiwa da turawa na wasu k'asashen ,ga gidajen man fetur dayake dasu Akusan state 7 dake Nigeria"baya yin sati a Nigeria sbd k'asashen waje dayake yawan zuwa.....sunan dollars yasamo Asali tun a skul bashida wata fira

sai idan yayi kud'i dollars zai dinga rabama jama'a "daga hakan sunan yabishi"sau tari zaiyi kyauta ko taimako Amma zai b'oye kansa"tun mutane basu saniba har suka fara sanin yana taimako sbd Allah"Ahaka yayi masoya da mak'iya " saidai dukda haka yana kulawa da komai na muslima fuska kawai kebe sakar mata sbd ya lura y'ar shagwab'a ce kuma y'ar renin wayoce"sau tari zai siyo mata komai na buk'ata yakaiwa kakarta yace inji daddy"baya kuma tun bayan sun Amsheta daddy yaji tsanarta ko zancenta bayaso"idanma gidan tazo fuska Ad'aure yake Amsa gaisuwarta saidai ta zauna sashen eyyah"ita kuwa muslima bata tab'a sanin dollars ne ke hidimta mata ba"tadai d'auka daddynta ke sakashi"sarai tasan irin sunan dayake dashi Aduniya da kuma dukiyar dayake da ita"saidai ko cikin k'awayenta bata tab'a nuna tanada Alak'a ta jini dashiba"sau tari Agabanta zataji wasu matan na fatan mallakarsa saidai taja tsaki kawai sbd haushinsu"saidai tasan daddynta da matarsa da yaransa basu sonta"Naseem ne kawai da yaran gidan Abba ke sonta...... dollars bashida Abokan da suka wuce suraj da sadeeq "saidai Suraj d'an uwansa ne"da kakan suraj da Abbie uwa d'aya uba d'aya "tun suna yara idan sunzo kano sai suraj ya lik'e shidai abarsa wajen Abokinsa muslim hakan yasa su daddy suka Amshesa yadawo nan da zama"Ayanzun haka dollars nada 38yrs suraj kuma 36 yrs"yayinda kabeer keda 34 yrs"Ramadan nada 31 yrs"Ayanzun cikin yaran gidan faruq ,Naseem sai siyama kawai suka rage tuni zainab dake bima Ramadan Aka mata Aure harda y'arta......

wannan book d'in nakudine
Regular grp 500
Vip grp 1000
Special grp 2k wato 3pages in a day

zaku biya kud'in ku ta wannan acc number👉2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK
Kituro shaidar biyanki what's app number d'ina  08100084251 500 kawai ake turo Kati idan bakida acc amma sauran payment d'in ta acc ne

banason transfer d'in Kati ko vtu photo d'in katin MTN zaki d'auka saiki turo  dan Allah banda kira❌

Y'an nijar kutuntub'i wannan n👉 +227 88 01 90 50

Regular 500f
Vip 1000f
Special grp 2000f

Dan girman Allah da darajan iyayenki karkimun mgn idan baki shirya ba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj

#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: 🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾

💰💸 DOLLARS 💸💰

🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾

Story & written by
mommyn fareesa

Dedicate to Rahama d'an sule 🥰🥰

Free page 5&6

........tunda hjy jamila tayi nassarar shiga tsakanin daddy da muslima kuma tayi Asirin da babu wata mace dake da k'ima a idon daddy sai ita sai hankalinta ya kwanta"yanzun babban burinta Aduniya shine dollars ya Auri malika sbd dukiyar dayake da ita da sunan da yayi Aduniya"Aganinta idan ummansa zata bata matsala zata kai sunanta wajen boka itama"sarai muslim kaf miyagun halayen Hjy jamila yasansu , Asali daga gaisuwa bbu Abinda ke had'asu da ita "kosu Malika d'in dayaga take takenta na Alamar tana sonsa saiya koma had'e mata fuska"gefe guda kuma Hjy naja'atu (umman Muslim) na zauna gidan mijinta dake nassarawa"su biyu ne itada uwar gidanta"yara biyu maza kawai ta k'ara Haifa Umar da Usman"yayinda yaran uwar gidanta 5 Aciki Akwai Amatallahi dake mutuwar son muslim "kuma Hjy naja tasha sanar masa tana muradin ya Auri yarinyar"saidai becewa komai sbd Asali shibe tab'a soyayyaba,harma Hjy naja na zaton kodai muslim bashida lafiya yana k'ok'arin shiga 40yrs Amma bashida mata"ba k'aramin kulawa da kafafa da kyautatama mahaifiyarsa yakeyi ba"komai gashi nan waja waja yawadata dashi itada y'an uwanta da danginta"yanzun haka Usman na k'asar Cairo yana karatun likitah "wanda muslim d'in shine yaturashi"Hjy naja nada kirki dason jama'a "saidai tunda ta fahimci irin wahalar da Hjy jamila tabama muslim da yadda taso ita ta Amshesa Daddy ya hanata hakan yasa gaba d'aya bata wani son dangin mahaifin muslim saidai Agaisa da juna idan yakama..... dollars kyakykyawan gaske ne Ajin farko,da wuya ya shiga cikin mata wasu basu yaba dashiba ko nuna son mallakarsa Amatsayin Abokin rayuwar su"yawan magana ba dabi'ar shi bace ba, Amma ba miskili bane idan yaga dama zai iya zama yayi firansa da wanda yaso musammun Eyyah ko Abbie"dollars dogo ne fari k'arfaffah"be cika son hayaniya da yawan surutuba domin yana sakasa fusata"beda tsoro saidai Akwai izzah hakan yasa wasu ke ganin yanada girman kai"Allah yamasa son girma be kuma d'aukar raini"shiyasa fira bata had'ashi da kabeer saidai kawai gaisuwa"sannan be tab'a bama kabeer damar ya Amfana da dukiyar saba"saidai kowa dake zaune a bugajes house nacin Arzik'in dollars,wanda shine yak'ara gyare gidan nasu ta hanyar siyen wasu filaye dake bayansu

aka shigo dasu cikin gidan Aka masa gini me k'ayatarwa tamkar kana k'asar a turai"dollars Allah yamasa son Abincin gargaji da fura"sannan yanada son nama nau'in gashashshe"be cika son nama a miya ko a farfesuba yafi son gashashshe "sannan Abincin zamani yana son snacks"mutum neshi da baya wasa da sallah Akwai k'ok'arin sauketa saidai yana gaba da kayanmu na Al'ada yana iya wata ukku be saka manyan kaya ba"dollars ya had'u tako Ina Akwai baiwar dad'in murya da kyawun sura"gashin kansa bak'i ne me sulb'i irin na buzaye be cika Askiba saidai kawai yarage ya gyara"sadeeq Abokinsa ne tun suna secondary school suke tare "sadeeq kuma yakasance me fuska biyu"Agaban idon dollars yana nuna masa k'auna Amma Azuciyarsa kamar yakashesa"ba k'aramin zafin dukiyar dollars yakejiba da yadda wasu ke yabonsa bisaga yadda yake taimakon Al'umma"sbd shi baya k'aramar kyauta"yana iya ganin magidanci talaka ya d'auki million 3 ko 5 yabashi yace yaje yagina kansa"duk yawanci idan yayiwa mutane irin haka saika suma sun haye sun sami rufin Asiri shiyasa Allah keta bud'e masa k'ofofin samu"idan har yana k'asar sashen eyyah yakecin Abinci kuma har d'aki guda garesa A sashen"yayinda yakan shiga shashensu Abba harma Abinci idan ummi ta masa tayi yakanci sbd batada matsala"saidai itama basu shiri da Hjy jamila"yanzun haka ummi kullum sai taje da safe ta gaido surukan nata Amma banda Hjy jamila sai tayi sati biyu batama shiga b'angaren suba...duk wata haka dollars ke jibge musu kayan Abinci dana cefane duka kowane shashe"Aganinsa komai zai yiwa daddy be biyashiba sbd yadda yasoshi yakula dashi Arayuwa"kuma ya rik'e masa Amanar dukiyar mahaifinsa saida ya girma ya damk'a masa Ahannunsa.......

*cigaban labarin*

Afannin malika tun tana saka ran fitowar dollars daga sashen daddy harta cire rai"sbd tuni yafita ta k'ofar baya"saidai daga baya yaturo wani yaronsa Akan ta bada Abincin "koda ta bayar tana jin dad'i kanta na fashewa "saidai babu jumawa yaron nasa yadawo da warmers d'in yanata murmushi had'e da yimata godiya"ta zabga masa harara had'e da cewa godiyar meye kakemun?"Ai yallab'ai ne yabamu Abincin mukaci shine muka masa godiya yace, kece zamu yimawa sbd danmu kikayi.....wata uwar Ashar Malika ta yayibo ta lailaya masa batare data duba girmansa ba"sbd zaiyi kusan 40yrs"bece komai ba zuciyarsa na zafi ya Ajiye basket d'in yajuya yafita"ta fashe da kuka tana tunanin sbd tasan be ciba shiyasa yace suyi mata godiya"tana kukan mommy ta fito daga cikin kitchen ta kalleta tana fad'in lafiya kike kuka?"tana kukan ta shiga sanar mata"saidai ran Hjy jamila haryafi na Malika b'aci "ta zauna fuska bbu rahama tace"na kusan yin maganin d'an iskan yaron nan"Ayi Abu sbd shi shine zai bama wasu y'an banza k'ask'antattu suci Abinci me rai da lafiya irin wannan da kayan Abincin da muke bama bak'i "Amma babu damuwa zanyi maganinsa"saidai kawai yaji Aiki Ajikinsa haka kawai zan saka Ayi "duk ranar daya dawo a tafin hannunmu wlh sai yadda mukayi dashi"na rasa wace irin kafaffiyar zuciya ce dashi"inda har bashida wannan dukiyar An fad'a masa ya Isama naso ki Aureshi ne?"nide mommy dan Allah kiyi iya bakin k'ok'arinki"shikenan babu damuwa"daga haka ta tashi ta wuce kitchen.....

befi saura mintina 10 Akira sallar magrib ba su dollars suka iso gida"har lokacin kuma muslima batada walwala saidai ta dena kukan sai Ajiyar zuciya datake saukewa Ab'oye"suna gama parking tayi saurin k'ok'arin fitowa da hanzari dollars yayi lock d'in back sit "sai murd'awa takeyi Amma k'ofar tak'i bud'ewa,suraj dai na lura Amma bece komai ba sbd ya fahimci shima haushinsa yakeji"saida yaga dama dan kansa kafin yabud'e driver sit yafito cike da shan

k'amshi"suraj daya rigashi fitowa yace"muje masjeed d'in ko?"time yaduba batare daya yi mgn ba"dan Allah dollars ka cire lock d'in ta fito mana"Anan ma be tankaba saidai yamatsa jikin motar yabud'e back sit d'in"k'irjinta ya buga batare data yadda ta kallesaba ta turo baki fuskarta Ad'aure....bance kije sashen su eyyah ba"kikai kayanki can part d'in su daddy"sannan daga baya kinje wajenta"yak'are maganar kamar Ammasa tilas "ita kuwa kamar ta koma fashema da wani sabon kukan taji"saidai batace komai ba ta fito rik'e da troley d'in kayanta "Alokacin har suraj da dollars sunyi hanyar part d'insu daddy"itadai tana biye dasu tana gulmar dollars Aranta yacika iyayi da takura"sune suka rigata shiga cikin parlourn"suraj yayi sallama sau biyu"yayinda uban gayyar ya d'aure kyakykyawar fuskar nan tasa yayi tsaye yana kallon hanyar dake gefen upstarts inda d'akunan baccin yaran gidan dana bak'i suke"Hjy jamila na zaune kan kujerah Malika tayi matashin kai da cinyarta"dukda haushin dollars da Hjy jamila keji haka ta danne ta k'ak'aro murmushin dole tana fad'in muslim kun dawo?....saidai kafin shida suraj su bata Amsa muslima ta shigo da sallama janye da troley d'in kayan ta....kafeta da Ido Hjy jamila tayi tana jin wani d'aci Azuciyarta, Atake ta had'e gabas da yamma ta tamke fuska "saidai suraj ne ya Amsa sallamar muslima"Malika kuwa gabanta ne yafad'i haka kawai yau ta tsinci kanta dajin zafin shigowar muslima da dollars "domin ranta yabata gidansu yaje kenan"batasan lokacin data tashi zaune tana kallon muslima data duk'a tana gaida mommy ba"da k'yar Hjy jamila ta Amsa kamar ta shak'eta ta mutu su huta haka taji Aranta"ba k'aramin tashi hankalin malika yayiba da taga yadda muslima ta k'ara kyau da gogewa had'e da wayewa"k'amshin turarukan jikinta har inda take zaune tana iya juyo k'amshin"Atake taji sabuwar tsanarta Aranta da k'yar ta Amsa gaisuwarta sbd yayarta ce ita, Malika ta bata 2yrs"dollars na tsaye yana danna waya duk yana lura da Hjy jamila da Malika"wani makirin murmushi ya sub'uce masa a karo na farko"Anutse yace"dama mommy yarinyar nan tadawo nan da zama shine nake zaton Abata wancan d'akin dake kusa dana Malika.....ban gane nadawo nan da zama ba?"cewar muslima Azuciyarta tana satar kallon dollars gabanta na fad'uwa sbd ta lura da irin kallon tsanar da Hjy jamila da Malika ke jifarta dashi.....yaushe har Akayi zancen zata dawo nan niban sani ba?"kuma bamuyi maganar da Alh ba"tamkar dollars bazaice komai ba sai kuma Anutse yace "koma dai miye zata iya dawowa nan da zama sbd itama y'ace kamar kowa"daga haka ya wuce cike da izzah yanufi gefen d'akunan "hakan yasa muslima mik'ewa tsaye tabisa"yayinda suraj kansa ke Ak'asa yana tausayawa Muslim da zaman da zatayi agidan"saidai zai rarrashi dollars Akan yamayar da ita sashen eyyah kawai......cikin tsoro ta iso bakin k'ofar d'akin daya tsaya"key d'in d'akin yacire yamik'a mata"batare daya ce komai ba yajuya....yaya muslimmmmmm! Ta kirashi cikin muryar shagwab'a "da farko yaso ya shareta Amma ganin su Hjy jamila zaune a parlourn yasaka yajuya sbd yasan tabbas kallonsu sukeyi da saurarensu"yana juyowa ya sauke golden eyes d'insa Akanta"ta sunkuyar da kanta "murya can k'asa yace"idan bakida Abin fad'a zan tafi"dama daddy nace ko...gaya m....sai kuma tayi shiru"bece komai ba yasan tanaso taji daddy yasan da zuwanta ko kuwa?"saida yaja k'aramin tsaki yace"besan da zuwan nakiba ninan ne nakawoki kuma baki Isa ki koma can kina fita sakaka duk inda kikaga dama ba"daga haka yayi tafiyarsa"ita kuma ta juya cikin jin zafinsa ta shige cikin d'akin ta murza key "zuciyar malika kamar zata fashe sbd kishi "Aganinta yadda dollars yajuya baya suna mgn da muslima rarrashinta yakeyi"shi kuwa kallon gefen da suke beyiba yafita suraj na binsa Abaya.....kam bala'i can !wai meke shirin faruwa komai na k'ok'arin kwabemun ni jamilah? miye ma'anar dawowar yarinyar nan gidan nan?"mommy bama wannan ba kiduba kiga yadda yaya muslim

yadamu da ita"wlh bazan iyaba koni ko ita Agidan nan"cewar Malika tana sakin gunjin kuka zata tashi ta nufi d'akin da muslima ta shiga"da sauri mommy ta dakatar da ita ta hanyar cewa"dallah ki nutsu musan Abinyi"ki bari Anjima daddynku yadawo daga masallaci zamuyita ta k'are gobe goben nan zatabar gidan nan"shi kuma muslim d'in dani yake mgn zanyi maganinsa.....suna fitowa suraj ya dubesa fuska Ad'aure yace" bansan meyasa wani time d'in bakada tausayiba"kasan wacece Hjy jamila shine zaka kai muslima baka gudun su cutar da ita tunda bbu Allah Aransu??tamkar dollars bazaiyi mgn ba saida suka iso bakin get kafin Anutse yace "bana Aiwatar da komai saina tabbar da idan na Aiwatar meye zai biyo baya?"shekarunta 20 cif yanzun"idan bata zauna cikin family nata tasan kowaba yaushe kakeso ta zauna ta sani?"daddy yanzun shine komai nata tunda Anty ta rasu"itama gidan ubanta ne tanada hakk'i Aciki basu Malika kawai ya Haifa ba"lokaci yayi daya kamata ta fito ta yak'i Hjy jamila ta nuna mata itama matsayinta guda dasu Malika"Ina mai tabbatar maka da cewa ta shigo kenan bbu zancen komawarta gidan Hjy"ban damu da duk yadda ka d'aukeni ba sbd na tursasata ta dawo gidan mahaifinta ba"iya Abinda nasani Daga sadda ka k'udurta niyarka Azuciyarka tofa baka tsoron komai..... yak'are maganar yana d'age kafad'a had'e da ficewa daga cikin get d'in gidan da sauri sbd su tafi masjeed"gaba d'aya sai suraj yaga be kyautaba, domin dollars yafishi tunani da hangen nesa"sai yanzun ya fahimci dawowar muslima gidan mahaifinta shine daidai kodan sbd wata ran Aure zatayi"idan yaranta suka tashi sukaga ita ba wata tsiya bace gidan ubanta Ai Akwai ciwo" lallai muslima batasan irin taimakon da dollars yamata Arayuwa ba da baza taji haushin saba"saidai yasan wata ran tana girma da hankali zata gane shiba mak'iyinta bane.....Ana gama sallar magrib dollars yafito ya tarbi Abbie yana rik'e da hannunsa suka shigo cikin gidan suka nufi parlourn Abbie "sai shagwab'a yakeyi wai Abbie yadena jidashi ko zuma yadena Ajiye masa"shidai tsohon na murmushi yanata kallonsa"can yace"dama Abbie inaso kayima daddy mgn kan muslima"Ayanzun haka nadawo da ita gidan nan sbd.....yamasa bayanin yasameta tsaye da saurayi ana ruwa"kuma tana tsoron su kabeer"ya kamata zuwa yanzun ta zauna da family nata tasan kowa kuma itama tayi tutiya da gidan mahaifinta"daga k'arshe yace"Abbie dan Allah karka bama daddy dama yarinyar nan tabar gidan nan"koban sanar makaba kasan wacece matarsa bason yarinyar nan takeyiba zata iya k'ullah makircin databar gidan nan...... kafad'arsa Abbie yadafa yana murmushin su irin na manya yace"babban mutum ! Masha Allah kanada hangen nesa"Allah yayi maka Albarka yajik'an Isma'il "ya Amsa da Ameen cikin jin dad'i"Abbie yaci gaba da cewa karka damu zanyi masa mgn yanzun idan mun dawo  dg sallar isha'i "dato dollars ya Amsa, Atare suka koma masjeed d'in..... Ab'angaren muslima kuwa tana shigowa d'akin ta rufe da key,kafin ta Ajiye troley d'in kayanta ta bud'e ta canza kaya sbd na jikinta nada lema"d'akin fas yake sbd kullum sai masu Aiki sun gyara"hakan yasa ta jona wayarta chargy ita kuma ta wuce bath room tayo Alwallah"harta fito tayi sallar ta gama batada walwala sbd bata wani son zaman gidan"ga haushin wannan mugun yaya muslim d'in Aranta"saidai tayi tagumi tana jin tausayin kanta data kasance batada d'an uwan da suke ciki guda sai y'an uba"sai kuma data tuna da naseem taji farin ciki sbd yaron na sonta"da wannan tunanin tayi sallar isha'i"taso tayi wanka Amma ta duba taga kayan wankan sun jima ita kuma tanada k'yank'yami "kawai saita watsa ruwan ta fito"ga yunwa tana ji"riga da wondo pencil ta saka ta zumbula hijab red gogaggiya ta fesa turare ta bud'e k'ofar d'akin ta fito ta saka key ta rufe"Malika da yaya kabeer na zaune a parlourn "saida taji fad'uwar gaba data gansu Amma saita dake kawai ta fara tafiyarta Anutse"sai gab da zata fita kafin tace"yaya kabeer Ina

wuni?"tsaki yaja batare daya tankataba"Malika ta tab'e baki tana fad'in cusa kai bbu kwajini"banza mayya kawai"duk tana jinta batace komai ba ta fita daga cikin parlourn sbd sashen iyah zataje....

Bayan Angama sallar isha'i dollars ya wuce sashensa ya d'auki sabon wanka ya shirya cikin sabuwar jallabiya milk colour"ba k'aramin kyau yayiba ga garin yayi d'an sanyi sbd yayyafin da Akayi "babu Abinda jikinsa keyi sai tashin k'amshi me kashe zuciya da gangar jiki"yunwa yakeji sosai"rabonsa da Abinci tun d'azun da rana dayaci cikin jirgi"yana tafiyarsa irinta kas'aitattun zaratan maza yana Amsa wayar jama'a har ya iso sashen Eyyah.....nide gaskiya Eyyah Anan zan kwana dan Allah karki sanarwa da mugun nan Anan zan kwana"kuma nide ki bani furan mana"shiba kina basaba ni kuma bak'uwa ce ko?"cewar muslima cikin shagwab'a kamar zata yi kuka Eyyah na k'ok'arin mgn taji daddad'an k'amshin turaren dollars"gaban muslima yafad'i fatanta Allah yasa beji meye tace ba?"ta d'ago kanta ta saci kallonsa taga yadda ya had'e rai kamar besan meye dariya ba"babban mutum na d'auka bazaka shigo ba Ai?"kaga wannan fitinanniyar takwarar tawa ta dameni da rigima"k'in mgn yayi ya zauna kan kujerah "da sauri muslima ta mik'e tsaye da nufin ta tafi sashen su Abba idan Tara da rabi tayi saita dawo nan "tasan dai muslim lokacin yatafi"sbd ita bata son zama inda yake"saidai tana k'ok'arin fita daddy da Abbie suka shigo cikin parlourn"naseem na biye dasu rik'e da wasu ledoji  Ahannunsa....✍️

wannan book d'in nakudine
Regular grp 500
Vip grp 1000
Special grp 2k wato 3pages in a day

zaku biya kud'in ku ta wannan acc number👉2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK
Kituro shaidar biyanki what's app number d'ina  08100084251 500 kawai ake turo Kati idan bakida acc amma sauran payment d'in ta acc ne

banason transfer d'in Kati ko vtu photo d'in katin MTN zaki d'auka saiki turo  dan Allah banda kira❌

Y'an nijar kutuntub'i wannan n👉 +227 88 01 90 50

Regular 500f
Vip 1000f
Special grp 2000f

Dan girman Allah da darajan iyayenki karkimun mgn idan baki shirya ba

#mommyn fareesa
#dollars

#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: 🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾

💰💸 DOLLARS 💸💰

🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾

Story & written by
mommyn fareesa

Free page 7&8

.......gaban muslima yakoma fad'uwa Akaro na biyu "da hanzari tayo baya had'e da saurin zama kan carpet ta sunkuyyar da kai"naseem na kallonta kasancewar parlourn k'anyar yake da haske"sosai murnan ganinta ya baiyana saman fuskarsa"dukda shibe fi wata ukku rabonsa da itaba sbd tayi wani zuwa nan ya ganta wajen Eyyah Amma ko sashen su daddy bata jeba Alokacin"Anty muslima kece dan Allah kome kama dake ce?"yak'are maganar yana Ajiye ledojin hannunsa gefen eyyah"muslima ta d'an hararesa ta kauda kanta Alamar fushi takeyi dashi"yayinda Abbie keta murmushi ya zauna gefen matarsa"daddy kuma ya zauna kan kujerah fuskarsa bbu walwala sbd yana jin haushin dawowar muslima Agidan ,gashi mahaifinsa ya sanar masa da babbar murya tadawo kenan Aure ne kawai zaya rabata da gidan in sha Allah"daddy sannu da zuwa! Ina wuni?"lafiya qlau"shine Abinda yafad'a batare daya kalletaba "Naseem na zaune gefenta yana mata mgn k'asa k'asa tak'i kulashi"yayinda tamkar babu dollars a parlourn "wanda bai saniba zai d'auka bacci yakeyi saboda idonsa a lumshe suke, sai dai ras yake kallo dasu dan ya kaisu k'asane kawai kamar ya lumshe su d'in..... Abbie Ina wuni?"sai yanzun kika ganni y'ar nema?"murmushi kawai tayi batace komai ba "daddy ya gaida mahaifiyar tasa ya kalli dollars da idanuwansa ke lumshe yafita"sbd ya d'auka bacci yakeyi"shi kuwa bayaso daddy ya fahimci shine yadawo da muslima gidan yayi laifi wajensa"bayan fitar daddy muslima ta kalli naseem tana fad'in Ina siyama?"kasancewar tana son yara kuma siyama kaf zuri'ar gidan itace k'arama tanada 7yrs"gashi ta shak'u da Naseem sosai"duk idan taje sashensu wajensa Hjy jamila ke korota"hakan yasa saidai shi yaje part d'in su suyi wasansu kota masa y'ar firan datake masa ta yara"fuskarsa bbu walwala yace"tana nan Anty muslima"sbd yatuna kwana 2 kenan da Hjy jamilah ta koreta datane wajensa"jeka d'akko ta mana"bece komai ba yamik'e tsaye saima lokacin yaji k'amshin turarukan dollars Acikin parlourn"da sauri ya kalli cikin parlourn ya hangosa zaune ya mik'e k'afafuwansa saman center table idanuwansa alumshe"yayi matuk'ar kyau kamar bature"eye lashes nasa kamar an zanasu tsabar cikarsu da yadda sukayi wara wara gwanin kyau....*Masha Allah! yaya yanada kyau"*

yafad'a Azuciyarsa kafin yace "yayaaa! bud'e kyawawan idanuwansa yayi yana kafe naseem dasu"shi kuma yayi murmushi kafin yace barka da dare"harara ya wurgo masa ya maida idonsa ya rufe"duk muslima na kallonsu Aranta tace maganinka kenan daka tanka shi"sai b'ata rai takeyi tana murgud'a d'an bakinta"yayinda shi kuma naseem ya fita"cike da kulawa Abbie yace"muslima yaya dai?"lafiya qlau Abbie"kin gama karatu ko?"Eh nagama diploma d'ina inaso na jona digree ne pls"uhmm "to islamiya fa?"d'an yamutsa fuska tayi tana satar kallon dollars da har lokacin idonsa ke a rufe kafin tace"nayi sauka fa tuni"to Ai hadda yaka mata ki fara ko?"tayi shiru"Abbie yaci gaba da cewa Alhamdulillah naji dad'i"domin cikin yaran gidan nan mata kece mace ta farko da kika sauke Alkur'ani me girma"zainab tana izuf 35 aka mata Aure "Malika ba zuwa islamiya takeba tunda ta girma"sai kuma yanzun siyama dana sakata ta hadda"kinga naseem da farooq suma k'ilan k'arshen shekara suyi sauka"Allah yayi miki Albarka yajik'an mahaifiyarki"cikin farin ciki ta Amsa da Ameen"Amma Alh yaka mata Asakata ko islamiyar week end ce"nifa Eyyah Ina zuwa islamiya basai An canza mun ba"kina nufin daga nan zakije can duk Asabar da lahadin?"cewar eyyah"Eh in sha Allah...."gaba d'aya suka bi dollars da kallo daya mik'e tsaye yanufi dining area da Alama firan tasu ta isheshi"ita muslima tama d'auka ko bacci yakeyi"yayinda Abbie da eyyah tsab sun san ba bacci yakeyi ba" sbd su saidai su bama wani labarin dollars...tashi kije ki kai masa fura na nan cikin fridge"ki dawo ki yanka kayan fruits d'in nan sbd naga muslim nashansu kafin ya kwanta bacci"sosai muslima taji haushin umarnin da eyyah ta bata saidai bbu yadda zata iya"koda ba'a nan takeba ta fahimci kowa yimusu biyayya yakeyi"ta kuma fahimci shid'in na musammun ne Awajen kakannin nasu"tana k'ok'arin tashi naseem ya shigo sab'e da siyama"sai surutu take masa yana biye mata yana murmushi"da hannu ya nuna mata muslima yace"kinsan wannan?"girgiza kanta tayi tace"ah ah"kaga Naseem ku jira nazo"ta fad'a tana tashi ta shige kitchen"harta d'akko furan sai kuma ta tsaya tafara y'an dube dube "can ta hango sugar"Atake ta saki murmushin mugunta ta matsa ta d'auki robar sugar d'in ta zuba cikin furan over ta motsa sannan ta fito"tana fitowa ta hango naseem tsaye gefen dollars dake dining area zaune"dukda batajin meya sanar masa sai taga naseem d'in yanufi inda ya zaunar da siyama ya d'auketa sun nufi k'ofa sun fita "kamar ta tsaidasu sai kuma ta fasa"gashi bbu Eyyah da Abbie cikin parlourn "Atsorace ta iso gefensa ta Ajiye kwanon furan zata juya....jirah! taji Amon jarumar muryansa me dad'in sauti"saida gabanta yafad'i bata juyoba tadai tsaya d'in kamar yadda ya buk'ata"shi kuwa furan ya bud'e yad'an motsa da spoon yayi spoon guda...da k'yar ya iya gimtse murmushin da ke son kufce masa batare daya kalletaba murya Adake yace "zauna ki shanye furan"mintina 3 na baki"Arikice ta juyo....saidai irin kallon data lura yake jifarta dashi yasaka ta had'iye tsiwar data so ta masa"sai wani shakkarsa ma dataji da wani irin mugun kwarjini daya mata Atake"jikinta Asanyaye ta zauna kan kujerar da kujerah biyu ce ta musu ta zara"kanta Ak'asa ta tsuke baki tana marairaice murya tace"dan Allah kayi hak'uri ni bana shan fura fa"ya d'auki kusan second 10 kafin yace"saiki fara daga yau "Atsarina bana maimaita mgn"hukunci kawai nake yankewa bayan na bada umarni an bujure" yak'are maganar yana cigaba dacin gashashshen namansa hankali kwance yana danna waya"muslima kuwa duk sonta da fura bata sonta da sugar"bata san k'aik'ayi zai koma kan  mashek'iyaba da batayi gigin zuba masa sugar Aciki ba"duk dollars na Ankare da yadda take tunanin zuci Amma Azahiri idan kallonsu kakeyi zaka d'auka kamarma bema san da zamanta wajen ba....yaya  Eyyah fa ta sakani Aiki ko?"banza yamata kamarma badashi take mgn ba"batada zab'in daya wuce ta d'auki furan ta kafa kai had'e da rintse Ido ta

d'auke numshi ta fara sha"saida tasha fin rabi kafin ta Ajiye kwanon"idanuwanta cike da k'wallah tace"na gama dan Allah......muddin kinsan baki shanyeba garama ki shanye kafin na duba"batace komai ba tana hawaye ta ida shanyewa"ta turo kwanon gabansa batare data yi mgn ba"yatab'e baki kamar Ammasa tilas yace"yanzun kin yadda nid'in mugu ne,ko kuwa saina k'ara miki wata muguntar zaki yadda??shiru tayi gabanta na fad'uwa "wato yaji d'azun ta kirashi da mugu?"ta tambayi kanta Aranta....hango shigowar Eyyah cikin parlourn yasaka tayi saurin mik'ewa tsaye ta baro masa wajen taje ta d'auki ledar kayan fruits d'in ta wuce kitchen "Eyyah dai na kallonta "tana mamakin meyasa ta d'aure fuska gashi kamar tayi kuka??.....tafi mintina 10 a kitchen d'in "sannan ta fito tama d'auka ko dollars yafita"saita hangosa zaune still a dining area d'in"*gaskiya mutumin nan Allah yamasa cin Abincin tsiya* da Ido Eyyah ta bita sbd zancen Afili yafito"dollars kuwa dayake Allah yamasa saurin ji, tsab yaji kalamanta"saiya d'an cije baki yana juya Ido "kije ki kai masa fruits d'in idan yagama yarakaki kije can shashanku ki kwanta"idan kuma zakici Abinci kije kici"nifa na k'oshi"kuma ni bana son can ko kayan wanka bbu sai tsaffi Ina kuma jin k'yank'yami "ta k'are maganar tana komawa kitchen d'in"duk kalamanta bbu wanda dollars bejiba "yakuma shirya yin maganinta"Ahankali ta iso ta Ajiye masa k'aramin tray data zubo fruits d'in ciki"tana k'ok'arin juyawa taji tattausan muryansa yana fad'in zaunah"da sauri ta kallesa taga waya yake dannawa"badan tasoba ta zauna"plate shak'e da farfesun kaji yatura mata gabanta "cikin bada umarni yace"mintina 7 na baki"cikin shagwab'a tace"nide bazan iya ciba na k'oshi furan yacika mun ciki"uffan bece mataba sai duba wristwatch d'insa yayi"hakan yasa ta maida hankalinta cikin parlourn taga bbu bbu kowa.....wlh! wlh!! kika b'atamun lokaci saina sab'a miki "yafad'a Afusace"da sauri taja plate d'in tana kuka tana ci"sbd tsabar muguntа irin tasa beci fruits d'in ba yatura mata gabanta yakoma had'e rai"bayan ta gama da farfesun kaji tafara da shan fruit"saida yaji tana kakarin Amai sannan yamata Alama da hannu ta Ajiye"da k'yar ta mik'e tsaye "cikinta yacika yayi hak'e hak'e sbd bata tab'a cin Abinci irin haka me yawa ba"saidai tasha Alwashin data koma d'akinsu zata saka yatsa abakinta tayi Amai kota huta"daga yanzun karki koma zuwa kiyi dare balle Ace na rakaki"batun cin Abinci dakike mgn cikin sati guda zaki gane kinfi kowa ci Agidan nan "Adaidai nake da duk wata fitsara taki yarinya"yak'are maganar yana mik'ewa tsaye batare daya kalletaba yayi hanyar waje"batace komai ba tafara biyosa da k'yar sbd yadda cikin nata yacika sosai"duk Anutse yake tafiyar ba kuma sauri yakeba saida yamata nisa"yaso yayi tafiyarsa tunda dare beyi sosaiba kuma ga haske ko Ina miye ace saiya wani rakota"saidai daya tuna idan yarakata har cikin gidan sai Hjy jamila taji kamar zuciyarta zatayi bindiga sai kawai ya tsaya bakin k'ofar parlourn yana danna waya harta iso"Amma har lokacin kuka takeyi"tak'i yarda su had'a Ido sbd jikinta yabata kallonta yakeyi "kinsan Allah? duk ranar danace kiyi abu kikamun kuka sai ranki yab'aci ninkin baninkin"dallah kije ga tiyo can ki wanke fuskarki"batace komai ba ta wuce ta d'auki tiyo ta d'aureye fuskar "da Alama dashi Ake bama flowers ruwa"bayan ta gama ta saka gefen hijab nata ta goge fuskarta"kafin ta iso Ahankali batace komai ba"shi kuma yana tsaye daga bakin k'ofar yak'i gyarawa balle ta wuce"nide dan Allah ka matsa na wuce ko?"idan nak'i fa?"tayi shiru"yatab'e baki yana murd'a handle d'in k'ofar yad'an saki fuska yashiga da sallama cikin sanyayyar muryarsa "muslima ta shigo itama biye dashi"da kallo Hjy jamila da Malika dake zaune a parlourn suka bisu"dama cikin haushi take yanzun sukayi sama da daddy sbd tace bata yadda da zaman muslima Ashashen ba"shi kuma yamata tas kan cewar koda Abbie bece ta zauna nanba shi yace ta zauna sbd itama shi haifeta kamar su kabeer"kan idon Hjy jamila

dollars yabud'e mata k'ofar d'akin da key ta shiga"sannan yazare key d'in ya mik'a mata"tana murgud'a d'an bakinta ta Amsa batare data kallesaba koyin mgn ta rufe k'ofar "shi kuma yajuya yafita batare dasu Hjy jamila sun sami Arzik'in ya kallesuba balle harya tanka musu.....kuka Malika ta fashe dashi ta nufi d'akin muslima Ahaukace"Hjy jamila bata hanataba sbd itama zuciyarta iya wuya take"saidai koda ta tura k'ofar Arufe take"bbu irin dukan da bata yiwa k'ofar ba Amma muslima ta share tak'i bud'ewa"ita Alokacin ma tana toilet tana Amai"koda ta fito har Malika ta gaji da dukan k'ofar ta gama zagin muslima ta uwa ta Uba da Aibatata had'e dashan mugun Alwashi Akanta,kafin ta juya tayi tafiyarta"ita kuwa muslima batasan tana yiba ta daiji bugun k'ofa takuma tabbatar malikace ko Hjy jamila "jikinta yabata ba Alkhairi ya kawosuba"shirin kwanciya bacci tayi ,harta kwanta sai kuma ta duba wayarta "taga miss call 3 da text message"tana dubawa ta karanta ta fahimci Aliyu ne"saita turo baki ta harari wayar ta kwanta bayan tayi Addu'a........

washe gari misalin k'arfe 9:11 am "muslima na zaune a parlourn kan kujerah, gefenta naseem ne da farooq"sunata Aikin rarrashinta tayi break fast tak'iyi"cup d'in tea na hannun Naseem"sai plate d'in chips na gabanta Ajiye da ledar bredi"tana sanye da doguwar riga light pink ta kanti"sai wani siririn mayafi saman kanta dake shara shara har Ana iya hango gashin kanta me tsawon gaske had'e da sulb'i "saidai becika yawaba sai tsayi"ko powder bata shafaba"tana yin wanka ta shafa turaruka ta fito"shima wankan tayishi ne sbd Eyyah ta Aiko mata dasu shower jal da soap masu kyau ,harda toothpaste da brush sabo sannan tayi wankan"bayan ta shirya naseem yamata knocking yace tazo tayi break sbd yaga bata fitoba"sai tace ta k'oshi "shinefa yaje ya had'a mata komai batare daya yadda mommy ta ganiba ko Malika ba"kafin yazo yace tazo inji daddy"Atsorace ta biyosa tasamu Farooq zaune a parlourn shine suka had'u suna rarrashinta"suna Ahaka zaune mommy ta fito daga shashen daddy"kallo d'aya ta musu ta d'aure fuska tana bin naseem da wani magun kallo tace zaman ubanme kakeyi Anan?"babu komai mommy"kin manta yau week end ne?"mitssssuw!! zaka tashi kabar nan ko kuwa?"kiyi hak'uri mommy dama inaso Anty muslima tayi break fast ne"wani matsiyacin kallo irin na tsana ta jefi muslima dashi ,da sauri ita kuma ta sunkuyar da kanta k'asa"k'aramar yarinya ce ita,ko kuwa yarinyar goyece ita da zaka damu da sai taci Abinci ne dan ubanka?"taci Abinci kokar taci meye damuwarka?"wlh ka fita idona na rufe....shiru tayi sbd shigowar dollars cikin parlourn"wanda sarai yaji duk masifar datakeyi"saidai ko a fuska be nuna yaji komai ba,yakuma fahimci dalilin dayasa take kumfan bakin.....wani irin mayatattun ƙamshin turaruka kashi-kashi suka fara rige-rigen afka mata cikin hanci"ta d'an lumshe Ido,sam bataji koda sallamarsaba"Ahankali ta d'ago kanta k'irjinta na tsananta bugawa ta saci kallonsa "ya wanku cikin suit coffee brown"Ya wani k'ara kyau da cikar kamala ,ga wani irin kwarjini na musammun mai k'ara yalwata haibarsa ga mai kallo....wata uwar harara ya watso mata daga ita harsu farooq da Naseem d'in dake rarrashin nata"tun kafin ya zauna kan kujerah su duka suka tashi suka fita sbd irin kallon dayake Aiko musu dashi"yayinda Hjy jamila ke tsaye tana binsa da kallo harya zauna kan kujerah"fuskarsa Ad'aure take tamau,dama daddy yazo ya gaida"shine Eyyah tace ya shigo tanan bata bayaba sbd yaduba tashin muslima "yasha Alwashin kuma bazai tankataba muddin bata masa mgn ba"saidai yana lura da yadda tayi k'asa dakai ga Hjy jamila dake tsaye tanata kallonsu"da k'yar ya iya furta mata kalmar mommy Ina kwana?"lafiya qlau"daga haka ta juya ta shige kitchen ta lab'e yadda zata iya hangosu"kusan second 10 kafin batare data kallesaba tace Ina kwana?"be Amsa ba sai cewa yayi Anan gidan daban gidan Hjy

ma daban"Abinci idan kinci cikin kine sbd haka baza'a koma lallashinkiba akan kici"nide na k'oshi bana ci"okay to shikenan Allah yasa na fito daga wajen daddy nasamu bakiyi break fast d'in ba"kinma je kin gaidosa ko kuwa sai zama cikin k'annanki kina musu iyayin gulma kika iya??"banjeba"tab'e baki yayi ya mik'e tsaye ya haura upstairs "muslima ta raka bayansa da harara tana sakkowa k'asan tafara break fast d'in"sbd tasan halinsa bata manta Azabar daya mata Adaren jiyaba"cikin mintina 10 kacal ta gama break d'in "kan idonta Hjy jamila ta fito daga cikin kitchen ta wuce d'akinta "ita dai kallo bata ishetaba ta kwashe kayan tamayar kitchen"tana fitowa daddy da dollars na sakkowa down stairs d'in "ta sunkuya har k'asa ta gaishe da daddy "ya Amsa kamar jiya suna fita tare da dollars "D'akinta ta koma tad'an gyara sannan ta d'akko wayarta ta kira Hjy suka gaisa"Ahaka kiran Aliyu ya shigo"haka nan ta daure ta d'auka da sallama ya Amsa Ahankali yace"muslima kin kyauta mun kenan?"dana maka me mlm?"ko gaisawa bazaka tsaya munyiba?"ta fad'a cikin tsiwa"yayi d'an murmushi yace"to Ina kwana?"uhmm nide Ina kwana?"to lafiya qlau "Anjima zanzo gidanku"wane gidan?"wane gida naga kin shiga jiya?"nide fa banan bane gidanmu"kuma basai kazo ba ko?"daga haka ta yanke wayar"tana gani yana kira Amma jan Ajinta ya hanata d'auka"dan babu k'arya muslima Akwai Jan aji da sanyin murya me dad'i musammun idan tana shagwab'a"shiyasa lokaci guda Aliyu yaji tayi bala'in shiga ransa,ga kuma sadam d'an yayar mahaifiyarta shima sonta yakeyi bedai furta mata ba.....fitowa daga cikin d'akin tayi da nufin taje tasha ruwa saita tafi sashen Eyyah ta gaidota"Malika da Naseem ne zaune a parlourn sai me Aiki dake  mopping"Malika tabita da kallon banza harta nufi gefen fridge d'in dake cikin parlourn"K! ta kirata cikin raini, banza muslima tayi mata "ke dan uwarki baki jina?"uban me kike nemar mana a fridge ?"duk muslima najin ta bata kulataba ta d'auki robar faro guda ta rufe fridge d'in"Agefen fridge d'in ta tsaya ta b'alle marfin ta kafa goran ruwan  Abaki tafara sha"Naseem ya girgiza kansa Ahankali yadda muslima bazata iya jiba yace"dan Allah ki k'yaleta Anty mal.....wani banzan kallo ta jefesa dashi tana tashi azabure ta nufi gaban muslima tana fad'in ke dan uwarki baki ji Ina miki mgn zaki mun banza?"ubanwa yasaka zaki bud'e mana fridge d'in? *uwarki ce tasaka na bud'e* shikenan?"Anan gidan ubanane babu wanda ya Isa ya takura mun ,matsayin mu guda dake, yadda aka haifeki nima haka.....marin da Malika ta d'auketa dashi yasaka ta kasa k'arasa sauran maganarta"ta dafe kuncinta tana sakin k'ara"Azabure ta finciko Malika cikin zafin zuciya suka fara dambe"Naseem yasaki salati yanufesu da nufin yarabasu sbd ya lura aka bar muslima nanda y'an mintina mugun duka zata iya yiwa Malika "sbd ba k'arfinsu gudaba,beyi zaton zata iya fin Malika k'arfi ba"yana k'ok'arin kai hannunsa da nufin yarabasu yaji muryar kabeer na danno Ashar yana fad'in"taya kika bari y'ar iskar yarinyar nan ta rainaki har haka kuke dambe?"be rufe bakiba Hjy jamila ta fito daga cikin d'akinta"salati tasaki tana kallon kabeer daya zaro belt d'in wondonsa "Atsawace tace yima shegiya mugun dukan da zaka kassarata....Naseem na ganin hakan yafita daga cikin parlourn Aguje "Aharaban gidan yasamu dollars da suraj da sadeeq zaune kan resting chairs suna mgn"kallo d'aya dollars yamasa ta k'asan Ido k'irjinsa yabuga!"domin ya fahimci Arud'e yake.....yayaaaaaaa! kataso yaya kabeer zai doki Anty muslima sbd suna fad'a itada Anty Malika"yak'are maganar yana hak'i had'e da nishi......✍️

🤔🫣🤭🤫 Free page yak'are maza ki biya naki tanan  yanzun za'a fara wasan😎
wannan book d'in nakudine

Regular grp 500
Vip grp 1000
Special grp 2k wato 3pages in a day

zaku biya kud'in ku ta wannan acc number👉2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK
Kituro shaidar biyanki what's app number d'ina 08100084251 500 kawai ake turo Kati idan bakida acc amma sauran payment d'in ta acc ne

banason transfer d'in Kati ko vtu photo d'in katin MTN zaki d'auka saiki turo dan Allah banda kira❌

Y'an nijar kutuntub'i wannan n👉 +227 88 01 90 50

Regular 500f
Vip 1000f
Special grp 2000f

Dan girman Allah da darajan iyayenki karkimun mgn idan baki shirya ba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: 🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾

💰💸 DOLLARS 💸💰

🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾🐾

Story & written by
mommyn fareesa

Dedicate to *rahinat hama, Aysha kyari wulgo& zainab hamisu wada* Ina yinku totally my commenters

Last free page 9&10 🙌

........Cikin sassanyar muryarsa mai d'an kauri had'e da bud'ewa yake furta "What?!!"da k'arfi

yana kafe Naseem da idanuwansa da lokaci guda suka fara sauya launi...sai kuma ya sauke numfashi tare da cewa"shi kabeer d'in ne zai daketa sbd sunyi fad'a da Malika? ya fad'a cikin yanayi najin k'aimi da tasowar mazantaka"Ahanzarce"ya mik'e tsaye yana kallon naseem daya kasa mgn "yayinda suraj da sadeeq ke zaune suna binsu da kallo"gefen zuciyar sadeeq na mamakin wacece sbd ita har dollars ya fusata irin haka?.....suraj kujirani Anan"ya furta cikin fusgo mgn yana barin wajen Ahanzarce"sbd yasan suraj zai iya biyosa yadakatar dashi gayima kabeee irin hukuncin daya gadama"dukda be tambayi meye ya had'asu ba"Amma ransa yabashi Malika ce zata tak'aleta da fitinah tunda ba k'aunarta sukeyiba"ya kuma san itama matsiwaciya ce bazata k'yale taba"yana wannan tunanin ya shigo cikin parlourn kamar An jehosa sbd k'ofar Abud'e take.tun kafin ya Ida shigowa yatsintsi muryar Hjy jamila na fad'in ka k'arama y'ar banza"yayinda shashshekar kukan muslima yakarad'e illahirin cikin parlourn "k'amshin turarensa kawai dataji yasaka taji k'irjinta yabuga tana duk'e ta d'ago kanta da sauri"kabeer na tsaye gabanta ganin shigowar dollars be hanashi dena dukanta da belt ba"Hjy jamila da malika kuwa ba k'aramin tsorata da yadda sukaga fuskar dollars tayiba sukayi"be tanka kowaba yanufi inda muslima take cikin izzah"Adaidai lokacin kuma ta d'ago kanta suka had'a Ido "da gudu ta mik'e tsaye ta fashe da kuka batasan lokacin dataje ta fad'a Ajikinsa ta rungumesa ba tana sakin wani marayan kuka....baki bud'e Hjy jamila ke kallonsu"yayinda Malika kamar zuciyarta ta fashe sbd ganin muslima Ajikin dollars "kuma be hanataba"yayinda kabeer yayi wurgi da belt d'in hannunsa yana huci ya kalleta tanata kukanta"Agadarance yace"Allah yasa hakan yakoma faruwa kiga yadda zanyi dake"babu wanda ya Isa ya hanani hukuntaki"idan kuwa Akwaishi ki turosa naga waye shi?yak'are maganar yana muzurai sbd Aganinsa yafi dollars iko da ita"sbd ita ubansu guda dashi, shi kuwa dollars dangi ne.....tunda ta rungumesa yayi tsaye k'ik'am yana jin wani zafi na sukar zuciyarsa"yana kallon yadda kabeer ke mata mgn cikin gadara"saida yayi shiru sannan yasaka hannunsa yad'ago kanta ya kalleta Ido cikin Ido yana fad'in "bana bama mai son ganin kukana dama a duk lokacin da yaso hakan, domin inaso na tabbatar masa da cewa damarsa itace nasarata a yau da kuma gobe na"yana fad'in hakan ya janyeta daga jikinsa ya nufi kabeer dake k'ok'arin tafiya"ta baya yayo jakin nasa yadawo gabansa"Afusace yajuyo da nufin ya gaya masa mgn, dollars ya d'aukesa da gigitaccen marin dayaga stars na masa shawagi!! fuska bbu Annuri yace"kace ba!babu wanda ya Isa ya hanaka ko?"toni na na hanaka koda bata turoniba"yak'are maganar cikin tsawa yana fincikosa yafara bashi puncher's tako Ina"salati Hjy jamila keyi tana zaro Ido had'e da dukan k'irji tace"me hakan ke nufi Muslim?"sbd ita zaka kama dukansa Agabana irin haka?"kai kuma bazaka ramaba zaka tsaya yana dukanka?duka shekara nawa yabaka ne?"ke kuma Algunguma yau saikin sani tunda kece sanadin komai"ta k'are maganar tana nufar muslima dake tsaye tana kallon yadda dollars yazage k'wanji yana jibgar kabeer Agaban uwarsa kamar Allah ya Aiko sa"yayinda Malika ta d'auki wayarta tafara k'ok'arin kiran daddy domin tasanar masa..... k'ara muslima tasaki sbd ganin Hjy jamila ta nufota"da sauri ta matsa ta nufi gefen dollars "Adaidai lokacin kuma ya hankad'a kabeer yafad'i kansa yadaki center table"Atake gefen goshinsa yayi kumburi dama ga hancinsa yafashe"dollars na huci batare daya damu da Abinda zai biyo baya ba yajuyo cikin zafin rai zai finciki hannunta Adaidai lokacin suraj yashigo cikin parlourn ,sbd yasan idan ran dollars na'a b'ace ko mgn beyi kuma zai iya yin d'anyan Aiki "kuka Hjy jamila ta fashe dashi tana fad'in wlh bazata yaddaba"suraj ya kalli muslima daketa sharb'an kuka jikinta duk shatin dukan da kabeer yamata yace"meke faruwa ne wai?"kasa mgn tayi dollars yaja

hannunta da k'arfi yana bin Malika dake waya da mugun kallo yana furta ki jira naki hukuncin"yana fad'in hakan yajata suka fita"bbu wanda yayi mgn cikinsu"yayinda suraj ke biye dasu har suka iso sashen Eyyah"ko sallama dollars beyiba suna shiga yacika hannunta"Eyyah dake zaune tabisu da kallo Atake ta fahimci ran y'an maza yab'aci"takuma tabbatar komai za'a yi bazaiyi mgn ba saiya huce"hakan yasa tayi shiru"dollars bebi takan suraj ba yanufi d'akinsa dake Anan sashen"yayinda har a lokacin muslima kuka takeyi"suraj ya zauna kan kujerah suka gaisa da Eyyah ta fara tambayarsa meke faruwa? yasanar mata iya Abinda yasani"bayan yagama yimata bayani ta dawo gefen muslima tafara rarrashinta harta sanar mata yadda Akayi tun daga farko har k'arshe....uhmmm!Abinda muslim yayi shine daidai"jamilah kuma lokaci yayi daya kamata mu nuna mata iyakarta tunda har yanzun tana kan bakanta nason ta raba zumuncin Allah da k'arfi da yaji"muslim yana so kisake kiyi Alfahari da gidan mahaifinki shiyasa ya jajirce har kika dawo" Anan gaba zaki gane dalilinsa ki kuma fahimcesa"shi kuma sulaiman d'in zai dawo yasameni(daddy)"gaba d'aya yaransa idan aka cire Naseem dake sauran biyun basuda tarbiya"naseem ma Allah ne kawai yasaka be biyo mugun halin taba"itadai muslima share hawayenta tayi tana tunani"tunda ta tashi ta fara wayo take jin haushin muslim sbd yadda yake bata umarni da yadda yake d'aure mata fuska"bata tab'a jin zatayi Alfahari dashi a matsayin d'an uwantaba sai yau"yanzun idan babushi da shikenan Malika ta Mari banza? hakama kabeer yadaki banza bbu Abinda za'a yi"tunda tasan dai daddy bazai d'auki mataki ba"saidai su Abbie,suma kuma fad'a ne kawai zasuyima kabeer d'in"gaba d'aya sai tayi shiru tana jinta wata iri"musammun idan ta tuna kalamansa dake tattare da gugar zana daya sanar mata d'azun sadda tana kuka"Ayanzun jin zuciyarta takeyi Adake ko Hjy jamila ta nemi takata bazata raga mataba"itama Ayanzun ji takeyi ta Isa tayi tunk'aho da gidan mahaifinta.....saita d'an turo baki sbd jin jikinta na k'amshin turaren dollars....nizan d'an fita Eyyah "idan d'an gidan naki ya huce zan dawo"Amma yaka mata muslima tad'an gasa jikinta ,ta kuma sha magani sbd kar tayi ciwon jiki"haka nima nake zato"kiyi hak'uri komai zai wuce"ta k'are maganar tana jan hannunta suka nufi d'akin baccin Eyyah d'in"yayinda Suraj yafita"ruwan zafi Eyyah ta had'a mata sannan ta fito tabarta cikin bath room d'in sbd tayi wankan ta gasa jikinta"ta jima kafin ta fito ta sami Eyyah zaune gefen bed tana waya da Alama da Abbie take wayar"gefen bed ta zauna har ta gama wayar"wai Eyyah yanaga bbu irin shower jal d'in da kika Aikamun dashi d'azun a toilet naki?"ni kuma?"Eh mana"kinga ni ban wani Aika miki da komai ba"da mamaki tace"Naseem ne yazo yakawo mun yace"injiki"kinga saka kaya ni Ina parlou"daga haka Eyyah ta fita"sosai muslima ke mamakin to waye yaturosa?saidai ganin batada Amsa yasaka taci gaba da hidimar gabanta.....misalin k'arfe 2:11 pm muslima ta fito daga cikin kitchen da warmers d'in Abinci Ahannun ta tanata y'an wak'e wak'enta"ta canza kaya zuwa doguwar riga ta lace pink gownt"wacce ta koma d'azun d'akinta ta canzo" kayan sun k'arbi jikinta d'as ,sosai coka cola shape nata yafito"juyowa tayi da sauri sbd k'amshin turarukan dollars da hancinta yashak'o...Aikuwa tayi Arba dashi zaune kan kujerah yana duba wasu jaridu"yaci sabon wanka na wondo 3 quarter da t shirt fara "fuskarsa bbu Alamar rahama cikinta"ga wani kwarjini dataji yamata"haka kawai taji dama beji tana wak'a ba"nunawa tayi kamarma bata ganshiba ta koma cikin kitchen d'in "shi kuwa sarai yana lura ta gansa saiya tab'e baki yana cigaba da duba jaridun"yana kuma tunanin muddin yasaka Akama kabeer be yiwa mutanan bugaja's house's Adalci ba"bayan haka da wlh a cell zai kwana"yana wannan tunanin naseem ya shigo parlourn cikin damuwa yana d'auke da siyama yad'an duk'a cikin girmamawa yace "yaya daddy

yace"kuzo kaida Anty muslima.... dollars na k'ok'arin yimasa mgn Anty habiba(k'anwar iyayen nasu )ta shigo da sallama itada y'arta ta biyu me suna husnah"wacce zasuyi age mate da Malika"dollars yad'an saki fuska yana Amsa sallamarta"tana murmushi tace"my son Ina fushi dakai"tuba nakeyi Anty nah"zanzo gidan in sha Allah"yaya Muslim Ina wuni?"cewar husnah tana zama kan kujera tana satar kallonsa tana jin inama inama"ya Amsa fuska bbu yabo bbu fallasa yana kallon Naseem dake gaida Anty habiba yace"jeka tana kitchen kasanar mata"dato ya Amsa, kan idonsa ya d'auki siyama suka nufi kitchen d'in"yabisu da kallo sbd tuna wani Abu daya wuce Abaya da yayi....Ina Eyyah d'in?"tana ciki Anty"okay ya kasuwa da office?"Alhamdulillah Anty"sageer yacemun kuna gaisawa ta online sbd ganinka sai mai sa'a "ba haka bane Anty kinsan week end nakeyi Anan....be rufe bakiba muslima da Naseem suka fito daga cikin kitchen d'in"saidai idanuwanta cike da k'wallah suke "fuskarta na nuna Alamar tsoro"sbd tana gudun kar daddy yadaketa "gaba d'aya jinta takeyi cikin k'unci"sbd tunda tadawo gidan daga jiya zuwa yau batada wata walwala "wanake gani kamar muslima?"itace Anty tadawo nan Ai "cewar naseem yana fita"ita kuma ta russinah suka gaisa dasu"Anty habiba ta tab'e baki tana fad'in nasan dai ba dad'in zama da Hjy jamila kikeyiba da wannan yarinyar me girman kai(Malika)"idan zaki cire tsoro ki zauna ki wala gidan ubanki shine zai fi miki daidai.....shigowar Abbie cikin parlourn yasaka Anty habiba yin shiru"Atare itada dollars suka masa sannu da zuwa"wanda kallo d'aya Abbie yamasa ya fahimci yana fushi da wani ko kuma b'ata masa rai Akayi "saidai bece komai ba ya zauna suna gaisawa da Anty habiba"sai Akayi sa'a muslima ta saci kallonsa "ya wurgo mata harara yana fad'in ki wuce muje"yak'are maganar yana mik'ewa tsaye "ita kuma ta warware veil d'in saman kanta ta yafa ya sakko har kafad'a"Abbie ya kallesu yace"Ina zakuje?"k'in mgn dollars yayi saidai ita tace daddy ne ke kiranmu"dato Abbie ya Amsa sbd shibe san meke faruwa ba"Eyyah dai takirashi tace"yadawo gida da wuri Akwai y'ar matsala"kasancewar sai 4:pm yake dawowa...suna fita Eyyah na shigowa cikin parlourn "da mamaki tace"Autah yaushe kika zone?"yanzun nan Eyyah bamu jimaba"Ashe muslima tadawo nan?"wlh kedai bari"hakan ai yafi naji dad'i wlh"sai bayan Eyyah ta zauna sun gaisa ta tura husnah sashen ummi sbd suyi mgn"cikin fahimta tayima Abbie bayanin komai.....shiru yayi na wasu mintina kafin yace "to yanzun sulaiman d'in Ai kiransu yakeyi suna canma "bara su dawo tukum sannan Nina yanke nawa hukuncin "muddin matarsa ta kaini bango bbu ruwana da sun jima tare saidai ya sallameta"na rasa me jamilah takeso ta maidashi?"da mace tasanar masa da mgn bbu bincike yake d'auka"Anty habiba tace"to Ai Abbie ba haka tabarsa ba idan nayi mgn kuk'i yadda"Amma wlh duk wanda yakoma dukanta sai kowa yagane kuransa"shidai Abbie shiru yayi yana tunani"iya saninsa da Muslim be tab'a ganin wacce yadamu da lamarinta irin muslima ba......

suna fitowa muslima taja ta toge daga bakin k'ofar tana shagwabe fuska idonta cike da k'wallah"kamar dollars ya shareta sai kuma yace"tsayuwar me kikeyi ?ko kuwa ranki kike buk'atar yab'aci ne?"nide Allah yaya muslim bazan jeba karfa daddy yadokeni"kuma harfa yanzun jikina bedena zafin dukan d'azun ba ko?"duk tana maganar ne cikin shagwab'a "rasa meye zaice mata yayi"yana dai tsaye kawai yana danna waya "hannunsa guda cikin Aljihun wondonsa"can ya kalleta yaga hawaye takeyi"kinsan Allah koki wuce muje ko kuwa na baki mamaki"miye Amfanin kukan da nuna jin tsoron "to bari kiji"mukaje kika k'i tsayawa kiyi masa bayani idan yatambayeki kece zaki jama kanki"yana fad'in hakan yatab'e baki yana yin gaba"batada zab'in daya wuce tabiyosa Abaya"sai satar kallon gashin kansa da manyan

k'wanjinsa takeyi tana gulmarsa wai yacika tsayi,jikinsa kuma duk gashi"shidai besan tanayiba"har suka iso cikin parlourn yana daga gaba tana biye dashi babu wanda yakoma mgn"daddy da Hjy jamila na zaune kan kujerah "daddy ya had'e rai fuskarsa bbu Annuri ko Alamar sassauci Acikinta"gefe guda kuma kan carpet kabeer ne zaune da fuska a kumbure"idanuwansa sunyi bala'in yin jajir"yana jin kamar ya d'auki wuk'a ya dab'ama dollars da muslima sbd zafinsu dayakeji Aransa"be tab'a zaton dollars nada irin wannan k'arfin ba"da tuni beyi gigin da yayiba....sau biyu dollars nayin sallama bbu wanda ya Amsa "hakan yasa kawai yad'an duk'a kan carpet ya d'od'ana ,da sauri itama muslima ta rab'a gefensa"Anutse cikin taushin muryansa yace"daddy barka da rana....ba dalilin dayasa ka kenan na kiraka ba"Ashe bakada mutunci Muslim?"sbd wannan y'ar iskar yarinyar zaka kama kabeer da duka kamar zaka rabashi da ransa"bayan ta zagesa sbd yana yayanta ya d'auki mataki saika nuna be isaba"to bari kaji ! idan kana tak'ama kanada kud'i har zakayi haka baka isaba"haihuwarka Akayi daga d'a baka kauba"ke kuma dan ubanki na baki minti 5 ki tattare inaki inaki ki barmun gidana...wani irin farin ciki Hjy jamila taji Aranta"yayinda tsakanin dollars da muslima bbu wanda yace komai"dollars ya fahimci daddy yayi nisa wajen b'atar dashi da Hjy jamila tayi"ya kuma fahimci k'arya kawai suka zauna suka kitsa masa"yad'ago kansa idanuwansa sunyi tamkar garwashin wuta sbd jaa"cikin k'asa da murya yace"kayi hak'uri daddy ka tsaya kayi bincike kaji meke faruwa?"binciken banza"k'arya za'a mata ne?"dan uwarki bazaki tashiba?"kaima daga yau karka koma zuwa bagajas house's saina nemeka"dukan dakayima kabeer kuwa bazai tashi Abanza ba"zaku tashi ku fita ko kuwa?"yafad'a Atsawace"Hjy jamila na marairaice murya tace"Amma Alh daka barsu kar Ace kuma....kar ace me?na gama mgn "dollars bece komai ba ya mik'e tsaye ya kalli muslima dake kukan bak'in ciki"Aranta tana jin bazata tab'a yadda ta Auri me mataba ko kuwa ta zauna da kishiya ba"yanzun dai uwarta ta mutu Amma gashi kishiyarta na kishi da ita"data san irin wannan to zarcin mahaifinta zai mata da bata yadda tadawo gidan ba.... lallausan yatsansa manuniya daya sauka saman fuskarta yana share mata hawayenta dashi yasaka tadawo tunaninta" da sauri ta d'ago kanta suka had'a Ido"girgiza mata kansa yayi Alamar ta bari kafin yakama hannunta guda batare dasun kalli kowaba suka fita daga cikin parlourn…......✍️

To masu karatu Anan free page yak'are sai mun had'e a paid grps Anan chakwakiya da zazzafar soyayya take kundai san alkalamin mom fareesa 😂🥰

wannan book d'in nakudine
Regular grp 500
Vip grp 1000
Special grp 2k wato 3pages in a day

zaku biya kud'in ku ta wannan acc number👉2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK
Kituro shaidar biyanki what's app number d'ina 08100084251 500 kawai ake turo Kati idan bakida acc amma sauran payment d'in ta acc ne

banason transfer d'in Kati ko vtu photo d'in katin MTN zaki d'auka saiki turo dan Allah banda kira❌

Y'an nijar kutuntub'i wannan n👉 +227 88 01 90 50

Regular 500f
Vip 1000f
Special grp 2000f

Dan girman Allah da darajan iyayenki karkimun mgn idan baki shirya ba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

.........yana rik'e da hannunta guda suka nufi parking lot batare da d'aya yayima d'an uwansa mgn ba"zuciyar dollars in bacin zafi da rad'ad'i babu Abinda takeyi"tunda yataso yarasa mahaifinsa be tab'a damuwaba sosaiba sai Addu'a yake masa"saidai Ayau yaji mutuwar mahaifin nasa ta dawo masa tamkar sabuwa"yasan tabbas koda daddy baya'a hayyacinsa muddin mahaifinsa na raye bazai masa irin wannan cin zarafin ba"saidai kuma daya tuna yadda yazage muslima tas ,ya koreta tana matsayin y'a mace sai yaji zuciyarsa na tsinkewa "be tab'a dana sanin maido yarinyar gidan ba sai yanzun"yasan kuma be kamata ya maida ita wajen kakarta ba"bazai kuma je yasanarwa su Eyyah da komai ba"zai bar gidan shida ita kamar yadda daddyn ya buk'ata..... subahanallahi! Ina kuma zakuje dollars?cak tunaninsa ya tsaya yabi suraj da kallo da jajayen idanuwansa "yayinda muslima keta sauke Ajiyar zuciya har lokacin kuma tana hawayen bak'in cikin mahaifinta da bakinsa yace tabar masa gidansa"kayi mgn mana ,kukan meye takeyi ne??"ya k'are maganar yana shan gabansu"dollars ya girgiza kansa murya babu Alamar wasa yake fad'in suraj bamu hanya mu wuce"idan na k'ara mintina 5 Agidan nan Abinda zai faru bame kyau bane"daga haka yayi shiru yaja hannunta sukayi gaba batare daya jira cewar suraj d'inba"yayinda suraj beji haushiba sbd ya lura dollars d'in na cikin b'acin rai "Amma ransa yabashi koma miye tsakaninsu da daddy ne ,zata iya yuyuwa Hjy jamila ta shirya wani makircin sbd Abinda yafaru d'azun"da hanzari yanufi sashen su Eyyah....har lokacin Abbie da Eyyah da Anty habiba na zaune a parlourn suna mgn"cikin wani yanayi suraj ya musu bayanin yadda yaga su dollars da kuma kalamansa"da sauri Abbie yatashi suka nufi parking lot ,saidai sadda suka iso tuni dollars da muslima sun dad'e da fita shida ita Amota batare daya nemi koda driver ba,hakama body quards"cikin b'acin rai Abbie yakira daddy ta waya yasanar masa yazo yanzun yanxu a parlournsa yana son mgn dashi"sannan ya bama mararsa Hjy jamila mintina 5 taje gidansu saiya nemeta"umarni ne ba shawaraba idan hakan bazai faruba yaciresa a lissafin y'ay'ansa"yana gama wayar yakashe yakoma parlourn sa"bayan mintina 15

saiga Abba da daddy"kallo d'aya sukayima mahaifin nasu kowa yasha jinin jikinsa"ba tare da Abbie ya Amsa sannun da suke masaba ya kalli daddy fuska babu Alamar wasa yace"meye kasanarwa muslim da muslima yanzun daka turo akirasu?? wani Abu muslim d'in ya sanar maka Abbie?"Ina tambayarka kana tambayata?"kayi bayani mana yaya"cewar Abba"kan daddy ak'asa yashiga yimasa bayanin yadda yakoresu"yad'ora da fad'in nayi hakane sbd suyi nadama karsu koma maimaita Abinda sukayi"kabeer yayanta ne yadace sbd yasakata Aiki tak'iyi ya mata mgn ta zagesa Abbie?shine kuma yamareta muslim zaizo ya dinga dukansa....saida yayi shiru kafin Abbie yayi murmushi yace"haka jamilar da kabeer d'in suka kitsa maka?batare da kayi bincikeba ka yarda?to yayi kyau "yanzun jamilar tana gidan ko ta tafi?"Abbie bazan iya tsallake umarnin kaba"nace taje matsayin ziyara takawo musu zuwa Anjima zanzo"uhmmm sulaiman kenan!"to Abarshi Amatsayin hakan in sha Allah wata ran da kanka zakazo ka kamun zancenta da irin hukuncin da zaka yanke mata"saidai ni nawa hukuncin da zan yanke ita da yaranta saiya girgiza su"inaso Anjima ka kira Muslim lokacin ya huce kace yadawo gida shida muslima ka janye k'udurinka sbd kaga be kamataba"sai Abu na gaba duk lokacin da makamancin haka yakoma faruwa kayi bincike ka kuma shawarceni kafin yanke hukunci"sai Abu na k'arshe dakace ka kori muslim"ka godema Allah baya daga cikin yaran wannan zamanin daya maka rashin kunya "karka manta "Allah shine gatan kowa Amma muslim shine gatan duk mutanan gidan nan"Akallah yakashema gidan nan million 100 "bayan gidan mahaifinsa na gado da filayen daya siya ya turo gidan nan Akayi Aikin gidan nan dasu aka zuba kayan More rayuwa dan kowa yaji dad'i .shine sbd rashin tunani dason mace yasaka ka kasa hangen nesa har zaka koresa"Ai idan aka bibiyama shine yake da damar dazai iya korar kowa Agidan nan"karka manta Asalin gidan nan marigayi Isma'il shine yaginasa yabaka yaba Habibu"sannan ya Ani nawa sashen"karka yadda mutuncin da muslim yake ganinku dashi yazube"kaje kayi tunani matarka ba k'aramar shed'aniya bace"inaso ka jawo muslima Ajikinka ka kula da ita kaji damuwarta"wlh Ina jiye maka ranar da Allah zai kamaka da hakkinta"har yanzun bata tab'a sanin tunda ta koma hannun dangin uwarta baka tab'a d'aukar nauyin taba"komai saidai Muslim yayi mata Amatsayin kaine kasaka shi"kosu dangin uwarta haka suke d'auka"yanzun koda kaine ka haifi Muslim iya Abinda zaiyi maka kenan"kasan dai kabeer kaika haifesa Amma bazai iya yimaka Abinda Muslim yamaka ba"babu gori koson na kare Muslim a maganata iya gaskiyata da nasiha nake maka"kaima habiba saika k'ara yimasa wata nasihar"zancena dakai na k'arshe muddin Muslim da muslima basu dawo gidan nan ba to karka sake jamilah tadawo"idan kuwa bakayi sannuba harni dana haifeka saita rabaka da ni"Abbie nakai Aya Azancensa ya mik'e tsaye yabar parlourn "Abba ya sauke numfashi yana kallon daddy da gaba d'aya jikinsa yayi mugun yin sanyi"ya tabbar da zancen Abbie gaskiya ne"saima yanzun yake dana sanin Abinda yayi yana tunanin to meya shiga kansa harya Aikata hakama?"gaba d'aya kunyar dollars yaji yanaji"saidai yarasa meyasa bayajin haushin Hjy jamila?"itama kanta muslima d'in sai yaji tausayinta.....zancen gaskiya yaya dole ka gyara kurakuranka"sannan yaka mata kadinga bincike idan Angaya maka mgn"kuma kadinga takema jamila burki Akan wasu Abubuwan na cikin gidanka"sai kuma dan Allah kadinga yawan Azkhar da addu'o ga iyalanka"Anjima nima zan kira Muslim d'in "na kuma shiga d'azun sashen su Abbie na samu habiba da Eyyah sun mun bayanin Abinda yafaru"yamasa bayanin komai....shiru daddy yayi yana tunani can ya sauke numfashi Ahankali yace"to shikenan Allah yakaimu "daga haka suka baro parlourn kowa yayi inda zashi.....tunda suka shiga mota dollars ya jata Ahaukace"yayinda

gaban muslima keta fad'uwa tana tambayar kanta Ina zashi da ita?"tanaso ta tambayesa saidai yadda taga kyakykyawar fuskarsa ta juye bbu Alamar sassauci Acikinta yasaka tayi shiru kawai"Amma ta dena kukan"saima karatun Alkur'ani me girma data kunnah tana saurare cikin kira'ar shaikh sudais.....cikin y'an mintina daga ita harshi kowane yasamu nutsuwa"itadai idonta na'a lumshe jin yana horn yasaka ta bud'e idanuwanta "ta hango Ana bud'e musu get d'in wani gida me kyau"da sauri ta kallesa"taga ya k'ara had'e rai"ta kauda kanta da k'yar tayi jarumtar cewa inane nan yaya?"banza yamata kamarma ba dashi take mgn ba"bayan ya gama parking yafito"ita kuma ta d'aure fuska tanata turo baki tak'i fitowa"cikin zafin rai ya bud'e k'ofar gefen datake ya finciko hannunta  da k'arfi"ta saki k'ara tana turjewa"ki fito muje karki koma b'atan Rai"idan kuma k'arfina kikeso na nuna miki zaki samu hakan"to waini inane nan d'in?"kawai saika taho dani inda bansan....bige mata baki yayi fuska Agimtse yake fad'in Idan kina mun mgn kina turan baki ko murgud'a mun saina dokesa yayi jini"siyar dake zanyi Agidan stupid kawai"yafad'a yana Ida fisgota ta fito"ta saki kukan shagwab'a tanata turjewa"sai bayan ya rufe k'ofar ya kalleta tak'i yarda ta kallesa"ya tab'e baki Ahankali yace"meyasa bakya jin maganata *halimatu*?" da sauri ta kallesa da mamaki"ya wurgo mata harara fuska Ad'aure yace"gulmar banza zaki wuce muje ko kuwa?"wlh mukaje Agaban ummah kika mun wani shirme ranki ne zai b'aci"shiru tayi sbd ta fahimci gidan mahaifiyarsa ne sukazo"dama ita bata tab'a ganin umman saba"tasan dai tana a raye"shi kuwa be koma mgn ba yana rik'e da hannunta yajata suka wuce ciki"saidai ta dena turjewar tadai shagwab'e fuska kawai"da sallama suka shigo cikin babban parlourn gidan"haka kawai muslima ta tsintsi kanta dajin fad'uwar gaba "Amatallahi da ummah da Farooq na zaune a parlourn sai musty dake wasa a tsakkiyar parlourn"wani irin bugawa k'irjin Amatallahi yayi dataga Muslim ya shigo rik'e da hannun wata"da Ido kawai ta tsaresu zuciyarta najin zafin kishi "dama jiya yazo da dare bata ganshiba sai yau.....yaya sannu da zuwa kaida bak'uwa kuke tafe?"cewar Farooq yana kallonsu ,zaiyi kusan 25yrs"kansa kawai dollars ya gyad'a masa yana k'ok'arin janta su zauna kan kujerah 2 seeter "ba k'aramin tsorata da irin kallon da ummah ke jifarta dashi muslima tayiba"hakan yasa yana cika hannunta ta sakko k'asa kan carpet ta gaisheta ta zauna"da k'yar ta Amsa mata"duk dollars na lura"hakan yasa koda Amatallahi ta gaidashi yayi kamar bejiba.....bakaji Ana gaida kaine?"yad'ago kansa yana Amsawa da lafiya qlau "sai a sannan muslima ta gaida Farooq ya Amsa da kulawa yana tambayar ko itace muslima?"kanta kawai ta gyad'a masa "ummah kuwa kamannin mahaifiyarta data gani Atare da ita yasaka tun kafin Farooq ya tambaya ta ganeta"mik'ewa tsaye ummah tayi tabar cikin parlourn " dollars yad'an kalli muslima"yaga suna hararan juna itada Amatallahi"murmushi yaso yasub'uce masa saidai ya dake ya mik'e tsaye yana mamakin fitinar yarinyar da fad'an ta....yaya muslim zansha ruwa" cewar muslima tamkar wata y'ar yarinya"kauda kansa yayi  ya kalli farooq yace"kamata ruwa"ke Amatallahi kamata ruwa da lemo"ni Allah bana son nata"ta fad'a cikin shagwab'a"Farooq yayi murmushi yatashi yanufi kitchen "muslima ta turo baki sbd ganin dollars zai tafi"to yaya Ina zakaje?"kijira mintina 5 nadawo mana"daga haka be koma bi takan taba yashige d'akin ummah"Amatallahi taja tsaki tana yatsina fuska tace"shishshigi da cusa kai bbu kwarjini"muslima na murmushi tace"ikon Allah! shifa kansa shishshigin sai mai matsayi keyi"wani bema ga hanyar dazaiyi shishshigin ba"ke dawaye kike?"da wanda ya tsargu"cewar muslima tana watso mata harara"ranta na bata yarinyar son dollars takeyi"Amatallahi na k'ok'arin mgn farooq yashigo cikin parlourn"hakan yasa tayi shiru tana jin mugun haushin muslima"wacce zasuyi age mate da juna"Agabanta ya

Ajiye mata, ruwan kawai ta zuba tasha tafara danne danne Awaya..... Azaune gefen bed yasami ummah fuskarta Ad'aure"yana shigowa tace"miye ma'anar zuwanka da wannan yarinyar harda rik'e mata hannu?"hakan dakayi daidai ne?"saman sofa ya zauna kansa a sunkuye yace"k'infa yadda tayi mu shigo ita sai taji inane nan?to dama nace maka Ina buk'atar zuwan natane?"ko kuwa so kakeyi aga kana yawo da mace Amaka wata fassarar tunda kak'iyin Aure? "sbd cin fuska shine kazo da ita nan kasan Amatallahi zata gani"yayi shiru yak'i mgn "yarasa meyasa ummah tak'i gane yarinyar bata masaba? ganin yayi shiru tace"idan wajena kazo kamaida ita inda ka d'akkota ka dawo"da sauri yad'ago kansa ya kalleta da idanuwansa da har yanzun da sauran jansu"ta kauda kanta sbd yadda yamata kama da mahaifinsa"nafa maida ita kikace ummah?"nafa kawota nan tad'an zauna ta miki kwana biyu sb......kanada hankali Muslim?"kamarya ta kwana 2?"yayi shiru yana tunani"wai yanzun sbd duk kan Amatallahi ummah zatak'i yarinyar da mahaifinta yasoshi ya inganta Arayuwarsa?"ya d'auka yadda daddy ya kula dashi ummah baza tak'i jinin daddyn ba"Ada yaso yamata bayanin matsalar data faru Amma ganin tayi hakan saiya fasa"saima ya mik'e tsaye cikin ladabi yace "zanje na maida ita Anjima da yamma zan dawo" shiru tayi tana tunani"saidai ta kasa gane komai game da tsakaninsa da yarinyar"Abaya dai tasan yashak'u da ita sosai"ko zuwa wajenta yayi zaita yimata firanta"lokacin kuma da Aka Amshi muslima d'in haka yazo nan yanata fushi har daga baya ya hak'ura yasaba.....muslim sbd ita yarinyar zakayi fushi ?"nifa umma banji komai ba"naga dai bakya son zuwan namu da itane"hannunta dana rik'e ban rik'e da wata manufa ba Allah ya sani"kuma naga ita d'in k'anwata ce"shiru tayi batace komai ba "shi kuma ya d'auki wayarsa k'arama da Aketa faman kira"d'agawa yayi be furta komai ba "daga d'ayan bangaren Aka masa sallama da fad'in yallab'ai idan babu damuwa muna son ganinka da k'arfe 4 zamuyi meeting pls"okay kawai yafad'a yana yanke wayar sbd manager d'in gidan man fetur d'insa ne dake Anguwar Jan bulo"time yaduba yaga 3:27 pm"ummah sai Anjiman"Allah yakaimu ta fad'a "shi kuma yafito"muslima ya kallah har lokacin tana zaune kan carpet tana danna waya"k'amshin turarensa dataji yasaka ta d'ago kanta suka had'a Ido"tashi muje "to yaya Muslim ka zauna kasha ruwan mana"ji yayi bazai iya disgata gaban su farooq ba"sai kawai ya zauna ta zuba masa ya Amsa yasha ya Ajiye cup d'in"kafin su mik'e tsaye tayiwa farooq sallama batare data kalli Amatallahi dake kallonsu tana hararar taba"fitowa sukayi suka nufi inda yayi parking"nifa yunwa nakeji gaskiya"yi yayi kamar be jitaba"ya bud'e k'ofar mazaunin driver sit ya shiga,ita kuma saita ja ta tsaya"kina jiran nace miki ki shigo ne?"na lura sbd Ina binki Ahankali shiyasa kikemun shirme ko?"nifa yaya muslim yunwa nace maka inaji ko?"yatab'e baki yana fad'in Amma d'azun ba saida Aka rarrashekiba kikaci Abinci yanzun kuma kike fad'in kina jin yunwa?"to Ai sbd na tsani cikin gidan ne"karki koma yiman zancen gidan can"tayi shiru "wlh kika bari na fito baki shigowaba sai kin sani"be rufe bakiba ta shigo yaja motar da k'arfi har saida ta saki k'ara "ta d'auka koma wata restaurant zasuje sai taga sunyi hanyar gidan mansa"batace komai ba tadai d'aure fuska tana danne danne Awaya "Tasha Alwashin bazata koma masa zancen yunwa take jiba"gashi taji Anfara kiraye kirayen sallar la'asar "rabonta da Abinci tun break fast"tana wannan tunanin kiran Aliyu yashigo cikin wayarta.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitarmun Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
 #sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

......haka kawai muslima ta tsintsi kanta dak'in son ta d'aga wayar Agaban dollars "gashi tanata ringing"satar kallonsa tayi taga driving nasa yakeyi cikin shan k'amshi tamkar besan da zamanta Amotar ba"saita tab'e baki Aranta tace"kaji dashi"duk wacce ta Aureka ta Aurar ma kanta problem"ta Ayyana hakan Aranta tana d'aga wayar "Adaidai lokacin kuma dollars yayi parking"sallama ta masa cikin muryarta me dad'in gaske, saidai tad'an shak'e ta rage siran taka sbd kukan data sha....daga d'ayan bangaren Aliyu ya lumshe Ido yana Amsawa kafin yace"ya kike?"Alhamdulillah "da gaske fa muslima zanzo yau d'in"hmm! Ina mamakin ta yama kasan sunana?"karkiyi mamaki idan mutum na muradin abu zaita bincikarsa har yasamu"Amma fad'amun kina wane Anguwa ne?nifa bazan sanar maka ba ,tam"ta k'are maganar cikin tsiwa..... mitsssssuww!! Dollars yadoka wani kakkauran tsaki yana yamutsa fuska da k'yar yace"K`` dallah fitarmun Amota idan yazama dole kiyi wayar sai kiyita daga waje"batace komai ba ta fito tana yanke wayar sbd taji zafin maganarsa"shi kuwa fuska Ad'aure cikin shan k'amshi ya fito daga cikin motar yana mamakin rashin kunya da tsiwar yarinyar "Abinda bazai iya d'auka ba kenan ga kowace yarinya ta dinga gaya masa mgn bbu ladabi" daya tattaka yarinya wlh....tun daga nesa sadeeq dake zaune saman mota ya hango fitowar muslima daga cikin mota tanata b'ata rai"sannan yaga dollars yafito shima fuskarsa bbu Annuri "ma'aikatan gidan man wasu nata tasowa suna kawo gaisuwa saidai yad'aga musu hannu kawai yayi gaba ,ita kuma tana biye dashi"yaja tsaki Ahankali yana fad'in na rasa meyasa koya matsiyacin mutumin nan yasaka suturah saita hau jikinsa ta masa kyau koda kuwa jallabiya ce?"dubesa kamar bad'an Nigeria ba"da Akwai hanyar da zanbi na rabashi da ransa dana bi tuni wlh....shiru yayi sbd ganin dollars yakusan isowa ta gefensa su wuce"sai kuma ya hango Hjy zarah (y'ar jarida) daga nesa ta fito daga cikin motarta"da Alama k'ilan son mgn takeyi da dollars "kasancewar tana yawan yima mutane hanya suzo ya taimaka musu"itama kuma ba wani sake mata fuska yakeba "hasalima sbd yayanta Ibrahim na Abokinsa shiyasa yabata wannan damar"dirowa daga saman motar yayi sbd dama yana son mgn da dollars ne"Ido suka had'a yad'an k'ak'aro murmushi yana fad'in Abokinah barka da shigowa"saida dollars ya d'auki kusan second 10 kafin yace barka dai iya saman red lips nasa, kafin ya giftashi ya wuce"kan idon muslima taga ya jefesa da mugun kallo yana shan kwafa"yana d'auke idonsa suka had'a Ido da ita"ita kuma bbu kunya ko tsoro ta wurgo masa harara tana d'auke kanta " da mamaki yabi yarinyar da kallo"lokaci guda yaji yarinyar ta burgesa , musammun yadda yaga irin dressing nata"ga coka cola shape nata daya

tafi da imaninsa...saidai besan meye Alak'arta da dollars ba"yana kuma jin shakkar hararарsa datayi"saidai ransa yabashi sbd ta lura da kallon tsanar da yayiwa dollars ne.....be dena kallon suba saida ya hango sun shiga office d'insa"sannan ya sauke numfashi da nufin idan Angama sallar la'asar yashiga suyi mgn....Ina wuni?"cewar Hjy zarah"wacce zatayi 28yrs" bazawara ce da y'arta guda"Amsawa yayi fuska Asake,itama tabi ta gefensa ta wuce.....wani ni'imtaccen sanyayyan k'amshi dake tashi cikin had'ad'd'an office d'in yadaki hancin muslima"Aranta ta furta wow! zama yayi kan kujerar gaban wani table yana y'an dube dube batare daya ce ta zauna ba"tana dai tsaye"ta wutsiyar Ido ya lura bata zaunaba"sosai ta k'ara bashi haushi ya lura yarinyar na hayak'i Amma daidai yake da ita"yasha Alwashin saidai ta kwana atsaye in har sai yace ta zauna"time ya duba yaga lokacin sallah yayi yanzunma Ankira sallar A masallaci dake cikin gidan man daga gefe"yana wannan tunanin sakatarensa yakira talephone yasanar masa yanada bak'uwa "ta shigo"ya furta Atak'aice "sai lokacin da muslima ta gaji da tsayuwa ta zauna kan wasu had'ad'd'un kujeru masu shegen kyau da suka koma k'awata tsarin office d'in"bayan ta zauna ta fara k'ok'arin kashe wayarta sbd kar Aliyu yakirata.....sallamar Hjy zarah ta saka ta d'ago kanta suka had'a Ido da ita"haka kawai muslima taji tana jin zafin matar"saita d'an ya mutsa fuska tak'i Amsa sallamar tata ,saidai uban gayyar ne ya Amsa shima fuska bbu walwala beko kalletaba"tanata iyayi ta zauna tana fad'in yallab'ai sannu da hutawa Ina wuni?"da k'yar ya Amsa da lafiya! muslima kuwa ba k'aramin mamaki yabata ba"saidai hakan da yayi ya burgeta"Amma tana ganin ita tafi k'arfin yin iyayi ko rawar kai sbd d'a namiji koda shine Autan maza kuwa "dubi yadda yaketa wani shan k'amshi , Amma kallo bata isheshiba " sbd rashin zuciya sai iyayin banza takeyi"a fuska kamar zatayi Aji Amm....idan babu damuwa pls ko waccan zata iya fita zamuyi mgn daga baya ta dawo....muryar Hjy zarah ta katse mata tunani "wani murmushin rainin wayo muslima ta saki Akaro na farko da shigowarta office d'in "tun kafin dollars yayi mgn tace"babu inda zanje Anty"kiyi maganarki ko kuma ki fasa, idan yaya muslim d'in yafita kunyi Amma wlh bbu inda zanje"ta k'are maganar cikin tsiwa"kasa mgn zarah tayi sbd mamakin tsaurin idon yarinyar"Amma ranta yabata tunda ta kirashi da yaya k'ilan k'anwarsace"tama d'auka zai yiwa yarinyar mgn sai taga Akasin hakan saima k'ok'arin cire Agogonsa yakeyi sbd zaiyi Alwallah"sai satar kallon damtsan hannunsa me gargasan gashi jajir takeyi....idan bazaki fad'i meke tafe dakeba zaki iya tafiya"ba kuma lalle idan kinzo next time ba na saurareki sbd inada Abinyi.... murmushi kawai muslima tayi domin dama ta k'udurta Aranta yace" ta fita rashin kunya zata masa ta gudu ta hau nafef ta koma gidan Hjy"tasan dai duk masifarsa bazai je gaban Hjy yamata wani abuba....dama wata bewar Allah ce tana cikin matsala "yanzun haka tana a mota nazo da ita ,na barta ciki sbd nafara sanar maka matsalarta daga baya saina kirata kaga ciwon.....basai nagani ba! ki kirata naji me take buk'ata?"saidai zaku iya jira Awaje kafin na fito daga sallah"daga haka yaja bakinsa ya kulle"zarah na k'ok'arin mgn Manager nasa yashigo da sallama da wasu ledoji Ahannunsa "Aladabce yace"yallab'ai gashi"da hannu yanuna masa mutuniyar tasa datake zaune tana ta kumbure kumbure"har inda take yamatsa yamik'a mata ledar kafin yafita"Cikin taushin muryansa yadubeta yana fad'in zanje nayi sallah saura kimun wani shirme kuma na b'ata miki rai"yak'are maganar yana tafowa da nufin yafita"yayinda zarah ke zaune tana kallon su"muslima kuwa da gayya ta saki kukan shagwab'a tana fad'in waini yaya muslim yarinya ce ne da Abu kad'an sai kace wai zanyi shirme?"shareta yayi be tankatаba"zarah ta mik'e tsaye ta rigashi fita"shi kuwa fasa fitar yayi ya kalleta fuska Ad'aure yace"daga yau idan nayi bak'i kika koma tanka musu wlh saikin raina

kanki"wannan bata girmeki ba?"tana k'ok'arin mgn yaja tsaki yafita yana doka k'ofar da k'arfi "muslima ta tab'e baki tana fad'in saina tanka muddin yakama na tanka d'in"haka kawai kazo dani nan ka Ajiye ni "toni Ina zanyi tawama sallar ne ?"sai kuma tayi shiru ta bud'e ledar data Amsa"lemo ne da ruwa da take aways guda biyu"tana dubawa taga fried rice ce da kaza"babu b'ata lokaci tafara cin Abincinta Anutse.....bayan ta gama ta goge bakinta da tissue"tana duba time kusan mintina 12 da fitarsa be dawoba"tana wannan tunanin ya shigo"satar kallonsa tayi"Atake ta fahimci ransa Amugun b'ace yake"ko sallama beyiba"jikin bango ya matsa gefen wasu lakoki"yayi danne danne ta tsakkiya ta bud'e, yazaro rafar kud'i y'an 1k guda biyar"sai bayan ya rufe ya wuce gaban table d'in ya zauna yasaka su a leda"Ahaka wata mata ta turo k'ofar da sallama ta shigo"kallo d'aya zaka mata kasan tana jin jiki ga halin rashi"batare daya kalle taba yace "gashi Allah yasawak'a yabaki lafiya"Nagode Nagode!! Allah yasaka da Alkhairi yak'ara bud'i yajik'an iyaye"muslima ta Amsa da Ameen tana jin tausayin matar Aranta"ita kuma ta fita cikin farin ciki"dubu d'ari 3 take buk'ata Amma gashi da Alama sunfi Abinda take buk'atar.....har cikin ranta muslima taji dollars ya burgeta daya kasance me taimako dan Allah "idan kuma zaiyi taimakon zai baka Abinda bazaka iya mantawa dashi ba.....yaya Muslim"ta kirashi cikin narke murya"menene?"ya fad'a Azafafe kamar yana jiranta"ganin yadda yayi maganar sai tak'i tankashi tayi masa shiru"ki tashi driver ya maidaki gida"wane gidan kenan?"ban saniba"dama bayan gidan daddy Akwai wani gidan da kike?"haba yaya! koratafa yayi, kafa sani agabanka?....kinga bana son dogon zance sbd zan iya fusata ki tashi kije yana waje"daga haka yayi shiru"kuka ta fashe dashi ta gyara mayafinta ta d'auki wayarta.....K! Kinada hankali kuwa da zaki fita kina irin wannan kukan bayan Akwai mutane Awaje?miye kike zaton zasu fassara?"kin tankashi tayi ta fita"saidai tana fita ta nutsu ta goge hawayenta sbd itama bazata so Ayimasa wata mummunar fassaraba"musammun data fahimci Aduniya kowa nada masoya da mak'iya"ranta kuma yabata mutumin nan na d'azun (sadeeq) mak'iyin dollars ne"zuciyarta na zafi ta wuce parking lot d'in ta sami driver na jiranta ,bata masa mgn ba ta shige motar kawai"tana Mai jin tausayin kanta"yanzun haka zata cigaba da rayuwar rashin y'anci da k'unci Agidan mahaifinta??"tunda take bata tab'a jin tana son tayi Aure ba sai yau"fatanta Allah yabata mesonta da gaskiya cikin samarinta tayi Aure tabar gidan daddy kawai"Ada bata wani tunanin Aure sbd bata kula mazan dake cewa suna sonta.....tun daga fitowarta zuwa shigarta mota da yadda ta share hawayenta duk dollars ya gani ta laptop d'insa daya saita da CTV camera"shi kansa ya taursasa kansa yamata mgn ne"Amma yadda yakejin zuciyarsa bazai koma gidan yauba"yanzun ma sbd Abbie ne yakirashi da Abba,bayan yafito daga masallaci suka rarrashesa sukace ya maidota gida shiyasa yace driver yamaida ita"yana kallon kiran daddy yak'i d'auka sbd har yanzun zuciyarsa najin rad'ad'in Abinda ya musu shida muslima "ga wata sabuwar tsanar Hjy jamila da family nata dayakeji Aransa...

yana cikin wannan yanayin sadeeq ya shigo cikin office d'in da sallama yanemi waje ya zauna Ahankali yace "Abokinah naga da Alama kana cikin damuwa ko?"dukda wani lokacin baka cika bari Aji Abinda ya shafe kaba"komai naka saidai suraj ke sani.... sadeeq bana son yawan surutu idan ba wani abu ya kawokaba pls kaje kawai"ya fad'a batare daya kallesaba"danne zafin maganar dollars yayi Aransa kafin yace"dama Ina neman Alfarmar ka Aramun kud'i nera Millon 100 dan Allah "bayan sati 2 in sha Allah zan mayar maka"Akwai motocin dazan siya kuma Akwai Alkhairin danake zaton zan samu idan na siyesu"shiru dollars yayi yana nazari can yace"kaje zuwa safe idan zaka samu zan kiraka.... Anya zan iya jure

d'agawar guy d'in nan kuwa?"yafad'a cikin zuciyarsa yana jin tsananin zafin dollars da k'insa"yaso ya Amince yabashi yanzun zuwa gobema zai maido masa yace yafasa sbd boka yabashi tsafin da zaiyi idan ya Amshi kud'in"saiya maido masa, shi kuma daya sakasu cikin kud'ad'ensa zasu fara lalacewa daga nan yasamu karayar Arzik'i"Aganinsa idan dollars ya tsiyace zai rage masoya kuma zai dawo k'asa dashi.....motsin turo k'ofar da suraj yayi yashigo cikin office d'in yasaka sadeeq mik'ewa tsaye yana k'ak'aro murmushi yace"shikenan Abokinah Allah yakaimu goben"daga haka yabama suraj hannu sukayi musabuha kafin yafita...shiru na mintina 5 yaratsa bayan zaman suraj"ganin zaman kuramen ya ishesa yayi saurin cewa"yaka mata ka koyi manta damuwa da kuma danneta" karka manta daddy baya hayyacinsa yana a cikin sharrin Hjy jamila"so kamata yayi kasake ka nuna komai ya wuce kodan sbd taji haushi"itama muslima d'in naganta yanzun driver ya sauketa sai kuka takeyi....Ina ruwana da kukanta?"duk yadda kake zaton yarinyar nan ta wuce tunaninka suraj"ya katse suraj yana tab'e baki"uhmm uzuri zaka mata k'uruciya ce ke damunta"yaka mata ka dinga rarrashin....kallon daya jefasa dashi yasaka yakama dariya"kaga suraj idan kaima b'atan rai zakayi kaje na yafe ziyarar taka dan Allah "rashin kunya da fitsarar yarinyar nan yayi yawa"bata jin tsoron kowa"sanin kankane bazan lamunci raini ba ka kuma sani"hmm! kayi hak'uri zata dena, ni bammaga wata rashin kunya data ke makaba"idan ban maka shishshigi ba meke take da sadeeq?"saida yagama shan k'amshinsa sannan yayiwa suraj bayani yana tunanin meyasa tsakanin suraj da sadeeq kowa keson kawo zugar 'dan uwansa a wajensa??"musammun ma sadeeq ya fahimci yatsani suraj"nunawa kawai kebe yi....idan har zakaji tawa karka bashi Aron kud'i har million 100 "motar da yace"yana siyarwa k'arya ne rubace kawai sbd Ace yanada kud'i "duk wanda yace shine ba shi bane"nanma dollars shiru yayi sbd yasan gaskiya suraj yasanar masa"dan sadeeq Akwai ruba dason nuna shi yana dashi"kaga nifa dama nazone muyi mgn wlh inason husnah"na kuma rasa taya zan sanar mata wlh"kodai ka....karma kasaka ni cikin zancen ! kai nan har kaga Abinso wajenta?"shakkar ta kakeyi kome da bazaka iya sanar mata ba"?"kaga nidai taimakamun nazo kayi ko Ansami contact nata"yamutsa fuska dollars yayi yace"kafi kowa sanin halina bana son raini "sbd haka kaje ka nemi contact nata"pls muma dena zancen nata"to shikenan yayi kyau"daga haka suraj yatashi ya fita da Alama yaji haushin kalaman dollars"shi kuma be bar office d'inba sai bayan sallar isha'i "kai tsaye katafaren gidansa dake G R A yanufa"dukda ba'a gama gina gidan ba"sbd tsarin ginin gidan irin gidajen k'asashen waje ne"kusan 2yrs kenan ana gina gidan Amma har yanzun basu Ida gamawa ba"kasancewar yana Ajiye kayansa Acan"shiyasa be damuba yana isowa yanufi bath room yasakarma kansa shower! yajima yana wanka kusan mintina 25 yadauk'a a toilet d'in kafin yafito ya shirya cikin jallabiya Ash colour sabuwa dal"sai zuwa wani irin fitinannan k'amshi yakeyi"Cikin nutsuwa yafito farfajiyar gidan sbd zai fita shida driver da body quards nasa yad'an je wani eatery yaci Abinci"rabonsa da Abinci tun break fast"daga kawai ad'aukesa Amasa rakkiya"saida motoci guda ukku zuk'a zuk'a suka fita Atare dashi"ni kuwa nace shegiya nera🤭.... A b'angaren muslima kuwa har suka iso bugajes house's kuka takeyi"idanuwanta sun koma yin ja da kumburi"hakama lips nata"ga k'asan zuciyarta tana jin zafin dollars "suna gama parking ta fito tana lura da suraj na kallonta ta wuce sashen su Eyyah batare data gaida shiba"Eyyah ce kawai a parlourn "Anty habiba tuni sun tafi gida"Abbie ma baya gidan"daga Eyyah sai masu Aikinta su biyu dake cikin kitchen"muslima na ganinta taje ta fad'a jikinta tana sakin sabon kuka"kinga ya Isa haka takwara! "komai yakusan xuwa k'arshe in sha Allah zakiyi

rayuwa me dad'i"Ina babban mutum d'in yake?"ta turo baki tace"yana can Eyyah "ni babu ruwana dashi"sai yaita mun tsawa ko?"uhmm zai dena yaka mata kisan haka shi yake ko fira sai yana ra'ayi yakeyi"yanzun ki tashi kiyi wanka kici Abinci "ni banajin yunwa Eyyah yaya yasiyamun Abinci ko?"zan dai yi sallah ne da wankan "to tashi maza kije kiyi"nide Eyyah nan zan zaunah kawai bana son can sashensu daddy"ah ah "kindai dinga zuwa kamar haka kiyi zamanki ranar da bbu islamiya "Amma zamanki sashen mahaifinki shine daidai "ta haka jamilah zata san kema y'a ce"Amma dawowarki nan gaba d'aya zai saka taga taci nassara kuma ta Isa"shiru dai muslima tayi batace komai ba ta tashi ta wuce d'akin baccin Eyyah.....

da dare......✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

.......da dare bayan sallar isha'i muslima na zaune a parlourn Eyyah tana cin fara soyayya "sai lumshe Ido takeyi tana ci da Alama tayi mata dad'i sosai"tana sanye da rigar bacci da hijab iya gwiwar hannu Ajikinta "sai sanyayyan k'amshi ke tashi Ajikinta"yayinda Abbie ke zaune yana kallon news na k'arfe 8:00 pm"gabansa kayan marmarine A ajiye yana d'an ci"saidai Azahiri zaka d'auka hankalinsa na wajen TV Amma a bad'ini yana tunanin dollars"k'asan ransa kuma yana jin tausayin sa"domin yasan tabbas Ayau sai yaji rad'ad'in mutuwar mahaifinsa sbd Abinda yafaru d'azun"sarai yasan halinsa be iya fushiba,kuma yana jumawa kafin ya manta da Abu "da wuya yazo gidan yau saidai k'ilan gobe kuma next week yazo.... Assalamu Alaikum! Abbie yad'ago kansa yaga naseem ne"Amsa masa sallamar yayi"shi kuma yabi muslima da kallo saida ya zauna gefenta kafin yace "Anty muslima kizo inji daddy"dam ! K'irjinta ya buga da k'arfi ta kallesa dan neman k'arin bayani....tashi maza ki canza hijab kuje"cewar Abbie fuskarsa bbu Alamar wasa"hakan yasa muslima kasa yi masa musu ,saidai idanuwanta har sun ciko da k'wallah "tana tunanin muddin wani wulak'anci za'a koma yimata wlh gobe guduwa zatayi gidan Hjy...jeka gata nan zuwa "dato Naseem ya Amsa yafita daga cikin parlourn"Abbie ya kalleta da kulawa yace"karki damu kinjiko? in sha Allah kiran naki Alkhairi ne"tashi maza kije "batace komai ba ta mik'e tsaye ta nufi d'akin Eyyah"babu jumawa suka fito Atare da Eyyah,ita Muslima

ta fita, yayinda Eyyah ta zauna gefen Abbie.....gaba d'aya su 5 d'in zaune suke cikin parlourn "Naseem ,Malika,kabeer duk suna zaune kan carpet"yayinda daddy da mommy ke zaune kan kujerah "bacin fad'uwa bbu Abinda gaban Hjy jamila keyi"gaba d'aya kanta ya k'ulle"gashi bbu fuskar ta tambayi daddy wani Abu"sbd tunda tadawo gidan gab da magrib yayi biris da ita"ko d'aukar tatama driver yatura shibe jeba"gashi kuma da magrib ya sanar da ita da Angama isha'i su taru itada yaranta yana son mgn dasu"taso tace taron me za'a yi? Amma sai taga bbu fuska"bata shiga damuwaba saida taga yatura Naseem yakirawo muslima"Anan ta fara d'aukar hannu game da cewa Ad'azun ta Ajiye Abinda takeyi ta tafi gida"gashi kuma d'azun da driver ya sauketa ta fito ta had'u da Abbie zai tafi masallaci ta gaidashi k'ememe tsohon yayi kamar bejiba,yanuna bemasan da itaba ya wuce Abinsa..... sallamar muslima data shigo parlourn cikin dakiya yasaka Hjy jamila koma jin fad'uwar gaba "Malika kuwa tsabar yadda takejin zafinta ko kallonta bata yiba"saidai daddy da naseem ne kawai suka Amsa sallamarta"daga gefe ta nemi waje ta zauna kanta Ak'asa ta daure tana fad'in daddy ina wuni?"lafiya qlau mama nah! gaba d'aya duk sukabi daddy da kallo har ita kanta muslima d'in "gyaran murya daddy yyi yace suyi salati 11 ga Annabi mohd S A W"bayan sun gama yafara da cewa"hak'ik'a banji dad'in Abinda yafaru d'azun ba"kun sanarmun Abinda kuka ga dama bayan Abin ba haka bane"ni kuma nayi kuskuran yanke hukunci babu bincike,muslima da kuke gani itama y'atace kamar ku"daku da ita duk matsayinku guda A wajena ,babu wanda yafi wani"sbd haka daga yau na haramta wani cikinku ya hanata iko da Abinda ke nan gidan"tazo zata sha ruwa ke Malika sbd bakida mutunci da tarbiya kika dinga zagin mahaifiyarta da hanata ta tab'a fridge sbd kece kika siya ko?"Amma Alh fis....kar in koma mgn ki samun baki"yafad'a fuskarsa Ad'aure "gaban Hjy jamila na fad'uwa tayi shiru tana mamakin meyasa komai ya sauya?...kai kuma dayake wawane kai bayan Malika ta mareta sun fara dambe shine saika shigarma Malika kadinga dukan muslima"ganin my friend ya shigo baka fasa ba ko? To daga yau komai tayi maka kafara sanar dani kafin ka yanke hukunci"Abinda muslim yayi maka yayi daidai"zumunci Abune me kyau wanda ya yankesa babu shi bbu rahamar ubangiji"wanda kuma yasadar dashi yanada d'umbin lada"muslima ki sake ki wala kiyi komai kikeso dabai taka shari'a ba nan gidan kune kina jina?" In sha Allah daddy"ta fad'a cikin jin dad'i"yayinda Malika da kabeer sukayi tsit zuciyoyinsu na tafasa"yayinda Naseem yaji dad'in wannan taro.....kabeer da Malika yayunkine ki basu girmansu banda rashin kunya "idan wani cikinsu ya miki ba daidaiba ki sanar mun"kai Naseem dama nasan bakada matsala"duka su ukkun yayunkane karka ware wani Acikinsu duk matsayinsu guda"Naseem na k'ok'arin yin mgn siyama ta shigo cikin parlourn Aguje ta fad'a jikinsa tana fad'in yaya Naseem shine bakazo munci Abinci ba inata jiranka ko?"saida yaji fad'uwar gaba yad'ago kansa ya saci kallon Hjy jamila"Aikuwa yaga tana jifar su da wani irin mugun kallo"kasa yima siyama mgn yayi"domin dai ta tona masa Asiri"mommy ta hanashi zuwa sashensu Amma da dare saiya sace jiki yatafi suyi dinner sannan yadawo d'akinsa ya kwanta"Abba ya kallesu sbd dama yasan sun shak'u da juna yace"Auta nah zomu gaisa kinjiko?"nide daddy ba yaya Naseem nazo kiraba zamuci Abinci"tashi ka bita kuje mana"yafad'a yana kallonsa saiya lura da yadda yake satar kallon gefen da uwar tasa take zaune"Aikuwa ya kalleta yaga yadda take hararar siyama"saidai tana juyowa suka had'a Ido da daddyn"sai tayi saurin kama kanta"daddy ya girgiza kansa ya mik'e tsaye yace"na sallami kowa"da sauri naseem ya d'auki siyama suka fita"yayinda muslima ta nufi d'akinta "Hjy jamila da y'an gaban goshinta basu tashiba"sai bayan kowa yatafi ,Malika ta d'ago kanta tana kukan b'akin ciki tace"meye mafitah yanzun mommy?"ki duba kiga yadda

komai yacab'e"ga yadda yaya muslim yadamu da shegiyar yarinyar nan karfa wani abu yafaru"murmushi Hjy jamila tayi me ciwo kafin tace"kima dena tunanin hakan niface jamilah"duk wanda yashiga gonata zan nuna masa iyakarsa"shi kansa daddyn naku na barsa ne sbd wasu dalilai Amma nasan tabbas tsohonsa ya zugashi"batun Muslim da wannan y'ar iskar yarinyar ki barshi a hannuna"karku sake wani Abu marar dad'i yakoma faruwa saidai babu ruwanku da ita....to mommy nimafa Akwai tawa matsalar sbd Ina son husnah wlh"cewar kabeer yana d'an murmushi"d'an jim mommy tayi sai kuma tayi murmushi tace "ba damuwa zan iya barinka ka Aureta kodan sbd dalilai guda biyu,na farko ubanta nadashi, tayi boko ,kuma ta waye"sai Abu na gaba inaso na wanke tsanar da habiba tamun Aranta ta sanadin soyayyar ku da ita"saidai bana son kasaka ran dole zaka sameta"idan ta k'iya Akwai wasu y'ay'an masu dashi daidai dakai"wad'anda suka fita komai"Amma yanzun dai musamu muslim ya Auri Malika tukum....kabeer bece komai Aransa yasha Alwashin zai nemi soyayyar husnah kawai....Afannin muslima taji dad'in wannan taro Aranta "ta kuma k'udurta bawa kowa girmansa Agidan cikin mutunci"Amma bazata d'auki raini ga kowa ba"sai bayan ta gama shirin kwanciya bacci tayi cin karo da text message na Aliyu "tana kuma hawa online nanma taga sak'onsa "murmushi kawai tayi domin dai kalaman soyayya ne irin na nuna kulawa ga mutum da sauransu"haka kawai taga kamar bata kyautama Aliyu ba na rashin kulashi da bata sonyi "hakan yasa ta daure ta masa reply d'in sak'onsa sannan ta kwanta bacci.....washe gari yakama sunday "tun wajen 8 am muslima tayi wankanta ta shirya cikin Abaya sabuwa da Eyyah ta bata maroon calour"ba k'aramin kyau tayiba"Anan tsakkiyar parlourn ta zauna tayi break fast"Agaban kowa taje ta d'ebi Abinda ranta keso"bayan ta gama ta nufi parlourn daddy sbd ta gaidashi "yana zaune yayi tagumi da Alama tunani yakeyi ta shigo"har k'asa ta duk'a ta gaidashi"ya Amsa da kulawa yana tambayarta ko Akwai Abinda take buk'ata??tana k'ok'arin bashi Amsa daddad'an k'amshin uban gayyar yafara kama hancinta ziyara"kafin kunnanta yaji mata Amon sautin nutsatstsiyar muryansa yana yin sallama"yayi matuk'ar kyau cikin shadda ash color data wadatu da jik'kak'en d'inki me kyau irin na zamani"wanda yafito da baiwar kyawun surar da ALLAH yayi masa"da gani basai An fad'aba, maik'onta kawai ya isa Amsa ga mai hasashen kud'inta"ya Aza hula k'ube datayi daidai da colour d'in zaren da Akayi Aikin shaddar"hakama takalmi da Agogo......su oh oh yau Antuna Al'ada kenan An Ajiye dabi'ar nasarah"ta fad'a cikin ranta tana d'aure fuska"shi kuma kallo d'aya yamata ya d'auke kansa yaduk'a ya gaisheda da daddy"my friend lafiya qlau da fatan ka huce bisa laifin danayi?"babu komai daddy ya wuce"to Masha Allah! yau zaka koma American ne?"Eh Amma saida yamma"yanzun haka munada meeting da governor da k'arfe 12 na safe......koda naji shiyasa yasaka manyan kaya"nifa tunda nake ban tab'a ganin yasaka manyan kaya ba.....mamanah bakiga yayankiba?"muryar daddy ta katse mata tunaninta"munfa gaisa dashi daddy a sashen Eyyah kafin nazo nan"ta k'are maganar tana mik'ewa tsaye ta fita"yayinda dollars ke saurаren k'aryar da muslima ta jero bedai tankaba sbd yasan jiya haushinsa takeji ya tursasata tadawo gidan"saidai shi kuma Aransa yatanadi irin muguntar dazai mata"shida yana shigowa gidan nan yafara yowa bemaje sashen su Eyyah ba"daddy bara natafi naga 9 am ta kusa"to shikenan my friend Allah yabada sa'a yayi muku Albarka "ya Amsa da Ameen yatashi yafita Aransa yana jin dad'in yadda yasamu daddyn shida muslima "yaga kuma tsanarta ta rage aran daddyn"yasan kuma hakan na daga cikin Aikin Abbie"wani irin tsananin k'aunar tsohon yaji ta k'aru Aransa"sakkowa yayi down stairs d'in ya lura da mommy da Malika"kallo basu isheshiba yafita"dan ko gaisuwar yauma yaji bazai iya

yiwa Hjy jamila ba.....tun kafin ya shigo cikin parlourn yafara jiyo surutun muryar muslima da dariyarta tana fad'in Allah nasan Eyyah yayi dad'i "kin kyauta da kika Ajiye mun baki bama Abbie yacinyeba.....shiru tayi sbd jin sallamar dollars"ya zauna kan kujerah fuskarsa bbu walwala ya gaida Eyyah "ta Amsa da kulawa tana fad'in ga Abin break fast can babban mutum"beyi mgn ba sai satar kallon bowl d'in gaban muslima dake cike da yam balls har guda 7 yayi"Adaidai lokacin kuma Eyyah ta mik'e tsaye"Akamun komai Anan zanci"yafad'a Anutse yana danna waya"to shikenan muslima tashi ki kamasa duk Abinda zai buk'ata Anan"badan tasoba ta tashi tana b'ata rai ta wuce"shi kuma yasaki murmushin mugunta yana Ajiye ledar daya shigo da ita kan kujerah ya d'auki bowl d'in yafita daga cikin parlourn "yayinda Eyyah ta nufi kitchen"muslima bata lura da babu bowl d'in ba saida ta gama shirya masa komai tanata gulmarsa Aranta sannan ta nufi inda Abinta yake da nufin ta d'auka saita bar masa parlourn gaba d'aya Anan taga wayam"ta d'an zaro Ido da mamaki tana waige waige Adaidai lokacin kuma dollars ya shigo da sallama can ciki"bata Amsaba sai binsa da kallo tayi"Aikuwa taga bowl d'in a hannunsa gashi yayi bala'in had'e rai"zama yayi yajawo center table d'in gabansa "kukan b'akin ciki ta saki tana fad'in meyasa zaka d'auka mun Abuna yaya Muslim??"banza yamata yafara k'ok'arin zuba kunun gyad'a cikin cup"Eyyah ! Eyyah!!!... kinsan Allah ?idan kika kirata kika sanar mata da wani Abu kukan da zakiyi sai yafi wannan dakike kan yi"Ayanzun Aikin tankamun koda badan Allah ba"d'azun kin gama yiwa daddyn k'aryar ne?"ko kuwa dama na fad'a miki Ina buk'atar ita gaisuwar taki ne?"ni wlh ban yafeba! me kikace?"yafad'a yana zaro mata fararen manyan idanuwansa" yawani sha mur"ba k'aramin kwarjini taji yama taba musammun yadda ya zaburo yana mata mgn cikin zare ido"saita kauda kanta tana fad'in nifa bada kai nakeba"shareta yayi yafara break fast nashi"tanata sharb'an kuka ta wuce zata shiga d'akin Eyyah "zoki Amsa"yafad'a kamar bashine yayi maganar ba"tama d'auka ko yam balls nata zai bata tana juyowa sai taga yana nuna mata wata leda bak'a da hannu"turo baki tayi tak'i matsawa ta d'auka"Da k'yar ya iya gimtse murmushin da ke son kufce masa ya harareta murya babu Alamar wasa yace "*halimatu* zonan! wani iri taji ,ta rasa meyasa baya kiranta da muslima sai Ainahin sunanta?"Anan ma k'in tankashi tayi saidai kawai tazo gabansa gefen k'afafuwansa ta duk'a still tana hawaye"ke kuka baya miki wahala ne?"ki goge hawayen zan siya miki wani"cikin shagwab'a tace"nidai ba wanda Eyyah tayiba nakeso shine ka Amshe ko?"ke kika sani"ki d'auki waccan ledar yunifoam ne Aciki kije ki canza "mintina 5 na baki ki fito zamu sauke ki a islamiyar....nifa yaya Muslim Inada islamiyar danake zuwa jiya da yaune kawai banjeba "kuma next week zanjefa"duk tana maganar ne kanta Ak'asa sbd bata iya kallon k'wayar idonsa ta masa musu ko tsiwa....na fahimci kinfi buk'atar koda yaushe kita yin kuka ko?"tayi shiru "baraki tafiba ki saka?"bana son waccan islamiyar wannan ita nagadamar maidaki ki hana idan zaki iya"bata samu damar yin mgn ba suraj ya shigo cikin parlourn"ledar kawai ta d'auka tana kuka ta nufi d'akin Eyyah"suraj kuwa fuskarsa Ad'aure ya zauna dama ya shigo su gaisa da Eyyah ne"bemayi zaton zai samu dollars Anan ba"saidai ya d'auke masa kai kamarma be ganshiba"yana tunanin meyasa yake yawan takura muslima da sakata kuka??.....suna zaune kusan mintina biyu babu me mgn"can dollars yatab'e baki yana Ajiye cup d'in hannunsa yace"uhmmm ! sbd kana son fara soyayya nak'i baka goyon baya shine kake fushi?"kaga mlm ka dena dawo da Abinda ya wuce"idan baka taimakamun na sametaba fasa rayuwa zanyi ne?"Ina Mai tabbatar maka da cewa in sha Allah itace maman yarana"kai kuma kana nan zaune ka Ida tuzurancewa....sai kuma yakama b'abb'aka dariya"Adaidai lokacin Eyyah da muslima

suka fito daga cikin d'akin baccin Eyyan" ba k'aramin kyau yunifoam d'in suka mataba"kalar coffee brown "hijab d'in d'inkin jalbab" idanuwanta sunyi jajir sbd kukan datasha da Alama data shiga d'akin Eyyah ta rarrasheta"harara Eyyah ta sakar masa"shi kuwa murmushin gefen baki yasaki yana yiwa suraj Alamar zasu had'u dashi ne"kuje ta kwara kinji?"kai kuma babban mutum zaka dawo kasameni"k'in tanka Eyyah yayi ya fice cikin k'asaita yanufi parking lot "kan idon muslima data biyosa ta hango body quards nasa sun bud'e masa back sit"sai rissina masa sukeyi"ta girgiza kanta tana fad'in duk dan sbd yanada kud'i"shi kuwa yadake yanata wani shan k'amshi kasancewar sa gwani wajen jin kai"d'an juyowa yayi suka had'a Ido da ita"yasakar mata harara"Aikuwa ta murgud'a masa d'an bakinta dan dama haushinsa takeji"ta rasa meyasa ikonsa yayi yawa Akanta?"meyasa baya takura Malika sai ita?"ta tabbatar Malika bata zuwa ita islamiyar ma gaba d'aya"tana wannan tunanin ta iso ta shiga back sit ta zauna nesa dashi"taci gaba da danne danne Awaya ga jakarta da littattafai na Addini a hannunta"ta nuna kamar batasan da zamansa a motar ba.....tayi mamakin motoci har hud'u dake binsa Abaya kamar wani governor ko wani shugaba"bata gama mamaki ba saida suka iso islamiyar tasu taga yadda Malaman ke masa mgn cikin ladabi suna rawar jiki"girgiza kanta kawai tayi sbd haushi taji sun bata"musammun sbd badan Allah suke hakanba sai dan sbd kud'i"saida Akayi komai ,har Aji an bata sannan dollars yayi tafiyarsa batare data samu Arzik'in yamata mgn ba"to itama bata buk'atar maganar tasa taci gaba da Aikin gabanta....sai wajen k'arfe 12 daidai aka tashi"tana fitowa ta sami driver zaune yana jiran fitowarta"cike da ladabi ya matso yana fad'in ranki yadad'e dama yallab'ai yace nazo na d'aukeki "dato ta Amsa ta bud'e back sit ta shiga"bayan sun hau saman hanya taga ba hanyar gida sukayiba sunmayi hanyar gidan gwabnati"da mamaki tace Ina zamuje ne?"dama ogah yace idan na d'akkoki na kaiki can kisamesa"kaga nifa bbu inda zanje kamaidani gida mana"dan Allah ki rufan Asiri wlh k'in zuwanki zai jawo na rasa Aiki nah gaba d'aya "yafad'a kamar zaiyi kuka.....✍️

Wannan book d'in na kudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar mun Allah ya isa banyafe miki ba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

..........ba k'aramin tausayi muslima taji mutumin yaba taba"tasan halin dollars tabbas zai iya

korarsa musammun idan yana Azuciye"saidai ta rasa miye ribarsa idan ya k'untata mata?"bata mantaba yau saida yasakata kuka da safe"Ayanzun kuma baza tayi kukan takaicin saba saidai itama ta k'unsa masa wani takaicin irin yadda yamata da safe....babu damuwa muje inda yace d'in"ta fad'a batare data kallesaba"godiya nake ranki yadad'e "batace komai ba tana tunanin meyasa wai Aliyu yana sonta yakasa fitowa fili yasanar mata?"kullum saidai yadameta da zafin kira da turo mata messages"sai taji dama bata bashi contact nataba"tana wannan tunanin suka iso cikin haraban gidan gwabnatin"ko Ina securities ne tsaitsaye suna gadi"bayan ya gama parking yakira dollars ta waya Amma be d'auka ba"hakan yasa ya juyo ya kalleta yace saidai mu jira tukum"na kirashi be d'auka ba"nasan zai kira"k'in mgn tayi ta bud'e k'ofar motar ta fito ta jingina bayanta Ajiki tana y'an kalle kalle"Aranta tace dama haka gidan gwabnatin yake?...tana wannan tunanin kiran Aliyu ya shigo cikin wayarta hakan yasa ta d'auka suka cigaba da mgn"kusan mintina 15 tana waya Amma bbu Alamar dollars "bayan ta gama wayar ta dinga jan tsaki sbd takaicin tsaidasun da yayi"kamar Ance ta d'ago kanta"Ido kawai ta tsurama dollars tun daga nesa"yana daga  gaba mutanan sa na biye dashi tamkar shine governor d'in"ga wani haskawa da kwarjini da yayi" ya wani k'ara tamke fuska tamkar wani basarake haka yake tafiyar cikin k'asaita da d'agawa"gama meeting d'in nasu kenan "governor yabama gidajen man fetur d'in dake garin tallafi"dollars kuwa Anan bayan Angama meeting d'in yarabama mutum 10 kyautar Millon 100 da aka basu na tallafin"sosai darajarsa ta k'aru ga mutane"dukda shi dan Allah yayi Amma wasu naganin sbd Riya yayi"hakan yasa y'an jarida suka masa caaa dazai fito"shi kuma ya musu banza yayi gaba Abinsa..... d'auke kanta daga barin kallonsa muslima tayi"saidai tana ganin naci da rashin zuciya irin na y'an jaridar"tunda yak'i kulasu miye Amfanin su dinga binsa yana yarfasu?"sarai dollars ya ganta Amma kallo bata isheshiba yabi ta gabansu ya wuce"mutane na biye dashi"yawanci duk masoyansa ne da body quards nasa"befi mintina 2 da wucewa ba taji driver d'in na waya dashi ,bayan ya gama wayar ya kalleta Ad'arare sbd ganin yadda ta had'a rai "ranki yadad'e yallab'ai yace kije wajen wa'ancan motocin zaku tafi"ka kirashi kace masa bazan jeba"ta fad'a cikin yamutsa fuska tana kauda kanta"dan Allah kiyi hakuri wlh bazan iya gaya masa haka ba"kinga lokaci na tafiya kuma beson Ab'ata masa lokaci"k'in mgn tayi ta gyara hijab nata kawai ta nufi bakin get"zuciyarta Adake sbd yabata haushi daya wuce ta gabanta yanuna kamar besan da zaman suba"bayan bisa tursasawarsa ta yadda tazo nan....sosai securities d'in dake bakin get suketa kallonta da mamakin taya ta shigo harma zata fita Anan tana mace?"tana gab da  ida fita daga cikin get d'in taji k'arar motocin dollars Abayanta"k'in juyawa tayi"tana k'ok'arin tafiya taga mota guda ta tsaya gabanta.... k'irjinta yabuga dataji motsin bud'e k'ofar"Atake taji k'amshin mutumin nata"kafin tayi wani Abu Akai taji An fisgi hannunta"ta juyo ta saki k'ara tana fad'in ni kacikamun hannuna"Akan me zan je kiranka bayan ka ganni ka wuce kamar baka sanniba?"kawai saina kwashi jiki na bika sbd ga sarkin shush ko? Ada ba k'aramin haushin k'in zuwan nata da tafiyarta yajiba"Amma wa'annan kalaman nata sun saka tama bashi dariya"wato taji haushin yanuna kamar besan taba"ya lura ba k'aramin jan Aji garetaba"Amma Afili saiya koma had'e rai yaturata cikin motar da k'arfi"ba tare daya damu da masu kallonsuba"Ada taso ta masa kuka Amma saita dake ta zauna tak'i yadda tako kalli gefen dayake zaune"saidai tasha Alwashin masifa zata masa koda zai daketa"saidai bazata masa A gaban yaran saba"sai turo baki takeyi tana mgn k'asa k'asa "duk yadda dollars yakeda yawan jin mgn komai k'ank'ancin sautin murya"Amma yanzun baiji me take fad'a ba"sai satar kallonta yakeyi yana kuma danna waya"basufi mintina 10 ba suka iso

wata had'ad'd'iyar private hospital"ita muslima batama san Asibiti suka zoba saida suka shigo cikin haraban Asibitin"sai tadinga mamakin meyasa zasu zo Asibiti koshi muslim d'inne beda lafiya?"tana wannan tunanin aka gama parking driver yafita da sauri"kan idonta Aka bud'e masa k'ofar back sit"be fitaba sai Ido daya zuba mata "tayi saurin yin k'asa da kanta"meye kikeson fad'a?"tunda gulmar da kikeyi Azuciya ta kasa b'oyuwa kina fiki fiki da baki...nide dan Allah idan kana yiwa Allah kasaka Amaidani gida"ni wlh garama ka koma America d'in....ta fad'a k'asa k'asa yadda bazai iya jiba"saidai sarai duk yana jinta"saima tamke fuska yayi yace"fita muje"Ina ke nan?"ban saniba"wai dan Allah yaya muslim ni meyasa bakamun Adalci"kabi ka tsaneni ?? sai kuma ta fashe da kuka"kinga kimun shiru  kona mareki"ke meyasa bakyajin mgn ta kin rainani ko sa'ankine ni?to mijin ummah zaki fito muje ki gaidashi da jiki"yana fad'in hakan yafito daga cikin motar"saida ta goge hawayenta sannan ta fito"shine daga gaba yaransa na biye dashi da kaya nik'i nik'i Ahannunsu"tunda suka shigo Ake kallonsu har suka iso Amenity room 8"saidai be shigaba yaransa ne suka fara shiga"ya juyo ya kalli mutuniyar tasa "sai faman cin magani takeyi Abu kad'an take jira ta b'are Baki tayi kuka"saidai ganin yayi tsaye yak'i shiga yasaka ta kallesa suka had'a Ido "saurin sunkuyyar da kanta tayi tana jin fad'uwar gaba"sbd wannan kallon daya jefeta dashi ta kasa gane ma'anarsa.....yaya muslim ka shiga mana"da sauri muslima ta d'ago kanta sbd jin muryar Amatallahi da tayi"Atare suka sakarma juna harara duk dollars na lura dasu...hmmm!Aikin banza, ta wace hanya yazama yayanki ? Inba kalan dangi ba"kince nayi shishshigi last time ke yanzun me kikayi?"duk muslima ta fad'a cikin masifa"Amatallahi taja tsaki tana fad'in banida lokacinki"ta k'are maganar zata wuce ta gabanta"Aikuwa muslima ta kara mata k'afarta"tayi taga taga zata fad'i "tayi saurin fincikota tana fad'in kin Isa kimun tsaki....hannunta kawai dollars ya fisge fuskarsa Ad'aure"ta saki k'ara tana fad'in ita wlh ya k'yaleta saita rama"shi mamaki ma tabashi"ya lura yarinyar nan ba k'aramin fad'ane da itaba bata barin saita kwana"hancinta yaja da k'arfi yajata suka nufi cikin d'akin"saidai yana shiga yacika hannunta sbd tuna ko umma tana ciki"ita kuwa taso yak'yaleta ta lallasa Amatallahi"ummah da Mamy (uwargidan ummah) suna zaune kan carpet dake shimfid'e Ak'asa"sai Abban na kwance saman bed yana bacci "kallo d'aya zaka masa kasan yana jin jiki"danma yana daurewa"Mamy ta Amsa sallamarsu"Atare suka duk'a suka gaidasu"muslima ta musu ya mai jiki kafin ta saci kallonsa taga ita yake kallo"Amma suna had'a Ido ya zabga mata harara ya d'auke kansa "Abban bacci yakeyi ne?"Eh k'ilan sai zuwa k'arfe 2 ya farka"munata ganin hidima Alh Muslim Allah yasaka da Alkhairi"bece komai ba saidai ummah ta Amsa "Aranta tana tambayar kanta meyasa duk inda zashi yake yawo da yarinyar nan?"mik'ewarsa tsaye yana fad'in umma zamu wuce yasaka ta kallesa tana tasowa suka fito daga cikin d'akin gaba d'aya "saidai ita muslima daga baya ta tsaya su kuma sukayi gaba"ba k'aramin sanyi jikinta yayiba sbd Alamomi sun nuna matar bata sonta....ke! k'aramar marar kunya kingama kurarin d'azun ne sbd kin ganshi?"taji muryar Amatallahi"yamutsa fuska tayi ta kalleta tace"uhmm! ke kuma sbd kin ganshi kin kasa mgn sai bayan idonsa sbd yace kinada hak'uri ko?"cewar muslima tana zaro Ido"Adaidai lokacin kuma ta hango ummah na nufo inda suke"hakan yasa kawai tayi gaba batare data koma bi takan Amatallahi ba"sbd ta fahimci sun gama mgn"tana wannan tunanin shima ta hangosa tsaye da Alama jiranta yakeyi"rab'awa gefen umman tayi ta wuce bbu wanda yakula wani cikinsu"tana isowa murya bbu Alamar wasa yace"na lura idan ba belt nasaka nafara zane miki jiki dashiba bazaki nutsu ki dena shirmeba"Ina ruwanki da ita da zaki tak'aleta da fitina?"shiru tayi tak'i mgn kawai tayi dai k'asa

da kanta"yaja tsaki ya wuce ta biyosa Abaya"koda suka shigo cikin motar k'in mgn tayi har suka iso wata super market ta musammun"Anan ma beyi mgn ba suka fito"Atare da ita suka shiga ciki"kai tsaye wajen ma'aikatan wurin yaje yanunata yace"zata zab'i komai takeso"shi kuma yafita Abinsa "da farko taso ta k'iya "Amma kuma sai kawai ta shiga jidar komai da gayya "kuma masu tsadar gaske take d'auka "dama gata gwana wajen shan zak'i"chacoolates, biscuits,stwwets, chewing gum,big booms,lemuka na gwangwani dasu madarori na gari dana ruwa"jidarsu kawai takeyi kamar hauka"ta d'ibi nata ta d'ibi na Naseem ,ta d'ibi na siyama"sannan ta d'auki bama roba biyu manya wai Eyyah ta d'aukar mawa"su kansu ma'aikatan mamakin irin yadda ta dinga jidar kayan sukeyi, tana lodawa saman wasu baskets tana turawa"wad'anda suka cika saita barsu ta wuce"basket ukku tayi"kowane tace su zuba A leda"ta saka Aka lik'a sunan naseem Ajikin babbar ledar kayan shopping nasa"hakama siyama"nata kuma ba'a sakaba"kayan shopping nata leda biyu ne"ga k'atuwar Teddy data d'auka wacce zatayi kusan 20k"sai murmushi takeyi domin tasan dai dole ransa yab'aci"kuma dole yabiya kodan sbd kar yaji kunya yana matsayin mai dukiya"suna k'ok'arin tafiya su sanar masa ya iso wajen da ATM card a hannunsa"Anan ya lura da ledojin da sunan dake a jiki"yakuma kalli yadda taketa fara'a"Atake ya fahimci me take nufi"shi kuwa murmushin gefen baki yasaki sbd ya shirya meye zai mata"yana tsaye aka zare dubu dariya biyar da ishirin harda biyar"body quards nasa suka shigo suka dinga jidar kayan suna fita"ita kuwa daga jakarta da teddy d'inta ne kawai Ahannunta ta fito.....wajen dawowar ma zaman kurame sukayi sbd ko kallonsa batayiba"lokacin kuma Anata kiran sallar magrib"bayan sun gama parking ta fito har zatayi gaba ya tsaida ita"ta hanyar cewa wait! batace komai ba ta tsaya"da kansa yamatsa jikin boot yasaka aka fito mata da ledojin kayan shopping d'inta "sai kuma taga An rufe boot d'in"da mamaki ta waiga ta kallesa cikin shagwab'a tace"sauran ledojin biyu fa?"tab'e baki yayi tare da fad'in sadakar su za'a yi"suma wa'annan daddy ne yabada kud'i Amiki"shine sbd iyayi da gulma zakiyiwa wasu shopping d'in sbd niga me kud'in banza na biya ko?"to ba'a tursasani"idan kina ganin kinyi hakan sbd dai Agaban mutane dole na biya ,to nabiya Amma bazan bayarba....to nima bana son nawa d'in ka had'a ka bayar"ta k'are maganar tana barin wajen da sauri"ya girgiza kansa kawai yasaka aka bita da kayan"sai Akayi sa'a sashen daddy ta nufa"tana k'ok'arin bud'e k'ofar d'akinta d'an Aiken yashigo da ledoji guda biyu "Hjy jamila dake hakimce saman kujerah tace"kai Ina zakaje da ledoji?"Hjy na muslima ne "ke wayabaki kaya haka?"daddy ne yamun shopping"Malika ta kalli uwar, ta kuma kalli kayan"saidai basuce komai ba har mutumin ya Ajiye kayan yafita"ba k'aramin hayayyak'a zuciyar Hjy jamila tayiba"saidai tabari daddy yadawo suyi wacce zasuyi"idan yace matsayin muslima da yaran guda meyasa zaiyi son kai ita yasiya mata abu bayan ga naseem da malika?"tana wannan tunanin Naseem ya shigo da Alama daga masallaci yake"wayarsa yajona chargy kafin ya zauna yana lura daga uwar tasa har malikar sunada damuwa"saidai yasan damuwar tasu bata rasa Alak'a da muslima"yana wannan tunanin siyama ta shigo cikin parlourn tana fad'in yaya naseem kazo inji yaya.....in kika sake kika hau masa jiki saina kakkaryaki"y'ar iskar yarinya kina neman b'atamun yaro"Abu kad'an k'atuwa dake saiki haye samansa"zaki wuce ko sainaci ubanki....haba mommy dan....rufemin baki mutumin banza! dama jiranka nakeyi"wato bazaka fita hanyar mutanan canba, bayan suna mak'iyana ko?"yayi shiru yana kallo siyama ta fita tana kuka"tashi tsaye yayi"Ina zakaje?"cup zan d'auka ruwa zansha"daga haka yanufi kitchen"ta k'ofar baya yafita da gudu yabi bayan siyama"sai Akayi sa'a yayi cin karo da ita Ahanya"saidai kawai taji yayi sama

da ita yana murmushi yace"kinga ki dena kuka karki sanarwa ummi komai"tak'i mgn ta turo baki "kinaso ummi kema ta hanaki zuwa guna?"saita girgiza kanta"shikenan karki sanar mata"yanzun waye ke kirana?"ba yaya Muslim bane"kuma yace"muje wajensa yana d'akinsa hardani"bece komai ba yana d'auke da ita suka nufi side d'in dollars.....muslima kuwa sbd kawai ta bama su mommy haushi yasaka ta Amshi kayan"Amma bayan wannan dalilin da bazata Amsa ba"tana shiga d'akin ta cire kaya tayi wanka da sallar Azahar "bayan ta shirya cikin riga da siket na Atamfa me golden  ta fito babban parlourn gidan sbd taci Abinci"kabeer da  Malika na zaune a dining area d'in"Ahankali ta musu sallama saidai bbu wanda ya Amsa mata"Malika ma sa tsaki taja tabar wajen"muslima bata damuba ta d'ibi Abinda take buk'ata ta koma d'akinta ta zauna tafara ci.....wajen k'arfe 2:30 daddy ya shigo cikin parlourn "da Alama lunch yadawo yayi"mommy na zaune cike da takaici biyu na daddy dana shigar da Naseem yayi kitchen be dawoba"hakan yanuna mata ta k'ofar baya yabi dake kitchen d'in yatafi wajen siyama"da k'yar ta Amsa sallamar daddy ko sannu da zuwa bata masaba"yayinda itama Malika ta d'aure fuska ko kallo mahaifin nata be ishetaba sbd tana jin zafinsa yayiwa muslima shopping ita banda ita"sosai daddy yayi mamakin Hjy jamila da yadda ta nuna ko inkula da dawowarsa"dama yasan idan tana fushi dashi ko tana son yamata wani Abu yak'i yi to zata dinga yimasa irin haka"sai kawai shima ya shareta ya wuce samansa"da hanzari ta tashi ta biyosa"ta samesa yana k'ok'arin zare rigar shaddar jikinsa"gefen bed ta zauna tana cika tana batsewa duk yana lura be tankataba" Alh yanzun sbd Allah Abinda kayi shine Adalci?"kayiwa muslima shopping bayan ga Malika da Naseem baka musuba"bayan kaika haifesu "Amma shine zakayi son kai.....shiyasa kenan da k'yar kika Amsa mun sallamata? "ita kuma y'ar gold d'in taki ko kallo ban ishetaba sbd kuna jin haushina ko? ita muslima d'in ce tace na mata shopping?"Eh "naga kayan na tambaya"bece komai ba yamaida rigarsa yafito tana biye dashi"suna sakkowa k'asan Adaidai lokacin kuma naseem ya shigo da ladar kayan shopping nasa bakinsa Awashe yana k'walama muslima kira"daddy dai ya kallesa ya kalli ledar ya lura harda sunansa Ajiki"zama yayi kan kujera yana fad'in Naseem Ina zaka da leda harda sunanka Ajiki?"daddy yaya muslim ne yabani yace"Anty muslima ce dazai mata shopping shine nima nida siyama saita d'aukar mana komai yabiya"daddy na k'ok'arin mgn muslima ta fito daga cikin d'akinta da plate d'in data gama cin Abinci Ahannunta....✍️

Oh Hjy jamila Anji ta idan An santa🤭🫣🤔

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kki siya kika fitar mun Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah

#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

..........shiru kawai daddy yayi yana tunani ,domin ya fahimci dollars ne yayiwa muslima shopping d'in yace"injishi kamar yadda yasaba d'aukar nauyinta Abaya Amatsayin shine ke sakashi"yana kallo ta zauna Naseem na bud'e ledar yana zaro komai yanata murna da yimata godiya"ita dai tana kallo tana murmushi kawai"tama d'auka dollars d'in bazai basuba kamar yadda yafad'a zaiyi sadaka"Azatonta sadakar zaiyi.... daddy rai b'ace yabi Hjy jamila da wani irin kallon datasha jinin jikinta kafin ya mik'e tsaye Adak'ile yace "yanzun kinji Amsar tambayar taki ko?"gobema idan kinji Abu kiyi k'ok'arin cigaba da fassarashi da yadda ranki yabaki"ya k'are maganar yana wucewa sama"tunani yakeyi Aransa tunda muslima dangin mamanta suka Amsheta besan komai nataba sai dollars ne ke d'aukar d'awainiyarta"Ayau d'in ma zata yuyu sbd tabasu haushi tace shine yasiya mata,ko kuma muslim d'in ne yace shine yasakashi yasiya mata"gashi Hjy jamila ta kama kumfar baki wai baya Adalci "wanda sarai Abaya tasan be d'aukar nauyin yarinyar kuma bata tab'a ce masa Alh yiwa muslima kaza da kazaba"koda kuwa lokacin bikin sallah ne....gefen bed ya zauna cikin damuwa da tunani"shi kansa yarasa meyasa yakeyiwa yarinyar haka?"shigowar Hjy jamila d'akin yasaka ya kalleta da sauri yana nuna mata k'ofa yace"maza ki koma inda kika fito bana buk'atar ki Anan "to shikenan yayi kyau nagode"daga haka ta juya ta fita.....Naseem da muslima na zaune sunata santin kayan yayinda Malika tsabar bak'in ciki da takaicin wai dollars ne yayi wannan uwar siyayyar yasaka tabar musu parlourn"sai firansu sukeyi Ahaka yaya Ramadan ya shigo da sallama"Naseem ya Amsa "muslima ta gaidashi"domin kwananta biyu kenan Agidan saima yau ta ganshi"kizo inji yaya yana barandar dake shashensa"ni wai?"bayan ke Akwai wata mace Anan?"yafad'a yana kallonta"batace komai ba ta kalli naseem tace"sweet bro tashi ka rakani"yad'an zaro Ido tare da fad'in kinsan yayafa beson shishshigi ki daure Anty nah kije kidawo zan jiraki"harara ta sakar masa ta mik'e tsaye ta fita"yayinda tuni Ramadan yafita"dan yana iya wata guda kofi bema shigo sashenba sbd mugun halin Hjy jamila bata sakewa kowa fuska"idan ya had'u da daddy Amasjeed da Asuba suke gaisawa....tana tafe tana gulmar dollars Aranta wai indai be takura mataba baya jin dad'i"Aidai tafiyarsa zaiyi zata huta"sosai farin ciki ya lullub'eta"dukda bata san idan ya tafi yaushe zai dawo ba? Amma dai tana murna da tafiyar tasa.....tunda doso inda yake zaune yafara binta da kallon k'asan Ido "Atake zuciyarsa ta sanar masa wannan walwalar datakeyi na murnan zai tafi ne sbd dama d'azun idan be mantaba tace"ai gara yatafi "sanye yake da t shirt fara da jeans dark blue da takalmi bak'ak'e boot"fuskarsa tayi fiyau tayi frash"saidai babu walwala cikinta"wayoyinsa guda ukku na zube saman cinyoyinsa yana danne danne.... Assalamu Alaikum! yaya gani! ya d'auki kusan second 15 kafin yace"baki iya gaisuwa ba?"kaifa kace d'azun baka buk'atar gaisuwata ko?"ta k'are maganar tana zama daga gefensa kan wasu kujeru masu shegen kyau na hutawa"ya mutsa fuska yayi yak'i mgn yana tambayar kansa meyasa batada mantuwa kuma bata b'oye Abu Aranta?"kud'i rafar y'an 500 guda d'aya ya jawo a bayansa yana fad'in Amshi nan"ta kallesa ta kalli kud'in"na meye ne yaya?"ya d'ago kansa ya zuba mata burkitattun idanuwansa"babu shiri ta matsa ta Amsa da hannu biyu"bani wayarki"babu musu ta mik'a masa batare data tambayi meye zaiyi da itaba?"tana satar kallonsa

kafin yayima driver Alamar ya tsaya da hannu"shidai suraj na zaune gefensa be koma tankawaba sbd ganin Abin yagirmi tunaninsa"har so yayi ya gumtsa masa labarin yafara zuwa gidansu husnah har contact nata ya Amsa saidai yadda yaga beda walwala saiya k'yalesa"ko sallama be masaba yafita......muslima tafi Awa guda tana bacci"saida yunwa ta fara damunta kafin ta farka tana hamma had'e da salati ta bud'e Ido"koma rufewa tayi ,ta kuma bud'e tana kallon kanta da kuma naseem dake zaune kan wata farar kujerah"k'irjinta yabuga dataji jikinta na k'amshin turarukan dollars"Naseem inane nan?"ta fad'a tana kallon drip d'in da aka zare mata"ga kanula a hannunta"wai Asibiti ne mukazo?"ta fad'a tana tashi zaune"hakane Anty muslima"sannu ya jikin naki?"da sauk'i sosai"meyasa bakya lafiya baki sanarwa kowaba?saida driver ya turoni nazo nadubaki, sbd ki fito yakaiki islamiya nasameki Asume"d'an yamutsa fuska tayi tace ciwon ciki nefa ke damuna"Amma taya nazo nan kuma?"uhmm! yayane yashigo ya d'akko ki muka shiga mota yakawoki Anan"bansan waye yasanar masa baki lafiya ba"sai nan nan Akeyi dake y'ar gatan yaya Muslim"harara ta balla masa tanajin fad'uwar gaba"itafa rabonta dashi tun ranar dayaso yadoketa Allah yasa Abbie yamasa mgn"nidai katashi kaje gida ka d'akko mun kayana da hijab ko?"ta fad'a cikin shagwab'a "dariya yakamayi ya fahimci ita shagwab'a ajininta take"yanzun bara na kira doctor d'in yadubaki "sbd yace idan kin farka na kirashi"shiru tayi tak'i mgn sbd wata Azababbiyar yunwa da takeji"ganin tak'i kulasa yasaka ya mik'e tsaye yafita"yana fitowa dollars na kawowa shida mutanansa sun sakosa Atsakkiya tamkar irin wani k'usan gwabnati "yayi matuk'ar kyau cikin shigar k'ananun kaya"jikinsa na fitar da daddad'an k'amshi me kashe jiki "y'ar ramar da yayi ta k'ara masa kyau matuk'a"fuskarsa Ad'aure tamau"cikin sanyayyar muryarsa me taushi da bud'ewa yace"Ina zakaje kabarta ita d'aya?"yaya ta farkane zanje na kira doctor d'in"okay kawai yace yanufi k'ofar d'akin yatura k'ofar yashiga "su kuma mutanansa suka tsaya daga waje.....jin motsin Anturo k'ofar yasaka muslima dake zaune ta kalli k'ofar da sauri"Atake idanuwanta suka nutse cikin manyan idanuwansa "saida yaji tsikar jikinsa ta tashi"da sauri muslima ta janye idanuwanta ta sunkuyyar dakai k'asa "Anutse ya iso gefen bed d'in gab da ita ya zaunah"hakan da yayi ba k'aramin mamaki yabata ba"gaba d'aya illahir jikinta rawa yakeyi fatanta Allah yasa ba mugunta zai mataba sbd rannan be samu nassarar dukan taba...ko meye Akansa kina bisa gadon Asibiti Ai bazai miki wani abu marar dad'i ba"gefen zuciyar ta Akasanar mata da hakan"....yaya Ina kwana?"me makon ya Amsa sai cewa yayi ya jikin naki?"da sauk'i"kuma ni yunwa nakeji Ai "ta fad'a kamar zatayi kuka"shiru yayi bece komai ba"sai suit cote nasa daya cire ya koma matsawa kusa da ita har jikinsu na gugar juna yaja hannunta tabar jikin bango"da Ido kawai take kallonsa sbd bata fahimci meye zaiyiba saida ya Aza mata suit d'in kafin murya bbu Alamar wasa yace"idan An barki haka zai shigo ya dubaki jikinki Abud'e?"koda yake babu mamaki

tunda kinyi girman shigewa wani d'an iska kina bashi ruwa"nifa yaya bafa bashi nayiba shine da kansa ya zuro bakinsa zai....yimun shiru! Adaidai lokacin kuma doctor d'in yaturo k'ofar shida naseem suka shigo"sosai dollars yakoma had'e rai"da k'yar yabashi hannu sukayi musabuha yana tambayarsa me jiki"yamasa banza yana zaune yana binsu da kallon k'asan Ido"yana jin yadda yake tambayar yadda takeji"kafin yace taci Abinci da magani zaizo yamata Allurai Anjima"kwab'e fuska tayi ta kallo dollars sai Akayi sa'a ya d'ago kansa sbd yaga yadda zatayi Anyi zancen Allura "yaya kaganshi ko wai Allura zayamun"ni Allah bana so"ta k'are maganar hawaye na zubo mata"subahanallahi Ashe patient d'in tawa matsoraciya ce"kuma gashi Alluran nada mahinmanci Ajikin....pls doctor zaka iya tafiya"idan da yuyuwar Amata zan maka mgn"yafad'a fuska bbu walwala"Atake doctor yayi waje"shidai Naseem na tsaye yana murmushi"kai kuma murmushin meye kakeyi ba kaya nace kaje ka d'aukamun ba? ta fad'a tana wurgo masa harara"shidai bece komai ba yanata kallonsu itada yayan nasu"ga suit nasa Ajikinta ta mata kyau"kanta ta Aza gefen kafadar dollars tana rintse Ido tace"wayyo yunwa!......wani irin bak'on yanayi dollars yatsintsi kansa Aciki "saidai yayi jarumtar dakewa"ya kalli naseem Aikuwa yaga kallonsu yakeyi"ba Aikenka tayiba"to yaya bara natafi"daga haka ya fita"yana fita tafara k'aramin kuka....bazaki mun shiru ba?"to niba murd'awa cikin yakeyiba"bece komai ba sbd k'ofar da aka turo"naseem ne yakoma dawowa da wasu ledoji Ahannunsa yace yaya gashi inji wani yace"nabaka"yak'are maganar yana Ajiye ledojin Agefen su ,kafin ya juya ya fita"hannunta guda kawai taji yakama ya aza mata ledar guda"kafin yace idan yaka miki kayan ga pads Anan ciki saiki shirya.....da sauri ta janye kanta daga gefen kafad'arsa cikin jin wata iriyar matsananciyar kunya"duk tsiwarta da fadanta tanada kunya"ta yaya yasani?....ke bana son gulma"tunda dai munzo nan An dubaki miye bazan iya saniba?"ya katse mata tunaninta"shiru tayi tak'i mgn kanta na'a k'asa "lura da yanayinta najin kunya saiya bashi dariya yakuma burgesa"shifa ya d'auka batada wata kunya tunda takema mutane tsiwa"ganin batada niyar tab'a Abinda yasaka Aka mata order yasaka ya Amshi ledar yafara bubbud'e komai"ita dai kanta na'a k'asa tana jin k'amshin Abincin"tana tunanin meyasa yake bata kulawa?"wani irin k'ima da mutuncinsa taji Aranta"gaba d'aya sai tayi dana sanin irin yadda Abaya take masa tsiwa da k'in gaidashi"Ayanzun tana jinsa tamkar uwa d'aya uba d'aya suka fito dashi"d'ago kanta tayi da nufin taga meye yakeyi?"sai kuma aka turo k'ofar Eyyah da me Aikinta da Abbie suka shigo suraj na bayansu"muslima ce kawai tayi k'arfin halin Amsa sallamar tasu"yayinda uban gayyar yayi tamkar besan da shigowar tasuba"shidai Abbie yana lura dashi yana kuma murmushinsa"dama yasan har yanzun bazai huceba"takwarah sannu ya jikin?"cewar Eyyah bayan sun shimfid'a darduma sun zauna"niba zan Amsaba Eyyah"Akanme kenan?"ko kuwa shi babban mutum d'in ne ya hanaki Amsawa?"shiru tayi batace komai ba"bayan me Aikin ta Ajiye komai ta juya ta fita"dollars ya sauka daga saman bed d'in yanufi gaban basket d'in da aka Ajiye yafara k'ok'arin had'a mata tea"yayinda suraj yakoma shiga Al'ajabi dayaga suit nasa Ajikin muslima "ita tama manta da rigar na'a jikinta"Abbie kuwa tunda ya shigo ya lura da hakan"kanta Ak'asa tana turo baki ta gaidasu gaba d'aya"Adaidai lokacin dollars ya Ajiye mata cup d'in tea gabanta da plate"ya d'auki take away na chips da pepper chicken yazuba mata Acikin plate d'in"duk beyi mgn ba ya d'auki wayarsa dake Ajiye ya matsa gefen Abbie yaduk'a ya rik'e hannunsa"haba takwarana ! Na d'auka Ai bazaka tankamun ba?"Ina kwana?"lafiya qlau"yajikin nata?"Alhamdulillah"Eyyah Ina kwana?"lafiya qlau babban mutum da fatan ka huce?"shiru yayi yak'i tankata"suraj yadinga dariya"Abbie na tayasa da murmushi "Adaidai lokacin kuma naseem

yadawo shida siyama tana rik'e da teddy d'inta da yunifoam na islamiya Ajikinta"shi kuma ledar kayan muslima na'a hannunsa"tana ganin dollars ta rirrik'e Naseem kamar zatayi kuka,sbd kwanaki ya shiga sashensu yasamu tana ihu da rigima "tsawa d'aya yamata ta saki fitsari"shiyasa cikin kwana 2 d'in take masifar tsoronsa"shi kuwa yana lura da ita yatab'e baki ya mik'e tsaye yana kallon suraj yace"idan kagama dariyar muje"beyi mgn ba yayima su Abbie sallama yabi bayan dollars suka fita"ita dai muslima tana zaune tana break fast d'inta"duk yadda Abbie da Eyyah sukaso ta musu bayanin meke damun ta k'iyawa tayi"data gama break fast d'in tasaka musu kuka ita wajen Hjy zata koma tunda babu wanda yadamu da ita sai yaya Muslim"yanzun idan da baya k'asarfa hakan yafaru?"ga daddy baya sonta yatsaneta dataje gaidashi zaita zaginta da Aibata ta.....daga Abbie har Eyyah shiru sukayi sbd sun san basu kyautaba Akwai nasu laifin"saidai Abbie yafahimci Hjy jamila ta koma k'ullah wani sabon makircin kenan tunda gashi daddy yaci gaba da nuna tsanar Muslim"sosai Eyyah ta rarrasheta ta bata baki har tasamu ta shiga wanka.....wajen k'arfe....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

........wajen k'arfe 1:25 pm suna zaune tare da Eyyah Adak'in, muslima na sanye da fara k'ar d'in doguwar riga Abaya irinta k'asar Egypt "wacce An k'awata rigar da zanen flowers golden "siririn mayafin rigar na'a saman kanta data yafa"sosai tayi wani irin sanyayyan kyau na musamun"suit cote d'in dollars na ninke gefenta ta Ajiye masa "doctor d'in d'azun ya shigo da sallama"Eyyah ce kawai ta Amsa masa"yayinda muslima ta had'e rai ta d'auke kanta,sbd gaba d'aya likitan ji tayi be mataba"ga wani irin kallo yana binta dashi wanda ta kasa gane fassararshi....my patien ya jikin?"ya fad'a idanunsa Akan ta" Alhamdulillah! shine ta furta batare data kallesaba"yana k'ok'arin mgn Hjy jamila da daddy da Malika suka shigo cikin d'akin"tsintar kanta muslima tayi dajin fad'uwar gaba"Atake Eyyah ta d'aure fuska "tana Amsa gaisuwar daddy "yayinda tayima Hjy jamila da Malika banza tak'i Amsa gaisuwar da suke mata"saima tayi kamar bata jisuba"sai kallon muslima Hjy jamila tayi tace"muslima ya jiki?"Alhamdulillah "daddy Ina wuni?"banza yamata yak'i tankata"saima harara daya watso mata"duk Eyyah na lura tayi dai shiru...idan ba

damuwa kizo muje zan miki Allura"cewar doctor.....nifa gaskiya doctor Abar Alluran nan tunda na war....zaki tashi kije ya miki Alluran ko saina kakkaryaki y'ar iskar yarinya kawai"cewar daddy fuska Ad'aure"daga Eyyah har likitan da kallo suka bishi"yayinda zuciyar Hjy jamila fes"mik'ewa tsaye kawai muslima tayi ta fita sbd kukan daya taso mata"shi kuma doctor d'in saiya bi bayanta..... Eyyah Ina wuni ya mai jiki?"ta koma maimaita mata gaisuwar"idan ban wuniba zaki ganni ne?"kinzo gaida me jiki bayan kina fatan Allah yasa ta mutu Anan d'in"kuma kinzo sbd kar ace baki zoba ko? haba Eyyah me.....rufemin baki mutumin banza! ku tashi ku bani waje tunda ka zama sallamamme"Akan me zan Amsa gaisuwar ta?"daga ita har y'ar tata gaisheni sukeyi ko kuwa da daraja suka d'aukeni??"to bari kiji ! duk Abinda kayi me kyau ko marar kyau Awannan rayuwar sai Ammaka"kema kin haifa nan gaba uwar miji zaki zama"sannan ga y'a mace kinada ita yadda kikayiwa kishiyarki ko y'ar kishiyarki haka kema za'a yiwa y'arki.... innalillahi! meyayi  zafi Eyyah? mena miki kika tsaneni?"cewar Hjy jamila tana sakin kukan munafurci"sulaiman tashi kaja matarka da y'arka ku bani waje tun kafin na sab'a maka"daddy bece komai ba ya kalli su hjy jamila da Malika ya musu Alamar su fita"shi kuma yayi k'asa da murya yana fara bama Eyyah hak'uri ta masa banza......muslima na fitowa daga cikin d'akin ta fashe da wani irin kuka mecin rai"ta rasa sai yaushe mahaifinta zai sota ya k'aunaceta kamar sauran y'ay'an sa? saidai tasan duk rashin uwa yaja mata haka" tana cikin kukan ta d'ago kanta "cikin sa'a ta hango dollars na doso ta shida yaransa"k'ara k'arfin kukanta tayi ta toge gefen bango"Adaidai lokacin doctor d'in yafito daga cikin d'akin shima"ada wajenta zai nufa saidai hango tafowar dollars yasaka yafasa yayi dai tsaye"shi kuwa mutumin naku daure fuska yayi tamau kamar besan meye dariya ba"tunda ya hangota tana kuka ransa yabashi game da Alluran ne"be gama tabbatar da hakan ba saida yaga doctor d'in yafito daga cikin d'akin "yana isowa tun kafin yatambayi meye dalilin kukan nata ta d'ago kanta suka had'a Ido dashi"daga gefenta kawai yaja yatsaya be tankaba "yaya ka ganshi wai dole sai yamun Allura"shine daddy yadinga zagina wai na bisa yamun ko?"koma had'e rai dollars yayi yana jin wani Azabebben kishi na taso masa"ya fahimci doctor d'in beda kunya besan Aikin saba"irin mugun kallon dayake Aiko masa dashi yasaka shi saurin cewa"yallab'ai inaso amata ...na tambayeka wani Abu ne?"sbd haka baza'ayi Alluran ba tunda bata so....be rufe bakiba Hjy jamila da Malika suka fito daga cikin d'akin "d'auke kai yayi tamkar be gan suba"sbd yau y'an jin kan nasa na kusa"su kuwa duk sunji kalamansu"Hjy jamila kuma tasha Alwashin sanar ma daddy ba'a yimata Alluran ba sbd ta rainashi kuma muslim na goyon bayanta"wuce ki koma d'akin Azo Abaki sallama"ya k'are maganar fuska Ahad'e "ba musu ta koma d'akin yaja tsaki yana d'age kafad'a yace" ka iya Aikinka ko kuwa nayi maka sanandin daka barsa har Abada"daga haka yayi gaba be jira cewar saba....daddy nata bama Eyyah hak'uri muslima ta shigo"ta nemi waje ta zauna"ka tashi kaje kabi matarka ku tafi "ni ban k'ullace kaba Araina ba sbd nasan baka hayyacinka"saidai nan gaba kad'an zamu kawo k'arshen ta "ita wannan marainiyar Allah kana Aibatata ba laifin tsaye bana zaune"sai Allah yasa itace ta k'warai Acikin yaran naka, sai kuma naseem dake tasowa Ayanzun" dandai kabeer da Malika ka sani mugun halin uwarsu suka d'auko....shiru dai daddy yayi bece komai ba"ya mike tsaye da nufin yafita"saiga dollars da wani doctor sun shigo Atare "d'an murmushi daddy yace"my son kayi wuyar gani"Ina busy ne daddy shiyasa"Ina wuni?"lafiya qlau"daga haka dollars yayi shiru sbd shima kansa yafara yarda Hjy jamila sai yadda tayi da daddy"Aganinsa yin baya da daddyn ko canza masa fuska bashine mafitah ba"daddy tafiya zakayi ne?"yafad'a da d'an murmushi saman fuskarsa "Eh "kai da yaushe zaka koma ne?"nifa

daddy sai next week zan koma fa "ko zaku wuce dasu Eyyah gida tunda sallama Ake rubata mata"dato daddy ya Amsa "shi kuwa dollars yayi hakane sbd Hjy jamila taji haushi "kuma Akwai inda zaije shida mutanansa "dukda idan yaso uzurinsa bazai hana yasaka koda driver ne yamik'a suba.....gaba d'aya suka fito daga cikin d'akin "dollars na rik'e da basket d'in da aka kawo Abin break fast Aciki"yayinda muslima keta d'aure fuska sbd bataso ta shiga motar daddy "body quards nasa na ganinsa rik'e da kaya suka nufesa sbd su Amsa saiya musu Alamar su bashshi"hakan ba k'aramin faranta ran daddy da Eyyah yayiba"hakan yanuna musu cewa komai dollars yazama Aduniya suna nan Amatsayin su na manyan shak'ik'ansa, kuma makusan tansa dake gaba dashi...."ita kanta muslima tayi mamakin d'aukar kayan da yayi"saidai kallo be ishetaba sbd yabata haushi daya ce subi daddy"Hjy jamila da Malika na tsaye gefen motar sunata k'ullah mugun nufinsu suka gansu kawai"dollars kallo bata isheshiba ya matsa ya bud'e back sit yana fad'in Eyyah kuzo ku shiga"Eyyah batace komai ba tazo ta shiga muslima kuwa turo baki tayi idonta taf k'wallah"duk dollars na ganinta"Allah ya gyaramun yarinyar nan"yafad'a Azuciyarsa yana isowa dab da ita"ya wani d'aure fuska yana fad'in meye kike jira da bazaki shigaba?"batace komai ba ta shiga ta rufe"malika ta bud'e daga gudan sashen ta shigo suka saka Eyyah A tsakkiya"yayinda Hjy jamila ke gidan gaba kusada daddy"ranta bak'i k'irin sbd bataso tafiyar tare dasu ba"tasan kuma daya saukesu tafiyarsa zaiyi"sadda zai dawo gida Agajiye"kuma dokar sace besan matsawa da dare, bbu zancen ta kamasa wata mgn....har suka iso gida babu me mgn Acikinsu "daga wajen get daddy yayi parking duk suka fita shi kuma ya juya yatafi Abinsa....."muslima tabi Eyyah zuwa sashenta ,yayinda su Malika suka wuce nasu sashen.....zaune suke shida suraj Awani wayayyan wajen cin Abinci na musammun suna lunch"dan har yanzun be Ida hucewa ba da Abinda su Eyyah da Abbie suka masa last 2days"yakuma sha Alwashin zai binciki waye yaron yak'ara masa warning da babbar murya yarabu da muslima tun kafin ya nuna masa true colour nasa"cikin Jan Aji da k'asaita yakecin Abincin yana danne danne Awaya"body quards nasa daga tsaye gefe.....can yaja tsaki sbd ganin kiran sadeeq ya shigo Awayarsa "lafiya mutumin? kaida Abu kad'an saiya fusataka"tab'e baki yayi yace"sadeeq ne"na rasa meya maidani?"yace kud'i yakeso cash nace saidai transfer"yanuna bayaso yanzun yadawo waina masa transfer bayan yagama d'agamun murya"An fad'a masa ya Isa ya d'aga mun murya ne?"uhmm dollars kenan! nasan sadeeq na yawan kamaka zugata"ni kuma Ina baka shawara ta k'warai game da yadda zakayi tarayya dashi"sai kake ganin kamar nida shi kowane yanada wata manufa Akanka ko?"to bari na fito maka Amutum sadeeq babban mak'iyinka ne! inada manyan  dalilai na fad'in hakan"sannan karka yadda ka bashi Aron kud'i ba wani motocin dayake siyarwa burgace kawai da rubar daya sabayi cikin Abokansa"jikina yabani yanada wata mummunar manufar daya keso ya Aiwatar idan ka bashi kud'in"shiru kawai dollars yayi yana nazarin kalamansa "Ahaka kiran ummah ya shigo wayarsa"kashewa yayi yabi kiran"bayan sun gaisa ta sanar masa An basu sallama sun dawo gida"yace Anjima da yamma zai shigo ya duba Abban da jiki"bayan ya Ajiye wayar suraj yace"idan kak'i taimakamun husnah ta zamo tawa "ni gashi nafara yak'in da kaina"koda safen nan  ta kirani da taga ban kirataba"nayi hakan sbd na gwadata"kana nan zaune zanyi Aure nah! d'an murmushi dollars yasaki Akaro na farko da zamansu Awajen "kafin yace"kaine dai sabon shiga Awannan babin"idan baka saniba ni har mata gareni shaidawa yarage kawai kuyi"uhmm matar da babu sadaki ko?"Amma wacce me sa'a ce haka?"very soon zaka santa"daga haka dollars yacanza wata firan"bayan sun bar wajen sukayi sallar la'asar "kafin su nufo bugaja's

House's sbd dollars zai d'auki wani sak'o d'akinsa yajema ummah dashi"bayan sun iso suraj yanufi d'akinsa dake gefen na Ramadan "dollars kuwa shima part nasa yanufa"befi mintina 35 ba yafito tamkar tauraron dake haskawa Asararin samaniya "wankane na kece raini ya d'auka"dukda ba wani nawa yayiba wajen shiryawar Amma yayi masifar yin kyau "sbd Ajininsane ko k'aramar sutura yasaka saita hau jikinsa"k'ananun kaya ne jeans bak'i da fara k'ar d'in t shirt irinta polo"sai takalmi sawu ciki "bak'ar sumarsa me sulb'i irinta buzaye sai k'yalli takeyi ya Aza pasincap samanta "yanata zuba k'amshi me kashe jiki yanufi sashen Eyyah, yana rik'e da wani Abu Aleda ga hannunsa guda "yayinda gudan hannun nasa ke zube cikin Aljihun wondonsa"har lokacin fuskarsa Ad'aure take "hakan kuma ba k'aramin kyau yak'ara yimasaba"saidai kuma Aransa rigimammiyar mutuniyar tasa ce yake tunani"ya fahimci idan beyi wani Abu Akai ba kishin yarinyar zai iya kashesa"yana wannan tunanin ya shigo da sallama cikin k'asaitacciyar muryarsa me laushi da taushi"muslima dake zaune kan kujerah tana Azkhar ta d'ago kanta tad'an lumshe Ido sbd daddad'an k'amshin turarensa data shak'a "murya can k'asa ta Amsa sallamar tana nuna kamar bata gansaba"itama tasha gayunta cikin sabon wankanta na Atamfa"......tana nufin bazata gaisheniba sbd nace ta shiga motar daddy?"yafad'a Azuciyarsa yana zama kan kujera "ya fahimci Eyyah na kitchen"shima biris yayi da ita dan beson raini"ta wutsiyar Ido yaga ta tashi ta shiga d'aki bata jimaba ta fito da ledar data saka masa suit nasa Aciki"gefensa tazo tad'an duk'a tana fad'in gashi nagode "banza yamata yak'i Amsa kuma beyi mgn ba"yaya Muslim! kanafa jina ka Amsa mana"kuma shine kasaka muka shiga mota ko?"d'ago kansa yayi yace"kina tuhumata ko *halimatu* ? ya fad'a da wani yanayi a muryarsa"shiru tayi ta sunkuyar dakai"na fahimci har yanzun ba zakiyi hankaliba ko?"ke gaba d'aya bakisan ki gaida mutaneba musammun idan y'an tsiwar naki na bisa kai"shiru tayi tak'i mgn"shi kuma yana danna waya can tace"wai yaya Muslim Ina wannan Amatallahi d'in?"ta fad'a cikin turo baki"da k'yar ya iya gimtse murmushin da ke son kufce masa yace"meye damuwarki dajin inda take?"ko kuwa kina tsoron ku had'u da itane.....Allah ya sawak'a naji tsoronta "ko rannan ma wlh in bacin ka hanani dana lallasa yarinya"ta fad'a cikin jin haushi"kinsan kuwa gidansu zanje yanzun"dan Allah yaya Muslim zanje"keda ba kyason bina har kuka kikeyi idan mun fita" yau sbd kinaso kija mgn zakice ki bini"to babu inda zanje dake"dan Allah fa nace"nifa bazan kulataba "Amma kuma karta tak'aleni ko? shiru yayi bece komai ba"kaji yaya dan Allah "ta fad'a cikin shagwab'a"ya tab'e baki yasan sbd yaje da ita take hakan"be kuma Amintaba sbd Allah zataje"yana zaton sbd ta tak'ali yarinyar suyi fad'a ne"motsin barinta wajen yadawo dashi tunaninsa"saiya mik'e tsaye shima da nufin yatafi"Adaidai lokacin Eyyah ta fito daga cikin kitchen"Ahhhh babban mutum kaine a parlourn nan?"nine Eyyah"zanje gidan ummah na dubo Abbah da jiki"wai har yanzun jikin dai?"Eh Amma da sauk'i sun baro Asibintin suna gida"to shikenan Allah yabashi lafiya in sha Allah zanje na gaidashi da jiki....beyi mgn ba sbd ganin fitowar muslima ta gyara d'aurin d'an kwalinta ta d'akko mayafi da takalmi ta fito"kallon second 5 yamata ya d'auke kansa"ba k'aramin kyau tama saba"saidai rigar jikinta ta bayyana coca cola shape d'inta.....ke kuwa Ina zakije yanzun da yamma?"Eyyah tare fa da yaya zamu tafi....dama nace zanje dake ne?"shiru tayi taje ta zauna kan kujerah batace komai ba "hakama Eyyah sai kitchen data koma"dollars kuwa fita yayi"befi mintina gomaba yakirata tana gani ta masa banza tak'i d'auka "sbd taji haushi saima ta kama kuka"muryar yaya Ramadan dataji yasaka ta janye tafikan hannayenta data rufe fuskarta dasu"yaya Muslim yace kizo kuma ki saka hijab"tamkar tace baza tajeba haka taji"saidai tasan k'in zuwan nata zai rufe Ido yakarta mata wani abu

marar dad'i "shidai Ramadan nata kallonta ya juya ya fita"ta mik'e tsaye tana share hawayenta ta koma d'akin Eyyah "cikin gogagun hijaban Eyyah sabbi ta zab'o irin kalar kayanta ta saka ta fito ta shiga kitchen "Eyyah ta bita da kallo tana fad'in waike meyasa bakya raina Abin kukane?"toba  shine yajaba"shine kuma zai Aiko wai nazo"ni Allah Eyyah bana zuwa kice masa kin Hanan..... mak'alewa maganar tata tayi sbd k'amshin turare dollars dataji.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
 Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
 #sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

........da sauri muslima ta maida kallonta Ajikin k'ofar kitchen sbd ta tabbatar da shid'in ne" "Aikuwa yana tsaye hakimce jikin k'ofar ,ya rungume dogayen hannuwansa Asaman faffad'an k'irjinsa ya tsareta da mayatattun idanuwansa yana binta da wani irin kallo me wuyar fassara ,yana cije red lips nasa na k'asa dake shek'i suna d'aukar idon me kallo"d'auke kanta tayi tana turo baki Aranta tace"ba laifi yaya Muslim yanada kyau....ki wuce kuje kina b'ata masa lokaci"cewar Eyyah da itama ta lura da tsayuwar tasa"ta kuma tabbatar da cewa bazai tankaba"nifa Eyyah ban....ganin yana doso inda take cikin Isa yasaka gabanta fad'uwa ta kasa k'arasa sauran maganarta"yad'an tab'e baki Aransa yace ga tsoro ga jan fad'a"zanfa bika yaya Muslim"ta k'are maganar tana juyawa tayi waje"ya sakarma bayanta harara"Eyyah tayi murmushi kawai tabisu da kallo har suka fita"suna fitowa tace"yaya Muslim da wace mota zaka fita?"miye Amfanin tambayar?"toba key d'in motarka zan bakaba"ki barshi Awajenki zan Amsa"yak'are maganar yana yin gaba "itadai bata tankaba"lokacin data iso parking lot d'in har driver ya shiga mota bayan ya bud'e masa ya shiga"hakan yasa itama ta bud'e back sit da kanta ta shiga ta zauna nesa dashi"sai satar kallonta yakeyi da yaga zata juya ko kallo inda take saiya d'auke kansa ya wani d'aure fuska "ita kuwa bata san yanayiba"har suka iso gidan ummah babu wata fira data had'asu"saima waya da yaketa Amsawa ta mutane jefi jefi"kuma yawanci masu kiran nasa yare ne"wani maganar yayi turanci ko faransanci ko labaraci"itadai tana saurare Aranta tana gulmar wai yana jin yare daban daban"bayan sun fito daga cikin motar ta tsaya ta sunkuyyar dakai "jin motsinsa gefenta yasaka tayi saurin d'ago kanta suka had'a Ido"hannunta guda kawai  yakama yasaka mata ledar dake hannunsa tamkar me koyon mgn yamotsa lips

nasa wajen fad'in ki bama ummah bayan kun gaisa"da tsoro cikin idanuwanta ta girgiza kanta batace komai ba ta kuma kasa rik'e ledar"shi kuwa d'aure fuska yayi yasakar mata ledar Ahannunta yayi gaba"batada zab'in daya wuce nabin bayansa zuwa cikin gidan"sai k'irjinta ke bugawa fat fat"haka ta dake tana lura da yadda masu gadi keta gaidashi yana d'aga musu hannu"koda ya iso bakin k'ofar shiga babban parlourn gidan  saida yajira isowarta yana daga tsaye ya bita da kallo ta sunkuyyar dakai"duk wannan fargaban na meye ko yau muka fara zuwa dake gidan ne?"babu komai fa yaya"to zoki fara shiga,"nok'e kafad'arta tayi tace nidai dan Allah kafara shiga ko?"kuma kaifa suka fara sani Ai "ta k'are maganar cikin shagwab'a"shiru yayi bece komai ba yatura k'ofar Anutse ya shiga kafin itama ta biyo bayansa"mamy ce dasu Farooq da wasu matasan samari guda biyu sai Amatallahi duk suna zaune Acikin parlourn.....sau biyu dollars yayi sallama Mamy ta Amsa tana masa sannu da zuwa ya zauna suka gaisa yamata yamai jiki"kafin sauran yaran su gaidashi"kallon mutuniyar tasa yayi sbd jin bata gaisheda mamy ba"yana kallonta yaga suna hararan juna itada Amatallahi"tana nuna mata waje da hannu"Alamar idan baga tsoroba su fita mana"tsareta da idanunsa masu kwajini yayi yana kallon ta fuskarsa Ad'aure "kamar Ance ta kallesa"Aikuwa ya wurgo matawata uwar harara "da sauri ta gaida mamy"shi kuma ya mik'e tsaye yana fad'in umman na ciki ne?"Eh yamzun ta shiga kuje Alhajin na parlourn sa"dato ya Amsa ya mik'e tsaye ya wuce "itama muslima saita tashi tabi bayansa"sadda ta shiga cikin parlourn yana zaune gefen Abban "babban mutum da ciwo yak'ara masa rama da tsufa"ya kishingid'a k'asa kan carpet da k'yar yake mgn cikin sanyin murya da murmushin k'arfin hali saman fuskarsa"Alokacin data shigo ta tsintsi muryansa yana cewa" Allah yayi maka Albarka yusuf"koda banine na haifekaba babu irin dawainiyar da baka mun ba Arayuwa"nasan ciwon nan da wuya natashi"shiyasa nacema naja'atu ta sanar maka Adena zancen fiddani k'asar wajen nan Abarni nan na jira lokaci....sai kuma yafara tari"dollars ya girgiza kai cike da tausayawa yace"kadena fad'in haka Abba zaka tashi in sha Allah "daga haka ya kalli muslima data shigo zata zauna tana bin Abban da kallon tausayi"zonan ku gaisa da Abba "batace komai ba ta matso kusa dashi ta duk'a tana fad'in Abba Ina wuni ya jikin?"Alhamdulillah y'ata "Allah yayi muku Albarka kinjiko?"kiyi hak'uri da duk yadda rayuwa tazo miki "ki Amshi k'addara me kyau ko marar kyau"sannan ki kasance me biyayya ga nagaba dake"muddin kikayi haka zakici nassarar rayuwa"sosai muslima taji wasu hawaye na tausayinsa da kuma jin nata tausayin"ita kanta tasan tana cikin jarabawa"gata rashin uwa"gata basa shiri da mahaifinta"ga y'an uwanta y'an uba basa k'aunarta ,ga kuma masifar matar uba"sai kuma ta girgiza kanta data tuna text message d'in da Aliyu yaturo mata d'azun"game da Abinda yafaru kwanaki beji dad'i ba kuma yarabu da ita tunda bata buk'atarsa Arayuwarta "dama tunda Akayi Abin be koma kiranta ba "dama itama bata tab'a kiran saba....sallamar ummah da motsin shigowarta cikin parlourn yasakata saurin nutsuwa ta dawo tunaninta"tana jin gabanta na fad'uwa"ummah kuwa tunda ta lura da yarinyar Annurin dake kan fuskarta ya dushe"saidai bata d'aure fuskar ba"ta kuma fara zaton muslim sonta yakeyi"saidai zata masa mgn karya koma zuwa mata da ita Agidan"idan yazama dole duk inda zai saka k'afarsa saida ita to ita bata buk'atar yadinga zuwa mata da ita"ummah sannu da fitowa Ina wuni?"cewar muslima kanta Ak'asa"lafiya qlau "yamai jiki?"gashi nan da sauk'i "sai sannan dollars ya gaisheta yana lura da hararar data jefa masa"muslima ta taso tadawo gefenta Aladabce ta mik'a mata ledar had'e da cewa gashi"da mamaki umman ta Amsa Amma bata bud'a ba"tashi kije bakin get ki jirani"dato ta Amsa ta mik'e tsaye ta fita"ummah ta wurgo masa

harara tana fad'in maganata dakai kenan ta k'arshe daga yau karka koma zuwamin da wannan yarinyar "tunda kaida ita kun zama tip da taya bbu rabuwa, duk inda kasanya k'afa tana biye sai kaje kayi tayi"ga wannan ka bata kayanta bana buk'ata"sai A sannan dollars da kansa ke Ak'asa ya d'ago ya kalleta yace"ummah turarukane fa tabani na baki sai nace tabiyo ni ita da kanta ta baki tunda nan zanzo"(yayi k'arya )batama lafiya ba'a jima da sallamota daga Asibiti ba d'azun...... Amma kiyi hak'uri in sha Allah bazan koma zuwa da itaba"dama Eyyah ma tace zatazo Amma zance kawai tabarsa tunda baki son ganin dangin mahaifinah na zuwa nan"daga haka yayi shiru"sbd beji dad'in Abin ba"musammun idan ya tuna yadda mahaifiyar muslima sadda take raye ta kula dashi ta kyautata masa lokacin da Hjy jamila ke gana masa Azaba"ga kuma daddy dashima ya kula da rayuwarsa"Aganinsa be cancanci ta nuna bata son jinin suba" mik'ewa tsaye yayi da nufin yafita"sbd na fad'i Abinda ke raina shine kakejin haushi"na fahimci kawai kana son yarinyar nan ko?"nifah ummah ba haka bane "girmanki da darajarki Awajena yasaka bakyamun laifi"kiyi hak'uri bazan koma zuwa da itaba"daga haka yasakai yafita "Abba dake sauraren komai ya sauke Ajiyar zuciya da k'yar yace"baki kyautaba naja'atu "ko kare yusuf yazo miki dashi Azatona zaki soshi ki karramashi balle d'an mutum"nifa be sanniba beda Alak'a dani"sbd kawai kina Aurenah ya girmamani ya kula dani yakashe mun dukiyarsa sbd neman lafiyata"dukfa sbd darajarki yamun haka"ke meyasa bazaki so Abinda yake soba?"kodan sbd kyautata warsa gareki" miye laifin wannan y'ar tatsitsiyar k'aramar yarinyar dazaki nuna mata k'i?"nasan be sanar miki yana sontaba sbd lura da yayi baki son Ahalin mahaifinsa"saidai ni Aganin dana musu yanzun na fahimci yana son yarinyar ba k'aramin soba"nasan kuma yadda yaron nan ke miki biyayya zai iya hak'ura da ita sbd farin cikin ki"ki sake tunani"ya k'are maganar yana fara tari saiga jini ta baka ta hanci na zuba"gaba d'aya illahir jikin ummah yayi sanyi"wata zuciyar tace mata idanda yarinyar daga tsatson Hjy jamila ta fito kinada hijjar nuna baki sonta dashi"duk sai taji bata kyautaba"saidai halin dataga mijin nata yasaka da sauri ta Isa gabansa tana d'ago kansa ta aza saman cinyarsa"tana Aikin yimasa sannu"hankali tashe ta d'auki wayarsa da nufin ta kira family doctor d'insu"hannunta ya rik'e yana d'an murmushin yak'e ya girgiza kansa yace"ki bari naja'atu ciwo ya warke"Ina sonki Ina kaunarki keda zuri'arki"Ina kuma k'aunar yarinyar nan me suna muslima"dan Allah kema kisota ki..... shakk'uwar dataci karfinsa yasaka yayi shiru yana sallati"zufa tafara ketoma ummah tana salati had'e da kalmar shahada"cikin ikon Allah Abba ya Amsa daga haka bakinsa ya datse, idanuwansa suka kafe,jikinsa yasaki Alamar rai yayi halinsa😢......*kullu nafsin za'ikatul maute*! Allah yasa mu cika da Imani.....cikin wani irin yanayi na b'acin rai da damuwa dollars yabaro parlourn "yana jin tsananin tausayin muslima"da ace yasan mahaifiyarsa bazata sotaba da tuni beyi gangancin saka soyayyarta Aransa ba "shida yakeso in har ta zama tashi tayi zaman farin ciki dashi"ummah ta maye mata gurbin uwa"yasha zama yayi tunani waiga muslima nan kwance saman cinyar ummah tanata yimata shagwab'a "ita kuma tana lallab'ata"Ashe ba zaiga ranar ba.......yaya Muslim! siririyar muryarta ta katse masa tunani" ya kalleta da sauri"ta turo baki "sai a lokacin ya lura har ya iso bakin get bema sani ba"ya jikin Abban?"da sauk'i"inaga jibi kawai India zasu tafi"dama rishin samun bizar da wuri yasaka suka kai har haka basu tafi ba"ya k'are maganar yana tsayawa daga gefenta"to Allah dai yabashi lafiya"wlh yabani tausayi "ita waccan y'ar rainin wayon mahaifinta baya lafiya ko Ajikinta.....tamkar bazai tankaba sai kuma ya yamutsa fuska yace"bayan fad'a da tsiwa da kika iya harda gulma kuma yanzun kika koyo??ni yaya Muslim gulmar me nayi daga fad'in gaskiya?"ta fad'a cikin tsiwa"be kulataba sbd

yanzunma kawai yadai tankatane Amma ransa bbu dad'i"be jira driver ba yabud'e masa k'ofar ba ya shiga da kansa"itama muslima shigowa tayi tanata kumbure kumbure ta zaunah "ya d'an kalleta ya girgiza kansa"yaya dan Allah muje gidan Hjy "shareta yayi ya jingina bayansa Ajikin kujera ya lumshe Ido"kallonsa tayi ta wurgo masa harara Azatonta baya ganinta"saidai ta makara duk yana kallonta ta k'asan Ido"saidai be tankataba ko nuna Alamar yaga meye takeyi....yaya Muslim dan Allah nace fa? bud'e lumsassun idanuwansa yayi yana duba time 6:11 pm "meyasa bakya jin mgn ne?"yanzun da yamma gab da magrib Ina zakije?"bayan kuma ba ishashshiyar lafiya ce dakeba"ko kuwa wannan d'an iskan kukayi Appointment dashi zaku had'u??"innalillahi! nifa mutunci ne kawai tsakanina dashi bayan....zaki mun shiru ko saina bige miki baki ne?"tayi tsit hawaye na cika idonta "yaja tsaki rai b'ace yace kika sake kikamun kuka saina mareki stupid! daga haka ya maida idonsa ya lumshe"har suka iso gida ko tari muslima batayiba"Ana gama parking ta bud'e da sauri ta fita"dollars ya girgiza kansa Aransa yace zan gyara miki zama"bayan sun Ajiyeta masjeed ya wuce sukayi sallar magrib bayan ya fito ummah ta kirashi cikin sanyin jiki da damuwa ta sanar masa rasuwar mijin nata"za'a yi zana'ida washe gari da safe da k'arfe goma..... innalillahi wa inna ilaihir raju'un! yafad'a yana yanke wayar cikin yanayi na damuwa"harga Allah yana son mijin mahaifiyar tasa sbd mutumin kirki ne"cikin rashin walwala ya nufi bugajes house's "ta k'ofar baya da zata kai mutum parlourn Abbie "Anan yashiga yasanar masa rasuwar"shi kuma yasanarwa Abba da daddy"kafin dollars ya wuce sashensa"bayan ya watso ruwa yatafi masallaci yayi sallar isha'i "dukda beda walwala Amma y'ar rigimar tasa na'a ransa"da kansa Ak'afa ya Isa nan bakin titi yasiya mata manyan dak'walan kaji gasassu yanufo cikin gidan"sai Akayi sa'a yana shigowa yasameta zaune a parlourn Eyyah tayi sabon wankanta"tana sanye da riga da wondo pencil da yayi matuk'ar kamata"ta rufe jikinta da wata mini hijab da iyakarta gwiwar hannu "tanata b'ata rai da Alama Akwai Abinda ke damunta"sallamarsa dataji yasaka ta kallesa suka had'a Ido"Amsawa tayi had'e da gaidashi"dukda taji haushin Abinda yamata d'azun "saidai ta share kawai sbd nasihar da mijin ummah yamata d'azun"be Amsaba iyaka ya k'araso ya zauna kan kujerah"meke damun ki?"shine ya furta kamar bashine yayi maganar ba"sbd tunda ya shigo ya lura fushi takeyi"kamar tana jira ta shagwab'e murya tace" kagani yaya Eyyah tuwo tayi ni kuma bana cin tuwo miyan taushe"kuma ni bana son Abincin su mommy"zoki Amsa "ya fad'a yana mik'a mata ledar"ba musu ta sakko ta iso gefensa ta mik'a hannu biyu ta Amsa tana masa godiya....bece komai ba saidai ya fahimci bata san mijin ummah yarasu ba...yana kallonta ta wuce kitchen "shi kuma ya rufe Ido yana tunani"harta fito ta zauna dining area ta fara bikin cin naman da viju milk dollars na zaune yad'an kishingid'a ya rufe Ido "Ahaka Eyyah ta shigo parlourn"ta kalleta tace "kin gama fushin ke bazaki ci tuwo ba?"Eh mana yaya ne yabani wannan"sai lokacin Eyyah ta lura dashi"k'arasowa gefensa tayi ta zauna"ya bud'e idanunsa"yanzun ka shigo ne babban mutum? uhmmm ! sai kuma mukaji rasuwa ko?" cak! muslima ta tsaya da bikin cin naman datakeyi dukda tama kusan kammalawa"ta juyo ta kallesu tana fad'in Eyyah waye yarasu?"mijin ummansa ko?......✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa banyafe

mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

........ innalillahi wa inna ilaihir raju'un! kalmar da muslima kenan ta fad'a cikin nuna Alhini "gaba d'aya sai taji komai ya fita Aranta"ta dafe kanta tana tuna Ashe d'azun ganin k'arshe suka masa itada dollars?"bata san lokacin data saki kukaba"musammun data tuna irin nasihar daya mata "daga Eyyah har uban gayyar duk suna sauraronta babu wanda yatankata har tabaro dining area d'in ta wuce d'aki"Ajiyar zuciya Eyyah ta sauke tana fad'in Allah ya jikinsa yasa jinyar da yayi ta zamo kaffara Agaresa"goben in sha Allah sai muje nida muslima muyi musu gaisuwa"shiru kawai yayi idanunsa Arufe kamar me bacci"kuma Eyyah tasan sarai ba baccin yakeyiba"tamkar yacema Eyyah su hak'ura da zuwan haka yaji"Amma sai yayi shiru daya tuna cewa hanatan zai saka ta zargi wani Abu"kuma dama shida muslima ne tace sudena zuwa tare"idan sunje tare da Eyyah Ai ba laifi bane"in bacin baya son family d'in mahaifinsa suyima mahaifiyarsa kallon rashin kyautawa da tuni ya hana kowa zuwa tunda bata buk'atarsu....nasan bakaci komai ba Adaren nan Aka maka tuwo da fura?jin muryar Eyyah yasaka ya bud'e kyawawan idanuwansa ya Azasu Akanta yad'an girgiza kansa tamkar bayaso ya furta Abani furan"daga haka yayi shiru"batace komai ba ta tashi tsaye ta wuce kitchen "bata jumaba ta dawo da gidauniyar damammiyar fura wacce taji kayan had'i ga sanyi tayi"saman center table ta Ajiye masa kafin ta juya ta wuce k'ofar da zata sada mutum da parlourn Abbie"yad'an furzan da wani irin huci daga bakinsa yana gyara zamansa"sai tunani yakeyi tunda yafara tasawa ya fahimci irin yadda Eyyah ke kulawa da Abbie dayi masa komai yakeso"gashi har sun tsufa irin haka bata dena ba"inama idan Allah yasa muslima rabon sace itama sukasance irin haka har tsufansu"tunawar da yayi may be har yanzun tana can tana kukan mutuwar Abba yasaka ya matso ya d'auki furan ya motsa yafara sha....saida yasha rabin kwanon kafin ya d'auki kwanon Anutse ya nufi d'akin baccin Eyyah da muslima ke ciki... shashshekar kukanta da yadda take sauke Ajiyar zuciya shi yafara ji yana sako kansa cikin d'akin"sau biyu yana sallama Amma bata jiba, tana kwance rub da ciki saman bed d'in ta cire hijab d'in jikinta"kallon second 5 yamata ya d'auke kansa da sauri sbd ganin kayan sun kama jikinta"gefen bed side drower ya zauna ,ya Ajiye kwanon k'asa kan carpet"ganin Alamar batasan da zamansa Adak'in ba yasaka yayi gyaran murya cikin taushin muryansa data canza yace"*halimatuuuuuuu*! saida taji gabanta yafad'i sbd yadda yaja sunan da kuma muryarsa dataji ta canza"da sauri ta rarumi hijab nata ta saka tana b'ata fuska tace" shine yaya muslim saidai Aganka kawai?"kina kukan zakiji sallamata?"tayi shiru"kinsha magani?"ah ah"Amshi kisha sannan kisha magani ki kwanta"nifa na k'osh....kallon daya jefeta dashi yasaka ta had'iye sauran maganarta"wasu sabbin hawayen

taji sun koma zubo mata "babu yanda ta iya ta matso ta d'auki furan tad'an sha ta Ajiye "tashi ki kamun maganin da ruwa"batace komai ba sai cin magani takeyi ta fita"ya girgiza kansa kawai yana d'aukar wayarsa da suraj ke kira"Anan ya sanar masa rasuwar da time d'in zana'ida"yana k'ok'arin kashe wayar ta shigo cikin d'akin"koki koma kiyi sallama kona b'ata miki rai "yafad'a fuska Ad'aure"batayi mgn ba ta juya kamar zata fashe sbd fushi ta fita"sai kuma ta dawo tayi sallamar"saida ya danne murmushin dake neman sub'uce masa kafin ya Amsa"sbd ganin yadda taketa cika tana batsewa"ta Ajiye masa ledar gabansa kafin ta zauna gefen bed d'in "magungunan ya duba kafin ya b'allo yabata"batace komai ba ta Amsa ta had'a da ruwan dake hannunta Tasha"dama duk month haka kikeyi?"uhmm! Ana kaiki Asibiti?"Eh yaya sadam na kaini"had'e rai yayi yace"sbd bakida kunya shine zaki sanar masa harya kaiki Asibiti??"da mamaki ta d'ago kanta suka had'a Ido ya zabga mata harara ta kauda kanta batace komai ba "saidai tana mamakin meyasa zai fad'i haka?"kamar yadda zumuncinsu yake da ita shima sadam haka"da mamanta da mamansa uwa d'aya uba d'aya"saidai tasan zai iya fin sadam iko da ita tunda shi fannin Uba ta had'a dashi....da k'arfe nawa Ake yin zana'idar?"ban saniba"baza kije gidan gaisuwar ba"shiru tayi tak'i mgn"shi kuma ya mik'e tsaye ya fita cikin tsananin zafin wutar kishinta Aransa "ita kuwa tab'e baki tayi sbd bataga Abin b'acin rai ba"Amma tunda yace baza tajeba ba matsala"daga haka ta d'auki kwanon furan da roban ruwa ta wuce kitchen ta mayar"kafin ta dawo ta d'auki hijab nata ta saka ta d'auki wayarta da ledar kayanta data cire ta fito ta wuce parlourn Abbie ta musu sallama"wajen k'arfe 9 da wasu y'an mintina ta iso sashen su"malika na zaune tana chats daya zame mata kamar ibada" Hjy jamila kuma tana kallon TV"saidai hankalinta ba'a kan TV d'in yake ba"tana can tunanin kalaman mlm na kwanaki dayace wani Abu zai faru marar dad'i Agidan "saita fara zaton to kodai mutuwar mijin Hjy naja'atu ce daya rasu yau ,may be kuma daga baya daddy yace ko zai Aureta"da kuwa Anyi d'an k'aramin yak'i "ta Ayyana Aranta tana huci"tare dashan Alwashin gobe zata tambayi zuwa gaisuwa sai kawai taje gidan bokanta"Aduba mata idan zancen shine Atari matsalar tunda wuri"domin tunda ya sanar mata da zancen batada nutsawa tanata y'an sak'e sak'e Aranta....kallon muslima tayi itada kayan dake hannunta taja tsaki tana fad'in "kwanannan zanyi maganin wata y'ar iska Agidan nan"duk muslima naji Amma batace komai ba ta shige d'akinta ta murza key "labulaye ta janye ta bud'e windows iskan hadarin dake k'ok'arin tasowa yadinga busowa cikin d'akin"ta lumshe Ido sbd tana son lokacin damuna....bath room ta shiga ta kama ruwa tayi brush kafin ta fito, kafin ta fara shirin kwanciya bacci, saidai fuskar Abba da kalamansa na mak'ale Aranta"gefen zuciyarta kuma haushin dollars ne"saima sannan ta tuna yaufa sunday yake barin k'asar Amma gashi be tafiba kome yasa?"sbd tasan dai badan rasuwaba"tunda da yamma Akayita gab da magrib shi kuma kafin lokacin yake tafiya"ta jima tana y'an tunane tunane kafin tayi Addu'a ta kwanta.....Afannin dollars kuwa Anan b'angaren sa dake cikin gidan yawuce yayi shirin bacci"sai bayan ya gama Addu'a ya d'auki babbar wayarsa ya shiga folders d'in da pictures d'in muslima suke sunfi Hamsin"wasu tun tana y'ar 12 yrs wasu 15 yrs wasu kuma tana a cikakkiyar budurwarta"saidai gaba d'aya duk bata sani yake d'aukarsu"sai d'an murmushi yakeyi yana girgiza kansa"dama ko k'asar yabari idan yana zaune shi kad'ai haka zaita lalibo pictures nata yana gani"dukda murmushin dake kwance saman fuskarsa hakan be hana k'asan zuciyarsa fushi da itaba"shi kansa tausayin kansa yakeyi"sbd ganin yana neman ya haukata kansa Akan kishin yarinyar"gaba d'aya wata iriyar tsanar sadam d'in yaji Aransa "saidai kawai yabasar yaci gaba da kallon pics d'in har bacci yasacesa.....washe

gari tun wajen 9 am dollars ya shirya cikin sabuwar farar shadda yabar gidan yanufi gidan ummah"ko break fast be nema ba,ba k'aramin kyau naban mamaki kayan suka masa ba"musammun da Akayi masa Aiki da b'akin zare yasaka komai bak'i"tamkar wani sabon Ango haka ya koma"ga wani ni'imtaccen sanyayyan k'amshi dake fita ajikinsa "ko wucewa yayi Aguri saiya bar k'amshinsa"muslima kuwa bisaga tursasawar Eyyah ta Amince ta bita bayan ta saka zunbulelen hijab har k'asa sky blue kalar Atamfar jikinta"sai b'ata rai takeyi sbd tuna jiya dollars yace bazata jeba"ita kuma tanaso ta nuna masa tana da zuciya"driver ne ya jasu suka tafi"lokacin da suka iso k'ofar gidan cike yake da mutane"befi saura mintina 25 Ayiwa gawar sallah ba"wani irin daburcewa muslima tayi da taga dandazon taron mazan "da wasunsu badan Allah suka zoba sai dan sbd suyi suna wajen dollars,wasu kuma su kalli matan mutane"rintse Ido tayi taji dama tasaka face mark's"hannunta guda Eyyah ta rik'e suka fara tafiya....dollars na zaune gefen suraj "tunda motar ta iso tayi parking ya tsareta da Ido yana kallo har suka fito dg cikin "ji yayi tunda yake da ita bata tab'a masa kyau irin yauba"sai yaga kamar duk ita mazan dake wajen suke kallo"kan idonsa ta rintse Ido har Eyyah taja hannunta suka wuce cikin gidan"ya lumshe Ido kawai....."kai tsaye Ababban parlourn gidan suka wuce"shima ba laifi cike yake da mata"su Amatallahi na gefe sunata kuka"ba k'aramin tausayi muslima taji ta bataba"daga sashen da ummah ke zaune da hijab Ajikinta suka iso suka zauna"ummah ta taso ta gaida Eyyah"Abin mamaki sai cewa tayi muslima dake Aka zo?"uhmm Ina kwana?"lafiya qlau "taso muje ki zauna wajensu Amatallahi"dato ta Amsa ta tashi tsaye suka wuce can ciki inda yara sa'anninta suke"kallon juna sukayi itada Amatallahi"saidai basu harari junaba kamar yadda suka saba Abaya"zama kawai muslima tayi"gaba d'aya parlourn yayi tsit"bayan wasu y'an mintinah Aka shigo d'aukar gawa dake can parlourn Abba"dollars da suka shigo da mutane sai y'an kalle kalle yakeyi sbd yaga ko zai gano mutuniyar tasa..... Aikuwa ya hangota zaune cikinsu Amatallahi fuskarta da Alamar tausayi"sai Akayi sa'a itama tad'an kallo mazan da suka shigo taga kota gansa ta b'oye sbd bataso yasan tazo"Aikuwa sai gashi idonta danashi sun sark'e"ta turo baki ta kauda kanta "shi kuma yana dai kallonta har suka nufi k'ofar aka fito da gawar"Anan fa Aka kama koke koke Aciki harda muslima"wanda Amatallahi data lura tayi mamaki"kasancewar mak'abartar kusa da gida take ba'a jimaba suka dawo"Anan Aka fara yiwa su ummah gaisuwa"bayan Eyyah sun koma gaisawa ta musu gaisuwa harda Mamy"itama muslima tasowa tayi ta musu gaisuwar"sannan ta koma wajensu Amatallahi ta kalleta tace sis ya hak'urin mu ?"Alhamdulillah! Allah yajikan Abba"ta Amsa da Ameen had'e da cewa Nagode "daga haka sukayi shiru"sai wajen k'arfe 11 Eyyah tace zasu tafi"Abin mamaki sai ummah cewa tayi Abar muslima nan idan badamuwa Anjima da yamma muslim zai dawo da ita gd"dato Eyyah ta Amsa "itadai muslima tayi mamakin umman"saidai batace komai ba..... Eyyah na fitowa dollars ya lura da babu muslima "kasa hak'ura yayi yataso yanufota yana fad'in tafiya zakuyi Eyyah?"Eh Amma wannan fitinanniyar nacan naja'atun tace Abarta da yamma ka maidota gida"ba k'aramin mamaki yayiba"musammun da yaga Ajiya tanata fad'a Akan yadena zuwa gidan da ita"Afili kuwa sai cewa yayi to Eyyah muje na taka miki"ah ah babban mutum koma kaje kayi zamanka ku cigaba da Amsar gaisuwa"bece komai ba yajuya cikin nutsuwa yakoma mazauninsa"yayinda Eyyah ta wuce ta shiga mota driver yaja suka tafi......tun wajen k'arfe 1 da wasu mintina Abinciccikan da dollars yasaka Ayi order daga manyan restaurant da hotels dan y'an zaman makoki suci  suka iso"da kuma  drinks masu sanyi"sannan cikin gida Aka damo fura Aka fiddo taji k'ank'aru"Abinka da masu hannu da shuni komai yayi waja waja

Awadace" tuni Aka fara rabama jamaa"dama kuma haka wasu keso"sunsan dole wajen Aci me kyau Asha me kyau tunda mamacin nada Alak'a da dollars"wajen k'arfe 2 ya shigo cikin gidan sbd yanaso ya tabbar da taci Abinci"gashi ba tsarki bane da ita zataso tayi wanka"yana rik'e da wata leda me d'an girma irinta shopping Ahannunsa
ya wuce cikin gidan"sai lokacin yaje ya gaida mamy yamata gaisuwa "kafin ya matsa yayiwa ummah gaisuwa itada danginta da suka zo"sai d'an kalle kalle yakeyi cikin basarwa sbd yaga koya hangota"Amma bbu Alamar tana'a main parlour d'in"can yad'an yi k'asa da murya yace"ummah Ina yarinyar nan?"inaga tana d'aki ko sallah takeyi"nan dai sukaci Abinci itada yaran.....wai yarinyar nan y'ar black beauty kuke mgn Hjy?cewar Anty Amira (k'anwar ummah)"Eh kawai ummah tace saidai shi gogan bece komai ba saima mik'ewa tsaye yayi yaji ummah na sanar mata k'anwarsace ce fannin mahaifinsa"kai gaskiya tanada kirki yarinyar ga son Aiki"kince na gyara bed room naki wlh itace ta gyara tanama toilet zata wanke na barota yanxun "iya nan dollars yaji yabar wajen yana d'an cije baki kasan ransa kuma murmushi yakeyi"fatansa Allah yasa komai ya canza ummansa taso muslima"sosai yaji dad'in Abinda tayi"saima lokacin yatuna be tab'a sakata gyaran d'aki ba "yana wannan tunanin ya turo k'ofar d'akin ya shigo"k'amshin turaren wuta yadaki hancinsa "yad'an lumshe Ido ya bud'e....muslima na'a toilet tana wankewa tabar k'ofar Abud'e"saidai taji sallamarsa ,ga k'amshin turarensa daya kai mata ziyara har cikin toilet d'in "tamkar tak'i fitowa sai kuma ta daure ta fito kanta na kallon k'asa bata yadda ta kallesaba"wayace ki kama yin wani Aiki?"babu kowa" kinci Abinci?"satar kallonsa tayi yana tsaye gefen mirror "sai lokacin ta lura da shaddar dake jikinsa"kina jiran na maimaita?"Amma yaya ba cewa kayiba bazan zoba kuma bak....sai tayi shiru "tuhumata kikeyi ko?"nafaci Abinci ,ta canza topic d'in"ya tab'e baki yana tunanin ko meyasa bata son kallonsa? ki d'auka ga wannan ledar nan kiyi wanka ki canza kaya"nima zanje nadawo"to Ina zakaje yaya Muslim?"inda kika Aikeni "kina mun mgn kina kallon wani waje sbd gulma"batace komai ba ta sunkuyyar dakai k'asa"ki d'auka ki duba"batace komai ba yanata kallonta ta jawo ledar ta fara dubawa"sabuwar doguwar riga ce jallabiya sky blue "sai ledar pad da sabuwar hand bag da pants guda biyu da bra....da sauri ta b'oye su tak'i fiddowa"duk yana kallonta sai kawai yanufi k'ofa"uhmm"yau yayi kyau daya saka manyan kaya....mgn kikeyi?"ah ah fa"hmm! cikin gulmar da kika fara koyo hadda tawa kikeyi"nifa yaya Muslim kaje dan Allah Anga ka shigo tun d'azun"banza yamata yak'i fita yama tsaya bakin k'ofar sbd Abud'e yabarta"kukan shagwab'a tasaka tana fad'in nidai katafi ko ?"ganin idan yaci gaba da tsayuwa tana wannan shagwab'ar da rigimar yanayinsa zai iya sauyawa sai kawai ya wuce Abinsa"yana fitowa ummah na kawowa zata shiga d'akin ,sbd jin shirun nashi yayi yawa"d'an shafa kansa yayi yace"kayanta na Amso mata wajen Eyyah sbd ta kirani tana so tayi wanka"to shikenan ka bari da yamma ka maida ita gida tunda ga yara nan zata sake cikinsu"to ummah bara naje"daga haka ya wuce yana jin zuciyarsa fess.... muslima kuwa Ajiye ledar kayan tayi ta koma toilet d'in "ta samu towels saita cire kayanta ta fara wankanta"bayan ta gama ta koma wanke toilet d'in tas sannan ta fito ta samu bbu kowa A d'akin"saita shirya Anutse "sauran kayan data cire ta saka cikin ledar"pad d'in kuma tasaka cikin hand bag d'in da wayarta"lokacin kuma k'arfe 3 tayi"tana k'ok'arin tama fito ummah ta shigo da sallama tana fad'in muslima harkin gama shiryawa?"Eh na gama"bara na baki turare ki saka ko?"dato ta Amsa"kanta na'a k'asa harta d'akko guda biyu ta matso ta mik'a mata "da hannu biyu ta Amsa tayi godiya"ita kuma ta juya ta fita"bayan ta gama shafawa ta Ajiye su saman mirror ta rufe k'ofar d'akin bayan ta fito"dama kina ciki inata nemanki?"taji

muryar Amatallahi"juyowa tayi ta kalleta kafin tace Eh wanka nayi"daga haka ta wuce taje ta zauna"tana lura da wasu mata nata yawan kallonta"ta kuma fahimci dangin ummah ne su.....sai wajen.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

.......Sai wajen gab da sallar magrib dollars ya shigo cikin gidan tare dasu daddy da Abbie"wanda tun kafin yashigo dasu saida yafara kiran ummah yasanar mata da zasu shigo"muslima na zaune inda sa'aninta suke ta hango dattijon kakan nata shida mahaifinta"sai dollars dake gefe ya canza kaya zuwa wani coffee brown d'in lallausan yadi me matuk'ar tsada "wanda ya haska farar fatar jikinsa"saidai kansa ba hula"yayi wani irin sanyayyan kyau"duk y'an matan dake zaune Awajen sai iyayi sukeyi sunaji inama inama....lolx"sai satar kallon mutuniyar tasa yakeyi yaga ta nuna kamar bata ganshiba, Abbie kawai tayima mgn"ko daddy bata tankaba sbd gudun karta masa mgn ya disgata cikin mutane"kan idonta ummah ta taso fuska Asake ta duk'a ta gaida Abbie yamata gaisuwa"kafin su gaisa da daddy"yayinda dollars ke tsaye duk wani motsin muslima yana lura dashi"can da zasu wuce suka had'a Ido da ita"da hannu yamata Alamar tazo "saita kauda kanta kamar bata ganiba"bayan fitarsu da mintina 3 farooq ya shigo cikin parlourn yana kallonta yace"yaya Muslim yace kizo"dato kawai ta Amsa sbd ganin idon mutane"bayan haka da bazata zoba"tasan k'ilan zaice tazo su tafi gida"ita kuma sai taji zaman cikin yaran yamata dad'i"tana wannan tunanin ta mik'e tsaye tana kallon Amatallahi da itama ita take kallo kuma ranta yabata muslima da dollars son juna sukeyi"zo muje ki rakani muje wajen yaya"ba musu ta taso suka jera suka fita"tana fitowa shi kuma yana k'ok'arin shigowa ciki....da sauri tayi baya sbd ganin zata fad'a masa"sai Akayi rashin sa'a k'afarta ta turgud'e kamar zata fad'i "yayi saurin rik'e hannunta guda"ita kuma ta rintse Ido.....saidai riketan da yayi yasaka ta bud'e Idon da sauri"sai suka nutse cikin nasa"ta turo baki cikin shagwab'a tace"shine yaya da kaja na fad'i ko?"meyasa bakya duban gabanki kina tafiya"nifa Allah Ina dubawa"shiru yayi sbd lura da Amatallahi dake tsaye Abayanta tana kallon su kamar TV....ki wuce ki d'auki kayanki kizo muje gida"yaya nifa ba yanzun b.....shiru tayi sbd irin kallon dayake jifar dashi da

idanuwansa masu kaifi da kwarjini"ita kuma ta shagwab'e fuska ta juya zata koma"kinsan Allah 2 minit na baki ki fito mu wuce kona b'ata miki rai "Amma yaya nifa ba tare dani kazoba kuma....nufo tan da yayi ya saka taja da baya Atsorace har tana bige Amatallahi dake bayanta"shi kuwa d'an murmushin gefen baki yasaki wanda wacce yayi dan ita bata ganiba sai Amatallahi "wacce tunda take bata tab'a ganin yana murmushi ko dariya ba"sai taga ada beda kyau sosai bisaga yanzun da taga yayi murmushi"sai ya mata kamar Aljani sbd kyawun da yayi"ga hakwaransa farare k'al daga tsakkiyar na k'asan Akwai wushirya"lallai muslima taji dad'i " da har yake sonta....sis muje mana"taji muryar muslima najan hannunta"yayinda tuni dollars yabar wajen"ya Isa parking lot yasanar da driver yagyara parking su wuce.....fuskarta bbu Alamar jin dad'i ta shigo cikin parlourn "kai tsaye ta wuce d'aki ta d'akko ledar kayanta ta Isa wajen ummah kanta Ak'asa tace"ummah zan tafi inji yaya"d'an murmushi tayi tace"to shikenan mun gode sosai Allah yabada ladar muslima"daga haka ta wuce sukayi sallama da Amatallahi kafin ta fita"dukda gab da magrib ne Amma haraban gidan cike yake da maza"tamkar ta fad'i haka taji sbd ganin Anata kallonta"lokacin data iso bakin get harma mutumin nata ya shiga mota"sai cin magani takeyi ta bud'e back sit ta shiga bata ko kallesaba"shi kuwa yana binta da kallon k'asan Ido yana duba wristwatch d'insa "yarasa meyasa yanzun ta shirya itada Amatallahi?"yaya kagani kaja ban Amshi contact d'in kawata Amatallahi ba"tamkar ya shareta sai kuma yatab'e baki yace"kin iya kalan dangi yaushe har tazama k'awar taki keda kuke fad'a da ita? shiru tayi tak'i mgn sbd ba k'aramin haushi yabata ba"shima dama ba wata doguwar fira yake da itaba saiya shareta"Aransa yana murmushi da irin darun yarinyar"suna isowa gidan driver yayi parking tafara k'ok'arin kiciniyar fita"Amshi nan"taji Amon jarumar muryansa me dad'in sauti "saida ta turo baki kafin ta juyo taga meye zai bata?"da mamaki ta kalli keys d'in sannan ta maida kallonta Asaman kyakykyawar fuskarsa daya d'an saki bbu d'aurewar daya saba yi"shima kallonta yakeyi bece komai ba"na meye ne?"bazaki karb'a bane? batayi mgn ba ta Amsa "keys d'in d'akina ne dake  part d'in Eyyah"kije ki gyaramun tunda ke ba sallar kikeba"inaso kafin nadawo daga masjeed kin gama"da sauri ta kalli gefen driver taga ya fita"saita turo baki tak'i mgn ta fito"ta rasa meyasa motsi kad'an zai wani ce bata sallah ko inama ruwansa?"tana wannan zancen zucin ta iso sashen Eyyah"Abin mamaki ta sami yaya sadam yaka mata ziyara sunata fira da Eyyah "gefe guda kuma husnah da suraj na zaune suma suna tasu firan....to! kaga gashi tama dawo kai me cewa tafiya zakayi kayi sallah daga can ka wuce gida ko?"cewar Eyyah "itadai muslima data shigo da sallama zama tayi tana Ajiye ledar kayanta gefen kujerah tace"sannunku Ina wuninku?"lafiya qlau"yaya sadam kwana 2?"saida yad'an kalleta kafin yace"Alhamdulillah "idan Ankira ki Ai bakya son d'auka ko?"bafa haka bane bana kusa"hmmm! yasu hjy?lafiya qlau tana gaidaki"tun d'azun kazo kenan?"ah ah banjima ba Eyyah tace kinje gidan gaisuwa ko?"yak'are maganar yana mik'ewa tsaye sbd ganin lokacin sallah yagabato"Eyyah da suraj na lura da yadda yaketa bin muslima da wani irin kallo me kama dana SO"badai tafiya ba?"bara naje nayi sallah"to saika dawo"duk suna maganar ne shi yana kallonta ita kuma bashi take kallo ba"nima bara na bika muje"cewar suraj yana murmushi da Ido yama husnah Alamar zasuje su dawo"ita dai murmushi kawai tayi"bayan fitarsu muslima tace"sis yasu Anty?"sai yanzun kika ganni?"to Ai naga gaba d'aya hankalinki na wajen yaya suraj"harara ta ballah mata tana fad'in kin manta"gaba d'aya sukayi dariya"Eyyah tace husnah tashi kije kiyi sallah "dato ta Amsa gaba d'aya suka nufi d'akin baccin Eyyah"muslima ta Ajiye kayanta ta sanarwa Eyyah zataje ta gyara masa d'akinsa.....Ahankali ta saka key d'in ta bud'e

k'ofar d'akin "sanyayyan k'amshin turarensa me dad'i d kashe jiki yafara dukan hancinta"set d'in had'ad'd'en bed irin na k'asar dubai ne Adak'in kalar milk, sai sofa da kujerah 3 seeter ,sai wani tsadaddan carpet me uban laushi daka Aza k'afarka zata lume Aciki "daga gefe guda kuma k'ofar toilet ne"saman bed d'in devut ne kawai shimfid'e.....ni banga Abinda d'akin nan yayiba shine zai wani ce ki gyaramun d'akina kafin nadawo"ta k'are maganar cikin kwaikwayon muryarsa tana fara k'ok'arin kakkab'e kakkabe "saida ta fara share d'akin sannan tayi mopping ta canza bed sheet"saida tayi Addu'a sannan ta shiga bath room d'in "tana shiga tayi cin karo da boxes d'insa kala biyu Arataye da Alama sauri takeyi ya barsu ba'a wankeba"ba k'aramin kunya tajiba"ta kauda kanta ta fara washing toilet d'in Agaggauce sbd bataso yashigo tana d'akin "gashi kuma sadam yace zai dawo idan yayi sallah"bayan ta idar ta wanke hannunta ta fito ta rufe k'ofar d'akin ta zare key d'in"Aikuwa tana shiga cikin parlourn ta sami suraj da sadam sun dawo sunata fira, yayinda Eyyah da husnah ke d'aki basu kaiga fitowaba"zoki zauna nan kiji wata mgn "yafad'a yana nuna mata daga gefensa"saidai kafin muslima tayi wani k'wak'wkwaran motsi dollars ya shigo cikin parlourn da sallama cikin k'asaitacciyar muryarsa"sarai yaji kalaman sadam"hakan yasa ya had'e girar sama data k'asa fuskarsa babu Annuri "ko kallon gefen da sadam ke zaune beyiba, cikin Isa da izzah ya zauna kan kujerah"Abokinah barka da shigowa"cewar suraj"da yauwa kawai ya Amsa yana satar kallon Muslima da har lokacin take Atsaye"yaya Muslim Ina wuni?"cewar husnah tana kauda kai"sbd bata son tana yawan ganinsa sbd jin sonsa takeyi nadawo mata Aranta "ya d'auki kusan second 5 kafin ya Amsa da lafiya qlau "yallab'ai Ina wuni ya hak'uri?"cewar sadam yana jin yamasa wani irin kwarjini"ba tare daya sami Arzik'in ya kallesaba yace Alhamdulillah da k'yar yana danne kishin dake taso masa"k'asan zuciyarsa yana mamakin beda mutuncin da muslima zata masa sannu da zuwa?....mik'ewar da sadam yayi tsaye yasaka yasaci kallonsa Adaidai lokacin dayake cewa"muslima muje ki takamun"haka nan taji kirjinta ya buga!"ta saci kallon mutumin nata"Aikuwa ya wurgo mata wata iriyar harara ya wani sha mur yana fad'in kin gama Abinda nasakaki?"Eh na gama"jeki d'akin cikin lokar bed side wata leda na nan kikamun"lura da yadda yaketa shan k'amshi yana hura hanci yasaka ta kasa masa musu"yayinda sadam yaji zafin Abin Aransa"dama beji dad'in yadda ya Amsa gaisuwar tasaba"saidai Aganinsa sbd yanada dukiya yake ganin zai iya taka kowa"toko meye be isa yarabashi da y'ar uwar saba"yaya sadam Ina zuwa"okay ki sameni Awaje"daga haka yayima suraj sallama beko kalli gefen da dollars yakeba yafita"tana barin parlourn dollars ya mik'e tsaye yabi bayanta"sbd yana so ya nunama sadam cewa yafishi iko Akanta"suraj ya sauke numfashi yana sakin wani shed'anin murmushi,sbd yadda yaga fuskar dollars da tashin da yayi yabita kawai yabashi Amsar Abinda yajima yana zato Aransa "yaji kuma matuk'ar dad'i"ya tabbatar idan dollars ya mallaki muslima Amatsayin matar Aurensa sai Hjy jamila ta kusa k'aramin hauka"musammun tunda yasan burinta dollars ya Auri malika.......yana isowa bakin k'ofar d'akin yaga tabar key d'in Ajiki"da sauri yajawo k'ofar yasaka key ya rufe yayi tsaye"yana Anan yaji tanata jijjigar k'ofar Amma Arufe "can kuma yaji shiru"securities ya kira ya tambayesu sadam ya tafi?"sbd ya misalta kamanninsa da irin motarsa daya gani fake Awaje"sukace yanzun yatafi"sanar musu yayi karsu koma barinsa shigowa cikin gidan daga yau in har yakoma zuwa"yana kashe wayar ya matsa ya bud'e d'akin"tana zaune k'asa kan carpet tanata sharb'an kuka "sbd ranta yabata shine yazo ya rufeta sbd karta fito suyi mgn da sadam"saidai ta kasa gane miye dalilinsa na Aikata hakan?"tasan dai iya iyawarsa yana kulawa da ita saidai batasan meyasa yake son b'ata mataba....jin motsin ya

bud'e k'ofar yasaka ta d'ago kanta idanunta shab'e shab'e da hawaye ta hangesa tsaye fuskarsa bbu Alamar rahama Acikinta"bata dena kukan ba ta mik'e tsaye kawai ta wuto ta gefensa bata tanka shiba ta fara k'ok'arin rab'ashi ta wuce"da sauri ya tare bakin k'ofar murya bbu Alamar wasa yace sbd  bakije wajen shashashan canba shine kike kuka?"wani irin ihu ta saki had'e da gunjin kuka tasaka hannuwanta duka tana turashi daga gabanta"saidai yayi tsaye k'ik'am kamar bashine take turawaba"yadai tsareta da shanyayyun idanuwansa da suka fara canza launi sbd kishi"yanata kallonta kawai"saidai ita ba kallonsa takeyiba"ganin yadda taketa masa ihu yasaka ya fisgota gaba d'aya ta fad'o jikinsa kawai taji ya rungumeta  Atsakkiyar faffad'an k'irjinsa "ni yaya ka cikani dan Allah! ta fad'a cikin muryar kuka"bari nayi ki gama motsa jikin naki saina cikaki shiyasa"tayi shiru tanata kiciniyar k'wacewa"wai meyasa bakya jin mgn halimatu?"ya fad'a da wani yanayi Amuryarsa "idan kinaso na barki ki tafi kiyi shiru"da sauri ta dena kukan sai Ajiyar zuciya datake saukewa A jajjere"yaya shine ka rufeni ko?"to meye zakije kiyi masa?"kinsan dai ban son shashanci ko?"yak'are maganar yana cikata"da sauri tayi k'ok'arin tafiya"kije ki wanke fuskarki"batace komai ba ta nufi toilet ,bayan ta wanke ta fito ta samesa zaune saman sofa yana danna waya"zonan! da gudu ta fita daga cikin d'akin "ya girgiza kansa kawai"tashi yayi yarage kayan jikinsa ya watso ruwa" be jimaba Adak'in yafita sbd yayi sallar isha'i"lokacin daya dawo daga masjeed d'in tana kwance kan 3 seeter da Alama har wanka tayi tana jin sallamarsa ta masa banza sbd ba k'aramin haushi yabata d'azun ba"shima yadawo ne sbd yaga kota dena fushin dashi sai yaga Alamar bata dena ba"sai d'aure fuska takeyi"shi kuma jin kansa ya hanashi tankata "kawai saiya wuce dining area yaje yafara dinner"waina ce ta farar shinkafa da miyar taushe"ga gashashshen naman rago da kifi gashashshe"saida yayima cikinsa k'at sannan yatashi yana juyo dariyar muslima itada Eyyah yatab'e baki kawai yayi gaba Abinsa"tare dashan Alwashin Ai gobe zataso ta bishi suje gidan gaisuwa ko?"da tunanin y'ar rigimar tasa yayi shirin kwanciya bacci yana tuna d'azun da zai shiga sashen daddy yanaji Hjy jamila nasanarwa Malika bataje gidan gaisuwar ba wani waje ta tafi ta nunama daddy taje kawai"suna ganinsa sukasha jinin jikinsu"sai yayi d'an murmushi ya gaisheta ya wuce kawai"shidama beson taje"idanma zuwanne yafiso ummi taje"yasan itama kilan gobe zataje"da wannan tunanin bacci me dad'in gaske ya d'aukesa.....washe gari be fito da wuri ba"sai wajen k'arfe 10, sbd da Asuba yajima A online suna mgn da mutanansa game da kasuwancinsa" kuma yanzun yanaso idan yafita yaje office nashi"ga bacin ran Hjy zarah data damesa da kira ta waya bayan ba wani abu me mahinmanci ne yasaka ta kiran nashi ba"yana sanye da suit red colour yayi wani irin sihirtaccen kyau"saidai fuskarsa bbu walwala "yana doso parlourn Eyyah yaji sautin muryarta tana cewa"to Eyyah ba gidan gaisuwar zamujeba nida yaya muslim shiyasa na saka hijab dayazo basai ya jiraniba saimu tafi "d'an murmushin mugunta ya saki yana cije baki ya shigo Anutse yana koma tamke fuska"yaya Ina kwana?"kallonta yayi cikin second 5 kafin ya d'auke kansa yak'i Amsawa duk Eyyah na lura dasu"ba k'aramin shak'a muslima tayiba"tana sanye da riga da siket na Atamfa super me Adon flowers da colour d'in black and purple"tana sanye da hijab tiyebo purple iya gwiwa,wacce taji guga tana d'aukar Ido"bayan ya zauna gefen kujera ya gaida Eyyah"sannan ya wuce sashen Abbie suka gaisa"koda yadawo Lipton kawai yasha yabaro dining area d'in"itadai Eyyah na zaune dama har ranta batason zuwan na muslima.....ganin zai fita yasaka tayi saurin cewa yaya Muslim na taso muje??.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa ban yafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

.....Cike da basarwa dollars ya juyo yad'an kalleta yana fad'in Ina kenan?"yo yaya gidan gaisuwar mana"ban tsara zuwanki Ayau ba"Amma fa harna shirya ko?"banza yamata kamarma be jiba yasa kai yafita yabar mata daddad'an k'amshin turarensa"kuka ta fashe dashi ta kwanta saman kujera harda shashsheka"da mamaki Eyyah ke binta da kallo tare da cewa lallai Abin naki me girmane"indai babban mutum ne kikace zakiyi ta kuka sbd takaicinsa Tofa yanzun kika fara"in ba shirmeba miye Amfanin zuwan naki yau?"tunda munje jiya kin musu gaisuwa kuma har kin yini Acan sai kuma dole kice yau kije....tana cikin maganar Abbie yafito daga cikin parlournsa yana kallon muslima yace"meya faru kuma take ihu haka?"itada babban mutum ne ! sbd yak'i zuwa da ita gidan zaman makokin....ni wlh babu ruwana dashi Abbie ka zama shaida ni ban had'a komai dashi ba"kuma gidan Hjy zan koma"ta fad'a cikin muryar kuka "Eyyah ta d'aure fuska zata yimata mgn"Abbie na murmushi ya girgiza mata kansa Alamar karta yi,kafin yace"to shikenan ba matsala"naji baki had'a komai dashiba"nifa meye kika had'a dani?"kaima ban had'a komai dakai ba ko?"ta fad'a cikin turo baki tana tashi tabar parlourn ta koma d'akin Eyyah..... dollars kuwa dama yasha Alwashin tunda tayi kuka da fushi dashi sbd wani banza saita san ta masa haka "yana driving d'in yana tuna baby face nata da d'an mitsitsin bakinta datake yawan turowa da yima mutane masifa dashi"Ahaka ya iso office yayi Abinda zaiyi kafin ya d'auki hanyar gidan ummah"sbd yau be nemi driver ko body quards nasaba musammun jiya dayaga mutane nata kallonsa gidan gaisuwar"bayan ya iso yayi parking A haraban gidan yafito"Atake mutane suka masa caaa! shi har mamaki yakeyi"sai gaidashi Akeyi da masa gaisuwa"saidai ya Amsa wasu yad'aga musu hannu "Aransa yayi murmushi kawai yana tuna yadda rayuwa ta zama"sai kanada shi kowa keyi dakai"wasuma sun haifesa Amma sbd yanada dukiya dubi yadda suke masa"Acan ya hango suraj Agefe,kusan Atare suka shiga cikin gidan "Anan babban parlourn gidan suka sami ummah itada sauran danginta zaune suna cigaba da karb'an gaisuwa"tunda suka gaisa ta fahimci ba tare da muslima yazoba "saida taga zai tashi tsaye daga duk'iyar da sukayi Agaban ta shida suraj"kafin tace"Ina kabaro muslima yau ko barata zoba ne?"yayi mamakin tambayar ta ummah Amma sai bai nunaba yace "tana gida ,yanzun haka fushi takeyi sbd nace yau barata zoba"be rufe bakiba Amatallahi itama data lura

dashi kuma bataga muslima d'in ba tayi saurin cewa yaya Muslim Ina muslima?"tana gida"yabata Amsa Atak'aice yana mik'ewa tsaye suka fita shida suraj"suna fitowa suraj yace"bakada kirki dollars "Abinda kayiwa sadam jiya ka kyauta?"wani banza kallo ya watso masa kafin yace dani dashi waye naka Acikin mu?"suraj na murmushi cikin tsokana yace shi"banza yamasa yak'i tankasa "yanzun dai kasaka a d'akko muslima tunda kaga Anata tambayarta sbd mugunta shine ka hanata zuwa ko?"hmm? nasan yanzun haka kuka takeyi tanata fushi bana zaton ko nace Aje a d'akkota zata yadda tazo"toka kirata mana"beyi mgn suka wuce wajen zamansu yana k'ok'arin kiranta"saidai harta fara ringing  ta tsinke bata d'aukaba"yakoma kira still bata d'auka ba "daga bisani ramadan ya kira yasanar masa komai yakeyi ya Ajiye yaje sashen Eyyah muslima nacan yasanar mata ta fito zai kawota nan gidan gaisuwar"suna gama wayar ya kashe yana tunani"yasan idan ba ramadan d'in yaturaba da wuya ta Amince ta biyo driver yakawota..... muslima kuwa tana ganin kiran nasa ta masa banza tayi kwanciyarta saman bed d'in Eyyah"ba k'aramin haushin dollars tajiba tsakanin jiya da yau"tana kwance tana chats sbd d'eb'e kewa Eyyah ta shigo cikin d'akin ta kalleta tace"kije inji ramadan"toni Eyyah meye zan masa?"ban saniba baza kije bane?"batace komai ba kamar zatayi kuka ta d'auki hijab nata ta saka ta fito rik'e da wayarta Ahannunta...yana tsaye a parlourn yana danna waya "sallamarta da yaji yasaka ya kalleta fuska bbu yabo bbu fallasa yace"yaya ne yace kizo muje na kaiki gidan gaisuwa"ni Allah yaya Ramadan bazan jeba"d'azun....kinada hankali muslima?"koni bana iya kallon tsabar idon yaya na masa musu saike zaki yi?"zaki wuce muje ko saina mammareki?"juyowa tayi taga Eyyah zaune tana kallon su da saurarensu bata tankaba"shi kuma fita yayi"Eyyah kinga yaya Muslim ko?"kiyi hak'uri ki saka takalmi kije yana jiranki"batace komai ba zuciyarta ba dad'i taje ta d'auki plate shoes d'inta ta saka ta fita"Eyyah ta sauke Ajiyar zuciya "Ada da Abbie ya sanar mata ya fahimci babban mutum nason muslima ta d'auka kawaidai yayi hasashe ne Amma yanzun ta yadda sonta yakeyi bedai furta ba"Amma kuma ita bata sonsa"Ayadda ta fahimta "Allah ya zab'a musu mafi Alkhairi"ta fad'a Afili ".....tunda ta shiga motar har suka d'auki hanya suka iso gidan muslima bata tanka yaya ramadan ba sbd shima haushi taji yana bata"kasancewar ta saka face masks a hand bag nata"yana gama parking ta fiddosa ta saka sannan ta fita"cikin nutsuwa take tafiyar tata tamkar me tausayin k'asa"idanuwanta sun k'ara girma ,sunyi d'an ja sbd kukan datayi"tana kallon Ramadan yanufi inda dollars da suraj ke zaune ta tab'e baki ta wuce cikin gidan"dollars yabita da kallo Aransa yace"*my dubulle y'ar rigimata*......kamar yadda yayi Ajiya yauma haka yayi bayan ya fito daga masallaci ya shigo cikin gidan sbd yaga gimbiyar zuciyar tasa taci Abinci"saidai ganin bbu ita Acikin parlourn yasaka ya nufi d'akin baccin umman"Aikuwa yasami muslima tayi d'aid'aiya saman royal bed d'in umma tanata baccinta hankali kwance"ga hijab nata da hand bag nata gefe"d'an kwalin kanta shima na gefen wuyanta da Alama cikin bacci yacire"dogon gashin kanta data d'aure yazubo saman gadon bayanta"ba k'aramin kyau baccin yama taba"besan lokacin daya furta ita kuma yau da y'an bacci tazo?"Eh wlh naga tanata hamma nace tazo ta kwanta"sai yanzun dana shigo nayi sallah naga tayi baccin"cewar ummah dake zaune saman prayer mate"saima Asannan dollars ya lura da ita"sbd tunda ya shigo cikin d'akin Akanta idanununsa suka fara sauka"d'an shafa kansa yayi ya rissinar tare da cewa taci Abinci?"Eh sunci itada Amatallahi"dato ya Amsa ya fita"koda ta farka saida tayi wanka ta maida kayan dake jikinta ta gyara saman bed d'in kafin ta fito parlourn.....da yamma da ummi da siyama da suka zo zasu tafi sai muslima tace zata bisu sbd batama so tabi dollars "Akan

idonsa suka fito suka shiga mota"hakan yatabbar masa da cewa ba k'aramin k'ullatarsa yarinyar tayiba Arantaba "......

bayan sallar isha'i yana zaune a parlourn Eyyah yana shan coffee muslima tayi sallama ta shigo"saidai tana ganinsa zaune tayi saurin juyawa tabar parlourn"duk yana lura da ita sai yayi kamar be ganiba"washe garin ranar yakama ranar Ake sadakar ukku"tunda sassafe data je ta gaishe dasu Eyyah bata koma zuwaba sbd bataso taga dollars "tana break fast ya shigo shashen su cikin zazzafan wankansa zai wuce ya gaida daddy"tana ganinsa ta d'aure fuska ta kauda kanta"Malika dake zaune a parlourn tana lura"tana ganin haka tafara iyayi wajen gaida dollars "ya Amsa mata Adak'ile ya wuce"Aikuwa muslima ta dinga b'abb'aka dariya domin ta lura Malika taji kunyar yarfawar daya mata "K ! da ubanwa kike wannan dariyar banzar da kikeyi?" muslima bata fasaba tace da uban wanda ya tsargu"kina nufin ubana kenan?"banza ta mata ta tashi tabar mata parlourn gaba d'aya.......

*3 days a go*

kimanin kwana ukku kenan muslima na wasan y'ar b'uya da dollars"tun yana d'aukar Abin shirmenta ne har Abin yafara damunsa"gashi sunday zai bar k'asar tunda har Abba yayi sati da rasuwa"shi ko bata masa mgn ba,tama bari yadinga ganinta "sau tari bata zuwa inda tasan zata gansa"idan kuma sun had'u zata bar wajen"ko wannan shagwab'ar tata datake masa koyiwa Eyyah duk yayi missing ji "ko jiya dayaje gidan ummah saida ta tambayesa tana Ina?"yace mata tana nan kawai"Acikin kwana 3 zuwa hud'u har yayi y'ar rama"saidai Asafiyar yau daya kama satday da y'ar walwala dollars ya tashi sbd gobe ne ranar bath day d'in muslima"yana so kuma yau ko yaya yasakata farin ciki "tun wajen 10 na safe yabar gidan sai wajen 12 pm yadawo rik'e da wani k'aton cake na musammun dake cikin ledarsa daya saka cikin wani had'ad'd'en kwali"be bari kowa ya d'aukar masaba da kansa ya d'auka yanufi sashen Eyyah dashi ya samu tana kitchen "saidai bbu Alamar muslima na'a shashen,hakan yasa ya wuce sashensu"da nufin yaga ko tana can"sai Akayi sa'a yana shigowa ita kuma tana fitowa daga cikin d'akinta"tana sanye da doguwar riga ta material d'inkin bubu"sai siririn mayafi data yane kanta dashi irin kalar zanen material "tanata k'amshin humrah da body sprays masu dad'i"yazun hannayenta sunji jan lalle datayi jiya"tana ganinsa gabanta yafad'i! ga wani irin bugawa k'irjinta nayi"ba k'aramin kyau k'ananun kayan dake jikinsa taga sun masaba"koma fad'uwa gabanta yayi,musammun dataga yana doso inda take"sai kawai ta tsaya cak! ta jingina Ajikin bango tana satar kallon kabeer da Hjy jamila da suke zaune cikin parlourn suketa kallon dollars da Abinda ke hannunsa"Ada tayi niyar juyawa ta koma Amma sbd ganin mak'iyanta Awajen saita tsaya harya iso"da sauri tace"yaya Ina wuni?"uhmmm! keda ke fushi dani"yak'are maganar yana tsura mata kyawawan idanuwansa"ta sunkuyar dakai "Sam su Hjy jamila da suka kashe kunne suji meye suke fad'a basujiba sbd daga ita harshi k'asa k'asa suke maganar"mik'a mata kwalin cake d'in yayi yana fad'in happy birthday in Advance! d'an ware Ido tayi murmushi na sub'uce mata ta Amsa ta bud'e tana fad'in wow"shidai yana tsaye yabada bayansa yana kallonta"su Hjy jamila basu ganin fuskarsa sai bayansa "tsabar murna muslima bata san lokacin data Ajiye kwalin cake d'in ba tasaki ihun murna ta rungumesa tana fad'in thank you so much my sweet yayanah!......wani irin electric chock dollars yaji Adukkan illahirin sassan jikinsa"sbd wannan karon ne na farko daya bari wata mace ta masa irin wannan rungumar"sbd rungumar me zafice ta shige jikinsa sosai ta mak'alk'alesa tana murna"yamata Alkhairi Arayuwa dayafi wannan Amma Ayau jitakeyi

yafi kullum faranta mata"ta d'auka itace kawai tasan gobe ne ranar zagayowar haihuwarta Ashe shima yasani....shidai ya d'an rintse Ido yana sakin d'an tak'aitaccen murmushi na dole sbd shine kawai yasan meye yakeji Ajikinsa"ko rannan daya rungumeta beji Abinda yajiba Ayau..... innalillahi wa inna ilaihir raju'un! duniya Ina zaki damu?"dama muna jin labari sama sama gashi mun gani Azahiri"Agabana bbu kunya ba tsoron Allah zaki kamasa ki rungume haka?"da sauri muslima tadawo nutsuwarta tsabar farin ciki yasaka bata d'auki Abinda tayiba wani Abu marar kyau"da sauri ta cikasa"shidai yana kallonta batare daya damu da kalaman Hjy jamila daya jisu kaf ba"yasan tunda hassada da k'iyayyarsu takeyi dole ta fassarasu da hakan"kan idonsa muslima ta d'auki cake d'in fuskarta da Alamar rashin jin dad'in maganganun Hjy jamila "gashi ta rasa meyasa taji kunyar ta koma kallonsa?"miye Amfanin ki damu bayan kinsan ba haka bane Aranki?"tattausan muryansa ta katse mata tunani"tad'an kallesa hawaye na ciko idonta tace"dama yaya ko kwanaki ba haka malika ta dinga fad'in irin wa'annan maganganun ba, da cewa har kwana nakeyi wajenka....shiru tayi sbd jin muryar daddy yana fad'in Ina y'ar iskar take?"nina san my friend yaron kirkine itace zata rungumesa ta b'ata mun yaro.....gaban muslima yafad'i ta d'ago kanta ta hango daddy tare da Hjy jamila suna k'ok'arin isowa inda suke tsaye"dollars na tsaye cike da b'acin rai yana tunanin wace irin zuciya ce da Hjy jamila?"ganin isowar daddyn wajen ga muslima tafara kuka yasakashi saurin kallonsa yana girgiza kansa yace"daddy kadena yadda da Abinda za'a sanar maka bayan baka binci kaba"kana nufin k'arya nayi kenan?"cewar Hjy jamila "wani mugun kallo irin na tsana dollars yajefeta dashi ya kauda kai"Adaidai lokacin daddy yace nagaji da mugun halin y'ar iskar yarinyar nan "gara na koreta tun kafin tafara kama mazan layi ta d'akko min mgn"haba daddy! inma laifin me nine keda laifi sbd nine na rungumeta sbd murnan zagayowar ranar haihuwarta"ka dena yadda da duk me kawo maka zuga sbd Ashiga tsakaninka da y'arka"ke kuma wlh kiji tsoron Allah Ina jiye miki ranar tonon Asiri"yak'are maganar yana kama hannun muslima yace"zo muje"kukan munafurci Hjy jamila ta fashe dashi yayinda daddy yakasa mgn"yanzun Alh ka yadda kenan?"tsaki yaja yace"daga yau karki koma sanar mun Abinda ban tambayeki ba daga haka ya wuce samansa ransa Ab'ace.....

suna fitowa yanufi cikin lambun gidan da ita"be cika hannuntaba saida suka iso inda gras carpet yake"sannan yaci kata ya zauna" d'an nesa dashi ta zauna tana Aza kwalin cake d'in saman cinyarta"tafara k'ok'arin share hawayenta....sai kallonta yakeyi yana jin tamkar ya janyota jikinsa ya rungumeta ya rarrasheta"Anutse yafara maganarsa me cike da iya tsara lafazi kamar haka"daga yau komai Hjy jamila zata fad'a Akanki ko Akaina ko kuma Akanmu gaba d'aya bance ki damuba balle harki zubar da hawayenki taji dad'i"ita kuma Malika data cika marar kunya Agabana yaka mata ta fad'i hakan ,dana mata tunin ko ita wacece "saidai lokaci zai bayyanar da hak'ik'anin gaskiya" ita rayuwar mutum ba'a so ta yuyu babu mak'iya! Iya Abinda nasani saida mak'iya Ake samun nassara"shikenan yaya nagode"bece komai ba hankalinsa na wajen wayarsa da sadeeq ke kiransa saidai yarasa meyasa jikinsa yak'i bashi ya d'auki wayar?"saima mik'ewa tsaye yayi sbd yanaso yaje yad'an kwanta tunda ya shawo kan y'ar rigimar tasa"yayaaa! juyowa yayi suka had'a Ido"dama Ina keys d'in shashenka dana d'akinka dake b'angaren su Eyyah??"beyi mgn ba yazaro keys d'in sashensa ya mik'a mata tare da cewa zanje can d'akin na kwanta"idan kingama da can zan baki na shashensu Eyyah d'inko"tunda yanzun kin huce kin dena gudun had'uwa dani "shiru kawai tayi tana Amsar keys d'in sbd bata san meye zatace masa ba"iya Abinda ta sani yafaranta mata ya goge haushinsa

data keji Aranta ,shiyasa itama ta zab'i faranta masa Ayau"lura da ta tafi duniyar tunani sai kawai yatafi Abinsa"shida yatafi sbd ya kwanta yayi baccin Amma yakasa baccin"daya rufe Ido yadda muslima ta rungumesa yake gani"ga b'acin rai da damuwar sharrin da Hjy jamila taso ta musu"ya b'oye mata damuwarsa game da Abin sbd karta damu Amma Abin yab'ata masa rai "shin yanzun yaya zaiyi ya tunkari muslima da zancen irin soyayyar dayake mata?"shi damuwarsa kar tak'i Amincewa ,idan zata Amince bazai damuba zai iya sanar mata"yanaso ya Aureta yabata gata da kulawa had'e da farin ciki"kai yama d'auketa subar k'asar gaba d'aya sai Ammaso Aganta"gaba d'aya sai yaji beson tafiya goben ya barta"yajima yanata juye juye da tunane tunane har k'arfe 1 na rana tayi"hakan yasa yatashi ya shiga wanka ,bayan yafito ya shirya cikin milk d'in jallabiya yafito da nufin yatafi masallaci"A babban parlourn su Eyyah suka had'u"ita zata shigo shi zai fita"had'a Ido sukayi ta sunkuyyar dakai"kin gama ne?"uhmm"to sannunki"canza topic d'in tayi da cewa wancen d'akin Abud'e yake?"ta k'are maganar tana bashi keys d'in "Abud'e yake Amma ki bari ki huta saiki gyara"ya k'are maganar yana Amsar keys d'in "nide bangajiba yaya Muslim zan gyara "kuma dan Allah kasaka Awanke motar can ko?"tayi maganar cikin shagwab'a" Ina zakije?"Anguwa"batada suna?nidai ba driver zaya kainiba.....ganin idan yabiyema sauraron wannan shagwab'ar tata Alwallah d'insa zata iya karyewa sai kawai ya fita Abinsa bece komai ba.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

........bayan fitar dollars daga cikin parlourn ta wuce d'aki ta sami Eyyah na sallah"hakan yasa ta zauna tana tina Abinda yafaru d'azun,bayan ta idar ta kalleta tace"kukan meye kikayi?"kanta Ak'asa ta shiga sanarwa Eyyah Abinda yafaru"bayan ta gama ta saka mata wani sabon kukan tana fad'in na rasa meyasa mahaifina baya k'aunata sai Aibatani dayake yawanyi koda yaushe Eyyah??"ki dena kuka kinjiko?"in sha Allah kukanki yazo k'arshe "cewar Eyyah cikin jin zafi da rad'ad'in Abinda yafaru"shiru kawai muslima tayi tana mamakin kalaman Eyyah "saidai ranta yabata wani mataki zasu d'auka....Ina babban mutum d'in?"yatafi masallaci inaga"d'akinsa ma zanje na gyara masa"dato kawai Eyyah ta Amsa ita kuma ta tashi ta fita.... dollars koda ya gama sallar kiran gaggawa yasamesa a office"hakan yasa yana dawowa gidan ya wuce

sashensa sbd yacanza kaya"tunda yabud'e k'ofar parlourn ya shigo k'amshi ne ke dukan hancinsa irin na turarukan wuta dana Air frishners ga kuma irin nasa k'amshin dake zaune daram A sashen nasa"komai yayi k'al fas dashi"my dubulle nah tasha Aiki dai sosai"yafad'a da d'an murmushi saman fuskarsa,yana kallon wajen tv stand daya san wajen yayi y'ar k'ura Amma gashi yanzun k'al yana d'aukar Ido"koda yashiga bed room d'inma shima komai gyare k'al"ga kayan gugarsa da aka kawo ta jera masa"harda turaren kaya tasaka masa cikin kayan nasa"saida yafara duba kayan dazai saka ya lura da wasu duwatsu kamar turaren wuta ,saiya d'auka ya shinshina yaji k'amshi "murmushi me fad'i yasaki"tunda yarinyar tafara wayo har taso fara rainashi bata tab'a faranta masa irin yau ba"inama ta d'ore haka"yafad'a Afili yana rufe ward rope d'in "Anutse ya shirya cikin t shirt red da farin wondo  jeans ya Aza pasin cape"kafin ya d'aura Agogon fata fara yasaka takalmi  chukka boot farare"uhmm ! idan Ana sallah ba'a mgn"sosai yafito a young bolonia d'insa "wayoyinsa daketa ruri sun damesa be d'aukaba ya d'auki key d'in wata tsadaddar sabuwar motar daya siya kwana 2 da suka wuce"waccan dayake matuk'ar so yabarma muslima baidai kaiga fad'i ba"sbd yasan duk wanda yaji yabata kyautar motar nera million 80 dole yayi mamaki Amasa wani zato"yanzun yanaso suje ummarah ta maulid dashi da ita da suraj da husnah"yana wannan tunanin ya fita daga cikin d'akin yanata zabga wani irin fitinannan k'amshi....cike da nutsuwa yake tafiyarsa irinta kas'aitattun zaratan mazan da suka Amsa sunansu maza "tun kafin ya Ida isowa mutum biyu cikin body quards nasa suka iso gefensa"beyi musu mgn ba kawai yamik'a musu keys d'in new car d'insa "ba b'ata lokaci Aka kaima babban driver "ya shiga yabata wuta"saida dollars ya gama Amsa wata waya kafin ya shiga back sit da Aka jima da bud'e masa ya zauna.....

zaune suke su ukku kan wasu kujeru Acikin wani club daga gefe"daga gabansu kuma matane mararsa tarbiya keta shan drinks da shisha"wasuma harda kayan maye sukesha"sadeeq ya kalli Adam dake kusa dashi yace"ba'a had'a game dani Atashi 0-1"saidai Atashi 1-1 ko kuma Atashi 0-0" najima Ina jin zafin dollars Araina "na had'a masa gadar zare sau kusan ukku Amma yana tsallakewa"na rasa wane irin jini ne dashi?"kai kwanaki har so nayi da kaina muje wani waje na dab'a masa wuk'a Amma wlh saina kasa sbd ba k'aramin jarumi bane"Adam yatab'e baki had'e da cewa an fad'a maka zai zauna bazai shirya kansa ba ,ya kuma horar da kansa da motsa jiki ba "bayan yanada dukiyar dako shi kansa besan Adadin taba"idan harda zakaji ta tawa daka hak'ura da wannan takun sak'ar da kake so kafara dashi sbd kaine zaka fad'i k'asa warwas "musammun idan yagane kai mak'iyinsane"wlh zai iya b'atar dakai da kowa naka ba'a komai tunda yanada kud'i,kuma yafik....kaga Adam karka mun maganar banza"ko kaima kana daga cikin masu zuwa maulane wajensa?"rai b'ace Adam yace"nafi k'arfin hakan kaima kasani"kaidai ne yaka mata ka Ajiye k'arya da burgan da kake mana kaje kayi maular wajensa"dan nasan ka cire girman kai ka nuna kana son yataimaka maka dan yabaka wata million 10 k'aramin Aikinsa ne"tsaki sadeeq yaja had'e da tashi yabar musu wajen "sbd yasan muddin yaci gaba da zama Awajen zasu iya samun matsala da Adam "batun dollars kuma yasha Alwashin koshi da kansa zai iya kashesa koda an kasheshi beda matsala burunsa Ai yacika....*Allah yarabamu da ciwon hassada*👏🥹

sai yamma likis dollars yanufo cikin gidan "ga gajiya da yunwa daya kwaso"rabonsa da Abinci tun break fast d'in safe"directly b'angaren su Eyyah yayima tsinke"tana zaune tana Azkhar "ga sunnah TV tana kallo"kanta ta d'ago ta Amsa sallamarsa tare da cewa "babban mutum! Eyyah sannu da gida"yauwa kai keda sannu"beyi mgn ba ya Ajiye ledar daya shigo da

ita gefen hular muslima dake Ajiye saman 2 seeter "duk Eyyah na lura Amma bata tankaba"bayan ya Ajiye ya wuce dining area yana tunanin k'ilan ko y'ar darun nasa nacan sashensu"tunda bega Alamar tana Anan ba"Abinciccikan yaduba"tuwon semovita da miyar kuka da taji naman shanu da man shanu"saiga sinasir da miyan kan rago"ga kula shak'e da had'in zobo da yaji cocumber da k'ank'ara"d'an shiru yayi sbd yasan Eyyah bata tab'a had'a masa irin wannan lemon na gargajiya ba,haka kuma bata tab'a yimasa sinasir ba"kamar ya tambayeta kodai bashi Aka Ajiye mawa ba sai kuma ya share"yayi serving d'in kansa yafara cin Abincn Anutse.....nama! A cikin Abinci ko farfesu be cika burge saba Amma yau yaji yamasa dad'i sosai "ko tuwon be ciba yayima cikinsa k'at"bayan ya gama ya goge bakinsa yabaro dining area d'in yana murmushi yace my sweet Eyyah irin wannan zazzafan girki haka me dad'i?"gaskiya bazan miki kishiyaba daga ke babu k'ari"tayi murmushi had'e da cewa babban mutum kenan"to bani bace nayi maka wannan girkin ba"takwarace tayi d'azun bayan sallar Azahar"ni tuwo nayima mijina"ita zaka gode mawa baniba"da zakazo kanamun dad'in baki "indai ka tsofe Agidan bashi kenan ba sai Aba daka sadaka"d'aure fuska yayi yak'i mgn yama bar parlourn ya wuce d'akinsa sbd ya watsa ruwa"saidai gaba d'aya ransa yatafi duniyar tunanin muslima"Ayau yadda yakejin zuciyarsa tamkar ya furta mata yana sonta"saidai k'asan zuciyarsa keta ce masa kul"yayi mamakin yadda ta iya girki haka"sai kuma yatuna tace tayi catering skul "saidai kawai ransa yabashi sbd yadda yafaranta mata Ayau shiyasa itama ta faranta masa"yana wannan tunanin yafara rage kayan jikinsa "saidai daya duba bega towels ba"sai yayi zaton koda ta gyara d'akin ta mayar dasu toilet"hakan yasa yanufi can"ya samesu guda ukku wanke Ashanye"tsura musu Ido kawai yayi yana kallo yana jin tsananin k'aunar yarinyar na karuwa Aransa "*Allah yasa ke rabona ce halimatu* yafad'a yana fara wankansa Anutse yana d'an murmushi da tunani"gaba d'aya sai yaji itama yake son gani"saidai daya tuna gobe zai tafi yabarta duk sai yaji wani iri..... yad'an jima tun daga wajen wankan har zuwa fitowa ya shiryawa"kamar d'azun ma haka jallabiya yasaka ,sai yayi kamar bature ko balarabe"lura da yayi wayarsa na haske yasaka ya matsa yaduba yaga sak'one daga Hjy zarah kamar haka *yallab'ai barka da wannan lokaci! kayi hak'uri da yawan kiranka danakeyi dan Allah ka dinga kulani"bazan b'oye makaba zuciyata ta kamu da matsananciyar soyay*........wani uban dogon tsaki yasaki batare daya Ida karantawaba yayi delete ya goge contact nata bayan yayi blocking. dama ya fahimci sonsa takeyi yabari dai ta furta sai ya d'auki matakin daya dace"yasha Alwashin ko mutanan dake buk'atar temako daya wakilta ta dinga kawosu, bayan ta tabbatar da gaskiyar su  to daga yau yacireta daga wannan matsayin"dama jiyama da dare wata y'ar tasha ta turo masa pics nata bbu kaya tadai b'oye fuskarta"wai idan ta masa su dinga hud'd'a koda bazai biya taba"sosai yaji gaba d'aya tsanar wasu matan"fuskarsa babu walwala yabar d'akin da nufin yaje yaga muslima yatafi masallaci sbd befi mintina 30 magrib tayi ba.....muslima kuwa dollars befi mintina 15 da barin parlourn ba ta shigo da sabon wankanta sbd d'azun ta gaji bacci taje tayi sosai"sai bayan ta tashi ta shirya ta nufo nan"da ledar daya Ajiye Amatsayin tsarabarta ta had'a Ido"sai kawai ta zauna gefen ledar"tana sanye da riga da siket na Atamfa sun kamata sosai"Eyyah ledar waye kuma miye Aciki?"ita ledar zaki tambaya bani ba"turo baki tayi tafara bud'ewa "chacoolates ne da biscuits masu Madara"harda irin wad'anda ta zab'o kwanaki daya mata chopping duk ta gani "nide Eyyah zan  d'auki biscuit guda d'aya"nima ba nawa bane babban mutum naga ya Ajiyesu"sbd haka ba ruwana"nide zan d'auka "kin manta kince ke ba ruwanki dashi kuma baki had'a komai dashiba? haba Eyyah ! dama ba b'atamun rai

yayiba,kuma yanzun Aina huce"harfa girki na masa me dad'i kan idonki....tsit tayi sbd ganin shigowarsa datayi cikin parlourn kamar daga sama"sarai yaji duka kalamanta"kamar yayi dariya saiya gimtse Abarsa"ya fahimci kwanaki kenan tace ba ruwanta dashi yanzun kuma ta huce"yana k'ok'arin zama Eyyah tace"toga babban mutum d'in nan saiki tambayesa yabaki?"meke nan Eyyah?"kinfini sani"k'in mgn tayi ta turo baki tak'i kallon gefen dayake zaune ,sbd bataso yasan tayi zancen Abinda ke cikin ledar yama rainata"yaya Ina wuni?"ta fad'a batare data kallesaba "shi kuwa gaba d'aya ita yake kallo"jin yayi shiru be Amsaba yasaka ta d'ago kanta da nufin ta saci kallonsa Aikuwa suka had'a Ido "da sauri ta kauda kanta"Adaidai lokacin Eyyah ta tashi tabar musu parlourn.....yaya Muslim kanaji na gaisheka shine kak'i Amsawa ko? kuma abu kad'an kace ban iya gaisuwa ba"ya d'auki kusan second 5 kafin yace"idan kinaso na Amsa saiki kalleni ki gaidani ba kina kallon wani wajen ba "meyasa bakya jin mgn ne?"mena yi dan Allah?"bance karki koma yin kuka bane?"saida taji wani iri batace komai ba tana tunanin meyasa ya gane?"ki d'auki tsarabarki dakike tambaya"nifa yaya Muslim ban wani tambayaba"okay bani Abuna tunda bakyaso"babu kyau ai maida kyauta "d'an murmushi kawai yayi bece komai ba"ita kuma tana dai zaune kanta Ak'asa"kin fasa fitar ne?"saifa gobe zamuje sunan yayar jidda data haihu"kikace kinyi fad'a da ita?"to Ai mun shirya"bazaki dena fad'a da mutaneba?"nifa yaya ba wani abu ya had'amu ba sbd yayanta ne"Atake ya had'e rai yana tsareta da mayatattun idanuwansa yace"meye had'inki dashi?"Akunyace tace toba yace yana sonaba"ni kuma bana sonsa"sai waye kike so?"yafad'a cikin wata iriyar muryar da bata san shanshi da itaba"har saida ta d'ago kanta tad'an kallesa ya d'aure fuska "nifa yaya ba kowa"bece komai ba yaci gaba da danna waya"can kuma yace"kin tuna wata yarinya da kuka had'u da ita a office nawa?"wannan sarkin iyayin da tura kai gun maza bbu Aji"da mamaki yadubeta yarasa meyasa bata son zarah?"saidai be tankaba"to yaya naganeta meya faru?"na fasa fad'a miki"ni Allah ka fad'amun"ta fad'a cikin shagwab'a"mik'ewa tsaye yayi yanufi k'ofa tare da cewa gobe in sha  zan koma jirgin k'arfe  12 zan hau"bejira cewar taba yayi ficewarsa yana dariyar kuruciyarta Aransa"yana fita ta d'auki ledar itama ta fita tana jin k'asan ranta kamar kar yatafi"musammun data fahimci daga wajensa sai wajen su Eyyah kawai takejin dad'i Agidan"koda ta shigo sashensu bata kula kowaba ta nufi d'akinta tayi shirin yin sallah sbd ta sami tsarki...sai bayan sallar isha'i dollars yanufo cikin gidan saidai koda yazo sashen Eyyah be samu y'ar darun tasaba"ga tsaraba yamata"kad'an kad'an dayaji motsi zai kalli k'ofa "duk Eyyah na lura dashi"saita tashi ta wuce kitchen ta d'akko Ayaba tasaka A leda ta fito rik'e da ita Ahannunta ta samesa zaune"babban mutum tunda ba wani abun kakeba jeka mik'a ma takwara ta wannan"dato ya Amsa yana kallonta ya wani marketurya yace toni Eyyah Ina nawa?"kaje kadawo tukum"yayi murmushi kawai yafita.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 300 normal grp vip grp 1000
Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba koki siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars

#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

........koda yafito daga shashen su Eyyah tafiyar yakeyi cikin nutsuwa yana rik'e da ledar da Eyyah tace Abata,da kuma ledar daya mata tsaraba "k'asan zuciyarsa na tunanin tayi bacci ko bata yiba?"yana gab da iza sashen yaji zuciyarsa na wani irin harbawa"Atake ya tuna Abinda yafaru d'azun"d'an d'age kafad'a yayi irin ko Ajikinsa d'in nan da duk yadda za'a fassarasu"kafin ya wuce cikin parlourn gidan....yana shigowa yayi clashing da Malika da muslima suna dambe"Naseem na k'ok'arin rabasu"wata rikitacciyar tsawa yadako musu"ba shiri Malika ta cikata"ita kuma muslima ta d'auketa da wani gigitaccen mari tana huci tace na rama marina"kukan kura malika ta komayi zata fincikota Aguje muslima ta nufi bayan dollars dake tsaye ya had'e rai yana kallonsu"saidai kawai yaji muslima tayi hugging nasa ta baya tana zuro kanta daga gefen damtsan hannunsa tana yiwa Malika gwalo"hakan yabama k'irjinta damar gugar faffad'an bayansa....ba shiri ya rintse Ido sbd wani irin yanayi me girgiza bawa daya tsintsi kansa Aciki "yah rabbih! ya furta Aransa yana saurin bud'e Idonsa ya hango Malika ta haye upstairs tana kuka da Alama k'ara zata kaima daddy"yayinda Naseem ke tsaye yana satar kallon su.....yaya kagani zataje ta sanarwa daddy ko?"ta k'are maganar cikin kukan shagwab'a"da sauri dollars yasaka hannunsa guda yajanye hannayenta data masa zobe dasu"ya tabbar suka k'ara mintina 3 Ahaka komai zai iya faruwa"gashi beso daddy yazo yasamesu Ahaka "da k'yar ya furta bakyajin mgn ko?"bance kidena biye mata ba?"itace fa yaya ta fara janta gaskiya"cewar Naseem"okay idan daddy yazo shiya kamata kama bayani"cewar dollars"saidai be rufe bakiba ya hango daddy na sakko k'asan Malika na biye dashi tana kuka"saida gaban dollars yabuga sbd yadda yaga fuskar daddy....Muslim fita ka bani waje"na lura duk wani iskancin da y'ar banzar yarinyar nan keyi kaine ke d'aure mata gindi"kuma da saka hannunka takeyin komai....dan Allah daddy kajira kaji meya faru"wlh laifin Anty Malika ne....yimun shiru mutumin banza na tambayeka ne?"shiru Naseem yayi ya sunkuyar dakai k'asa"tsabar irin yadda dollars ya hassala kasa mgn yayi"yana dai tsaye k'ik'am be tafinba "yayinda muslima itama take tsaye gefensa gabanta nata fad'uwa"K! zonan"idan ba jikinki ya gaya miki ba bazaki dinga girmama na gaba dake ba"Atake muslima ta tsure ta fara sakin k'aramin kuka ta b'uya bayan dollars"girgiza kansa dollars yayi Ahankali yace"kayi hak'uri daddy karka daketa"ba goyon bayanta nakeyiba Amma ka tsaya Amaka bayanin meya faru?"wai Muslim Ina wasa dakai ne?"bazaka tafiba?"ke kuma bazaki zoba ne?"juyowa yayi ya kalleta cike da tausayi sbd yasan tun tana yarinya tanada tsoron duka"dan uwarki bazaki zoba saina zone?"cewar daddy cikin daka tsawa"tana k'ok'arin tafiya Abbie yaturo k'ofar fuskarsa A murtuke ko sallama beyiba yana kallon daddy yace"sulaiman biyoni zanyi mgn dakai"ke kuma halimatu wuce kije"yana fad'in hakan ya juya ya fita"wata b'oyayyar Ajiyar zuciya dollars ya sauke"jikinsa ya bashi Naseem ne yaje ya sanarwa Abbie sbd ya lura tunda daddy ya disgashi ya fita daga cikin parlourn " yayahhh! yaji siririyar muryarta"juyowa yayi suka had'a Ido "to miye

na kuka ?"ya k'are maganar yana kallon cikin parlourn ya lura bbu daddy da malika"daga shi sai muslima ne suka rage "ita dai sunkuyar da kanta k'asa tayi"zoki k'arba ki tafi d'aki "batayi mgn ba ta matso ta Amshi ledojin da hannu biyu tare da cewa Nagode "beyi mgn ba yana dai kallonta harta nufi k'ofar d'akinta ta bud'e ta shiga"ya sauke numfashi yana tunanin Anya zai jure cigaba da ganin yarinyar cikin irin wannan matsalar??"motsin mutum da yaji yasaka yadawo tunaninsa"kabeer ne ya shigo babu ko sallama sai huci yakeyi"da Alama yana cikin b'acin rai"kallo be ishi dollars ba yajuya ya fita"sbd tun dukan daya masa yadena gaidashi"shi kuma ko Ajikinsa da baya gaidashi"yana fitowa yasami suraj da Abbie da daddy duk suna Atsaye "kafin ya iso wajen su yaji Abbie na fad'in gaba d'aya yaran Jamila idan Aka cire naseem basuda mutunci da tarbiya"surajo ba yayansa bane sbd mace zai shak'esa"har Ina masa mgn yana maidamun shi d'an iska"wlh in bacin marinsa da kayi da Adaren yau ka gama zama da uwarshi"kallonsu kawai dollars keyi yana jin wani irin yanayi na zafin zuciya da fushi na taso masa"idan ya fahimta wato kabeer rashin kunya yaso yayiwa Abbie sai daddy ya maresa"yana wannan tunanin Abbie yace"Allah yakaimu ranar juma'a hukuncin dana yankewa kowa zai fito tunda bakuda mutunci"yana fad'in hakan yayi gaba"suraj na lura da dollars yabiyo bayansa yana fad'in Abokinah kana ciki kenan?"juyowa yayi suka had'a Ido ya tsaya yana kallonsa yace"meya had'aka da wannan yaron harya shak'eka?"yak'are maganar yana huci"wlh Akan husnah nefa! kai kuma shine ka tsaya yaro k'arami yamaka haka bazaka bazar dashi ko fidda masa jini ba? d'an murmushi suraj yayi yace"ban kaika zafin zuciya ba dollars"sannan na barsa ne sbd Abbie da daddy"kasan husnah yakeso niban ma saniba"naga dai kashi biyu muna had'uwa dashi gidansu"shine yau yasanar mata yana sonta"shine ita kuma tace ni takeso"shikenan laifin fa"kawai zan wuce sashen su Ummy nasha coffee muka had'u dashi tamkar wani sa'anshi yasha gabana wai na fita harkan husnah koya b'atar dani"shine naturashi ina gaya masa mgn Abbie ya hango mu yakiramu"shinefa yaxo yayima Abbie rashin kunya sai daddy da suke tsaye Atare ya maresa....wani irin zazzafan huci dollars ya sauke rai b'ace yace"uhmmm! dole na d'auki mataki nima bayan matakin da Abbie d'in zai d'auka"yana fad'in hakan yayi gaba Abinsa.....jiki Asanyaye muslima ta shigo cikin d'akin ta zauna kan carpet ta sauke Ajiyar zuciya tana tunanin yanzun idan da dollars be zoba Abinda zai faru bamai kyau bane"ta kuma tabbatar da Naseem ne yaje yasanarwa Abbie"tabbas naseem da yaya muslim ba k'aramin garkuwa bane gareta cikin gidan "gaba d'aya sai taji fargaban tafiyar tasa gobe da rashin jin dad'i... kiran sadam ne yakatse mata tunaninta kasancewar batada nutsawa saita yamutsa fuska tak'i d'aukar wayar"saima ledojin da dollars yabata ta fara dubawa"Ayaba da kilishi ne sabo yanata tashin k'amshi"tayi shiru tana tunani"Allah sarki yaya Muslim Allah yak'ara bud'i"ta furta cikin jin dad'i tana fara cin Ayabar "saidai shi kilishin ta Ajiyesa zuwa safe zataci"Ayabar ma tacine sbd tana bala'in son kayan marmari.....bayan ta gama shirin kwanciya bacci ta kwanta"saidai damuwa da b'acin rai sun hanata baccin"duk idan ta tuna yadda mahaifinta ke Aibatata sai taji wasu zafafan hawaye na zubo mata "daga k'arshe tashi tayi tayo Alwallah tazo tafara jera nafilfili,tana kuka tana Addu'ar samun mafita ga rayuwarta"da kuma samun jituwa tsakaninta da mahaifinta"sannan tayima mahaifiyarta Addu'ar samun rahama Akabarinta"kafin tayi karatun Alkur'ani me girma "sosai taji zuciyarta tayi wasai sai gashi tafara jin bacci"hakan yasa ta rufe Alkur'anin taje ta kwanta....washe gari misalin karfe 9:47 am"dollars ne zaune Akafaren parlournsa dayaji kayan more rayuwa"tamkar ba'a cikin k'asar Nigeria yakeba"yana sanye da k'ananun kayan da sukayi matuk'ar haskashi"yayi wani irin kyau na

musammun "dogayen k'afafuwansa na sark'e "saidai k'wayar idonsa na b'oye cikin eye glass black"sbd gaba d'aya yau baya jin dad'in jikinsa haka yatashi, ko baccin kirki beyi ba Adaren jiya sbd b'acin ran Abinda yafaru da kuma rungumar da muslima ta masa"wacce gaba d'aya daya tuna Abin shine kawai yasan meye yakeji Ajikinsa"tun Asuba bayan yadawo daga masallaci yaje ya gaidasu Eyyah be koma sashen nasuba"Ayanzun haka yanada niyar yaje ya musu sallama daga nan yaje ya gaida umma suyi sallama saiya tafi Airport "yanata danne danne a laptop dake gabansa a Ajiye saman center table....Ahaka yaji Anturo k'ofar"sautin siririyar muryarta yayi daidai da bugawar zuciyarsa"saida yad'an lumshe idanunsa ya d'ago kansa yad'an kalleta cikin second 5 yana Amsa sallamar can k'asan mak'oshi"tana sanye da riga da siket da suka kamata da mini hijab"Acikin y'an sakanni ya fahimci tayi kuka Adaren jiya kuma da damuwa ta kwana"musammun daya lura da batada walwala"sannan idanunta sun d'an kod'e daga saman eye lashes nata sun kumbura.... Adaidai gefen laptop d'in gabansa ta Ajiye tray d'in hannunta da Eyyah ta shiryo masa Abin break fast"taji shiru be zoba ,kuma tasan yau zai tafi shiyasa ta turo Aka masa yayi karin Anan"tana daga duk'en tace"gashi inji Eyyah ,Ina kwana?.......jin yayi shiru yasaka ta d'an d'ago kanta....meyasa bakya jin mgn ne?"yafad'a in a low voice! saida ta yamutsa fuska had'e da cinno masa d'an mitsitsin bakinta Agaba kafin tace"mena yi kuma yaya muslim?" bance karki koma yin kuka ba?"sunkuyar dakai k'asa tayi idanunta na koma cikowa da wasu sabbin k'wallah d'in tace"idan katafi yaushe zaka dawo?"da d'an mamaki ya kalleta beyi mgn ba"hakan yasa ta mik'e tsaye sbd taji haushi zata tafi"Ina zakije?"kukan datake rik'ewa ta sakar masa"wai meye haka? kinsan dai bana son kuka ko?"zoki zauna ki fad'amun menene?"bakai bane zaka tafi ko?"d'an murmushi ya sub'uce masa"dukda bata ganiba tanama share hawayenta ta koma zama d'an nesa dashi"*halimatuuuuu!*. halinki sai ke "kwanaki fa har murna kikeyi mugu zai tafi sbd ki wala yanzun kuma shine kike rigimar zan tafi?"to yaya bakasan bana jin dad'in zaman gidan ba?nidai wajen Eyyah zan koma gaba d'aya"ban Amince ba"ki cigaba da zuwa kamar yadda kika saba Amma babu zancen zama ki kwana koyin wani Abu "ni kuma ranar friday zan dawo shikenan?"saita nok'e kafad'arta "zoki had'amun ko tea ne nasha kafin na wuce"saiki fad'amun meye kikeso ko kike buk'ata?"

batayi mgn ba ta taso Ahankali zuwa gabansa"shi kuma yana binta da kallon k'asan Ido ta cikin glass d'insa"wanda inda wani ke kallonsu kai tsaye ba'a ce kallonta yakeba"bayan tagama had'a masa tea d'in"ta zuba masa naman rago gashashshe dayaji kayan yaji yanata k'amshi ga ruwa ruwa Ajikinsa sa"Agefe ta  zuba masa yam balls dukta turo masa gabansa"sai kuma ta mik'e tsaye....saurin meye kikeyi ne wai?"yafad'a yana d'aukar cup d'in shayin"batayi mgn ba tad'an zauna ta sunkuyyar dakai tana wasa da zoban Azurfan dake Ayatsanta na hannu"Ahankali tace"yaya muslim dan Allah ka canzamun waya ko? ni bana son waccan yanzun....saida yad'an jima kafin yace"shikenan idan mun fita yanzun sai muje ki zab'a"da murna saman fuskarta ta fara masa godiya"beyi dai mgn ba yana break fast d'insa"yaya zanje kafin ka fito"bazaki mun rakkiya Air port ba?"da harma da gidan ummah zamuje"da murmushi saman fuskarta cikin yarinta tace"zanje pls"shareta yayi yaci gaba da break fast d'insa"bayan ya idar ya mik'e tsaye ya wuce ciki be jimaba yadawo janye da troley d'in kayansa"yayinda keys d'in sashen ke'a hannunsa"muslima na tsaye dai kanta ak'asa saidai taji yace"k'arbi nan"ta d'ago kanta ta Amshi keys d'in sashen "shi dai yanata kallonta yanufi k'ofa ta biyosa Abaya tana gulmar ya rufe Ido da eye glass"mutum biyu ta samu suna jiran fitowar tasa"Aranta tace baya jira saidai ajirashi"har ita kanta cikin ladabi suka gaida ita suna Amsar troley d'in suka nufi

parking lot da nufin su jira fitowarsa"Ajere da farko suke tafiyar"saidai daga bisani shi dayake yafita dogon tak'i saiya wuceta"ita kuwa cikin sanyin jiki take tafiyar kamar me tausayin k'asa "hakan yasa ya rigata Isa shashen su Eyyah"koda ta shigo tsintar sautin lallausan muryansa taji yana fad'in gaskiya Abbie ka koma ja masa kunne"muddin hakan yakoma maimaita kansa Abinda zai faru bame kyau bane"karka damu babban mutum "Allah yabaka sa'a da nassara ya tsareka"yana d'an murmushin gefen baki ya Amsa da Ameen "yana satar kallon mutuniyar tasa data zauna gefen Eyyah"wacce Ayanzun dataji Abinda yakoma faruwa Adaren jiya taji bazata iya bari Hjy jamila taci gaba da rayuwa ita kad'ai da d'anta ba....my sweet Eyyah zan wuce! to babban mutum Allah yatsare yayi maka Albarka "ya Amsa da Ameen ya matso yabduk'a ya rungumeta"tayi murmushi kawai "ganin muslima batada niyar tasowa ta biyosa yasaka harya kai bakin k'ofa ya juyo ya kalleta murya Akausashe yace"kina kiran nace ki taso ne?"ta turo baki tana mik'ewa tsaye tace"Eyyah zan bishi na Amshi sak'o "daga haka ta fita"suka bisu da kallo suna murmushi Atare.....tunda suka shigo motar babu wanda yatanka d'an uwansa"shi yanata Amsa kiran mutane jefi jefi"ita kuma tana gulmar haka masu kud'i suke babu hutu game da waya"any time Amsa ta sukeyi"saidai ta fahimci wannan jin kan nasa harsuma mazan y'an uwansa yimawa yakeyi"ita kanta wayar cikin nutsuwa da Aji yakeyinta ba hayaniya....fitar driver daya gama parking yadawo da ita tunaninta"da sauri ta dubesa yana k'ok'arin fita "yaya Muslim Amma Anan zaka barni ko?"banza ya mata ya had'e rai yafito daga cikin motar "sai bata koma gigin tankashiba tabi bayansa suka nufi cikin gidan....ummah ce kawai da wasu k'ananun yara 3 Acikin parlourn suketa wasa"tana sanye da hijab Ajikinta sai casbaza dake A hannunta tana lazimi"da fara'a saman fuskarta ta Amsa sallamar tasu had'e da cewa Ahhhhhh muslima kece yau Agidan?"Eh ummah Ina kwana?"ta fad'a tana kok'arin duk'awa "yayinda uban gayyar ya zauna kan kujerah"lafiya qlau yasu Eyyah ?" Alhamdulillah"saita kalli dollars murya Amarairaice tace"dan Allah yaya zanje d'akin su Amatallahi"banza yamata yak'i tankata"ummah tace"jeki ku gaisa ko jiya haka tayita yawan tambayarki"da sauri ta tashi tabar parlourn"sai sannan dollars ya gaisheta"ta Amsa tana murmushi tace"Amma Anan zaka bar mana muslima d'in ko?"ah ah ummah islamiya zataje"yak'are maganar Adaidai lokacin da yaransa keta shigowa da kayan Abinci da provisions sunata jibgewa"baka gajiya da hidima had'e da d'awainiya muslim?"Allah ya yimaka Albarka yabaka mace ta gari da zuria d'ayyiba"Allah yakareka daga sharrin mak'iya yajik'an mahaifinka da Alh"cikin jin dad'in Addu'arta ya Amsa da Ameen "yana Ajiye mata rafar y'an 1k guda ukku gabanta"muslim kabar kud'in nan yanzun haka dubu d'ari biyar d'in daka bani ranar sadakar ukku suna nan banyi komai dasuba sbd ba Abinda na nema na rasa"No ummah ki barsu ko taimako ko sadaka kinyi"daga haka yayi shiru sbd ganin shigowar mamy cikin parlourn "Aladabce ya gaida ita ,ta Amsa had'e da masa godiyar d'awainiya"bayan barinta cikin parlourn ya mik'e yana duba wristwatch d'insa yace"ummah bara mu tafi"ita kuma tana can tak'i fitowa"be rufe bakiba muslima da Amatallahi suka shigo cikin parlourn "bayan Amatallahi ta gaidasa sukayi sallama da muslima"ummah na kallonta tace"yayanki yace tafiya zaiyi dake bazai barki Anan ba"ranar friday zanzo Ai ummah"fad'a kanta a sunkuye "to shikenan Allah yakaimu"daga haka sukayi sallama "har cikin ransa Muslim yaji dad'in yadda ummah yanzun take sakema muslima fuska"saidai suna fitowa ta saki kukan shagwab'a ya kalleta be tankataba "saidai yasan data san meye yakeji bazata dinga yimasa shagwab'a irin haka ba bayan be kaiga mallkartaba Amatsayin matarsa....dama yaya kasan bazaka barni Ananba kazo dani?"ko yanzun bata b'aci ba saiki koma"yafad'a fuska Ad'aure yana k'ok'arin shiga mota da Aka bud'e

masa"tanata cin magani itama ta shigo ta zauna nesa dashi"be komabi ta kantaba ya jingina bayansa Ajikin kujerar ya lumshe Ido"saida suka iso wajen siyar da wayoyin sannan yafita shi kad'ai bece ta fitoba sbd ta bashi haushi "Ada yana murna sbd yana zaton tafara damuwa dashi Ashe ba haka bane shirmenta ne....be jimaba yadawo rik'e da ledar da kwalin wayar ke ciki ya Aza mata saman cinyarta batare daya yi mgn ba "saita turo baki kamar zatayi kuka tace"Amma yaya ba zab'a kace zanyiba shine kaje kai d'aya ko?"idan wannan bata miki ba saiki bani kayata"Amma kasan ba kyau maida hannun kyauta ko?"Eh hakane"Amma zaki iya bani sai kiyi istighifari ko?"shiru tayi ta juya masa baya"yad'an girgiza kansa kawai....har suka iso Air port d'in muslima batayi mgn ba "Alokacin kuma 11:35 am"jin motsin bud'e k'ofar yasaka ta juyo suka had'a Ido dashi saiga hawaye"kukan na meye kuma?"tayi shiru kanta ak'asa "ya matso kusa da ita har jikinsu na gugar juna ya kama hannunta guda yasaka mata rafar y'an 1k da ledar da wayar ke ciki"karki damu bazan jimaba zan dawo"yak'are maganar yana cika hannunta yad'ago fuskarta"saita lumshe idanuwanta"ya tsurama kyakykyawar fuskarta Ido"yana jin kamar yayi kissing nata"Ahankali yasaka yatsun hannunsa yafara share mata hawayenta tas"ita dai ta lumshe Ido "*bud'e idon ko dubulle y'ar bak'a?* da sauri ta bud'e idon tana b'ata fuska tace"kai yaya Muslim shine zaka b'atamun suna ko?"by surprise taji ya dafa kafad'arta "k'irjinta yabuga! ta kasa kallon k'wayar idonsa"ki kalleni ki fad'amun hakan mana?"yak'are maganar yana jan karan hancinta "tad'an saci kallonsa"gabanta yafad'i sbd yacire eye glass d'in nasa"ko idonsa ke ciwo ne?"ta fad'a Aranta sbd ganin idanunsa jajir....zan tafi! ya katse mata tunaninta "Agefen kafad'arsa ta kwanto tana sakin k'aramin kuka"ba k'aramin jarumtar danne yanayin daya tsintsi kansa yayiba yad'an shafi bayanta yace"kimun Addu'a kinji nasan An fara kiran sunayen pasingers"Allah yatsare ya saukeku lafiya"ta fad'a Akunyace tana janye jikinta daga nasa"da Ameen yah Amsa yana maida eye glass d'in nasa"kanta Asunkuye gaba d'aya jikinta irin k'amshin jikinsa yakeyi"bance ki dinga fita barkatai ba"su Malika da uwarsu babu ruwanki dasu bayan gaisuwa"to yaya zan kiyaye saika dawo"sosai yaji ta bashi tausayi"saidai shi yafita damuwa da rashinta"yasan sbd yana kulawa da ita Agidan shiyasa bataso yatafi badan sbd wani Abuba"da wannan tunanin yafito daga cikin motar ya kalli driver da body quards nasa dake jiran fitowarsa ya musu Alamar suje kawai"shi kuma mutum guda yabishi da troley d'in kayansa......✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba koki siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy

#sadeeq

[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

...........tunda driver ya juya Akalar motar suka doshi hanyar gida muslima keta fushi ko tari batayiba Acikin motar har suka iso gida"kai tsaye sashensu Eyyah ta yada zango"yadda Eyyah d'in ta lura da fuskarta bbu walwala yasaka tafara zaton kodai muslima da muslim sun fara soyayya ne Amma su basu sani ba?".....wai Eyyah sai mutum yayita sallama ki masa shiru ko?"Eh nayi shirun, meya hana ki bud'e murya kiyi mgn"tayi shiru ta zauna kan kujerah"Ina zaki da kud'i?"cewar Eyyah tana kallon kud'in da ledar hannunta"yaya ne ya bani"dama Ina son zuwa kasuwa na d'inko sabbin hijabai, na kuma  siyo wasu Abubuwan "ya kyauta kin gode"batayi mgn ba saima sannan tafara k'ok'arin zaro kwalin wayar daga cikin ledar"dam ! k'irjinta yabuga dataga wayar k'irar iPhone14 Pro max! Anya Eyyah yana sane yasiyamun wannan  wayar kuwa?"sai kuma ta tuna da keys d'in motarsa dataga kud'inta Awaya 80 million suna hannunta be k'arba ba"wayar zatayi nawa ne?"bansan kud'in taba Amma itace waya k'arshen tsada koshi itace hannunsa"kije ki Adana idan baza kiyi Amfani da itaba"idan yadawo kin tambayesa"nide Amfani zanyi da Abuna"kallonta kawai Eyyah tayi batace komai ba "ta tabbatar idan muslim ya mallaki yarinyar sai tafi haka shagwab'ewa sbd tasan k'ara sangartata zaiyi da yimata gata"tana wannan tunanin Muslima ta tashi cike da murna ta nufi sashen su"tunda ta shigo tayi sallama sau biyu bbu wanda ya Amsa"ta kalli Hjy jamila dake zaune kan kujerah ga Naseem k'asa kan carpet Agabanta yayi kneedown,kabeer na tsaye  rik'e da belt, d'auke kanta tayi ta  wuce d'aki"saidai ranta yabata k'ilan sun gane shine ya sanarwa Abbie Abinda yafaru shine zata hukunta shi"gaba d'aya suka bita da kallo itada kwalin wayar hannunta"mommy iPhone14 Pro max cefa hannun yarinyar can"waye kake ganin zai siya mata inba muslim ba?"wlh in bacin gudun Abinda zai je ya dawo da dare nayi badda kama na d'auke shegiyar wayar balle harta hura hanci A kanta"koni iphone 13 ce nake da ita sai ita banza zata rik'e irin wannan wayar da saika kai wani  shege kake rik'eta"shidai naseem na saurarensu be tankaba"yakuma sha Alwashin sanarwa muslima ta b'oye kayanta"Hjy jamila kuwa shiru tayi sbd ganin Naseem na nan"wai kabeer me kake jira dashi ne da bazaka fara jibgarmun d'an iska me kunnan k'ashi ba?"taraka nakeyi dama,kasan kwanaki na rabaka da siyama Amma kak'i ji ko?"na lura y'ar iskar yarinyar nan tamkar ta tsafeka itada muslim "yaron dake gaba dani baya tankamun Amma shine keda mutunci A wajenka sbd baka kishina"kafi sonsu dasu Malika dakuke ciki guda  ko?"kiyi hak'uri mommy ni Ina son kowa kawai bak.....dukansa da kabeer ya fara yasaka yayi shiru "tun yana jurewa har yafara ihu"muslima dake cikin d'aki tafara juyo ihunsa "kukan tausayinsa ta saki "tasan ko taje ta basu hak'uri bazasu kyaleshiba"tun tana juyo ihunsa har tadena ji"tayi tagumi tana tunani"can ta sauke Ajiyar zuciya tana fad'in Allah yasa yayan ya Aminice"daga haka tafara k'ok'arin kiran layinsa"sai gab da zata tsinke ya d'aga wayar cikin kasalalliyar murya yace hellow !! yaya Muslim! *Uhmm dubulle y'ar baka*"kuka ta sakar masa"kinga tunda bakyason sunan nadena fad'a"nifa yaya ba haka bane "to menene?"ba yaya kabeer bane yaketa dukan naseem be masa komai ba"kuma mommy ce tasaka ya dakesa"shiru yayi yak'i mgn yana tunani k'ilan sun gane shine jiya yaje  ya sanarwa Abbie komai daya faru....yaya Muslim dan Allah zan rok'i wata Alfarma wajenka badan na isaba sai dan Allah zaka mun  "murmushi yayi marar sauti yadda bazata jiba yace"meye ne?"yaya dan

Allah ka fidda Naseem k'asar waje yaje yayi karatunsa koya huta da fitinarsu"ko can inda kake ne ka kaisa (America)"sai yayi karatun kana jin motsinsa"shikenan idan nadawo zan sanarwa da daddy"ihun murna tayi tana yanke wayar.....kafin ta d'auki sabuwar wayar ta saka chargy da nufin idan ta cika ta maida komai dake a tsohuwar wayarta cikin sabuwar"bayan ta saka chargy d'in ta kwanta bacci"sai bayan sallar Azahar tafarka"saida tafara yin sallah sannan tayi wanka"ta shirya cikin dubai Abaya lemon green"fitowa tayi daga cikin d'akin da nufin taje tayi lunch"tana fitowa ta  hango Hjy jamila ta bud'e warmer d'in Miya tana zuba wani Abu ciki me kama da magani.... innalillahi wa inna ilaihir raju'un! ta fad'a Aranta tana juyawa ta koma ciki"kuka ta fashe dashi Afili tace meye zan miki kisoni mommy?"wace irin tsanace kikamun haka?"kowa yaci Abinci niban ciba shine kika zuba wani mugun abun ciki sbd ki cutar da rayuwata"Aikuwa nagama cin Abincin gidan nan"tana cikin wannan yanayin naseem yaturo k'ofar ya shigo ya murza key"da Ido ta tsaresa tana masa  kallon tambaya"idanunsa sunyi jawur Alamar yasha kuka"Naseem meye ma'anar hakan dakayi?"mgn zamuyi Anty muslima"yafad'a yana zama gefenta"murya can k'asa yace"waye yasiya miki wayar d'anaga  kin shigo da ita d'azun ? babu wani b'oye b'oye tasanar masa sbd ta yadda da Naseem"murmushi me ciwo yasaki yace"dama nasan shine zai siya miki nadai tambayane sbd na tabbatar "to ki d'auki wayarki Anjima ki kaita d'akin Eyyah ki Adana"sbd naji yaya kabeer yace zaizo ya d'auketa ke baki Isa ki rik'e waya me tsada kamar taba "saidai dan Allah karki sanarwa kowa Anty muslima"kinga ko yanzun yadakeni sbd jiya na kira Abbie na sanar masa kunyi fad'a da Anty Malika daddy ya goyi bayanta zai dakeki.....karka damu Naseem babu wanda zaiji"niko kwanama bazan yiba Anan"to ki rufe d'akin,sannan ki d'auki keys d'in motar yaya dake wajenki"sbd gudun kar Asami matsala"duk zanyi naseem "nagode da k'auna da son zumunci dani dakakeyi"Ina jinka kamar uwa d'aya muke dakai d'an uwana"sai ta saka mishi kuka"yamatso ya rungumeta yana share mata hawayenta yana janta da fira"sai gashi ta sake harda yin murmushi"ta rab'a kud'in da dollars yabata zata bashi yasanar mata shima yabashi 50k"batace komai ba ta maida kud'in ta bashi tsohuwar wayarta kyauta"ba k'aramin murna yayiba sbd wayar babbace zatayi 200k sabuwarta"bayan ya Amsa ya bud'e k'ofar d'akin yad'an lek'a yaga bbu kowa a parlourn sannan yafito"ita kuma ta saka hijab ta d'auki keys d'in shashensa dana motarsa ta nufi sashen Eyyah da nufin taje taci Abinci..... Adaren ranar muslima sashen su Eyyah ta kwana"

tun bayan kabeer ya gama dukan naseem Hjy jamila tajashi d'akinta ta bashi spire key tace"cikin dare yaje ya bud'e d'akin muslima ya d'akko mata wayar da keys d'in motar dollars dake wajenta"Abinda yafaru kenan"koda yabud'e be sameta Ad'akin ba"yayi bincike sosai duk ya hargitsa d'akin ya watso mata kaya k'asa da saman bed"Amma bega wayaba da keys d'in mota ba"Atake ransa yabashi Naseem ne dayaji yana maganar zaizo ya sanar mata shine ta gudu"saidai yasha Alwashin bazai masa komai ba zai nunama mommy bega komai ba....Awashe garin ranar data dawo ta d'auki kayan sawarta tazo tasami d'akin Ahaka, ta girgiza kanta tana Addu'ar Allah yaka mata k'arshen Abin.....

*bayan kwana 5*

tunda kabeer ya shiga d'akinta yayi bincike muslima ta dena kwana saidai tazo tayi Abinda yaka mata ta koma shashen su Eyyah "hakama tadena cin Abincin gidan wajen Eyyah take cin Abinci"tsakaninta da Muslim tun ranar data kirashi game da Naseem basu koma yin wayaba"har yau Friday da take tunanin zai dawo"tun jiya ta gyaro sashen sa tas"yau kuma ta tashi da d'okin

zuwanta gidan ummah"so takeyi daya dawo bayan sallar la'asar yasaka Akaita"saidai tarasa meyasa tun safe taketa jin fad'uwar gaba? ga wani irin kyau Ayau taga tayi na musammun??"tana cikin yanayin hakan kuma Abba ya sanar Anjima da yamma Abbie yace"Ataru Aparloun sa za'a yi family meeting"in bacin tasan dole taje data hak'ura da zuwa family meeting d'in tayi tafiyarta gidan ummah......."Atare itada Eyyah suka shiryama uban gayyar Abinciccika masu rai da lafiya"bayan Antaso masallaci Anty habiba da husnah da yaya zainab y'ar Abba me Aure duk sukazo gidan wajen taron family meeting d'in sbd kowa Ansanar masa.... Ab'angaren Hjy jamila kuwa ,tasan tsawon zamanta da daddy kusan shekara 35 sau biyu Aka tab'a yin family meeting a bugaje's house's"saidai yanzun jikinta bata yakeyi kamar babu Alkhairi Awannan taron"Amma zata zuba Ido taga idan Antaru wace uwar za'a yi?....misalin k'arfe 3:11 pm muslima na zaune a parlourn Eyyah "husnah nata yarfa mata kalba k'anana"suna d'an tab'a fira jefi jefi sbd sun kusan idarwa"k'ananun kaya ne riga da wondo Ajikin muslima"sun kamata sosai musammun rigar data matseta sosai"wondon ya fidda shape d'in k'ugunta"saidai tad'an ratayo milk d'in hijab nata daga gefen bayanta ta sauka zuwa har k'ugunta"tayi hakane sbd batasan ko wani namiji ya shigo ba"gaba d'aya yau zafi Akeyi sbd hadarin dake sararin samaniya"shiyasa ta sanya k'ananun kaya"kasancewar tanada yawan jin zafi duk iskan fanka dana AC dake Akwai parlourn be ishetaba saida ta kunnah fanka ta girke ta Ajiye gabanta"gaba d'aya ta zubama wayarta Ido tana chats da k'awarta jidda"yayinda husnah ke mata kalbar tana satar kallon wayar Aranta tana mamaki"sai kuma data tuna da dollars saita cire mamakin domin tasan bayanshi babu wanda zai siyama muslima irin wannan tsadaddar wayar tunda bata kula samari....husnah bata gama wannan tunanin ba "ma'aikatan gidan ,irinsu cleaners da masu bama flowers ruwa suka fara shigowa da manyan ledoji"wani irin mummunan fad'uwa gaban muslima yayi"wanda itama batasan daliliba"ganin Ana shigowa da kayan kawai yasaka ta fahimci dollars yadawo"bata gama wannan tunanin ba taji sautin Amon jarumar muryansa me matuk'ar d'aukar hankalin y'an matan zamani"gaba d'aya husnah ta bishi da kallo tana tasbihi Aranta "kullum idan ta gansa sai tayi Addu'ar Allah ya Ida cire mata sonsa Arai"tasan suraj ya had'u shima"saidai dollars me gaba d'aya ne"idan suraj  na tare dashi ko kyawunsa bata gani.... Atake k'irjin muslima yabuga dataji muryansa "da sauri taja hijab d'in da nufin ta rufe jikinta baki d'aya"saidai dayake hijab d'in sulb'i gareta saita zame.....tunda ya shigo cikin parlourn da bayanta idanuwansa suka farayon  tozali"da wani irin kallo irin na k'asan Ido yake jifar bayanta dashi Atake yaji kasala"husnah dai cika mata gashi tayi ta gaidashi yana k'ok'arin zama kan kujera "gaba d'aya k'amshin turarensa yacika parlourn"yana sanye da suit coffee brown "da sukayi matuk'ar yi masa kyau"sai bayan ya zauna ya Amsa gaisuwar husnah tare da tambayarta Anty habiba"kafin ta bashi Amsa Eyyah ta fito daga cikin kitchen baki washe tana fad'in ga babban mutum ga babban mutum"d'an murmushi yasakar mata beyi mgn ba yana dai kallon mutuniyar tasa datake k'ok'arin saka hijab "Aransa yace"*my world!* kenan! har wanka na miki miye za'a b'oyemun?"gefensa Eyyah ta zauna tana mamakin meye yasakashi yin rama ne?"ga k'asumba ta cika masa fuska....yaya sannu da zuwa! Cewar muslima batare data kallesaba, tadai juyo ta gyara zamanta"bakaji takwara na maka  mgn?"cewar Eyyah"ya mutsa fuska yayi yace"barta Eyyah ba tun d'azun ta ganniba"dariya husnah ta saki"muslima ta mik'e tsaye ranta Ab'ace idanuwanta cike da k'wallah tace"ke kuma sis meye Abin yin wani dariya?"har kalban bana so ki idamun zan tsefe wacce kikayi tun....sai tayi shiru da gudu ta wuce d'akin Eyyah"dollars dai afuska be nuna komai ba"saidai Azuciyarsa beji dad'in kukan

nataba beyi zaton zata masa kukaba dabai tsokane taba....babban mutum kaje kaci Abinci ko wankan zaka fara yi ne?"no Eyyah bana jin yunwa zansha fura idan na fito"sosai tayi mamaki sbd be tab'a dawowa ba yak'i cin girkinta"saidai zata bari idan ya nutsu ta tambayesa rashin lafiya yayine daya zabga irin wannan ramar haka??"motsin tashinsa tsaye yana Amsa waya yasakata binsa da kallo harya b'acewa ganinta"yana wayar harya iso d'akinsa dake Anan sashen nasu Eyyah"tunda yashigo yaketa d'an murmushi Afili yace "na gaji da b'oye soyayyarki danake dako tsawon shekaru da dama halimatu"yak'are maganar yana kwanciya saman luntsumemen bed d'insa ya lumshe Ido batare daya zare takalmin k'afarsa sawu ciki ba"kasancewar gangar jikinsa ne kawai saman bed d'in "ko Ina gwanin kyau Atsabtace"ya d'an bud'e Idonsa yakoma lumshewa Aransa yace"yarinyar nan zansha fama da ita wajen saurin kuka"sai kuma wata zuciyar tace idan baka same taba fa?gabansa yafad'i ya tashi zaune yafara tunanin kodai yasanarwa suraj Anjima koda Akwai wata shawaran dazai bashi game da lamarin ?"sai kuma ya girgiza kansa sbd yatuna dayazo neman shawaransa sbd yana son husnah k'in goyon bayansa yayi....yajima yana sak'a da warwara"har lokacin sallar la'asar yayi duk yana tunani"saida kiran suraj ya shigo wayarsa yaduba Anan ya lura da lokaci"da hanzari ya tashi tsaye yafara rage kayan jikinsa kafin yasaka bathrope yashiga wanka"koda ya fito Anan cikin d'aki yayi sallarsa sbd wasu masallatan duk sun gama sallar"bayan ya idar yad'an shafa creams da turaruka yasaka jallabiya dark brown"yana k'ok'arin fitowa daga cikin d'akin kiran suraj yakoma shigowa cikin wayarsa"oh suraj ka bani da jaraba"irin wannan dogon kira haka"yak'are maganar yana yamutsa fuska ya d'auka beyi mgn ba "wai Abokinah kana Ina?"d'akina! yafad'a Atak'aice"okay kazo inji Abbie,kai kawai Ake jira kowa yataru Anan parlourn sa za'a yi family meeting "tsintar kansa dollars yayi dajin fad'uwar gaba"da k'yar yayi jarumtar cewa gani nan zuwa!.... daga haka ya yanke wayar yanufi parlourn Abbie sbd shi saima yanzun yasan za'a yi wani family meeting d'in.....kusan mutum  yafi Ashirin ne zaune A parlour"Abbie da Eyyah ne kawai zaune kan kujerah Amma harsu daddy duk suna zaune kan carpet"muslima na daga gefen zainab"tasha Alwashin da Angama zata fita ta hau Adaidai ta ta tafi gidan ummah"bazata sanarwa dollars yasaka Akai taba sbd fushi takeyi dashi"tanajin sallamarsa gabanta yafad'i bata san lokacin data d'ago kanta suka had'a Ido dashi ba"Atare k'irjinsu yabuga"harara ta ballah masa had'e da murgud'a masa d'an bakinta "Abin mamaki sai taga ya kasheta da wani tsadaddan murmushin da yayi bala'in yimasa kyau,yana d'auke kansa ya nemi waje gefen suraj da Ramadan ya zauna"Abbie ya bisa da kallo yana fad'in sallu Anal nabiyil Kareem"bayan Angama salatin Abba yayi saurin kallon muslima yace" mamana cika mana da Addu'a "bazata iya musu da Abba ba kanta Ak'asa tashiga yin Addua cikin zak'in murya"daga Abban har muslima d'in da mugun kallo Hjy jamila ke jifarsu duk ummi da Eyyah na lura da ita"bayan Angama Abbie yayi gyaran murya yana fad'in Alhamdulillah!  muna godiya ga Allah d'aya nuna mana zuwan wannan rana me Albarka"muna fatan Allah yajik'an Isma'il da Aysha (mahaifin dollars da mahaifiyar muslima) duk suka Amsa da Ameen,banda Hjy jamila da Malika da kabeer"Abaya Abubuwa sun faru masu kyau da mararsa kyau"Amatsayina na Uba gareku sulaiman da kuma kaka gareku ku yara na yanke hukunci kuma har na zartar Ayau bayan tasowa daga sallar juma'a Anan masallacin Anguwar nan mutane sun shaida d'aurin Auren *yusuf da halimatu* wato Muslim da muslima ...na gaji da ganin babban mutum ba iyali !na zab'a masa halimatu sbd nasan zai rik'eta bisaga Amana"duk lokacin da kuka so zaku tare Abinku"kaima suraj na zab'a maka husnah Amatsayin Abokiyar rayuwarka"An saka ranar

Aurenku da ita wata 6 masu zuwa"kabeer da Ramadan inaso kafin wata 6 yacika ku fito da mataye ko kuwa na had'aku Aure da wad'anda na gadama"sai Abu na gaba sulaiman kaima zaka k'ara Aure nanda wata 4 masu zuwa in sha Allah nine zan zab'a maka wacce zaka Aura"umarni ne ba shawaraba"kai kuma habibu bazance ka k'araba sbd kayi dacen mace ta gari idan kuma kana buk'atar K'arin zaka iya"sai mgn ta k'arshe Naseem nanda sati biyu zai koma America da karatunsa ,babban mutum ne yabiya masa"ke kuma marar mutunci na baki kema wata 6 ki fiddo miji ko kiji labarin Aurenki "yak'are maganar yana kallon Malika da jinta na wucin gadi ya d'auke........✍️

zazzafan sharhi guys😎

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba koki siya kika fitar Allah ya isa banyafeba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

.........gaba d'aya parlourn tsit yayi"kowa nabin Abbie da kallo"wasu zuciyoyinsu fal farin ciki dajin dad'in wannan Had'i da Abbie yayi"yayinda wasu kad'an daga ciki zuciyoyinsu bak'i k'irin suna tafasa.....tunda yaji kalaman Abbie yake taunar lip nasa na k'asa kamar zai hudashi"saida yaji zafi ya tabbatar da ba mafarki bane yakeyi da gaske ne"saidai Abin yamasa tamkar Almara"ko a mafarki bai tab'a zaton zai samu muslima da sauk'i irin hakaba"d'azun fa yaketa tunanin yadda zai samu mafita Ashe A lokacin tama jima da zama matarsa"tamkar yaje ya rungume Abbie haka yakeji sbd tsananin k'aunar tsohon dayaji tana k'aruwa Aransa "Atake Annuri da farin ciki suka da baibaiye fuskarsa da zuciyarsa....sam wannan ba Adalci bane! kuma ni Ancimun fuska da Akace Alh yak'ara Aure "wato niba mace ta gari bace kenan?kowa yasan kabeer shike son husnah shine za'a bama sur....yimun shiru! daddy yakatse Hjy jamila cikin zafin rai yana cigaba da cewa" kin isa ki nunawa mahaifina Abinda yafi daidai ne?"kuka ta fashe dashi tana kallon su Malika tace ku tashi muje"Naseem kuwa ko Ajikinsa da mommy sbd yasan halinta yaja mata"murna biyu yakeyi zai koma k'asar waje ga kuma murnan Auren muslima da dollars "saidai idan yatuna zai rabu da siyama sai yaji wani iri... shashshekar kukanta yasaka gaba d'aya sauran mutanan dake cikin parlourn binta da kallo"mama nah lafiya?"cewar Abba"nifa Abba yayana ne uwa d'aya uba d'aya haka na d'auke sa,shine kuma

zai zama mijina ?ni bana sonsa kuma kunya zanji daz.....kallon da daddy ya watso mata yasaka ta had'iye sauran maganarta"tashi ki bama mutane waje"kar Allah yasa ki soshi d'in"shidai dollars nata kallonta har Naseem ya matsa kusa da ita yamik'ar da ita tsaye suka fita"da Ido yarakasu har suka fice daga cikin parlourn "ya sauke numfashi yana makama suraj harara dake zungurinsa da k'afa"tunani yakeyi dama Abinda ya guda kenan tun farko, kar tace bata sonsa shiyasa be sanar mata soyayyarsa tun tuniba"yakuma ji dad'in yadda tace ta d'aukesa kamar uwa d'aya uba d'aya"Amma zai nuna mata cewa ba wannan yanzun tsakaninsu ,da kansa zai koya mata yadda zata soshi....my friend yaya dai ko kanada Abin cewa?"banida shi daddy"Abbie nagode sosai da zab'in ka"yafad'a cikin nutsatstsiyar muryansa yana mik'ewa tsaye suka fita shida suraj.....ahhh lallai mutumin kace yau tazo maka Asa'a tunda ka zama Ango ,sai kaje ka cire jallabiyar ka saka shadda yau Akwai hidima fa"d'an murmushi yasaki beyi mgn ba sbd tsabar farin cikin dayake ciki"ada ban yadda da maganarka da kace kanada mataba sai yanzun na Amince"ko yanzun karma ka Amince "k'ilan sai kaganta da baby nah zaka yadda"suraj yadinga dariya yana fad'in kaida ko zancen tarewa da shagalin biki ba'a yiba?"dama Atsarina bana son bidi'a sbd haka babu wani Abinda za'a yi"zan d'auki matata mu tafi"dollars Ai dama tuni na dad'e da fahimtar son muslima kakeyi"Amma kayi hak'uri zamu shawo kanta"sharesa yayi yak'i mgn ya wuce side d'insa dake cikin gidan.....suna fitowa daga cikin parlourn ta k'ara k'arfin kukanta"Naseem beyi mgn ba saida suka iso can cikin lambun gidan suka zauna kan wasu kujeru na hutawa" Ahankali yace"uhmmm Anty muslima na d'auka farin ciki zakiyi sbd kin mallaki yaya Amatsayin mijin Aurenki?"kinga yadda y'an mata ke haukan cewa suna sonsa"kofa Anty Malika tana sonsa Amma baya sonta"kedai nasan zai soki....kaga Naseem ka k'yaleni da zancen wani so"idan har yana sona zai dinga b'atan rai ne? ko yau daya dawo kaga irin disgin daya mun daga na gaidashi"bazan iyaba ni bana sonsa"okay to shikenan kije kici gaba da k'in nasa"yafad'a cikin gatse fuskarsa bbu walwala yamik'e tsaye tana kiran sunansa yamata banza ya tafi"ba k'aramin haushi Naseem yaji ta bashiba"ace kamar yaya Muslim ga kyau , kud'i,jan aji,kwalisa Amma duk tace bata sonsa"lallai sokuwace ita"zai k'yaleta yaga zata sakko ko kuwa tana Akan bakanta na bata sonsa....

uban kuturu yayi kad'an ballan tana na makaho!" Cewar Hjy jamila da tsantsar tashin hankali da razani ke  Acikin k'wayar idonta"tana tsaye sai huci takeyi tamkar kububuwa "ta nuna kanta da d'an yatsa tana fad'in,ni za'a yiwa iskanci da d'iban Albarka"wlh daidai nake da kowa Agidan nan "gaban idona tsohon nan zaici fuskata....dan Allah mommy kiyi shiru musami mafitah"bazan zaunah wannan y'ar iskar yarinyar ta finiba ta dinga d'agan kai da huran hanci itaga matar bolonia"cewar Malika dake kukan b'akin ciki"kabeer yaci gaba da cewa harda wani gulmar Naseem zai tafi America "ni bai burgeniba da kud'in yabashi da shine zamuji dad'i....shiru sukayi sbd shigowar daddy cikin parlourn"gaba d'aya kabeer da Malika suka tashi"suna fita Hjy jamila ta kalli daddy ta fashe da sabon kuka"wai Alh yanzun da gaske Auren zaka k'ara kenan?"sannan Akan idonka zaka bari a Aurama muslim yarinyar nan bayan nasha nasar maka yana son Malika itama tana son....kinga da Allah ya Isa haka! musu ko jayayya kikeso nayi da mahaifina ne?"Aikin gama yariga ya gama, da muslima da Malika duka y'ay'ana ne babu wanda yafi wani A cikinsu"batun Aure muddin yana kan bakansa kinsan sbd ke bazan bujurewa umarnin mahaifinah ba....haka kace?"Eh Ai kinji"yafad'a yana tashi ya wuce samansa..... muslima ce zaune a d'akin Eyyah tanata sharb'an kuka daga Eyyah har Anty habiba babu irin rarrashin da basuyi mataba Amma tak'iji itaba bata son dollars yayanta ne "duk

idan tace wai kunya zataji ace mijin tane daga Eyyah har Anty habiba sai sunyi murmushi"ganin tak'i jin rarrashi yasaka suma sukayi biris da ita"Abbie kuwa uffan bece mataba"shidai Abinda yasani daga ita har muslim d'in gata ya musu"yasan nan gaba kad'an zata soshi..... dollars kuwa cikin farin ciki ya canza kaya zuwa milk d'in sabuwar shadda giznah wacce Akayima Aikin hannu da orange d'in zare"takalmi,hula , Agogo duk orange yasaka"ga hular yad'an kasheta daga gaban goshi ,yad'an gyara zagayayyen k'asumbarsa dake salk'i tana d'aukar Idon me kallo " yau irin k'amshin daya keyi na musammun ne"kasan ransa yana tunanin mutuniyar tasa ko tayi shiru ta hak'ura ko kuwa tana can tana kukan?? oho"Anutse yake tafiyar yana nufowa parking lot yana Amsa waya.....yaya muslim mijin Anty muslima "juyowa yayi suka had'a da Naseem dake kallonsa yana murmushi yace kayi kyau sosai yaya"Allah yasa Alkhairi "saida yagama wayar kafin ya kallesa da d'an murmushi saman fuskarsa kafin yace"Naseem yau nikake zolaya ko?"ba haka bane yaya da gaske ne "tun d'azun nake jiran fitowar ka sbd na maka godiya"naji dad'i zanbar k'asar nan ,nagode Allah yasaka da Alkhairi"Ameen ya Isa haka"Ina ka baro k'awarka taka kuma Antyn ka?"nifa ba ruwana da ita yanzun tunda bata jin shawara "ko mgn bazan koma yima taba sai idan ta Amince da Aurenku"d'an murmushi yasaki domin ya fahimci Naseem na kafa gwabnatinsa wajen muslima"beyi mgn ba kawai ya wuce yayi gaba Abinsa"kasancewar harda wasu daga cikin hadiman gidan suka ziyarci d'aurin Auren"hakan yasa suka dinga yimasa Allah yasa Alkhairi "iya lab'b'ansa kawai yake Amsawa kafin Abud'e masa mota ya shiga"su kansu duk wand'anda ke'a k'ark'ashinsa sun fahimci yau ogan nasu na cikin farin ciki"sbd yawan walwalar da suka gani saman fuskarsa"kai tsaye gidan ummansa suka nufa"k'asan ransa yana fargaban yaya ummah zata d'auki zancen Auren nasa idan ya sanar masa?"shi bema san ta yaya zai soma sanar mata ba?"fatansa Allah yasa tayi farin ciki da Auren,ta kuma saka musu Albarka"da wannan tunanin suka iso.....tun A haraban gidan daya fito daga mota yaketa yima masu gadi kyauta ta musammun harya wuto cikin gidan"Mamy ce zaune a parlourn itada yara"cikin ladabi ya gaisheta kafin ya wuce d'akin umman"tana zaune gefen bed suna vedio call da Usman "fuskarta d'auke da murmushi"jin sallamar dollars yasaka ta d'ago kanta ta kallesa tana Amsawa kafin tace"ka koma kirana daga baya ga yayanku nan ya shigo"daga haka ta katse wayar tana d'an murmushi had'e da binsa da kallo"sbd wani irin kyau na musammun dataga yak'ara yimata"ga murnan ta ganshi da manyan kaya"dama bata son k'in saka kayan Al'ada da bayayi"saidai tayi mamakin yadda ya zabga uwar rama irin haka"saman sofa ya zauna yana d'an murmushi yace"ummah Ina wuni?"na sameku lafiya?"Alhamdulillah Muslim"wai rashin lafiya kayine daka tafi? sunkuyyar dakai yayi yace"uhmm kawai"tayi shiru can tace"Ina kabaro muslima na d'auka koma tare zaku zo da ita? tana can tanata fushi da koke ita bata sona ni yayanta ne bazat....shiru yayi sbd ya manta da yayi sub'utar baki "kallon banganeba ummah ta jefesa dashi"yad'an shafa gemunsa yana koma yin k'asa da murya yace"kiyi hak'uri ummah Abbie ne yau ya d'aura min Aure da ita"ba tare daya shawarci kowaba sai d'azun yasanar mana a family meeting da Akayi", Amamakin sa sai yaji tace"Allah yasa Alkhairi "yad'an kalleta yaga babu damuwa saman fuskarta"kiyi hak'uri ummah wlh babu saka hannuna A Auren kuma....kaga niban ce komai ba muslim"nina haifeka bakai ka haifeni ba"tuni nasan son muslima kakeyi kadai b'oyemun sbd nace ku daidata da Amatallahi"itama muslima d'in nasan zata soka yanzun k'uruciya ke damunta"zancen gaskiya Ada bana sonka da yarinyar"saidai tunda Alh yamun nasiha bayan yagama ya rasu Aranar da kazo ita bayan kun tafi ya rasu"jikina yayi sanyi matuk'a"kuma na dinga tuna Alkhairin

mahaifinta da yadda uwarta ta kula dakai sadda jamila ke gallaza maka"sai naga ban kyautaba"Allah yasa Alkhairi yabaku zaman lafiya da zuria ta gari"cikin farin ciki ya Amsa da Ameen yana jin shifa yau tazo masa Asa'a"yanzun yaushe za'a yi hidimar bikin?"wlh ban saniba ummah"Abbie dai yace duk sadda na tashi mu tare gidana"to shikenan saika fara k'ok'arin had'o kayan lefe ka bata"kodai ba'a yi komai ba Anyi walima sbd neman Albarkan Auren"shidai kansa na'a k'asa yanajin idan ta shine yauma Ace su tare"dole yasamu cikin wata guda ko 40days a Ida Aikin gidansa su koma"may be daga baya ya d'auki kayarsa su tafi honey moon"ungo samun contact nata ma dinga waya"tun jiya Amatallahi ke dokin zuwan nata Ashe Ammata laifi"ta k'are maganar tana mik'a masa wayar"saida ya Amsa kafin yace"to ummah ita basai taje gidan ta kamata ziyara ba"kawai idan ta taho saiki kirani natura Naseem yashigo da ita ciki "ita muslima d'in bazata zoba?"ummah gaskiya fitanta ba yanzun ba"ko islamiya bara taje ba gobe "shiru tayi batace komai ba sai d'an murmushi tana jin dad'in wannan Aure"sbd ta gaji da ganinsa ba iyali ,tana son kafin ta mutu taga jikokinta....gashi ummah bara na tafi"yafad'a yana Ajiye mata wayar yana duba time "zuwa safen zan shigo in sha Allah"be rufe bakiba kiran sadeeq ya shigo cikin wayarsa "d'auka yayi beyi mgn ba"daga d'ayan bangaren sadeeq ya daure yana fad'in Ango Ango!! saidai muji Asama baza'a sanar mana ba?"uhmm haka Abin yazo ya gida?"Alhamdulillah! Ina wani uzurine zan kiraka"yana fad'in hakan yakashe wayar "Atare suka fito tare da ummah sbd ta masa rakkiya"Anan Amatallahi ta gaidashi"sai bayan ya fita tace ummah Ina muslima?"tana murmushi tace"muslima ta zama Amarya b'oyenta muslim keyi"Ayau aka d'aura Auren su"kai Masha Allah! Allah yasa Alkhairi"cewar Mamy cikin nuna jin dad'in ta"yayinda Amatallahi jikinta yayi sanyi"Ayanzun ta Ida yadda itada samun dollars har Abada"fatanta Allah yabata mesonta Acikin manemanta itama tayi Aurenta "daka Auri wanda baya sonka gara ka Auri me sonka"ta jima da zaton shida muslima son juna sukeyi"gashi har sun kaiga mallakar juna Amatsayin ma'aurata.....

Dollars be shigo cikin gidan ba sai bayan sallar isha'i shima sbd yunwar dake damunsa"rabonsa da Abinci tun break fast d'in safe"shiko yunwar ba yaji sbd ba Abincin bane gabansa"sai yanzun yafara jin yunwar sama sama"Addu'a yakeyi Aransa Allah yasa yasamu y'ar darun nasa "Aikuwa yasameta zaune tana cin tuffa"kanta bbu d'an kwali ta wani d'aure fuska "idanuwanta sunyi ja da kumburi sbd kukan data sharb'a"tana jin haushin Eyyah na d'aure mata fuska sbd tace bata son yaya Muslim"hakama Anty habiba da husnah ko sallama basuyi mataba suka tafi"ga Naseem shima fushi yakeyi da ita....gabanta ya fad'i dataji muryanshi yana yin sallama"kan idonsa ta tashi da sauri tabar parlourn "ya girgiza kansa yana Addu'ar Allah yasa taci Abinci"babban mutum! Uhmm Eyyah sannu da gida"yauwa sannunka"yanzun aka maka wani abun ko shima bazaka ciba?"Akamun Abinda yasamu"Ina fatan kin bama matata Abinci taci  ta k'oshi "d'aure fuska tayi tace"Ina ruwana da taci ko bataciba?"idan kadamu saika tambayeta"daga haka ta mik'e tsaye ta nufi dining area "shidai be tankaba "bema so sbd tana wannan shirmen suji haushin ta"yana mata kallon k'uruciya ke damunta Amma yasan maganinta"plate d'in naman kaji gashashshe da bowl d'in fruit salad had'e da kwanon fura ta Ajiye masa"Amm Eyyah karki dinga barinta fita saida izinina"kamar Eyyah tayi dariya saita dake ta Amsa dato kawai"Aranta tace bawan Allah shi yana sonta ita kuma ja'ira tana wulak'anci nasan yadda zanma y'ar banza"bayan Eyyah ta wuce d'aki shi kuma yaci gaba dacin Abinsa yana tunanin sahibar tasa"bayan yagama beko bi takan Eyyah ba ya wuce sashensa sbd Agajiye yake....

washe garin ranar yakama satday"kamar ko wane week hakama yau tun 8:30 am muslima data kwana d'akin Eyyah ta shirin zuwa islamiya "dukda tare da Eyyah dame Aikinta suka had'a break fast Amma Eyyan tak'i tankata"ita yanzun niyarta daga islamiya ta gudu gidan Hjy tunda ba'a sonta Agidan "ba wani break fast d'in kirki tayiba tea ne kawai tasha ta zumbula hijab ta d'auki jakarta ta fito daga cikin d'akin"tana fitowa Eyyah da Abbie dake zaune suka bita da kallo"kinada hankali kuwa halimatu?"cewar Abbie yana kallonta sbd ganin zata fita "menayi ni to?"fita naga zakiyi ne"ko kin nemi izinin babban mutum d'in ne?"nifa Abbie ban tambayesa ko?"ta fad'a cikin shagwab'a tana sakin k'aramin kuka"cak! Dollars dake k'ok'arin shigowa ya lab'e yana murmushi yana jin yadda taketa shagwab'a "ke dallah ki nutsu ko ranki yab'aci"ah ah bita Ahankali "cewar Abbie yana kallon Eyyah"kafin yamaida dubansa ga muslima yace"yusuf shine shugabanki yanzun"saikin bisa ki samu Aljannah kin sani tunda ba jahila bace ke"kije ki gaidasa yana b'angaren sa ki nemi izininsa idan ya Amince saiki je"to Abbie kasanfa halin yaya karfa yadokeni ni tsoro nakeji"Abbie na murmushi shi kansa yasan dole muslim zaisha fama da k'uruciyarta"kije bazai dokeki ba"to Abbie kodai ka kirashi tunda yana jin maganarka"ke kuma bakijin tawa ko?"bafa haka bane"to kije mana"dollars daketa dariyar shirmenta da sauri ya koma inda yafito sbd karta gansa ta fasa zuwa"yasha Alwashin kuma bbu wata islamiyar da zataje"saima ta tayashi sunyi baccin da ciwon mara ya hanashi yayi Adaren jiya.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba koki siya kika fitar Allah ya isa banyafeba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

........tunda muslima ta doshi hanyar sashen nasa zuciyarta ke harbawa had'e da bugawa"gaba d'aya yau tsintar kanta tayi dajin tsoron shiga shashen nasa"wai yanzun nan ita matar yaya Muslim ce?"saita turo baki ta zaro keys d'in motarsa daga cikin jakarta ta islamiya da nufin ta bashi idan ta shiga"tana isowa bakin k'ofar sashen saida ta harari k'ofar sannan tad'an murd'a handle d'in, sai taga ta bud'e "Ahankali ta d'an lek'a kanta, taga cikin parlourn wayam babu kowa ,saita b'ata fuska kamar ta juya komai ta tuna? oho saita shiga ciki"dollars na tsaye Asaman bene ta glass yana hangota yana d'an murmushi"daga shi sai t shirt me gajeran hannu da wondo 3 quarter "k'afarsa sanye da silipas masu taushi irin na k'asar Amuruka"cikin nutsuwar data zama jinin jikinsa yabaro inda yake tsaye yabud'e k'ofa yafita daga cikin d'akin baccin nasa"yana fitowa idanuwansa sukayi tozali da ita,tana tsaye bakin k'ofar tana shawaran

ta shiga kota k'wank'wasa??ta wani tsuke fuska "tana jin ya murd'a k'ofar gabanta yafad'i"tadai dake tad'an zabura tana matsawa baya batare data yadda tama yi gigin kallonsa fuskarsa ba....Ido yazuba mata yaga kanta Asunkuye tana wasa da yatsun hannunta "saidai ya lura da yadda jikinta ke kirma"beyi mgn ba ya wuce ya zauna kan 3 seeter tare dashan Alwashin bazai mata mgn ba,kuma zaiga bazata tanka shiba haka zata yita tsayuwa"remote d'in TV ya d'auka yafara k'ok'arin kunnah kallo"yayinda k'irjin muslima keta fat fat! kamar zatayi kuka tace"yaya Muslim Ina kwana?cikin deep husky voice d'insa yace" tsayuwar meye kikeyi Anan? yak'are maganar batare daya Amsa gaisuwar tata ba saidai kallonta dayakeyi"wannan karon ba kallon k'asan Ido daya saba jifarta dashi bane" ah ah da fararen kyawawan idanunsa yake kallon nata Azahiri"zonan ki zauna ki fad'amun menene kiketa fushi?"d'an numfashi ta sauke Ahankali ta iso d'an nesa dashi....no zoki zauna Anan "ya nuna kusa dashi"d'ago kanta tayi suka had'a Ido....babu shiri ta d'auke kanta da sauri sbd ganin irin kallon dayake Aiko mata dashi"Atake taji ta daburce had'e dajin jikinta ya mutu"Ad'arare ta zauna gefensa daga can k'arshe "oya fad'amun tura bakin na meye kikeyi?"tayi d'an mamaki sbd be cika yimata mgn fuska Asake irin haka ba"ta d'auka ko shima beson Auren...halimtuuuuuuu! uhmm ,tunanin meye kikeyi?"to yaya Muslim bakai bane baka Amsa gaisuwa taba"kuma wannan Abbie d'in ya hanani zuwa islamiya ko?"murmushinsa ya danne yace"yaushe da yaushe ne kika gaidani ban Amsaba?"saida tad'an b'ata fuska kafin Ashagwab'e tace"ba jiya bane har husnah ta dinga dariya"kuma yanzun ma baka Amsaba"tamkar bazaiyi mgn ba sai kuma taji yace"dama haka aka koya miki gaida miji ne?"da sauri ta kallesa"ya d'age gira "ta kauda kanta"yes haka Akace ki gaisheni kina can nesa dani, Nima Ina nesa dake? uhmmm?tayi shiru"bayan haka Ai bazan Amsa gaisuwar wacce bata sona ba"da safe na Amsa gaisuwar budurwata datake sona! gimtse fuska tayi tak'i mgn"saidai ta rasa meyasa taji zafin kalamansa har fuskarta ta kasa b'oyewa? "shi kuma kallonta yakeyi Aransa yanata cin dariya...can yace"meyasa Abbie ya hanaki zuwa islamiya?"tayi shiru"dake nake mgn"toba cewa yayi saina tambayeka ba"ya kyauta"da kinyi gigin fita ba tare dana saniba dana b'ata miki rai Amarya"ko dayake uwar gidama tunda inada Amaryata ko?"da sauri ta kallesa fuska Atsuke "ya kasheta da murmushi"ta d'auke kanta cikin mamaki "sbd ita bata tab'a ganin yana murmushi ba"tanata cin magani tace"niba uwar gida bace"kuma ni Ina ruwana da Amaryar"?ta k'are maganar tana k'ok'arin tashi sbd ba k'aramin haushi yabata ba"Ina zakije?"islamiya"da izinin waye?"kanta Ak'asa tana share hawayen daba tasan dalilin zuwan nasuba"yad'an girgiza kansa yace"kinsan gwabnati ta hana Aikin banza ko?"islamiya zakije driver saiya kaiki"Amma zauna ki matsamun k'afana na mintina 15 ko nayi bacci saiki tafi.... Amma yaya babu ky..."sai kuma tayi shiru"bakyaji ko my *noory*? noory kuma? ta tambayi kanta"shi kuwa waskewa yayi sbd sunan daya saka mata Azuciyarsa kenan"idan barakiyi ba kije kawai"yafad'a cikin gatse sbd ya gwadata"ta turo baki tak'i tafiya sbd tasan ba kyau k'in bin umarnin miji"badan tasoba ta saci kallonsa ta gansa zaune yana danna waya "k'asa ta sakko tace"to zan fara yimaka"bari nayi ki gama kukan saiki mun"wato had'ani da Eyyah zakije kiyi ko?"salan tace wani abun na miki...nifa bbu ruwana da ita"bece komai ba yad'an kwanta rigingine saman kujerah d'in "ita kuma ta matso tana gulmarsa cikin ranta wai yaje ya kira Amaryar tasa tazo ta masa mana"dama yaje da ita gidansu Amaryar data gane kuranta....sarai ya fahimci zancen zuci takeyi saidai kawai taji yaja karan hancinta da shafar gefen kumatunta"ta d'an sauke numfashi ta sunkuyyar dakai"zoki fara yimun"batace komai ta kalli dogayen santala santalan k'afafuwansa dake sumul jajir kamar na jinjirin da baya taka k'asa"hannunta har kirma

k'insa"yaso ya Amince yabashi yanzun zuwa gobema zai maido masa yace yafasa sbd boka yabashi tsafin da zaiyi idan ya Amshi kud'in"saiya maido masa, shi kuma daya sakasu cikin kud'ad'ensa zasu fara lalacewa daga nan yasamu karayar Arzik'i"Aganinsa idan dollars ya tsiyace zai rage masoya kuma zai dawo k'asa dashi.....motsin turo k'ofar da suraj yayi yashigo cikin office d'in yasaka sadeeq mik'ewa tsaye yana k'ak'aro murmushi yace"shikenan Abokinah Allah yakaimu goben"daga haka yabama suraj hannu sukayi musabuha kafin yafita...shiru na mintina 5 yaratsa bayan zaman suraj"ganin zaman kuramen ya ishesa yayi saurin cewa"yaka mata ka koyi manta damuwa da kuma danneta" karka manta daddy baya hayyacinsa yana a cikin sharrin Hjy jamila"so kamata yayi kasake ka nuna komai ya wuce kodan sbd taji haushi"itama muslima d'in naganta yanzun driver ya sauketa sai kuka takeyi....Ina ruwana da kukanta?"duk yadda kake zaton yarinyar nan ta wuce tunaninka suraj"ya katse suraj yana tab'e baki"uhmm uzuri zaka mata k'uruciya ce ke damunta"yaka mata ka dinga rarrashin....kallon daya jefasa dashi yasaka yakama dariya"kaga suraj idan kaima b'atan rai zakayi kaje na yafe ziyarar taka dan Allah "rashin kunya da fitsarar yarinyar nan yayi yawa"bata jin tsoron kowa"sanin kankane bazan lamunci raini ba ka kuma sani"hmm! kayi hak'uri zata dena, ni bammaga wata rashin kunya data ke makaba"idan ban maka shishshigi ba meke take da sadeeq?"saida yagama shan k'amshinsa sannan yayiwa suraj bayani yana tunanin meyasa tsakanin suraj da sadeeq kowa keson kawo zugar 'dan uwansa a wajensa??"musammun ma sadeeq ya fahimci yatsani suraj"nunawa kawai kebe yi....idan har zakaji tawa karka bashi Aron kud'i har million 100 "motar da yace"yana siyarwa k'arya ne rubace kawai sbd Ace yanada kud'i "duk wanda yace shine ba shi bane"nanma dollars shiru yayi sbd yasan gaskiya suraj yasanar masa"dan sadeeq Akwai ruba dason nuna shi yana dashi"kaga nifa dama nazone muyi mgn wlh inason husnah"na kuma rasa taya zan sanar mata wlh"kodai ka....karma kasaka ni cikin zancen ! kai nan har kaga Abinso wajenta?"shakkar ta kakeyi kome da bazaka iya sanar mata ba"?"kaga nidai taimakamun nazo kayi ko Ansami contact nata"yamutsa fuska dollars yayi yace"kafi kowa sanin halina bana son raini "sbd haka kaje ka nemi contact nata"pls muma dena zancen nata"to shikenan yayi kyau"daga haka suraj yatashi ya fita da Alama yaji haushin kalaman dollars"shi kuma be bar office d'inba sai bayan sallar isha'i "kai tsaye katafaren gidansa dake G R A yanufa"dukda ba'a gama gina gidan ba"sbd tsarin ginin gidan irin gidajen k'asashen waje ne"kusan 2yrs kenan ana gina gidan Amma har yanzun basu Ida gamawa ba"kasancewar yana Ajiye kayansa Acan"shiyasa be damuba yana isowa yanufi bath room yasakarma kansa shower! yajima yana wanka kusan mintina 25 yadauk'a a toilet d'in kafin yafito ya shirya cikin jallabiya Ash colour sabuwa dal"sai zuwa wani irin fitinannan k'amshi yakeyi"Cikin nutsuwa yafito farfajiyar gidan sbd zai fita shida driver da body quards nasa yad'an je wani eatery yaci Abinci"rabonsa da Abinci tun break fast"daga kawai ad'aukesa Amasa rakkiya"saida motoci guda ukku zuk'a zuk'a suka fita Atare dashi"ni kuwa nace shegiya nera🤭.... A b'angaren muslima kuwa har suka iso bugajes house's kuka takeyi"idanuwanta sun koma yin ja da kumburi"hakama lips nata"ga k'asan zuciyarta tana jin zafin dollars "suna gama parking ta fito tana lura da suraj na kallonta ta wuce sashen su Eyyah batare data gaida shiba"Eyyah ce kawai a parlourn "Anty habiba tuni sun tafi gida"Abbie ma baya gidan"daga Eyyah sai masu Aikinta su biyu dake cikin kitchen"muslima na ganinta taje ta fad'a jikinta tana sakin sabon kuka"kinga ya Isa haka takwara! "komai yakusan xuwa k'arshe in sha Allah zakiyi rayuwa me dad'i"Ina babban mutum d'in yake?"ta turo baki tace"yana can Eyyah "ni babu

ruwana dashi"sai yaita mun tsawa ko?"uhmm zai dena yaka mata kisan haka shi yake ko fira sai yana ra'ayi yakeyi"yanzun ki tashi kiyi wanka kici Abinci "ni banajin yunwa Eyyah yaya yasiyamun Abinci ko?"zan dai yi sallah ne da wankan "to tashi maza kije kiyi"nide Eyyah nan zan zaunah kawai bana son can sashensu daddy"ah ah "kindai dinga zuwa kamar haka kiyi zamanki ranar da bbu islamiya "Amma zamanki sashen mahaifinki shine daidai "ta haka jamilah zata san kema y'a ce"Amma dawowarki nan gaba d'aya zai saka taga taci nassara kuma ta Isa"shiru dai muslima tayi batace komai ba ta tashi ta wuce d'akin baccin Eyyah.....

da dare......✍

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

.......da dare bayan sallar isha'i muslima na zaune a parlourn Eyyah tana cin fara soyayya "sai lumshe Ido takeyi tana ci da Alama tayi mata dad'i sosai"tana sanye da rigar bacci da hijab iya gwiwar hannu Ajikinta "sai sanyayyan k'amshi ke tashi Ajikinta"yayinda Abbie ke zaune yana kallon news na k'arfe 8:00 pm"gabansa kayan marmarine A ajiye yana d'an ci"saidai Azahiri zaka d'auka hankalinsa na wajen TV Amma a bad'ini yana tunanin dollars"k'asan ransa kuma yana jin tausayin sa"domin yasan tabbas Ayau sai yaji rad'ad'in mutuwar mahaifinsa sbd Abinda yafaru d'azun"sarai yasan halinsa be iya fushiba,kuma yana jumawa kafin ya manta da Abu "da wuya yazo gidan yau saidai k'ilan gobe kuma next week yazo.... Assalamu Alaikum! Abbie yad'ago kansa yaga naseem ne"Amsa masa sallamar yayi"shi kuma yabi muslima da kallo saida ya zauna gefenta kafin yace "Anty muslima kizo inji daddy"dam ! K'irjinta ya buga da k'arfi ta kallesa dan neman k'arin bayani....tashi maza ki canza hijab kuje"cewar Abbie fuskarsa bbu Alamar wasa"hakan yasa muslima kasa yi masa musu ,saidai idanuwanta har sun ciko da k'wallah "tana tunanin muddin wani wulak'anci za'a koma yimata wlh gobe guduwa zatayi gidan Hjy...jeka gata nan zuwa "dato Naseem ya Amsa yafita daga cikin parlourn"Abbie ya kalleta da kulawa yace"karki damu kinjiko? in sha Allah kiran naki Alkhairi ne"tashi maza kije "batace komai ba ta mik'e tsaye ta nufi d'akin Eyyah"babu jumawa suka fito Atare da Eyyah,ita Muslima ta fita, yayinda Eyyah ta zauna gefen Abbie.....gaba d'aya su 5 d'in zaune suke cikin parlourn

"Naseem ,Malika,kabeer duk suna zaune kan carpet"yayinda daddy da mommy ke zaune kan kujerah "bacin fad'uwa bbu Abinda gaban Hjy jamila keyi"gaba d'aya kanta ya k'ulle"gashi bbu fuskar ta  tambayi daddy wani Abu"sbd tunda tadawo gidan gab da magrib  yayi biris da ita"ko d'aukar tatama driver yatura shibe jeba"gashi kuma da magrib ya sanar da ita da Angama isha'i su taru itada yaranta yana son mgn dasu"taso tace taron me za'a yi? Amma sai taga bbu fuska"bata shiga damuwaba saida taga yatura Naseem yakirawo muslima"Anan ta fara d'aukar hannu game da cewa Ad'azun ta Ajiye Abinda takeyi ta tafi gida"gashi kuma d'azun da driver ya sauketa ta fito ta had'u da Abbie zai tafi masallaci ta gaidashi k'ememe tsohon yayi kamar bejiba,yanuna bemasan da itaba ya wuce Abinsa..... sallamar muslima data shigo parlourn cikin dakiya yasaka Hjy jamila koma jin fad'uwar gaba "Malika kuwa tsabar yadda takejin zafinta ko kallonta bata yiba"saidai daddy da naseem ne kawai suka Amsa sallamarta"daga gefe ta nemi waje ta zauna kanta Ak'asa ta daure tana fad'in daddy ina wuni?"lafiya qlau mama nah! gaba d'aya duk sukabi daddy da kallo har ita kanta muslima d'in "gyaran murya daddy yyi yace suyi salati 11 ga Annabi mohd S A W"bayan sun gama yafara da cewa"hak'ik'a banji dad'in Abinda yafaru d'azun ba"kun sanarmun Abinda kuka ga dama bayan Abin ba haka bane"ni kuma nayi kuskuran  yanke hukunci babu bincike,muslima da kuke gani itama y'atace kamar ku"daku da ita duk matsayinku guda A wajena ,babu wanda yafi wani"sbd haka daga yau na haramta wani cikinku ya hanata iko da Abinda ke nan gidan"tazo zata sha ruwa ke Malika sbd bakida mutunci da tarbiya kika dinga zagin mahaifiyarta da hanata ta tab'a fridge sbd kece kika siya ko?"Amma Alh fis....kar in koma mgn ki samun baki"yafad'a fuskarsa Ad'aure "gaban Hjy jamila na fad'uwa tayi shiru tana mamakin meyasa komai ya sauya?...kai kuma dayake wawane kai bayan Malika ta mareta sun fara dambe shine  saika shigarma Malika kadinga dukan muslima"ganin my friend ya shigo baka fasa ba ko? To daga yau komai tayi maka kafara sanar dani kafin ka yanke hukunci"Abinda muslim yayi maka yayi daidai"zumunci Abune me kyau wanda ya yankesa babu shi bbu rahamar ubangiji"wanda kuma yasadar dashi yanada d'umbin lada"muslima ki sake ki wala kiyi komai kikeso dabai taka shari'a ba nan gidan kune kina jina?" In sha Allah daddy"ta fad'a cikin jin dad'i"yayinda Malika da kabeer sukayi tsit zuciyoyinsu na tafasa"yayinda Naseem yaji dad'in wannan taro.....kabeer da Malika yayunkine ki basu girmansu banda rashin kunya "idan wani cikinsu ya miki ba daidaiba ki sanar mun"kai Naseem dama nasan  bakada matsala"duka su ukkun yayunkane karka ware wani Acikinsu duk matsayinsu guda"Naseem na k'ok'arin yin mgn siyama ta shigo cikin parlourn Aguje ta fad'a jikinsa tana fad'in yaya Naseem shine bakazo munci Abinci ba inata jiranka ko?"saida yaji fad'uwar gaba yad'ago kansa ya saci kallon Hjy jamila"Aikuwa yaga tana jifar su da wani irin mugun kallo"kasa yima siyama mgn yayi"domin dai ta tona masa Asiri"mommy ta hanashi zuwa sashensu Amma da dare saiya sace jiki yatafi suyi dinner sannan yadawo d'akinsa ya kwanta"Abba ya kallesu sbd dama yasan sun shak'u da juna yace"Auta nah zomu gaisa kinjiko?"nide daddy ba yaya Naseem nazo kiraba zamuci Abinci"tashi ka bita kuje mana"yafad'a yana kallonsa saiya lura da yadda yake satar kallon gefen da  uwar tasa take zaune"Aikuwa ya kalleta yaga yadda take hararar siyama"saidai tana juyowa suka had'a Ido da daddyn"sai tayi saurin kama kanta"daddy ya girgiza kansa ya mik'e tsaye yace"na sallami kowa"da sauri naseem ya d'auki siyama suka fita"yayinda muslima ta nufi d'akinta "Hjy jamila da y'an gaban goshinta basu tashiba"sai bayan kowa yatafi ,Malika ta d'ago kanta tana kukan b'akin ciki tace"meye mafitah yanzun mommy?"ki duba kiga yadda komai yacab'e"ga yadda yaya muslim yadamu da shegiyar yarinyar nan karfa wani abu

yafaru"murmushi Hjy jamila tayi me ciwo kafin tace"kima dena tunanin hakan niface jamilah"duk wanda yashiga gonata zan nuna masa iyakarsa"shi kansa daddyn naku na barsa ne sbd wasu dalilai Amma nasan tabbas tsohonsa ya zugashi"batun Muslim da wannan y'ar iskar yarinyar ki barshi a hannuna"karku sake wani Abu marar dad'i yakoma faruwa saidai babu ruwanku da ita....to mommy nimafa Akwai tawa matsalar sbd Ina son husnah wlh"cewar kabeer yana d'an murmushi"d'an jim mommy tayi sai kuma tayi murmushi tace "ba damuwa zan iya barinka ka Aureta kodan sbd dalilai guda biyu,na farko ubanta nadashi, tayi boko ,kuma ta waye"sai Abu na gaba inaso na wanke tsanar da habiba tamun Aranta ta sanadin soyayyar ku da ita"saidai bana son kasaka ran dole zaka sameta"idan ta k'iya Akwai wasu y'ay'an masu dashi daidai dakai"wad'anda suka fita komai"Amma yanzun dai musamu muslim ya Auri Malika tukum....kabeer bece komai Aransa yasha Alwashin zai nemi soyayyar husnah kawai....Afannin muslima taji dad'in wannan taro Aranta "ta kuma k'udurta bawa kowa girmansa Agidan cikin mutunci"Amma bazata d'auki raini ga kowa ba"sai bayan ta gama shirin kwanciya bacci tayi cin karo da text message na Aliyu "tana kuma hawa online nanma taga sak'onsa "murmushi kawai tayi domin dai kalaman soyayya ne irin na nuna kulawa ga mutum da sauransu"haka kawai taga kamar bata kyautama Aliyu ba na rashin kulashi da bata sonyi "hakan yasa ta daure ta masa reply d'in sak'onsa sannan ta kwanta bacci.....washe gari yakama sunday "tun wajen 8 am muslima tayi wankanta ta shirya cikin Abaya sabuwa da Eyyah ta bata maroon calour"ba k'aramin kyau tayiba"Anan tsakkiyar parlourn ta zauna tayi break fast"Agaban kowa taje ta d'ebi Abinda ranta keso"bayan ta gama ta nufi parlourn daddy sbd ta gaidashi "yana zaune yayi tagumi da Alama tunani yakeyi ta shigo"har k'asa ta duk'a ta gaidashi"ya Amsa da kulawa yana tambayarta ko Akwai Abinda take buk'ata??tana k'ok'arin bashi Amsa daddad'an k'amshin uban gayyar yafara kama hancinta ziyara"kafin kunnanta yaji mata Amon sautin nutsatstsiyar muryansa yana yin sallama"yayi matuk'ar kyau cikin shadda ash color data wadatu da jik'kak'en d'inki me kyau irin na zamani"wanda yafito da baiwar kyawun surar da ALLAH yayi masa"da gani basai An fad'aba, maik'onta kawai ya isa Amsa ga mai hasashen kud'inta"ya Aza hula k'ube datayi daidai da colour d'in zaren da Akayi Aikin shaddar"hakama takalmi da Agogo......su oh oh yau Antuna Al'ada kenan An Ajiye dabi'ar nasarah"ta fad'a cikin ranta tana d'aure fuska"shi kuma kallo d'aya yamata ya d'auke kansa yaduk'a ya gaisheda da daddy"my friend lafiya qlau da fatan ka huce bisa laifin danayi?"babu komai daddy ya wuce"to Masha Allah! yau zaka koma American ne?"Eh Amma saida yamma"yanzun haka munada meeting da governor da k'arfe 12 na safe......koda naji shiyasa yasaka manyan kaya"nifa tunda nake ban tab'a ganin yasaka manyan kaya ba.....mamanah bakiga yayankiba?"muryar daddy ta katse mata tunaninta"munfa gaisa dashi daddy a sashen Eyyah kafin nazo nan"ta k'are maganar tana mik'ewa tsaye ta fita"yayinda dollars ke sauraren k'aryar da muslima ta jero bedai tankaba sbd yasan jiya haushinsa takeji ya tursasata tadawo gidan"saidai shi kuma Aransa yatanadi irin muguntar dazai mata"shida yana shigowa gidan nan yafara yowa bemaje sashen su Eyyah ba"daddy bara natafi naga 9 am ta kusa"to shikenan my friend Allah yabada sa'a yayi muku Albarka "ya Amsa da Ameen yatashi yafita Aransa yana jin dad'in yadda yasamu daddyn shida muslima "yaga kuma tsanarta ta rage aran daddyn"yasan kuma hakan na daga cikin Aikin Abbie"wani irin tsananin k'aunar tsohon yaji ta k'aru Aransa"sakkowa yayi down stairs d'in ya lura da mommy da Malika"kallo basu isheshiba yafita"dan ko gaisuwar yauma yaji bazai iya yiwa Hjy jamila ba.....tun kafin ya shigo cikin parlourn yafara jiyo surutun muryar muslima da

dariyarta tana fad'in Allah nasan Eyyah yayi dad'i "kin kyauta da kika Ajiye mun baki bama Abbie yacinyeba.....shiru tayi sbd jin sallamar dollars"ya zauna kan kujerah fuskarsa bbu walwala ya gaida Eyyah "ta Amsa da kulawa tana fad'in ga Abin break fast can babban mutum"beyi mgn ba sai satar kallon bowl d'in gaban muslima dake cike da yam balls har guda 7 yayi"Adaidai lokacin kuma Eyyah ta mik'e tsaye"Akamun komai Anan zanci"yafad'a Anutse yana danna waya"to shikenan muslima tashi ki kamasa duk Abinda zai buk'ata Anan"badan tasoba ta tashi tana b'ata rai ta wuce"shi kuma yasaki murmushin mugunta yana Ajiye ledar daya shigo da ita kan kujerah ya d'auki bowl d'in yafita daga cikin parlourn "yayinda Eyyah ta nufi kitchen"muslima bata lura da babu bowl d'in ba saida ta gama shirya masa komai tanata gulmarsa Aranta sannan ta nufi inda Abinta yake da nufin ta d'auka saita bar masa parlourn gaba d'aya Anan taga wayam"ta d'an zaro Ido da mamaki tana waige waige Adaidai lokacin kuma dollars ya shigo da sallama can ciki"bata Amsaba sai binsa da kallo tayi"Aikuwa taga bowl d'in a hannunsa gashi yayi bala'in had'e rai"zama yayi yajawo center table d'in gabansa "kukan b'akin ciki ta saki tana fad'in meyasa zaka d'auka mun Abuna yaya Muslim??"banza yamata yafara k'ok'arin zuba kunun gyad'a cikin cup"Eyyah ! Eyyah!!!... kinsan Allah ?idan kika kirata kika sanar mata da wani Abu kukan da zakiyi sai yafi wannan dakike kan yi"Ayanzun Aikin tankamun koda badan Allah ba"d'azun kin gama yiwa daddyn k'aryar ne?"ko kuwa dama na fad'a miki Ina buk'atar ita gaisuwar taki ne?"ni wlh ban yafeba! me kikace?"yafad'a yana zaro mata fararen manyan idanuwansa" yawani sha mur"ba k'aramin kwarjini taji yama taba musammun yadda ya zaburo yana mata mgn cikin zare ido"saita kauda kanta tana fad'in nifa bada kai nakeba"shareta yayi yafara break fast nashi"tanata sharb'an kuka ta wuce zata shiga d'akin Eyyah "zoki Amsa"yafad'a kamar bashine yayi maganar ba"tama d'auka ko yam balls nata zai bata tana juyowa sai taga yana nuna mata wata leda  bak'a da hannu"turo baki tayi tak'i matsawa ta d'auka"Da k'yar ya iya gimtse murmushin da ke son kufce masa ya harareta murya babu Alamar wasa yace "*halimatu* zonan! wani iri taji ,ta rasa meyasa baya kiranta da muslima sai Ainahin sunanta?"Anan ma k'in tankashi tayi saidai kawai tazo gabansa gefen k'afafuwansa ta duk'a still tana hawaye"ke kuka baya miki wahala ne?"ki goge hawayen zan siya miki wani"cikin shagwab'a tace"nidai ba wanda Eyyah tayiba nakeso shine ka Amshe ko?"ke kika sani"ki d'auki waccan ledar yunifoam ne Aciki kije ki canza "mintina 5 na baki ki fito zamu sauke ki a islamiyar....nifa yaya Muslim Inada islamiyar danake zuwa jiya da yaune kawai banjeba "kuma next week zanjefa"duk tana maganar ne kanta Ak'asa sbd bata iya kallon k'wayar idonsa ta masa musu ko tsiwa....na fahimci kinfi buk'atar koda yaushe kita yin kuka ko?"tayi shiru "baraki tafiba ki saka?"bana son waccan islamiyar wannan ita nagadamar maidaki ki hana idan zaki iya"bata samu damar yin mgn ba suraj ya shigo cikin parlourn"ledar kawai ta d'auka tana kuka ta nufi d'akin Eyyah"suraj kuwa fuskarsa Ad'aure ya zauna dama ya shigo su gaisa da Eyyah ne"bemayi zaton zai samu dollars Anan ba"saidai ya d'auke masa kai kamarma be ganshiba"yana tunanin meyasa yake yawan takura muslima da sakata kuka??.....suna zaune kusan mintina biyu babu me mgn"can dollars yatab'e baki yana Ajiye cup d'in hannunsa yace"uhmmm ! sbd kana son fara soyayya nak'i baka goyon baya shine kake fushi?"kaga mlm ka dena dawo da Abinda ya wuce"idan baka taimakamun na sametaba fasa rayuwa zanyi ne?"Ina Mai tabbatar maka da cewa in sha Allah itace maman yarana"kai kuma kana nan zaune ka Ida tuzurancewa....sai kuma yakama b'abb'aka dariya"Adaidai lokacin Eyyah da muslima suka fito daga cikin d'akin baccin Eyyan" ba k'aramin kyau yunifoam d'in suka mataba"kalar

coffee brown "hijab d'in d'inkin jalbab" idanuwanta sunyi jajir sbd kukan datasha da Alama data shiga d'akin Eyyah ta rarrasheta"harara Eyyah ta sakar masa"shi kuwa murmushin gefen baki yasaki yana yiwa suraj Alamar zasu had'u dashi ne"kuje ta kwara kinji?"kai kuma babban mutum zaka dawo kasameni"k'in tanka Eyyah yayi ya fice cikin k'asaita yanufi parking lot "kan idon muslima data biyosa ta hango body quards nasa sun bud'e masa back sit"sai rissina masa sukeyi"ta girgiza kanta tana fad'in duk dan sbd yanada kud'i"shi kuwa yadake yanata wani shan k'amshi kasancewar sa gwani wajen jin kai"d'an juyowa yayi suka had'a Ido da ita"yasakar mata harara"Aikuwa ta murgud'a masa d'an bakinta dan dama haushinsa takeji"ta rasa meyasa ikonsa yayi yawa Akanta?"meyasa baya takura Malika sai ita?"ta tabbatar Malika bata zuwa ita islamiyar ma gaba d'aya"tana wannan tunanin ta iso ta shiga back sit ta zauna nesa dashi"taci gaba da danne danne Awaya ga jakarta da littattafai na Addini a hannunta"ta nuna kamar batasan da zamansa a motar ba.....tayi mamakin motoci har hud'u dake binsa Abaya kamar wani governor ko wani shugaba"bata gama mamaki ba saida suka iso islamiyar tasu taga yadda Malaman ke masa mgn cikin ladabi suna rawar jiki"girgiza kanta kawai tayi sbd haushi taji sun bata"musammun sbd badan Allah suke hakanba sai dan sbd kud'i"saida Akayi komai ,har Aji an bata sannan dollars yayi tafiyarsa batare data samu Arzik'in yamata mgn ba"to itama bata buk'atar maganar tasa taci gaba da Aikin gabanta....sai wajen k'arfe 12 daidai aka tashi"tana fitowa ta sami driver zaune yana jiran fitowarta"cike da ladabi ya matso yana fad'in ranki yadad'e dama yallab'ai yace nazo na d'aukeki "dato ta Amsa ta bud'e back sit ta shiga"bayan sun hau saman hanya taga ba hanyar gida sukayiba sunmayi hanyar gidan gwabnati"da mamaki tace Ina zamuje ne?"dama ogah yace idan na d'akkoki na kaiki can kisamesa"kaga nifa bbu inda zanje kamaidani gida mana"dan Allah ki rufan Asiri wlh k'in zuwanki zai jawo na rasa Aiki nah gaba d'aya "yafad'a kamar zaiyi kuka.....✍️

Wannan book d'in na kudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar mun Allah ya isa banyafe miki ba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

..........ba k'aramin tausayi muslima taji mutumin yaba taba"tasan halin dollars tabbas zai iya korarsa musammun idan yana Azuciye"saidai ta rasa miye ribarsa idan ya k'untata mata?"bata

mantaba yau saida yasakata kuka da safe"Ayanzun kuma baza tayi kukan takaicin saba saidai itama ta k'unsa masa wani takaicin irin yadda yamata da safe....babu damuwa muje inda yace d'in"ta fad'a batare data kallesaba"godiya nake ranki yadad'e "batace komai ba tana tunanin meyasa wai Aliyu yana sonta yakasa fitowa fili yasanar mata?"kullum saidai yadameta da zafin kira da turo mata messages"sai taji dama bata bashi contact nataba"tana wannan tunanin suka iso cikin haraban gidan gwabnatin"ko Ina securities ne tsaitsaye suna gadi"bayan ya gama parking yakira dollars ta waya Amma be d'auka ba"hakan yasa ya juyo ya kalleta yace saidai mu jira tukum"na kirashi be d'auka ba"nasan zai kira"k'in mgn tayi ta bud'e k'ofar motar ta fito ta jingina bayanta Ajiki tana y'an kalle kalle"Aranta tace dama haka gidan gwabnatin yake?...tana wannan tunanin kiran Aliyu ya shigo cikin wayarta hakan yasa ta d'auka suka cigaba da mgn"kusan mintina 15 tana waya Amma bbu Alamar dollars "bayan ta gama wayar ta dinga jan tsaki sbd takaicin tsaidasun da yayi"kamar Ance ta d'ago kanta"Ido kawai ta tsurama dollars tun daga nesa"yana daga  gaba mutanan sa na biye dashi tamkar shine governor d'in"ga wani haskawa da kwarjini da yayi" ya wani k'ara tamke fuska tamkar wani basarake haka yake tafiyar cikin k'asaita da d'agawa"gama meeting d'in nasu kenan "governor yabama gidajen man fetur d'in dake garin tallafi"dollars kuwa Anan bayan Angama meeting d'in yarabama mutum 10 kyautar Millon 100 da aka basu na tallafin"sosai darajarsa ta k'aru ga mutane"dukda shi dan Allah yayi Amma wasu naganin sbd Riya yayi"hakan yasa y'an jarida suka masa caaa dazai fito"shi kuma ya musu banza yayi gaba Abinsa..... d'auke kanta daga barin kallonsa muslima tayi"saidai tana ganin naci da rashin zuciya irin na y'an jaridar"tunda yak'i kulasu miye Amfanin su dinga binsa yana yarfasu?"sarai dollars ya ganta Amma kallo bata isheshiba yabi ta gabansu ya wuce"mutane na biye dashi"yawanci duk masoyansa ne da body quards nasa"befi mintina 2 da wucewa ba taji driver d'in na waya dashi ,bayan ya gama wayar ya kalleta Ad'arare sbd ganin yadda ta had'a rai "ranki yadad'e yallab'ai yace kije wajen wa'ancan motocin zaku tafi"ka kirashi kace masa bazan jeba"ta fad'a cikin yamutsa fuska tana kauda kanta"dan Allah kiyi hakuri wlh bazan iya gaya masa haka ba"kinga lokaci na tafiya kuma beson Ab'ata masa lokaci"k'in mgn tayi ta gyara hijab nata kawai ta nufi bakin get"zuciyarta Adake sbd yabata haushi daya wuce ta gabanta yanuna kamar besan da zaman suba"bayan bisa tursasawarsa ta yadda tazo nan....sosai securities d'in dake bakin get suketa kallonta da mamakin taya ta shigo harma zata fita Anan tana mace?"tana gab da  ida fita daga cikin get d'in taji k'arar motocin dollars Abayanta"k'in juyawa tayi"tana k'ok'arin tafiya taga mota guda ta tsaya gabanta.... k'irjinta yabuga dataji motsin bud'e k'ofar"Atake taji k'amshin mutumin nata"kafin tayi wani Abu Akai taji An fisgi hannunta"ta juyo ta saki k'ara tana fad'in ni kacikamun hannuna"Akan me zan je kiranka bayan ka ganni ka wuce kamar baka sanniba?"kawai saina kwashi jiki na bika sbd ga sarkin shush ko? Ada ba k'aramin haushin k'in zuwan nata da tafiyarta yajiba"Amma wa'annan kalaman nata sun saka tama bashi dariya"wato taji haushin yanuna kamar besan taba"ya lura ba k'aramin jan Aji garetaba"Amma Afili saiya koma had'e rai yaturata cikin motar da k'arfi"ba tare daya damu da masu kallonsuba"Ada taso ta masa kuka Amma saita dake ta zauna tak'i yadda tako kalli gefen dayake zaune"saidai tasha Alwashin masifa zata masa koda zai daketa"saidai bazata masa A gaban yaran saba"sai turo baki takeyi tana mgn k'asa k'asa "duk yadda dollars yakeda yawan jin mgn komai k'ank'ancin sautin murya"Amma yanzun baiji me take fad'a ba"sai satar kallonta yakeyi yana kuma danna waya"basufi mintina 10 ba suka iso wata had'ad'd'iyar private hospital"ita muslima batama san Asibiti suka zoba saida suka shigo

cikin haraban Asibitin"sai tadinga mamakin meyasa zasu zo Asibiti koshi muslim d'inne beda lafiya?"tana wannan tunanin aka gama parking driver yafita da sauri"kan idonta Aka bud'e masa k'ofar back sit"be fitaba sai Ido daya zuba mata "tayi saurin yin k'asa da kanta"meye kikeson fad'a?"tunda gulmar da kikeyi Azuciya ta kasa b'oyuwa kina fiki fiki da baki...nide dan Allah idan kana yiwa Allah kasaka Amaidani gida"ni wlh garama ka koma America d'in....ta fad'a k'asa k'asa yadda bazai iya jiba"saidai sarai duk yana jinta"saima tamke fuska yayi yace"fita muje"Ina ke nan?"ban saniba"wai dan Allah yaya muslim ni meyasa bakamun Adalci"kabi ka tsaneni ?? sai kuma ta fashe da kuka"kinga kimun shiru  kona mareki"ke meyasa bakyajin mgn ta kin rainani ko sa'ankine ni?to mijin ummah zaki fito muje ki gaidashi da jiki"yana fad'in hakan yafito daga cikin motar"saida ta goge hawayenta sannan ta fito"shine daga gaba yaransa na biye dashi da kaya nik'i nik'i Ahannunsu"tunda suka shigo Ake kallonsu har suka iso Amenity room 8"saidai be shigaba yaransa ne suka fara shiga"ya juyo ya kalli mutuniyar tasa "sai faman cin magani takeyi Abu kad'an take jira ta b'are Baki tayi kuka"saidai ganin yayi tsaye yak'i shiga yasaka ta kallesa suka had'a Ido "saurin sunkuyyar da kanta tayi tana jin fad'uwar gaba"sbd wannan kallon daya jefeta dashi ta kasa gane ma'anarsa.....yaya muslim ka shiga mana"da sauri muslima ta d'ago kanta sbd jin muryar Amatallahi da tayi"Atare suka sakarma juna harara duk dollars na lura dasu...hmmm!Aikin banza, ta wace hanya yazama yayanki ? Inba kalan dangi ba"kince nayi shishshigi last time ke yanzun me kikayi?"duk muslima ta fad'a cikin masifa"Amatallahi taja tsaki tana fad'in banida lokacinki"ta k'are maganar zata wuce ta gabanta"Aikuwa muslima ta kara mata k'afarta"tayi taga taga zata fad'i "tayi saurin fincikota tana fad'in kin Isa kimun tsaki....hannunta kawai dollars ya fisge fuskarsa Ad'aure"ta saki k'ara tana fad'in ita wlh ya k'yaleta saita rama"shi mamaki ma tabashi"ya lura yarinyar nan ba k'aramin fad'ane da itaba bata barin saita kwana"hancinta yaja da k'arfi yajata suka nufi cikin d'akin"saidai yana shiga yacika hannunta sbd tuna ko umma tana ciki"ita kuwa taso yak'yaleta ta lallasa Amatallahi"ummah da Mamy (uwargidan ummah) suna zaune kan carpet dake shimfid'e Ak'asa"sai Abban na kwance saman bed yana bacci "kallo d'aya zaka masa kasan yana jin jiki"danma yana daurewa"Mamy ta Amsa sallamarsu"Atare suka duk'a suka gaidasu"muslima ta musu ya mai jiki kafin ta saci kallonsa taga ita yake kallo"Amma suna had'a Ido ya zabga mata harara ya d'auke kansa "Abban bacci yakeyi ne?"Eh k'ilan sai zuwa k'arfe 2 ya farka"munata ganin hidima Alh Muslim Allah yasaka da Alkhairi"bece komai ba saidai ummah ta Amsa "Aranta tana tambayar kanta meyasa duk inda zashi yake yawo da yarinyar nan?"mik'ewarsa tsaye yana fad'in umma zamu wuce yasaka ta kallesa tana tasowa suka fito daga cikin d'akin gaba d'aya "saidai ita muslima daga baya ta tsaya su kuma sukayi gaba"ba k'aramin sanyi jikinta yayiba sbd Alamomi sun nuna matar bata sonta....ke! k'aramar marar kunya kingama kurarin d'azun ne sbd kin ganshi?"taji muryar Amatallahi"yamutsa fuska tayi ta kalleta tace"uhmm! ke kuma sbd kin ganshi kin kasa mgn sai bayan idonsa sbd yace kinada hak'uri ko?"cewar muslima tana zaro Ido"Adaidai lokacin kuma ta hango ummah na nufo inda suke"hakan yasa kawai tayi gaba batare data koma bi takan Amatallahi ba"sbd ta fahimci sun gama mgn"tana wannan tunanin shima ta hangosa tsaye da Alama jiranta yakeyi"rab'awa gefen umman tayi ta wuce bbu wanda yakula wani cikinsu"tana isowa murya bbu Alamar wasa yace"na lura idan ba belt nasaka nafara zane miki jiki dashiba bazaki nutsu ki dena shirmeba"Ina ruwanki da ita da zaki tak'aleta da fitina?"shiru tayi tak'i mgn kawai tayi dai k'asa da kanta"yaja tsaki ya wuce ta biyosa Abaya"koda suka shigo cikin motar k'in mgn tayi har suka

iso wata super market ta musammun"Anan ma beyi mgn ba suka fito"Atare da ita suka shiga ciki"kai tsaye wajen ma'aikatan wurin yaje yanunata yace"zata zab'i komai takeso"shi kuma yafita Abinsa "da farko taso ta k'iya "Amma kuma sai kawai ta shiga jidar komai da gayya "kuma masu tsadar gaske take d'auka "dama gata gwana wajen shan zak'i"chacoolates, biscuits,stwwets, chewing gum,big booms,lemuka na gwangwani dasu madarori na gari dana ruwa"jidarsu kawai takeyi kamar hauka"ta d'ibi nata ta d'ibi na Naseem ,ta d'ibi na siyama"sannan ta d'auki bama roba biyu manya wai Eyyah ta d'aukar mawa"su kansu ma'aikatan mamakin irin yadda ta dinga jidar kayan sukeyi, tana lodawa saman wasu baskets tana turawa"wad'anda suka cika saita barsu ta wuce"basket ukku tayi"kowane tace su zuba A leda"ta saka Aka lik'a sunan naseem Ajikin babbar ledar kayan shopping nasa"hakama siyama"nata kuma ba'a sakaba"kayan shopping nata leda biyu ne"ga k'atuwar Teddy data d'auka wacce zatayi kusan 20k"sai murmushi takeyi domin tasan dai dole ransa yab'aci"kuma dole yabiya kodan sbd kar yaji kunya yana matsayin mai dukiya"suna k'ok'arin tafiya su sanar masa ya iso wajen da ATM card a hannunsa"Anan ya lura da ledojin da sunan dake a jiki"yakuma kalli yadda taketa fara'a"Atake ya fahimci me take nufi"shi kuwa murmushin gefen baki yasaki sbd ya shirya meye zai mata"yana tsaye aka zare dubu dariya biyar da ishirin harda biyar"body quards nasa suka shigo suka dinga jidar kayan suna fita"ita kuwa daga jakarta da teddy d'inta ne kawai Ahannunta ta fito.....wajen dawowar ma zaman kurame sukayi sbd ko kallonsa batayiba"lokacin kuma Anata kiran sallar magrib"bayan sun gama parking ta fito har zatayi gaba ya tsaida ita"ta hanyar cewa wait! batace komai ba ta tsaya"da kansa yamatsa jikin boot yasaka aka fito mata da ledojin kayan shopping d'inta "sai kuma taga An rufe boot d'in"da mamaki ta waiga ta kallesa cikin shagwab'a tace"sauran ledojin biyu fa?"tab'e baki yayi tare da fad'in sadakar su za'a yi"suma wa'annan daddy ne yabada kud'i Amiki"shine sbd iyayi da gulma zakiyiwa wasu shopping d'in sbd niga me kud'in banza na biya ko?"to ba'a tursasani"idan kina ganin kinyi hakan sbd dai Agaban mutane dole na biya ,to nabiya Amma bazan bayarba....to nima bana son nawa d'in ka had'a ka bayar"ta k'are maganar tana barin wajen da sauri"ya girgiza kansa kawai yasaka aka bita da kayan"sai Akayi sa'a sashen daddy ta nufa"tana k'ok'arin bud'e k'ofar d'akinta d'an Aiken yashigo da ledoji guda biyu "Hjy jamila dake hakimce saman kujerah tace"kai Ina zakaje da ledoji?"Hjy na muslima ne "ke wayabaki kaya haka?"daddy ne yamun shopping"Malika ta kalli uwar, ta kuma kalli kayan"saidai basuce komai ba har mutumin ya Ajiye kayan yafita"ba k'aramin hayayyak'a zuciyar Hjy jamila tayiba"saidai tabari daddy yadawo suyi wacce zasuyi"idan yace matsayin muslima da yaran guda meyasa zaiyi son kai ita yasiya mata abu bayan ga naseem da malika?"tana wannan tunanin Naseem ya shigo da Alama daga masallaci yake"wayarsa yajona chargy kafin ya zauna yana lura daga uwar tasa har malikar sunada damuwa"saidai yasan damuwar tasu bata rasa Alak'a da muslima"yana wannan tunanin siyama ta shigo cikin parlourn tana fad'in yaya naseem kazo inji yaya.....in kika sake kika hau masa jiki saina kakkaryaki"y'ar iskar yarinya kina neman b'atamun yaro"Abu kad'an k'atuwa dake saiki haye samansa"zaki wuce ko sainaci ubanki....haba mommy dan....rufemin baki mutumin banza! dama jiranka nakeyi"wato bazaka fita hanyar mutanan canba, bayan suna mak'iyana ko?"yayi shiru yana kallo siyama ta fita tana kuka"tashi tsaye yayi"Ina zakaje?"cup zan d'auka ruwa zansha"daga haka yanufi kitchen"ta k'ofar baya yafita da gudu yabi bayan siyama"sai Akayi sa'a yayi cin karo da ita Ahanya"saidai kawai taji yayi sama da ita yana murmushi yace"kinga ki dena kuka karki sanarwa ummi komai"tak'i mgn ta turo baki

"kinaso ummi kema ta hanaki zuwa guna?"saita girgiza kanta"shikenan karki sanar mata"yanzun waye ke kirana?"ba yaya Muslim bane"kuma yace"muje wajensa yana d'akinsa hardani"bece komai ba yana d'auke da ita suka nufi side d'in dollars.....muslima kuwa sbd kawai ta bama su mommy haushi yasaka ta Amshi kayan"Amma bayan wannan dalilin da bazata Amsa ba"tana shiga d'akin ta cire kaya tayi wanka da sallar Azahar "bayan ta shirya cikin riga da siket na Atamfa me golden  ta fito babban parlourn gidan sbd taci Abinci"kabeer da  Malika na zaune a dining area d'in"Ahankali ta musu sallama saidai bbu wanda ya Amsa mata"Malika ma sa tsaki taja tabar wajen"muslima bata damuba ta d'ibi Abinda take buk'ata ta koma d'akinta ta zauna tafara ci.....wajen k'arfe 2:30 daddy ya shigo cikin parlourn "da Alama lunch yadawo yayi"mommy na zaune cike da takaici biyu na daddy dana shigar da Naseem yayi kitchen be dawoba"hakan yanuna mata ta k'ofar baya yabi dake kitchen d'in yatafi wajen siyama"da k'yar ta Amsa sallamar daddy ko sannu da zuwa bata masaba"yayinda itama Malika ta d'aure fuska ko kallo mahaifin nata be ishetaba sbd tana jin zafinsa yayiwa muslima shopping ita banda ita"sosai daddy yayi mamakin Hjy jamila da yadda ta nuna ko inkula da dawowarsa"dama yasan idan tana fushi dashi ko tana son yamata wani Abu yak'i yi to zata dinga yimasa irin haka"sai kawai shima ya shareta ya wuce samansa"da hanzari ta tashi ta biyosa"ta samesa yana k'ok'arin zare rigar shaddar jikinsa"gefen bed ta zauna tana cika tana batsewa duk yana lura be tankataba" Alh yanzun sbd Allah Abinda kayi shine Adalci?"kayiwa muslima shopping bayan ga Malika da Naseem baka musuba"bayan kaika haifesu "Amma shine zakayi son kai.....shiyasa kenan da k'yar kika Amsa mun sallamata? "ita kuma y'ar gold d'in taki ko kallo ban ishetaba sbd kuna jin haushina ko? ita muslima d'in ce tace na mata shopping?"Eh "naga kayan na tambaya"bece komai ba yamaida rigarsa yafito tana biye dashi"suna sakkowa k'asan Adaidai lokacin kuma naseem ya shigo da ladar kayan shopping nasa bakinsa Awashe yana k'walama muslima kira"daddy dai ya kallesa ya kalli ledar ya lura harda sunansa Ajiki"zama yayi kan kujera yana fad'in Naseem Ina zaka da leda harda sunanka Ajiki?"daddy yaya muslim ne yabani yace"Anty muslima ce dazai mata shopping shine nima nida siyama saita d'aukar mana komai yabiya"daddy na k'ok'arin mgn muslima ta fito daga cikin d'akinta da plate d'in data gama cin Abinci Ahannunta....✍️

Oh Hjy jamila Anji ta idan An santa🤭🫣🤔

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
 Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kki siya kika fitar mun Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah

#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

..........shiru kawai daddy yayi yana tunani ,domin ya fahimci dollars ne yayiwa muslima shopping d'in yace"injishi kamar yadda yasaba d'aukar nauyinta Abaya Amatsayin shine ke sakashi"yana kallo ta zauna Naseem na bud'e ledar yana zaro komai yanata murna da yimata godiya"ita dai tana kallo tana murmushi kawai"tama d'auka dollars d'in bazai basuba kamar yadda yafad'a zaiyi sadaka"Azatonta sadakar zaiyi.... daddy rai b'ace yabi Hjy jamila da wani irin kallon datasha jinin jikinta kafin ya mik'e tsaye Adak'ile yace "yanzun kinji Amsar tambayar taki ko?"gobema idan kinji Abu kiyi k'ok'arin cigaba da fassarashi da yadda ranki yabaki"ya k'are maganar yana wucewa sama"tunani yakeyi Aransa tunda muslima dangin mamanta suka Amsheta besan komai nataba sai dollars ne ke d'aukar d'awainiyarta"Ayau d'in ma zata yuyu sbd tabasu haushi tace shine yasiya mata,ko kuma muslim d'in ne yace shine yasakashi yasiya mata"gashi Hjy jamila ta kama kumfar baki wai baya Adalci "wanda sarai Abaya tasan be d'aukar nauyin yarinyar kuma bata tab'a ce masa Alh yiwa muslima kaza da kazaba"koda kuwa lokacin bikin sallah ne....gefen bed ya zauna cikin damuwa da tunani"shi kansa yarasa meyasa yakeyiwa yarinyar haka?"shigowar Hjy jamila d'akin yasaka ya kalleta da sauri yana nuna mata k'ofa yace"maza ki koma inda kika fito bana buk'atar ki Anan "to shikenan yayi kyau nagode"daga haka ta juya ta fita.....Naseem da muslima na zaune sunata santin kayan yayinda Malika tsabar bak'in ciki da takaicin wai dollars ne yayi wannan uwar siyayyar yasaka tabar musu parlourn"sai firansu sukeyi Ahaka yaya Ramadan ya shigo da sallama"Naseem ya Amsa "muslima ta gaidashi"domin kwananta biyu kenan Agidan saima yau ta ganshi"kizo inji yaya yana barandar dake shashensa"ni wai?"bayan ke Akwai wata mace Anan?"yafad'a yana kallonta"batace komai ba ta kalli naseem tace"sweet bro tashi ka rakani"yad'an zaro Ido tare da fad'in kinsan yayafa beson shishshigi ki daure Anty nah kije kidawo zan jiraki"harara ta sakar masa ta mik'e tsaye ta fita"yayinda tuni Ramadan yafita"dan yana iya wata guda kofi bema shigo sashenba sbd mugun halin Hjy jamila bata sakewa kowa fuska"idan ya had'u da daddy Amasjeed da Asuba suke gaisawa....tana tafe tana gulmar dollars Aranta wai indai be takura mataba baya jin dad'i"Aidai tafiyarsa zaiyi zata huta"sosai farin ciki ya lullub'eta"dukda bata san idan ya tafi yaushe zai dawo ba? Amma dai tana murna da tafiyar tasa.....tunda doso inda yake zaune yafara binta da kallon k'asan Ido "Atake zuciyarsa ta sanar masa wannan walwalar datakeyi na murnan zai tafi ne sbd dama d'azun idan be mantaba tace"ai gara yatafi "sanye yake da t shirt fara da jeans dark blue da takalmi bak'ak'e boot"fuskarsa tayi fiyau tayi frash"saidai babu walwala cikinta"wayoyinsa guda ukku na zube saman cinyoyinsa yana danne danne.... Assalamu Alaikum! yaya gani! ya d'auki kusan second 15 kafin yace"baki iya gaisuwa ba?"kaifa kace d'azun baka buk'atar gaisuwata ko?"ta k'are maganar tana zama daga gefensa kan wasu kujeru masu shegen kyau na hutawa"ya mutsa fuska yayi yak'i mgn yana tambayar kansa meyasa batada mantuwa kuma bata b'oye Abu Aranta?"kud'i rafar y'an 500 guda d'aya ya jawo a bayansa yana fad'in Amshi nan"ta kallesa ta kalli kud'in"na meye ne yaya?"ya d'ago kansa ya zuba mata burkitattun idanuwansa"babu shiri ta matsa ta Amsa da hannu biyu"bani wayarki"babu musu ta mik'a masa batare data tambayi meye zaiyi da itaba?"tana satar kallonsa yanata y'an danne danne Awayar tata"kafin can yamik'o mata batare daya kalletaba yace "daga

yau duk week end da yamma driver zai dinga kaiki catering skul"ta d'aure fuska tace nifa yaya Muslim wlh na iya girki basai najeba"kofa Hjy tasani catering skul nayi kusan wata ukku Ina zuwa....yayi shiru yak'i mgn"kaji dan Allah?" saida ya mula yasha iska kafin yace"naji shikenan"batun zuwana yau America babu shi....meyasa dan Allah?"nide wlh naso Ace katafi"d'ago kansa kawai yayi yana kallon ta "Atake ya gano k'in jin dad'in tafiyar tasa saman fuskarta" *wato yarinyar nan ba k'aramin k'i takemun ba* yafad'a Azuciyarsa"Amma Afili saiya ce bakiji dad'in kin tafiyar tawaba sbd kinaso na tafi kiyi yadda kika gadama ko?"to da Ina can da Ina nan bbu Abinda zai sauya"sai murnan taki tadawo Ayau da k'arfe 4pm zan tafi"ki dena jin haushin wanda baki k'auna zai zauna....nide yaya ka fahimceni man....rufemin baki! tayi shiru "tana wasa da kud'in hannunta"Ahankali tace "to idan katafi yaushe zaka dawo?"Ina ruwanki da dawowata? "ko mutuwa nayi Acan kinada matsala da hakan ne?"nasan murnama zakiyi ko?"tayi shiru tak'i yin mgn sbd yabata haushi da yadda yaketa fassarata"bayan ita ba haka bane Aranta..... shashshekar kukanta yasaka yad'ago kansa yana binta da kallo ransa Ab'ace "yarasa me yarinyar ta maidashi ne?"tashi kibani waje kona tattakaki sai kiyi kukan da hujjah"Akan me zaki tasani gaba kinamun kuka?"gaba d'aya bakida wani burin daya wuce ki b'atamun rai.....Amma ni yaya Muslim meyasa zaka dinga fassarani damun zargin da bahaka bane Araina ko?"yayi shiru"ita kuma ta share hawayenta ta mik'e tsaye "da nufin ta tafi" Ina zakije?"sashen su Eyyah"zakimun rakkiya ne?"sosai taji yabata mamaki"wai air port?"kin sani kuma kike tambaya"ta turo baki tace"wa'annan kud'in na meye kabani to?"ki kashe kawai"to yaya Muslim Ina na naseem da siyama? had'e rai yayi yace"ban saniba"meyasa duk idan Ammiki Abu saikin tambayi nasu? Toba friends d'ina bane"da k'yar ya iya gimtse murmushin da ke son kufce masa sbd yanayin yadda tayi mgn ta bashi dariya"ya lura yarinyar daruntа yayi yawa"komawa tayi ta zauna ta wani marairaice murya wajen cewa da gaske nakeyi yaya sunefa kawai abokaina "dama bayan jidda ni banida wata k'awa "itama kuma fad'a mukayi da ita"sbd wai y....dama na tambayeki?"tayi shiru"Allah sai nace nama fasa yimaka rakkiyar "ta fad'a k'asa k'asa"dole kije kimun tunda kin Amsa "nifa yaya ban Amsa bako?"zancen kikeso"yak'are maganar yana mik'ewa tsaye ya kara wayarsa Akunne yafara mgn"itama mik'ewa tsayen tayi"da hannu yanuna mata pasin cap nasa da sauran phones nasa guda biyu "ba musu ta d'auka"shine daga gaba sai ita Abayansa "sai kallonsa takeyi"sashen Eyyah ya nufa"hakan yasa ta bishi"tasan sallama zai musu.... Eyyah da Abbie na zaune kan carpet da Alama Abinci Abbie ya gama ci"dollars yafara shigowa kafin muslima"duk kakannin nasu suka bisu da kallo"ita tayi tsaye shi ya zauna suka fara mgn da Abbie "yasanar masa yanzun Air port zasu tafi Acan zaiyi la'asar sannan idan 4 ta Ida ya hau jirgi" ke wai bazaki zaunaba kikayi tsaye ne?"nifa Eyyah yaya nake jira ko?"Abbie yayi murmushin su irin na manya"suna cigaba da mgn"can muslima tace"yaya nide kataso muje Allah kuwa "k'arfe ukku ta wuce ko?"Abbie yace"bazaki dena fitinah ba?"ta turo baki "shidai uban gayyar yana kallonta da sauraronta saida suka gama maganarsu sannan yatashi ya musu sallama "sai Addu'a da saka masa Albarka sukeyi"yayinda muslima tacika tayi fam"sai fushi takeyi"suna fitowa tace"yanzun yaya ka kyauta kabarni tsaye ?"me kikace ?"tayi shiru "yatab'e baki"saita matso gefensa tace gashi"harara ya ballah mata yace ki yar ak'asa mana"sai batayi mgn ba kawai ta rik'e wayoyin ,ga kuma gudan hannunta kud'in daya bata ne"tun kafin su iso aka bud'e masa mota"suna shiga muslima tace yaya dan Allah kabarmun motar nan idan zan fita sai driver yajani da ita "tanada kyau sosai"kansa kawai ya gyad'a mata "shiru tayi sbd bata yadda zai bata Adinga kaita duk inda

takeso"tadai bari taga su dawo gida ta gani ko zai saka Abar motar Anan"dama neman mgn yasaka ta tambayesa"sbd ita kanta tasan motar ba k'aramar mota bace"ta hasaso kudinta million 50 ,saidai Azahirin gaskiya zatayi Millon 80 motar "sbd tana daga cikin motocinsa na fita tsara da kece raini.....tunda muslima take bata tab'a zuwa air port ba sai yau"tun suna cikin motar ta glass taketa y'an kalle kalle "kinga malama karkimun k'auyanci dallah"saurin nutsawa tayi sbd Arayuwa tana bala'in kama ajinta"saidai bata tankashiba sbd ba k'aramin haushi yabata ba dayace kartayi k'auyanci.....fita yayi daga cikin motar"ita kuma ta tab'e baki taci gaba da danne danne Awaya "can ta d'ago kanta Aikuwa ta hango dollars tsaye da sadeeq suna mgn"gabanta taji yafad'i "sbd ita dai tun jiya taji hankalinta be kwanta da mutumin ba"haka kawai ta bud'e k'ofar motar ta fito tabar wayoyinsa ciki"da farko dollars be lura da itaba"suna mgn da sadeeq Akan kud'in dazai Ara masa yace"cash yakeso"shi kuma dollars yace saidai yamasa transfer "suna Ahaka sadeeq yafara lura da muslima"sannan dollars ya ganta,daure fuska yayi yana tsareta da kyawawan idanuwansa yace"wayace ki fito?"Toba kiranka ummah keyiba"kin d'aga ne?"ah ah "Ajiyar zuciya ya sauke Ab'oye "yayi kuma mamakin k'ememe datayi bata gaida sadeeq ba"bayan kuma duk wanda tagansu tare tana gaidasu....jeki gani nan"Amma yaya karta gaji da kira ko?"ta fad'a cikin narke murya"satar kallon sadeeq dollars yayi yaga gaba d'aya ya maida duka Attention nasa akan muslima"bazaki wuce kijeba? yafad'a cikin zafin rai "batace komai ba ta juya ta tafi"sai a lokacin sadeeq ya sauke numfashi tare da cewa" Abokinah wacece yarinyar nan?jiyama naganka da ita"nasan kuma bayan Malika bakada k'anwa mace....banza dollars yamasa yana kallon muslima harta shige mota kafin ya maido dubansa kan sadeeq d'in Adak'ile yace"sanin bazai Amfaneka da komai ba" ni masjeed zanje idan baka son transfer d'in shikenan! haba dollars ya kakeson gayan mgn sbd Ina neman Aron kud'i wajenka?"in bacin sbd na riga na sayi wasu motocin sanin kankane inada fin million d'ari"balle kamun burgan kanada kud'i....look sadeeq! karka sake ka gayan mgn ko d'agamun murya "ko nawa zaka mallaka banida damuwa da hakan koda ni banida ko sisi"kud'i ga yadda nace zan baka tunda bakada muradi so what?"yafad'a yana d'age kafad'a"sadeeq tsabar bak'in ciki kamar ya shak'i dollars yaji"saidai yasan koda wasa yayi hakan shine a ruwa"sai yayi shiru ya wuce ya nufi wajen motarsa"dollars kuwa gaba yayi"sai bayan ya gama sallah sannan yadawo ya bud'e k'ofar motar fuskarsa bbu Annuri ya jefeta da wani irin kallon daya saka taji mugun shakkarsa"meyasa bakida hankali bakyajin mgn??"daga yau nakoma ganinki inda ban kirakiba wlh sai ranki yab'aci "yak'are maganar yana zuro kansa ya fusge wayoyinsa yafara dubawa"saidai bega kiran ummah ba"ya d'ago kansa ya kalleta yaga ta tsuke baki tana son yin kuka"ya girgiza kansa yana sauke Ajiyar zuciya ya d'an jingina bayansa Ajikin motar"yama rasa meye zaice mata"saidai yanaso yasan meyasa taje ta masa k'aryar ummah ta kirashi???" nide idan ba yanzun zaka tafiba kasaka Amaidani gida nayi sallah"nasan kuma ka duba kaga ummah bata kiraba"nayi hakane sbd karka tsaya ka kula wancan mugun ko?Ta k'are maganar cikin tsiwa.....sosai yayi mamakin kalamanta da dalilinta na kiran sadeeq mugu"saidai zafin kansa ya hanashi tambayarsa muguntar meya mata?"ya fahimci ita mutum ce da bata k'arya ko b'oye Abu zata fad'i gaskiya saidai A mutu ko Ayi rai"dama yaso yamata warning game da k'in gaida sadeeq d'in da batayiba"sai gashi kuma ta sanar masa da hakan.....yallab'ai An fara kiran sunaye fa"muryar wani body quards nasa ta katse masa tunani"ya kallesa ya jinjina masa kansa kawai beyi mgn ba"kafin yabi muslima da kallo sai d'aure fuska takeyi"*halimatoo* zan tafi! wannan karon fad'uwar gaba taji daya kira sunan nata ,yamasa wani jaa had'e da lankwasa"to

yaya Allah yatsare yabada sa'a"sosai yaji dad'in adduarta Amma ko a fuska be nunaba"iya saman lips nasa ya Amsa da Ameen kafin yace"kina jina?"uhmmm! bance ki fita ko inaba saida izinin Eyyah ko daddy ko Abbie"tayi shiru "bakya jina ne?"nafa ce to"beyi mgn ba sai matsowa yayi by surprise taji yaja karan hancinta yana fad'in matsiwaciya dake "daga haka ya juya yabar mata daddad'an k'amshin turarensa "ita kuma ta turo baki batace komai ba"saidai Aranta tayi mamakin Abinda yamata sbd tasan dai baya wasa da yara"ko siyama dake k'arama Agidan bayan wasa da ita"basar da wani tunaninsa tayi taci gaba da danne danne Awaya "Ahaka driver ya shigo yaja motar suka hau saman titi....

Abin mamaki suna isowa gidan bayan driver  ya gama parking ta fito"shima fitowa yayi har zata wuce yayi saurin dakatar da ita ya mik'a mata key d'in motar yana fad'in gashi"banganeba?"yallab'ai yace dama idan na saukeki na baki key d'in ki Ajiye duk idan zaki fita saiki bani na kaiki Anguwa.......✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa banyafeba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

.........tsaye sororo muslima tayi tana bin key d'in motar da kallo"tsabar mamakin kalaman driver d'in tama kasa mgn"itafa dama sbd kawai taja mgn yasaka ta masa zancen"kuma da gaske har cikin ranta tana masifar son motar..... Amsa kawai tayi ba tare datace komai ba ta wuce"saidai ranta yabata kodai sbd yanaso wani Abu yasami motar shiyasa yabada key d'in Abata "ta yadda idan yatashi yimata hukunci bbu wanda zaiga laifinsa"gaba d'aya zuciyarta sai hasashe hasashe take mata "tak'i yadda cewa dollars tsakaninsa ga Allah ya Amince  yabada key d'in babu wata manufa Aransa..... Anty muslima Ina zaki da wa'annan sabbin kud'in bugun Abuja?"taji muryar Naseem"da sauri ta sauke Ajiyar zuciya tana kallon gabanta"Ashe har ta shigo cikin babban parlourn sashen batama saniba sbd tayi zurfi atunani"lura da irin kallon tsanar da Hjy jamila ke zaune tana jifarta dashi yasaka ta zauna gefen naseem batare datayi niyar zaman ba"wai wani wajen kikaje ne Anty muslima?"Eh mana "ba nace kazo ka rakaniba kak'i?"kaga dakaje kaima daka samu bugun Abuja d'in Awajen yaya Muslim"wai dama shine yabaki?"Eh mana "air port na rakasa dawowata kenan....Ido kawai Hjy jamila ta tsurama

fuska Ad'aure"daga Eyyah har likitan da kallo suka bishi"yayinda zuciyar Hjy jamila fes"mik'ewa tsaye kawai muslima tayi ta fita sbd kukan daya taso mata"shi kuma doctor d'in saiya bi bayanta..... Eyyah Ina wuni ya mai jiki?"ta koma maimaita mata gaisuwar"idan ban wuniba zaki ganni ne?"kinzo gaida me jiki bayan kina fatan Allah yasa ta mutu Anan d'in"kuma kinzo sbd kar ace baki zoba ko? haba Eyyah me.....rufemin baki mutumin banza! ku tashi ku bani waje tunda ka zama sallamamme"Akan me zan Amsa gaisuwar ta?"daga ita har y'ar tata gaisheni sukeyi ko kuwa da daraja suka d'aukeni??"to bari kiji ! duk Abinda kayi me kyau ko marar kyau Awannan rayuwar sai Ammaka"kema kin haifa nan gaba uwar miji zaki zama"sannan ga y'a mace kinada ita yadda kikayiwa kishiyarki ko y'ar kishiyarki haka kema za'a yiwa y'arki.... innalillahi! meyayi  zafi Eyyah? mena miki kika tsaneni?"cewar Hjy jamila tana sakin kukan munafurci"sulaiman tashi kaja matarka da y'arka ku bani waje tun kafin na sab'a maka"daddy bece komai ba ya kalli su hjy jamila da Malika ya musu Alamar su fita"shi kuma yayi k'asa da murya yana fara bama Eyyah hak'uri ta masa banza......muslima na fitowa daga cikin d'akin ta fashe da wani irin kuka mecin rai"ta rasa sai yaushe mahaifinta zai sota ya k'aunaceta kamar sauran y'ay'an sa? saidai tasan duk rashin uwa yaja mata haka" tana cikin kukan ta d'ago kanta "cikin sa'a ta hango dollars na doso ta shida yaransa"k'ara k'arfin kukanta tayi ta toge gefen bango"Adaidai lokacin doctor d'in yafito daga cikin d'akin shima"ada wajenta zai nufa saidai hango tafowar dollars yasaka yafasa yayi dai tsaye"shi kuwa mutumin naku daure fuska yayi tamau kamar besan meye dariya ba"tunda ya hangota tana kuka ransa yabashi game da Alluran ne"be gama tabbatar da hakan ba saida yaga doctor d'in yafito daga cikin d'akin "yana isowa tun kafin yatambayi meye dalilin kukan nata ta d'ago kanta suka had'a Ido dashi"daga gefenta kawai yaja yatsaya be tankaba "yaya ka ganshi wai dole sai yamun Allura"shine daddy yadinga zagina wai na bisa yamun ko?"koma had'e rai dollars yayi yana jin wani Azabebben kishi na taso masa"ya fahimci doctor d'in beda kunya besan Aikin saba"irin mugun kallon dayake Aiko masa dashi yasaka shi saurin cewa"yallab'ai inaso amata ...na tambayeka wani Abu ne?"sbd haka baza'ayi Alluran ba tunda bata so....be rufe bakiba Hjy jamila da Malika suka fito daga cikin d'akin "d'auke kai yayi tamkar be gan suba"sbd yau y'an jin kan nasa na kusa"su kuwa duk sunji kalamansu"Hjy jamila kuma tasha Alwashin sanar ma daddy ba'a yimata Alluran ba sbd ta rainashi kuma muslim na goyon bayanta"wuce ki koma d'akin Azo Abaki sallama"ya k'are maganar fuska Ahad'e "ba musu ta koma d'akin yaja tsaki yana d'age kafad'a yace" ka iya Aikinka ko kuwa nayi maka sanandin daka barsa har Abada"daga haka yayi gaba be jira cewar saba....daddy nata bama Eyyah hak'uri muslima ta shigo"ta nemi waje ta zauna"ka tashi kaje kabi matarka ku tafi "ni ban k'ullace kaba Araina ba sbd nasan baka hayyacinka"saidai nan gaba kad'an zamu kawo k'arshen ta "ita wannan marainiyar Allah kana Aibatata ba laifin tsaye bana zaune"sai Allah yasa itace ta k'warai Acikin yaran naka, sai kuma naseem dake tasowa Ayanzun" dandai kabeer da Malika ka sani mugun halin uwarsu suka d'auko....shiru dai daddy yayi bece komai ba"ya mike tsaye da nufin yafita"saiga dollars da wani doctor sun shigo Atare "d'an murmushi daddy yace"my son kayi wuyar gani"Ina busy ne daddy shiyasa"Ina wuni?"lafiya qlau"daga haka dollars yayi shiru sbd shima kansa yafara yarda Hjy jamila sai yadda tayi da daddy"Aganinsa yin baya da daddyn ko canza masa fuska bashine mafitah ba"daddy tafiya zakayi ne?"yafad'a da d'an murmushi saman fuskarsa "Eh "kai da yaushe zaka koma ne?"nifa daddy sai next week zan koma fa "ko zaku wuce dasu Eyyah gida tunda sallama Ake rubata mata"dato daddy ya Amsa "shi kuwa dollars yayi hakane sbd Hjy jamila taji haushi "kuma Akwai

inda zaije shida mutanansa "dukda idan yaso uzurinsa bazai hana yasaka koda driver ne yamik'a suba.....gaba d'aya suka fito daga cikin d'akin "dollars na rik'e da basket d'in da aka kawo Abin break fast Aciki"yayinda muslima keta d'aure fuska sbd bataso ta shiga motar daddy "body quards nasa na ganinsa rik'e da kaya suka nufesa sbd su Amsa saiya musu Alamar su bashshi"hakan ba k'aramin faranta ran daddy da Eyyah yayiba"hakan yanuna musu cewa komai dollars yazama Aduniya suna nan Amatsayin su na manyan shak'ik'ansa, kuma makusan tansa dake gaba dashi...."ita kanta muslima tayi mamakin d'aukar kayan da yayi"saidai kallo be ishetaba sbd yabata haushi daya ce subi daddy"Hjy jamila da Malika na tsaye gefen motar sunata k'ullah mugun nufinsu suka gansu kawai"dollars kallo bata isheshiba ya matsa ya bud'e back sit yana fad'in Eyyah kuzo ku shiga"Eyyah batace komai ba tazo ta shiga muslima kuwa turo baki tayi idonta taf k'wallah"duk dollars na ganinta"Allah ya gyaramun yarinyar nan"yafad'a Azuciyarsa yana isowa dab da ita"ya wani d'aure fuska yana fad'in meye kike jira da bazaki shigaba?"batace komai ba ta shiga ta rufe"malika ta bud'e daga gudan sashen ta shigo suka saka Eyyah A tsakkiya"yayinda Hjy jamila ke gidan gaba kusada daddy"ranta bak'i k'irin sbd bataso tafiyar tare dasu ba"tasan kuma daya saukesu tafiyarsa zaiyi"sadda zai dawo gida Agajiye"kuma dokar sace besan matsawa da dare, bbu zancen ta kamasa wata mgn....har suka iso gida babu me mgn Acikinsu "daga wajen get daddy yayi parking duk suka fita shi kuma ya juya yatafi Abinsa....."muslima tabi Eyyah zuwa sashenta ,yayinda su Malika suka wuce nasu sashen.....zaune suke shida suraj Awani wayayyan wajen cin Abinci na musammun suna lunch"dan har yanzun be Ida hucewa ba da Abinda su Eyyah da Abbie suka masa last 2days"yakuma sha Alwashin zai binciki waye yaron yak'ara masa warning da babbar murya yarabu da muslima tun kafin ya nuna masa true colour nasa"cikin Jan Aji da k'asaita yakecin Abincin yana danne danne Awaya"body quards nasa daga tsaye gefe.....can yaja tsaki sbd ganin kiran sadeeq ya shigo Awayarsa "lafiya mutumin? kaida Abu kad'an saiya fusataka"tab'e baki yayi yace"sadeeq ne"na rasa meya maidani?"yace kud'i yakeso cash nace saidai transfer"yanuna bayaso yanzun yadawo waina masa transfer bayan yagama d'agamun murya"An fad'a masa ya Isa ya d'aga mun murya ne?"uhmm dollars kenan! nasan sadeeq na yawan kamaka zugata"ni kuma Ina baka shawara ta k'warai game da yadda zakayi tarayya dashi"sai kake ganin kamar nida shi kowane yanada wata manufa Akanka ko?"to bari na fito maka Amutum sadeeq babban mak'iyinka ne! inada manyan dalilai na fad'in hakan"sannan karka yadda ka bashi Aron kud'i ba wani motocin dayake siyarwa burgace kawai da rubar daya sabayi cikin Abokansa"jikina yabani yanada wata mummunar manufar daya keso ya Aiwatar idan ka bashi kud'in"shiru kawai dollars yayi yana nazarin kalamansa "Ahaka kiran ummah ya shigo wayarsa"kashewa yayi yabi kiran"bayan sun gaisa ta sanar masa An basu sallama sun dawo gida"yace Anjima da yamma zai shigo ya duba Abban da jiki"bayan ya Ajiye wayar suraj yace"idan kak'i taimakamun husnah ta zamo tawa "ni gashi nafara yak'in da kaina"koda safen nan ta kirani da taga ban kirataba"nayi hakan sbd na gwadata"kana nan zaune zanyi Aure nah! d'an murmushi dollars yasaki Akaro na farko da zamansu Awajen "kafin yace"kaine dai sabon shiga Awannan babin"idan baka saniba ni har mata gareni shaidawa yarage kawai kuyi"uhmm matar da babu sadaki ko?"Amma wacce me sa'a ce haka?"very soon zaka santa"daga haka dollars yacanza wata firan"bayan sun bar wajen sukayi sallar la'asar "kafin su nufo bugaja's House's sbd dollars zai d'auki wani sak'o d'akinsa yajema ummah dashi"bayan sun iso suraj yanufi d'akinsa dake gefen na Ramadan "dollars kuwa shima part nasa yanufa"befi mintina 35

ba yafito tamkar tauraron dake haskawa Asararin samaniya "wankane na kece raini ya d'auka"dukda ba wani nawa yayiba wajen shiryawar Amma yayi masifar yin kyau "sbd Ajininsane ko k'aramar sutura yasaka saita hau jikinsa"k'ananun kaya ne jeans bak'i da fara k'ar d'in t shirt irinta polo"sai takalmi sawu ciki "bak'ar sumarsa me sulb'i irinta buzaye sai k'yalli takeyi ya Aza pasincap samanta "yanata zuba k'amshi me kashe jiki yanufi sashen Eyyah, yana rik'e da wani Abu Aleda ga hannunsa guda "yayinda gudan hannun nasa ke zube cikin Aljihun wondonsa"har lokacin fuskarsa Ad'aure take "hakan kuma ba k'aramin kyau yak'ara yimasaba"saidai kuma Aransa rigimammiyar mutuniyar tasa ce yake tunani"ya fahimci idan beyi wani Abu Akai ba kishin yarinyar zai iya kashesa"yana wannan tunanin ya shigo da sallama cikin k'asaitacciyar muryarsa me laushi da taushi"muslima dake zaune kan kujerah tana Azkhar ta d'ago kanta tad'an lumshe Ido sbd daddad'an k'amshin turarensa data shak'a "murya can k'asa ta Amsa sallamar tana nuna kamar bata gansaba"itama tasha gayunta cikin sabon wankanta na Atamfa"......tana nufin bazata gaisheniba sbd nace ta shiga motar daddy?"yafad'a Azuciyarsa yana zama kan kujera "ya fahimci Eyyah na kitchen"shima biris yayi da ita dan beson raini"ta wutsiyar Ido yaga ta tashi ta shiga d'aki bata jimaba ta fito da ledar data saka masa suit nasa Aciki"gefensa tazo tad'an duk'a tana fad'in gashi nagode "banza yamata yak'i Amsa kuma beyi mgn ba"yaya Muslim! kanafa jina ka Amsa mana"kuma shine kasaka muka shiga mota ko?"d'ago kansa yayi yace"kina tuhumata ko *halimatu* ? ya fad'a da wani yanayi a muryarsa"shiru tayi ta sunkuyar dakai"na fahimci har yanzun ba zakiyi hankaliba ko?"ke gaba d'aya bakisan ki gaida mutaneba musammun idan y'an tsiwar naki na bisa kai"shiru tayi tak'i mgn"shi kuma yana danna waya can tace"wai yaya Muslim Ina wannan Amatallahi d'in?"ta fad'a cikin turo baki"da k'yar ya iya gimtse murmushin da ke son kufce masa yace"meye damuwarki dajin inda take?"ko kuwa kina tsoron ku had'u da itane.....Allah ya sawak'a naji tsoronta "ko rannan ma wlh in bacin ka hanani dana lallasa yarinya"ta fad'a cikin jin haushi"kinsan kuwa gidansu zanje yanzun"dan Allah yaya Muslim zanje"keda ba kyason bina har kuka kikeyi idan mun fita" yau sbd kinaso kija mgn zakice ki bini"to babu inda zanje dake"dan Allah fa nace"nifa bazan kulataba "Amma kuma karta tak'aleni ko? shiru yayi bece komai ba"kaji yaya dan Allah "ta fad'a cikin shagwab'a"ya tab'e baki yasan sbd yaje da ita take hakan"be kuma Amintaba sbd Allah zataje"yana zaton sbd ta tak'ali yarinyar suyi fad'a ne"motsin barinta wajen yadawo dashi tunaninsa"saiya mik'e tsaye shima da nufin yatafi"Adaidai lokacin Eyyah ta fito daga cikin kitchen"Ahhhh babban mutum kaine a parlourn nan?"nine Eyyah"zanje gidan ummah na dubo Abbah da jiki"wai har yanzun jikin dai?"Eh Amma da sauk'i sun baro Asibintin suna gida"to shikenan Allah yabashi lafiya in sha Allah zanje na gaidashi da jiki....beyi mgn ba sbd ganin fitowar muslima ta gyara d'aurin d'an kwalinta ta d'akko mayafi da takalmi ta fito"kallon second 5 yamata ya d'auke kansa"ba k'aramin kyau tama saba"saidai rigar jikinta ta bayyana coca cola shape d'inta.....ke kuwa Ina zakije yanzun da yamma?"Eyyah tare fa da yaya zamu tafi....dama nace zanje dake ne?"shiru tayi taje ta zauna kan kujerah batace komai ba "hakama Eyyah sai kitchen data koma"dollars kuwa fita yayi"befi mintina gomaba yakirata tana gani ta masa banza tak'i d'auka "sbd taji haushi saima ta kama kuka"muryar yaya Ramadan dataji yasaka ta janye tafikan hannayenta data rufe fuskarta dasu"yaya Muslim yace kizo kuma ki saka hijab"tamkar tace baza tajeba haka taji"saidai tasan k'in zuwan nata zai rufe Ido yakarta mata wani abu marar dad'i "shidai Ramadan nata kallonta ya juya ya fita"ta mik'e tsaye tana share hawayenta ta koma d'akin Eyyah "cikin gogagun hijaban Eyyah sabbi ta zab'o irin kalar kayanta ta saka ta

fito ta shiga kitchen "Eyyah ta bita da kallo tana fad'in waike meyasa bakya raina Abin kukane?"toba  shine yajaba"shine kuma zai Aiko wai nazo"ni Allah Eyyah bana zuwa kice masa kin Hanan..... mak'alewa maganar tata tayi sbd k'amshin turare dollars dataji.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
 Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
 #sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

........da sauri muslima ta maida kallonta Ajikin k'ofar kitchen sbd ta tabbatar da shid'in ne" "Aikuwa yana tsaye hakimce jikin k'ofar ,ya rungume dogayen hannuwansa Asaman faffad'an k'irjinsa ya tsareta da mayatattun idanuwansa yana binta da wani irin kallo me wuyar fassara ,yana cije red lips nasa na k'asa dake shek'i suna d'aukar idon me kallo"d'auke kanta tayi tana turo baki Aranta tace"ba laifi yaya Muslim yanada kyau....ki wuce kuje kina b'ata masa lokaci"cewar Eyyah da itama ta lura da tsayuwar tasa"ta kuma tabbatar da cewa bazai tankaba"nifa Eyyah ban....ganin yana doso inda take cikin Isa yasaka gabanta fad'uwa ta kasa k'arasa sauran maganarta"yad'an tab'e baki Aransa yace ga tsoro ga jan fad'a"zanfa bika yaya Muslim"ta k'are maganar tana juyawa tayi waje"ya sakarma bayanta harara"Eyyah tayi murmushi kawai tabisu da kallo har suka fita"suna fitowa tace"yaya Muslim da wace mota zaka fita?"miye Amfanin tambayar?"toba key d'in motarka zan bakaba"ki barshi Awajenki zan Amsa"yak'are maganar yana yin gaba "itadai bata tankaba"lokacin data iso parking lot d'in har driver ya shiga mota bayan ya bud'e masa ya shiga"hakan yasa itama ta bud'e back sit da kanta ta shiga ta zauna nesa dashi"sai satar kallonta yakeyi da yaga zata juya ko kallo inda take saiya d'auke kansa ya wani d'aure fuska "ita kuwa bata san yanayiba"har suka iso gidan ummah babu wata fira data had'asu"saima waya da yaketa Amsawa ta mutane jefi jefi"kuma yawanci masu kiran nasa yare ne"wani maganar yayi turanci ko faransanci ko labaraci"itadai tana saurare Aranta tana gulmar wai yana jin yare daban daban"bayan sun fito daga cikin motar ta tsaya ta sunkuyyar dakai "jin motsinsa gefenta yasaka tayi saurin d'ago kanta suka had'a Ido"hannunta guda kawai  yakama yasaka mata ledar dake hannunsa tamkar me koyon mgn yamotsa lips nasa wajen fad'in ki bama ummah bayan kun gaisa"da tsoro cikin idanuwanta ta girgiza kanta batace komai ba ta kuma kasa rik'e ledar"shi kuwa d'aure fuska yayi yasakar mata ledar

Ahannunta yayi gaba"batada zab'in daya wuce nabin bayansa zuwa cikin gidan"sai k'irjinta ke bugawa fat fat"haka ta dake tana lura da yadda masu gadi keta gaidashi yana d'aga musu hannu"koda ya iso bakin k'ofar shiga babban parlourn gidan  saida yajira isowarta yana daga tsaye ya bita da kallo ta sunkuyyar dakai"duk wannan fargaban na meye ko yau muka fara zuwa dake gidan ne?"babu komai fa yaya"to zoki fara shiga,"nok'e kafad'arta tayi tace nidai dan Allah kafara shiga ko?"kuma kaifa suka fara sani Ai "ta k'are maganar cikin shagwab'a"shiru yayi bece komai ba yatura k'ofar Anutse ya shiga kafin itama ta biyo bayansa"mamy ce dasu Farooq da wasu matasan samari guda biyu sai Amatallahi duk suna zaune Acikin parlourn.....sau biyu dollars yayi sallama Mamy ta Amsa tana masa sannu da zuwa ya zauna suka gaisa yamata yamai jiki"kafin sauran yaran su gaidashi"kallon mutuniyar tasa yayi sbd jin bata gaisheda mamy ba"yana kallonta yaga suna hararan juna itada Amatallahi"tana nuna mata waje da hannu"Alamar idan baga tsoroba su fita mana"tsareta da idanunsa masu kwajini yayi yana kallon ta fuskarsa Ad'aure "kamar Ance ta kallesa"Aikuwa ya wurgo matawata uwar harara "da sauri ta gaida mamy"shi kuma ya mik'e tsaye yana fad'in umman na ciki ne?"Eh yamzun ta shiga kuje Alhajin na parlourn sa"dato ya Amsa ya mik'e tsaye ya wuce "itama muslima saita tashi tabi bayansa"sadda ta shiga cikin parlourn yana zaune gefen Abban "babban mutum da ciwo yak'ara masa rama da tsufa"ya kishingid'a k'asa kan carpet da k'yar yake mgn cikin sanyin murya da murmushin k'arfin hali saman fuskarsa"Alokacin data shigo ta tsintsi muryansa yana cewa" Allah yayi maka Albarka yusuf"koda banine na haifekaba babu irin dawainiyar da baka mun ba Arayuwa"nasan ciwon nan da wuya natashi"shiyasa nacema naja'atu ta sanar maka Adena zancen fiddani k'asar wajen nan Abarni nan na jira lokaci....sai kuma yafara tari"dollars ya girgiza kai cike da tausayawa yace"kadena fad'in haka Abba zaka tashi in sha Allah "daga haka ya kalli muslima data shigo zata zauna tana bin Abban da kallon tausayi"zonan ku gaisa da Abba "batace komai ba ta matso kusa dashi ta duk'a tana fad'in Abba Ina wuni ya jikin?"Alhamdulillah y'ata "Allah yayi muku Albarka kinjiko?"kiyi hak'uri da duk yadda rayuwa tazo miki "ki Amshi k'addara me kyau ko marar kyau"sannan ki kasance me biyayya ga nagaba dake"muddin kikayi haka zakici nassarar rayuwa"sosai muslima taji wasu hawaye na tausayinsa da kuma jin nata tausayin"ita kanta tasan tana cikin jarabawa"gata rashin uwa"gata basa shiri da mahaifinta"ga y'an uwanta y'an uba basa k'aunarta ,ga kuma masifar matar uba"sai kuma ta girgiza kanta data tuna text message d'in da Aliyu yaturo mata d'azun"game da Abinda yafaru kwanaki beji dad'i ba kuma yarabu da ita tunda bata buk'atarsa Arayuwarta "dama tunda Akayi Abin be koma kiranta ba "dama itama bata tab'a kiran saba....sallamar ummah da motsin shigowarta cikin parlourn yasakata saurin nutsuwa ta dawo tunaninta"tana jin gabanta na fad'uwa"ummah kuwa tunda ta lura da yarinyar Annurin dake kan fuskarta ya dushe"saidai bata d'aure fuskar ba"ta kuma fara zaton muslim sonta yakeyi"saidai zata masa mgn karya koma zuwa mata da ita Agidan"idan yazama dole duk inda zai saka k'afarsa saida ita to ita bata buk'atar yadinga zuwa mata da ita"ummah sannu da fitowa Ina wuni?"cewar muslima kanta Ak'asa"lafiya qlau "yamai jiki?"gashi nan da sauk'i "sai sannan dollars ya gaisheta yana lura da hararar data jefa masa"muslima ta taso tadawo gefenta Aladabce ta mik'a mata ledar had'e da cewa gashi"da mamaki umman ta Amsa Amma bata bud'a ba"tashi kije bakin get ki jirani"dato ta Amsa ta mik'e tsaye ta fita"ummah ta wurgo masa harara tana fad'in maganata dakai kenan ta k'arshe daga yau karka koma zuwamin da wannan yarinyar "tunda kaida ita kun zama tip da taya bbu rabuwa, duk inda kasanya k'afa tana biye sai

kaje kayi tayi"ga wannan ka bata kayanta bana buk'ata"sai A sannan dollars da kansa ke Ak'asa ya d'ago ya kalleta yace"ummah turarukane fa tabani na baki sai nace tabiyo ni ita da kanta ta baki tunda nan zanzo"(yayi k'arya )batama lafiya ba'a jima da sallamota daga Asibiti ba d'azun...... Amma kiyi hak'uri in sha Allah bazan koma zuwa da itaba"dama Eyyah ma tace zatazo Amma zance kawai tabarsa tunda baki son ganin dangin mahaifinah na zuwa nan"daga haka yayi shiru"sbd beji dad'in Abin ba"musammun idan ya tuna yadda mahaifiyar muslima sadda take raye ta kula dashi ta kyautata masa lokacin da Hjy jamila ke gana masa Azaba"ga kuma daddy dashima ya kula da rayuwarsa"Aganinsa be cancanci ta nuna bata son jinin suba" mik'ewa tsaye yayi da nufin yafita"sbd na fad'i Abinda ke raina shine kakejin haushi"na fahimci kawai kana son yarinyar nan ko?"nifah ummah ba haka bane "girmanki da darajarki Awajena yasaka bakyamun laifi"kiyi hak'uri bazan koma zuwa da itaba"daga haka yasakai yafita "Abba dake sauraren komai ya sauke Ajiyar zuciya da k'yar yace"baki kyautaba naja'atu "ko kare yusuf yazo miki dashi Azatona zaki soshi ki karramashi balle d'an mutum"nifa be sanniba beda Alak'a dani"sbd kawai kina Aurenah ya girmamani ya kula dani yakashe mun dukiyarsa sbd neman lafiyata"dukfa sbd darajarki yamun haka"ke meyasa bazaki so Abinda yake soba?"kodan sbd kyautata warsa gareki" miye laifin wannan y'ar tatsitsiyar k'aramar yarinyar dazaki nuna mata k'i?"nasan be sanar miki yana sontaba sbd lura da yayi baki son Ahalin mahaifinsa"saidai ni Aganin dana musu yanzun na fahimci yana son yarinyar ba k'aramin soba"nasan kuma yadda yaron nan ke miki biyayya zai iya hak'ura da ita sbd farin cikin ki"ki sake tunani"ya k'are maganar yana fara tari saiga jini ta baka ta hanci na zuba"gaba d'aya illahir jikin ummah yayi sanyi"wata zuciyar tace mata idanda yarinyar daga tsatson Hjy jamila ta fito kinada hijjar nuna baki sonta dashi"duk sai taji bata kyautaba"saidai halin dataga mijin nata yasaka da sauri ta Isa gabansa tana d'ago kansa ta aza saman cinyarsa"tana Aikin yimasa sannu"hankali tashe ta d'auki wayarsa da nufin ta kira family doctor d'insu"hannunta ya rik'e yana d'an murmushin yak'e ya girgiza kansa yace"ki bari naja'atu ciwo ya warke"Ina sonki Ina kaunarki keda zuri'arki"Ina kuma k'aunar yarinyar nan me suna  muslima"dan Allah kema kisota ki..... shakk'uwar dataci karfinsa yasaka yayi shiru yana sallati"zufa tafara ketoma ummah tana salati had'e da kalmar shahada"cikin ikon Allah Abba ya Amsa daga haka bakinsa ya datse, idanuwansa suka kafe,jikinsa yasaki Alamar rai yayi halinsa😢......*kullu nafsin za'ikatul maute*! Allah yasa mu cika da Imani.....cikin wani irin yanayi na b'acin rai da damuwa dollars yabaro parlourn "yana jin tsananin tausayin muslima"da ace yasan mahaifiyarsa bazata sotaba da tuni beyi gangancin saka soyayyarta Aransa ba "shida yakeso in har ta zama tashi tayi zaman farin ciki dashi"ummah ta maye mata gurbin uwa"yasha zama yayi tunani waiga muslima nan kwance saman cinyar ummah tanata yimata shagwab'a "ita kuma tana lallab'ata"Ashe ba zaiga ranar ba.......yaya Muslim! siririyar muryarta ta katse masa tunani" ya kalleta da sauri"ta turo baki "sai a lokacin ya lura har ya iso bakin get bema sani ba"ya jikin Abban?"da sauk'i"inaga jibi kawai India zasu tafi"dama rishin samun bizar da wuri yasaka suka kai har haka basu tafi ba"ya k'are maganar yana tsayawa daga gefenta"to Allah dai yabashi lafiya"wlh yabani tausayi "ita waccan y'ar rainin wayon mahaifinta baya lafiya ko Ajikinta.....tamkar bazai tankaba sai kuma ya yamutsa fuska yace"bayan fad'a da tsiwa da kika iya harda gulma kuma yanzun kika koyo??ni yaya Muslim gulmar me nayi daga fad'in gaskiya?"ta fad'a cikin tsiwa"be kulataba sbd yanzunma kawai yadai tankatane Amma ransa bbu dad'i"be jira driver ba yabud'e masa  k'ofar ba ya shiga da kansa"itama muslima shigowa tayi tanata kumbure kumbure ta zaunah "ya d'an

kalleta ya girgiza kansa"yaya dan Allah muje gidan Hjy "shareta yayi ya jingina bayansa Ajikin kujera ya lumshe Ido"kallonsa tayi ta wurgo masa harara Azatonta baya ganinta"saidai ta makara duk yana kallonta ta k'asan Ido"saidai be tankataba ko nuna Alamar yaga meye takeyi....yaya Muslim dan Allah nace fa? bud'e lumsassun idanuwansa yayi yana duba time 6:11 pm "meyasa bakya jin mgn ne?"yanzun da yamma gab da magrib Ina zakije?"bayan kuma ba ishashshiyar lafiya ce dakeba"ko kuwa wannan d'an iskan kukayi Appointment dashi zaku had'u??"innalillahi! nifa mutunci ne kawai tsakanina dashi bayan....zaki mun shiru ko saina bige miki baki ne?"tayi tsit hawaye na cika idonta "yaja tsaki rai b'ace yace kika sake kikamun kuka saina mareki stupid! daga haka ya maida idonsa ya lumshe"har suka iso gida ko tari muslima batayiba"Ana gama parking ta bud'e da sauri ta fita"dollars ya girgiza kansa Aransa yace zan gyara miki zama"bayan sun Ajiyeta masjeed ya wuce sukayi sallar magrib bayan ya fito ummah ta kirashi cikin sanyin jiki da damuwa ta sanar masa rasuwar mijin nata"za'a yi zana'ida washe gari da safe da k'arfe goma..... innalillahi wa inna ilaihir raju'un! yafad'a yana yanke wayar cikin yanayi na damuwa"harga Allah yana son mijin mahaifiyar tasa sbd mutumin kirki ne"cikin rashin walwala ya nufi bugajes house's "ta k'ofar baya da zata kai mutum parlourn Abbie "Anan yashiga yasanar masa rasuwar"shi kuma yasanarwa Abba da daddy"kafin dollars ya wuce sashensa"bayan ya watso ruwa yatafi masallaci yayi sallar isha'i "dukda beda walwala Amma y'ar rigimar tasa na'a ransa"da kansa Ak'afa ya Isa nan bakin titi yasiya mata manyan dak'walan kaji gasassu yanufo cikin gidan"sai Akayi sa'a yana shigowa yasameta zaune a parlourn Eyyah tayi sabon wankanta"tana sanye da riga da wondo pencil da yayi matuk'ar kamata"ta rufe jikinta da wata mini hijab da iyakarta gwiwar hannu "tanata b'ata rai da Alama Akwai Abinda ke damunta"sallamarsa dataji yasaka ta kallesa suka had'a Ido"Amsawa tayi had'e da gaidashi"dukda taji haushin Abinda yamata d'azun "saidai ta share kawai sbd nasihar da mijin ummah yamata d'azun"be Amsaba iyaka ya k'araso ya zauna kan kujerah"meke damun ki?"shine ya furta kamar bashine yayi maganar ba"sbd tunda ya shigo ya lura fushi takeyi"kamar tana jira ta shagwab'e murya tace" kagani yaya Eyyah tuwo tayi ni kuma bana cin tuwo miyan taushe"kuma ni bana son Abincin su mommy"zoki Amsa "ya fad'a yana mik'a mata ledar"ba musu ta sakko ta iso gefensa ta mik'a hannu biyu ta Amsa tana masa godiya....bece komai ba saidai ya fahimci bata san mijin ummah yarasu ba...yana kallonta ta wuce kitchen "shi kuma ya rufe Ido yana tunani"harta fito ta zauna dining area ta fara bikin cin naman da viju milk dollars na zaune yad'an kishingid'a ya rufe Ido "Ahaka Eyyah ta shigo parlourn"ta kalleta tace "kin gama fushin ke bazaki ci tuwo ba?"Eh mana yaya ne yabani wannan"sai lokacin Eyyah ta lura dashi"k'arasowa gefensa tayi ta zauna"ya bud'e idanunsa"yanzun ka shigo ne babban mutum? uhmmm ! sai kuma mukaji rasuwa ko?" cak! muslima ta tsaya da bikin cin naman datakeyi dukda tama kusan kammalawa"ta juyo ta kallesu tana fad'in Eyyah waye yarasu?"mijin ummansa ko?......✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

........ innalillahi wa inna ilaihir raju'un! kalmar da muslima kenan ta fad'a cikin nuna Alhini "gaba d'aya sai taji komai ya fita Aranta"ta dafe kanta tana tuna Ashe d'azun ganin k'arshe suka masa itada dollars?"bata san lokacin data saki kukaba"musammun data tuna irin nasihar daya mata "daga Eyyah har uban gayyar duk suna sauraronta babu wanda yatankata har tabaro dining area d'in ta wuce d'aki"Ajiyar zuciya Eyyah ta sauke tana fad'in Allah ya jikinsa yasa jinyar da yayi ta zamo kaffara Agaresa"goben in sha Allah sai muje nida muslima muyi musu gaisuwa"shiru kawai yayi idanunsa Arufe kamar me bacci"kuma Eyyah tasan sarai ba baccin yakeyiba"tamkar yacema Eyyah su hak'ura da zuwan haka yaji"Amma sai yayi shiru daya tuna cewa hanatan zai saka ta zargi wani Abu"kuma dama shida muslima ne tace sudena zuwa tare"idan sunje tare da Eyyah Ai ba laifi bane"in bacin baya son family d'in mahaifinsa suyima mahaifiyarsa kallon rashin kyautawa da tuni ya hana kowa zuwa tunda bata buk'atarsu....nasan bakaci komai ba Adaren nan Aka maka tuwo da fura?jin muryar Eyyah yasaka ya bud'e kyawawan idanuwansa ya Azasu Akanta yad'an girgiza kansa tamkar bayaso ya furta Abani furan"daga haka yayi shiru"batace komai ba ta tashi tsaye ta wuce kitchen "bata jumaba ta dawo da gidauniyar damammiyar fura wacce taji kayan had'i ga sanyi tayi"saman center table ta Ajiye masa kafin ta juya ta wuce k'ofar da zata sada mutum da parlourn Abbie"yad'an furzan da wani irin huci daga bakinsa yana gyara zamansa"sai tunani yakeyi tunda yafara tasawa ya fahimci irin yadda Eyyah ke kulawa da Abbie dayi masa komai yakeso"gashi har sun tsufa irin haka bata dena ba"inama idan Allah yasa muslima rabon sace itama sukasance irin haka har tsufansu"tunawar da yayi may be har yanzun tana can tana kukan mutuwar Abba yasaka ya matso ya d'auki furan ya motsa yafara sha....saida yasha rabin kwanon kafin ya d'auki kwanon Anutse ya nufi d'akin baccin Eyyah da muslima ke ciki... shashshekar kukanta da yadda take sauke Ajiyar zuciya shi yafara ji yana sako kansa cikin d'akin"sau biyu yana sallama Amma bata jiba, tana kwance rub da ciki saman bed d'in ta cire hijab d'in jikinta"kallon second 5 yamata ya d'auke kansa da sauri sbd ganin kayan sun kama jikinta"gefen bed side drower ya zauna ,ya Ajiye kwanon k'asa kan carpet"ganin Alamar batasan da zamansa Adak'in ba yasaka yayi gyaran murya cikin taushin muryansa data canza yace"*halimatuuuuuuu*! saida taji gabanta yafad'i sbd yadda yaja sunan da kuma muryarsa dataji ta canza"da sauri ta rarumi hijab nata ta saka tana b'ata fuska tace" shine yaya muslim saidai Aganka kawai?"kina kukan zakiji sallamata?"tayi shiru"kinsha magani?"ah ah"Amshi kisha sannan kisha magani ki kwanta"nifa na k'osh....kallon daya jefeta dashi yasaka ta had'iye sauran maganarta"wasu sabbin hawayen taji sun koma zubo mata "babu yanda ta iya ta matso ta d'auki furan tad'an sha ta Ajiye "tashi ki kamun maganin da ruwa"batace komai ba sai cin magani takeyi ta fita"ya girgiza kansa kawai

yana d'aukar wayarsa da suraj ke kira"Anan ya sanar masa rasuwar da time d'in zana'ida"yana k'ok'arin kashe wayar ta shigo cikin d'akin"koki koma kiyi sallama kona b'ata miki rai "yafad'a fuska Ad'aure"batayi mgn ba ta juya kamar zata fashe sbd fushi ta fita"sai kuma ta dawo tayi sallamar"saida ya danne murmushin dake neman sub'uce masa kafin ya Amsa"sbd ganin yadda taketa cika tana batsewa"ta Ajiye masa ledar gabansa kafin ta zauna gefen bed d'in "magungunan ya duba kafin ya b'allo yabata"batace komai ba ta Amsa ta had'a da ruwan dake hannunta Tasha"dama duk month haka kikeyi?"uhmm! Ana kaiki Asibiti?"Eh yaya sadam na kaini"had'e rai yayi yace"sbd bakida kunya shine zaki sanar masa harya kaiki Asibiti??"da mamaki ta d'ago kanta suka had'a Ido ya zabga mata harara ta kauda kanta batace komai ba "saidai tana mamakin meyasa zai fad'i haka?"kamar yadda zumuncinsu yake da ita shima sadam haka"da mamanta da mamansa uwa d'aya uba d'aya"saidai tasan zai iya fin sadam iko da ita tunda shi fannin Uba ta had'a dashi....da k'arfe nawa Ake yin zana'idar?"ban saniba"baza kije gidan gaisuwar ba"shiru tayi tak'i mgn"shi kuma ya mik'e tsaye ya fita cikin tsananin zafin wutar kishinta Aransa "ita kuwa tab'e baki tayi sbd bataga Abin b'acin rai ba"Amma tunda yace baza tajeba ba matsala"daga haka ta d'auki kwanon furan da roban ruwa ta wuce kitchen ta mayar"kafin ta dawo ta d'auki hijab nata ta saka ta d'auki wayarta da ledar kayanta data cire ta fito ta wuce parlourn Abbie ta musu sallama"wajen k'arfe 9 da wasu y'an mintina ta iso sashen su"malika na zaune tana chats daya zame mata kamar ibada" Hjy jamila kuma tana kallon TV"saidai hankalinta ba'a kan TV d'in yake ba"tana can tunanin kalaman mlm na kwanaki dayace wani Abu zai faru marar dad'i Agidan "saita fara zaton to kodai mutuwar mijin Hjy naja'atu ce daya rasu yau ,may be kuma daga baya daddy yace ko zai Aureta"da kuwa Anyi d'an k'aramin yak'i "ta Ayyana Aranta tana huci"tare dashan Alwashin gobe zata tambayi zuwa gaisuwa sai kawai taje gidan bokanta"Aduba mata idan zancen shine Atari matsalar tunda wuri"domin tunda ya sanar mata da zancen batada nutsawa tanata y'an sak'e sak'e Aranta....kallon muslima tayi itada kayan dake hannunta taja tsaki tana fad'in "kwanannan zanyi maganin wata y'ar iska Agidan nan"duk muslima naji Amma batace komai ba ta shige d'akinta ta murza key "labulaye ta janye ta bud'e windows iskan hadarin dake k'ok'arin tasowa yadinga busowa cikin d'akin"ta lumshe Ido sbd tana son lokacin damuna....bath room ta shiga ta kama ruwa tayi brush kafin ta fito, kafin ta fara shirin kwanciya bacci, saidai fuskar Abba da kalamansa na mak'ale Aranta"gefen zuciyarta kuma haushin dollars ne"saima sannan ta tuna yaufa sunday yake barin k'asar Amma gashi be tafiba kome yasa?"sbd tasan dai badan rasuwaba"tunda da yamma Akayita gab da magrib shi kuma kafin lokacin yake tafiya"ta jima tana y'an tunane tunane kafin tayi Addu'a ta kwanta.....Afannin dollars kuwa Anan b'angaren sa dake cikin gidan yawuce yayi shirin bacci"sai bayan ya gama Addu'a ya d'auki babbar wayarsa ya shiga folders d'in da pictures d'in muslima suke sunfi Hamsin"wasu tun tana y'ar 12 yrs wasu 15 yrs wasu kuma tana a cikakkiyar budurwarta"saidai gaba d'aya duk bata sani yake d'aukarsu"sai d'an murmushi yakeyi yana girgiza kansa"dama ko k'asar yabari idan yana zaune shi kad'ai haka zaita lalibo pictures nata yana gani"dukda murmushin dake kwance saman fuskarsa hakan be hana k'asan zuciyarsa fushi da itaba"shi kansa tausayin kansa yakeyi"sbd ganin yana neman ya haukata kansa Akan kishin yarinyar"gaba d'aya wata iriyar tsanar sadam d'in yaji Aransa "saidai kawai yabasar yaci gaba da kallon pics d'in har bacci yasacesa.....washe gari tun wajen 9 am dollars ya shirya cikin sabuwar farar shadda yabar gidan yanufi gidan ummah"ko break fast be nema ba,ba k'aramin kyau naban mamaki kayan suka masa

ba"musammun da Akayi masa Aiki da b'akin zare yasaka komai bak'i"tamkar wani sabon Ango haka ya koma"ga wani ni'imtaccen sanyayyan k'amshi dake fita ajikinsa "ko wucewa yayi Aguri saiya bar k'amshinsa"muslima kuwa bisaga tursasawar Eyyah ta Amince ta bita bayan ta saka zunbulelen hijab har k'asa sky blue kalar Atamfar jikinta"sai b'ata rai takeyi sbd tuna jiya dollars yace bazata jeba"ita kuma tanaso ta nuna masa tana da zuciya"driver ne ya jasu suka tafi"lokacin da suka iso k'ofar gidan cike yake da mutane"befi saura mintina 25 Ayiwa gawar sallah ba"wani irin daburcewa muslima tayi da taga dandazon taron mazan "da wasunsu badan Allah suka zoba sai dan sbd suyi suna wajen dollars,wasu kuma su kalli matan mutane"rintse Ido tayi taji dama tasaka face mark's"hannunta guda Eyyah ta rik'e suka fara tafiya....dollars na zaune gefen suraj "tunda motar ta iso tayi parking ya tsareta da Ido yana kallo har suka fito dg cikin "ji yayi tunda yake da ita bata tab'a masa kyau irin yauba"sai yaga kamar duk ita mazan dake wajen suke kallo"kan idonsa ta rintse Ido har Eyyah taja hannunta suka wuce cikin gidan"ya lumshe Ido kawai....."kai tsaye Ababban parlourn gidan suka wuce"shima ba laifi cike yake da mata"su Amatallahi na gefe sunata kuka"ba k'aramin tausayi muslima taji ta bataba"daga sashen da ummah ke zaune da hijab Ajikinta suka iso suka zauna"ummah ta taso ta gaida Eyyah"Abin mamaki sai cewa tayi muslima dake Aka zo?"uhmm Ina kwana?"lafiya qlau "taso muje ki zauna wajensu Amatallahi"dato ta Amsa ta tashi tsaye suka wuce can ciki inda yara sa'anninta suke"kallon juna sukayi itada Amatallahi"saidai basu harari junaba kamar yadda suka saba Abaya"zama kawai muslima tayi"gaba d'aya parlourn yayi tsit"bayan wasu y'an mintinah Aka shigo d'aukar gawa dake can parlourn Abba"dollars da suka shigo da mutane sai y'an kalle kalle yakeyi sbd yaga ko zai gano mutuniyar tasa..... Aikuwa ya hangota zaune cikinsu Amatallahi fuskarta da Alamar tausayi"sai Akayi sa'a itama tad'an kallo mazan da suka shigo taga kota gansa ta b'oye sbd bataso yasan tazo"Aikuwa sai gashi idonta danashi sun sark'e"ta turo baki ta kauda kanta "shi kuma yana dai kallonta har suka nufi k'ofar aka fito da gawar"Anan fa Aka kama koke koke Aciki harda muslima"wanda Amatallahi data lura tayi mamaki"kasancewar mak'abartar kusa da gida take ba'a jimaba suka dawo"Anan Aka fara yiwa su ummah gaisuwa"bayan Eyyah sun koma gaisawa ta musu gaisuwa harda Mamy"itama muslima tasowa tayi ta musu gaisuwar"sannan ta koma wajensu Amatallahi ta kalleta tace sis ya hak'urin mu ?"Alhamdulillah! Allah yajikan Abba"ta Amsa da Ameen had'e da cewa Nagode "daga haka sukayi shiru"sai wajen k'arfe 11 Eyyah tace zasu tafi"Abin mamaki sai ummah cewa tayi Abar muslima nan idan badamuwa Anjima da yamma muslim zai dawo da ita gd"dato Eyyah ta Amsa "itadai muslima tayi mamakin umman"saidai batace komai ba..... Eyyah na fitowa dollars ya lura da babu muslima "kasa hak'ura yayi yataso yanufota yana fad'in tafiya zakuyi Eyyah?"Eh Amma wannan fitinanniyar nacan naja'atun tace Abarta da yamma ka maidota gida"ba k'aramin mamaki yayiba"musammun da yaga Ajiya tanata fad'a Akan yadena zuwa gidan da ita"Afili kuwa sai cewa yayi to Eyyah muje na taka miki"ah ah babban mutum koma kaje kayi zamanka ku cigaba da Amsar gaisuwa"bece komai ba yajuya cikin nutsuwa yakoma mazauninsa"yayinda Eyyah ta wuce ta shiga mota driver yaja suka tafi......tun wajen k'arfe 1 da wasu mintina Abinciccikan da dollars yasaka Ayi order daga manyan restaurant da hotels dan y'an zaman makoki suci  suka iso"da kuma  drinks masu sanyi"sannan cikin gida Aka damo fura Aka fiddo taji k'ank'aru"Abinka da masu hannu da shuni komai yayi waja waja Awadace" tuni Aka fara rabama jamaa"dama kuma haka wasu keso"sunsan dole wajen Aci me kyau Asha me kyau tunda mamacin nada Alak'a da dollars"wajen k'arfe 2 ya shigo cikin gidan

sbd yanaso ya tabbar da taci Abinci"gashi ba tsarki bane da ita zataso tayi wanka"yana rik'e da wata leda me d'an girma irinta shopping Ahannunsa
ya wuce cikin gidan"sai lokacin yaje ya gaida mamy yamata gaisuwa "kafin ya matsa yayiwa ummah gaisuwa itada danginta da suka zo"sai d'an kalle kalle yakeyi cikin basarwa sbd yaga koya hangota"Amma bbu Alamar tana'a main parlour d'in"can yad'an yi k'asa da murya yace"ummah Ina yarinyar nan?"inaga tana d'aki ko sallah takeyi"nan dai sukaci Abinci itada yaran.....wai yarinyar nan y'ar black beauty kuke mgn Hjy?cewar Anty Amira (k'anwar ummah)"Eh kawai ummah tace saidai shi gogan bece komai ba saima mik'ewa tsaye yayi yaji ummah na sanar mata k'anwarsace ce fannin mahaifinsa"kai gaskiya tanada kirki yarinyar ga son Aiki"kince na gyara bed room naki wlh itace ta gyara tanama toilet zata wanke na barota yanxun "iya nan dollars yaji yabar wajen yana d'an cije baki kasan ransa kuma murmushi yakeyi"fatansa Allah yasa komai ya canza ummansa taso muslima"sosai yaji dad'in Abinda tayi"saima lokacin yatuna be tab'a sakata gyaran d'aki ba "yana wannan tunanin ya turo k'ofar d'akin ya shigo"k'amshin turaren wuta yadaki hancinsa "yad'an lumshe Ido ya bud'e....muslima na'a toilet tana wankewa tabar k'ofar Abud'e"saidai taji sallamarsa ,ga k'amshin turarensa daya kai mata ziyara har cikin toilet d'in "tamkar tak'i fitowa sai kuma ta daure ta fito kanta na kallon k'asa bata yadda ta kallesaba"wayace ki kama yin wani Aiki?"babu kowa" kinci Abinci?"satar kallonsa tayi yana tsaye gefen mirror "sai lokacin ta lura da shaddar dake jikinsa"kina jiran na maimaita?"Amma yaya ba cewa kayiba bazan zoba kuma bak....sai tayi shiru "tuhumata kikeyi ko?"nafaci Abinci ,ta canza topic d'in"ya tab'e baki yana tunanin ko meyasa bata son kallonsa? ki d'auka ga wannan ledar nan kiyi wanka ki canza kaya"nima zanje nadawo"to Ina zakaje yaya Muslim?"inda kika Aikeni "kina mun mgn kina kallon wani waje sbd gulma"batace komai ba ta sunkuyyar dakai k'asa"ki d'auka ki duba"batace komai ba yanata kallonta ta jawo ledar ta fara dubawa"sabuwar doguwar riga ce jallabiya sky blue "sai ledar pad da sabuwar hand bag da pants guda biyu da bra....da sauri ta b'oye su tak'i fiddowa"duk yana kallonta sai kawai yanufi k'ofa"uhmm"yau yayi kyau daya saka manyan kaya....mgn kikeyi?"ah ah fa"hmm! cikin gulmar da kika fara koyo hadda tawa kikeyi"nifa yaya Muslim kaje dan Allah Anga ka shigo tun d'azun"banza yamata yak'i fita yama tsaya bakin k'ofar sbd Abud'e yabarta"kukan shagwab'a tasaka tana fad'in nidai katafi ko ?"ganin idan yaci gaba da tsayuwa tana wannan shagwab'ar da rigimar yanayinsa zai iya sauyawa sai kawai ya wuce Abinsa"yana fitowa ummah na kawowa zata shiga d'akin ,sbd jin shirun nashi yayi yawa"d'an shafa kansa yayi yace"kayanta na Amso mata wajen Eyyah sbd ta kirani tana so tayi wanka"to shikenan ka bari da yamma ka maida ita gida tunda ga yara nan zata sake cikinsu"to ummah bara naje"daga haka ya wuce yana jin zuciyarsa fess.... muslima kuwa Ajiye ledar kayan tayi ta koma toilet d'in "ta samu towels saita cire kayanta ta fara wankanta"bayan ta gama ta koma wanke toilet d'in tas sannan ta fito ta samu bbu kowa A d'akin"saita shirya Anutse "sauran kayan data cire ta saka cikin ledar"pad d'in kuma tasaka cikin hand bag d'in da wayarta"lokacin kuma k'arfe 3 tayi"tana k'ok'arin tama fito ummah ta shigo da sallama tana fad'in muslima harkin gama shiryawa?"Eh na gama"bara na baki turare ki saka ko?"dato ta Amsa"kanta na'a k'asa harta d'akko guda biyu ta matso ta mik'a mata "da hannu biyu ta Amsa tayi godiya"ita kuma ta juya ta fita"bayan ta gama shafawa ta Ajiye su saman mirror ta rufe k'ofar d'akin bayan ta fito"dama kina ciki inata nemanki?"taji muryar Amatallahi"juyowa tayi ta kalleta kafin tace Eh wanka nayi"daga haka ta wuce taje ta zauna"tana lura da wasu mata nata yawan kallonta"ta kuma fahimci dangin ummah ne su.....sai

wajen.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
 Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
 #sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

.......Sai wajen gab da sallar magrib dollars ya shigo cikin gidan tare dasu daddy da Abbie"wanda tun kafin yashigo dasu saida yafara kiran ummah yasanar mata da zasu shigo"muslima na zaune inda sa'aninta suke ta hango dattijon kakan nata shida mahaifinta"sai dollars dake gefe ya canza kaya zuwa wani coffee brown  d'in lallausan yadi me matuk'ar tsada "wanda ya haska farar fatar jikinsa"saidai kansa ba hula"yayi wani irin sanyayyan kyau"duk y'an matan dake zaune Awajen sai iyayi sukeyi sunaji inama inama....lolx"sai satar kallon mutuniyar tasa yakeyi yaga ta nuna kamar bata ganshiba, Abbie kawai tayima mgn"ko daddy bata tankaba sbd gudun karta masa mgn ya disgata cikin mutane"kan idonta ummah ta taso fuska Asake ta duk'a ta gaida  Abbie yamata gaisuwa"kafin su gaisa da daddy"yayinda dollars ke tsaye duk wani motsin muslima yana lura dashi"can da zasu wuce suka had'a Ido da ita"da hannu yamata Alamar tazo "saita kauda kanta kamar bata ganiba"bayan fitarsu da mintina 3 farooq ya shigo cikin parlourn yana kallonta  yace"yaya Muslim yace kizo"dato kawai ta Amsa sbd ganin idon mutane"bayan haka da bazata zoba"tasan k'ilan zaice tazo su tafi gida"ita kuma sai taji zaman cikin yaran yamata dad'i"tana wannan tunanin ta mik'e tsaye tana kallon Amatallahi da itama ita take kallo kuma ranta yabata muslima da dollars son juna sukeyi"zo muje ki rakani muje wajen yaya"ba musu ta taso suka jera suka fita"tana fitowa shi kuma yana k'ok'arin shigowa ciki....da sauri tayi baya sbd ganin zata fad'a masa"sai Akayi rashin sa'a k'afarta ta turgud'e kamar zata fad'i "yayi saurin rik'e hannunta guda"ita kuma ta rintse Ido.....saidai riketan da yayi yasaka ta bud'e Idon da sauri"sai suka nutse cikin nasa"ta turo baki cikin shagwab'a tace"shine yaya da kaja na fad'i ko?"meyasa bakya duban gabanki kina tafiya"nifa Allah Ina dubawa"shiru yayi sbd lura da Amatallahi dake tsaye Abayanta tana kallon su kamar TV....ki wuce ki d'auki kayanki kizo muje gida"yaya nifa ba yanzun b.....shiru tayi sbd irin kallon dayake jifar dashi da idanuwansa masu kaifi da kwarjini"ita kuma ta shagwab'e fuska ta juya zata koma"kinsan Allah 2 minit na baki ki fito mu wuce kona b'ata miki rai "Amma yaya nifa ba tare dani kazoba

kuma....nufo tan da yayi ya saka taja da baya Atsorace har tana bige Amatallahi dake bayanta"shi kuwa d'an murmushin gefen baki yasaki wanda wacce yayi dan ita bata ganiba sai Amatallahi "wacce tunda take bata tab'a ganin yana murmushi ko dariya ba"sai taga ada beda kyau sosai bisaga yanzun da taga yayi murmushi"sai ya mata kamar Aljani sbd kyawun da yayi"ga hakwaransa farare k'al daga tsakkiyar na k'asan Akwai wushirya"lallai muslima taji dad'i " da har yake sonta....sis muje mana"taji muryar muslima najan hannunta"yayinda tuni dollars yabar wajen"ya Isa parking lot yasanar da driver yagyara parking su wuce.....fuskarta bbu Alamar jin dad'i ta shigo cikin parlourn "kai tsaye ta wuce d'aki ta d'akko ledar kayanta ta Isa wajen ummah kanta Ak'asa tace"ummah zan tafi inji yaya"d'an murmushi tayi tace"to shikenan mun gode sosai Allah yabada ladar muslima"daga haka ta wuce sukayi sallama da Amatallahi kafin ta fita"dukda gab da magrib ne Amma haraban gidan cike yake da maza"tamkar ta fad'i haka taji sbd ganin Anata kallonta"lokacin data iso bakin get harma mutumin nata ya shiga mota"sai cin magani takeyi ta bud'e back sit ta shiga bata ko kallesaba"shi kuwa yana binta da kallon k'asan Ido yana duba wristwatch d'insa "yarasa meyasa yanzun ta shirya itada Amatallahi?"yaya kagani kaja ban Amshi contact d'in kawata Amatallahi ba"tamkar ya shareta sai kuma yatab'e baki yace"kin iya kalan dangi yaushe har tazama k'awar taki keda kuke fad'a da ita? shiru tayi tak'i mgn sbd ba k'aramin haushi yabata ba"shima dama ba wata doguwar fira yake da itaba saiya shareta"Aransa yana murmushi da irin darun yarinyar"suna isowa gidan driver yayi parking tafara k'ok'arin kiciniyar fita"Amshi nan"taji Amon jarumar muryansa me dad'in sauti "saida ta turo baki kafin ta juyo taga meye zai bata?"da mamaki ta kalli keys d'in sannan ta maida kallonta Asaman kyakykyawar fuskarsa daya d'an saki bbu d'aurewar daya saba yi"shima kallonta yakeyi bece komai ba"na meye ne?"bazaki karb'a bane? batayi mgn ba ta Amsa "keys d'in d'akina ne dake  part d'in Eyyah"kije ki gyaramun tunda ke ba sallar kikeba"inaso kafin nadawo daga masjeed kin gama"da sauri ta kalli gefen driver taga ya fita"saita turo baki tak'i mgn ta fito"ta rasa meyasa motsi kad'an zai wani ce bata sallah ko inama ruwansa?"tana wannan zancen zucin ta iso sashen Eyyah"Abin mamaki ta sami yaya sadam yaka mata ziyara sunata fira da Eyyah "gefe guda kuma husnah da suraj na zaune suma suna tasu firan....to! kaga gashi tama dawo kai me cewa tafiya zakayi kayi sallah daga can ka wuce gida ko?"cewar Eyyah "itadai muslima data shigo da sallama zama tayi tana Ajiye ledar kayanta gefen kujerah tace"sannunku Ina wuninku?"lafiya qlau"yaya sadam kwana 2?"saida yad'an kalleta kafin yace"Alhamdulillah "idan Ankira ki Ai bakya son d'auka ko?"bafa haka bane bana kusa"hmmm! yasu hjy?lafiya qlau tana gaidaki"tun d'azun kazo kenan?"ah ah banjima ba Eyyah tace kinje gidan gaisuwa ko?"yak'are maganar yana mik'ewa tsaye sbd ganin lokacin sallah yagabato"Eyyah da suraj na lura da yadda yaketa bin muslima da wani irin kallo me kama dana SO"badai tafiya ba?"bara naje nayi sallah"to saika dawo"duk suna maganar ne shi yana kallonta ita kuma bashi take kallo ba"nima bara na bika muje"cewar suraj yana murmushi da Ido yama husnah Alamar zasuje su dawo"ita dai murmushi kawai tayi"bayan fitarsu muslima tace"sis yasu Anty?"sai yanzun kika ganni?"to Ai naga gaba d'aya hankalinki na wajen yaya suraj"harara ta ballah mata tana fad'in kin manta"gaba d'aya sukayi dariya"Eyyah tace husnah tashi kije kiyi sallah "dato ta Amsa gaba d'aya suka nufi d'akin baccin Eyyah"muslima ta Ajiye kayanta ta sanarwa Eyyah zataje ta gyara masa d'akinsa.....Ahankali ta saka key d'in ta bud'e k'ofar d'akin "sanyayyan k'amshin turarensa me dad'i d kashe jiki yafara dukan hancinta"set d'in had'ad'd'en bed irin na k'asar dubai ne Adak'in kalar milk, sai sofa da kujerah 3 seeter ,sai wani

tsadaddan carpet me uban laushi daka Aza k'afarka zata lume Aciki "daga gefe guda kuma k'ofar toilet ne"saman bed d'in devut ne kawai  shimfid'e.....ni banga Abinda d'akin nan yayiba shine zai wani ce ki gyaramun d'akina kafin nadawo"ta k'are maganar cikin kwaikwayon muryarsa tana fara k'ok'arin kakkab'e kakkabe "saida ta fara share d'akin sannan tayi mopping ta canza bed sheet"saida tayi Addu'a sannan ta shiga bath room d'in "tana shiga tayi cin karo da boxes d'insa kala biyu Arataye da Alama sauri takeyi ya barsu ba'a wankeba"ba k'aramin kunya tajiba"ta kauda  kanta ta fara washing toilet d'in Agaggauce sbd bataso yashigo tana d'akin "gashi kuma sadam yace zai dawo idan yayi sallah"bayan ta idar ta wanke hannunta ta  fito ta rufe k'ofar d'akin ta zare key d'in"Aikuwa tana shiga cikin parlourn ta sami suraj da sadam sun dawo sunata fira, yayinda Eyyah da husnah ke d'aki basu kaiga  fitowaba"zoki zauna nan kiji wata mgn "yafad'a yana nuna mata daga  gefensa"saidai kafin muslima tayi wani k'wak'wkwaran motsi  dollars ya shigo cikin parlourn da sallama cikin k'asaitacciyar muryarsa"sarai yaji kalaman sadam"hakan yasa ya had'e girar sama data k'asa fuskarsa babu Annuri "ko kallon gefen da sadam ke zaune  beyiba, cikin Isa da izzah ya zauna kan kujerah"Abokinah barka da shigowa"cewar suraj"da yauwa kawai ya Amsa yana satar kallon Muslima da har lokacin take Atsaye"yaya Muslim Ina wuni?"cewar husnah tana kauda kai"sbd bata son tana yawan ganinsa sbd jin sonsa takeyi nadawo mata Aranta "ya d'auki kusan second 5 kafin ya Amsa da lafiya qlau "yallab'ai Ina wuni ya hak'uri?"cewar sadam yana jin yamasa wani irin kwarjini"ba tare daya sami Arzik'in ya kallesaba yace Alhamdulillah da k'yar yana danne kishin dake taso masa"k'asan zuciyarsa yana mamakin beda mutuncin da muslima zata masa sannu da zuwa?....mik'ewar da sadam yayi tsaye yasaka yasaci kallonsa Adaidai lokacin dayake cewa"muslima muje ki takamun"haka nan taji kirjinta ya buga!"ta saci kallon mutumin nata"Aikuwa ya wurgo mata wata iriyar  harara ya wani sha mur yana fad'in kin gama Abinda nasakaki?"Eh na gama"jeki d'akin cikin lokar bed side wata leda na nan kikamun"lura da yadda yaketa shan k'amshi yana hura hanci yasaka ta kasa masa musu"yayinda sadam yaji zafin Abin Aransa"dama beji dad'in yadda ya Amsa gaisuwar tasaba"saidai Aganinsa sbd yanada dukiya yake ganin zai iya taka kowa"toko meye be isa yarabashi da y'ar uwar saba"yaya sadam Ina zuwa"okay ki sameni Awaje"daga haka yayima suraj sallama beko kalli gefen da dollars yakeba yafita"tana barin parlourn dollars ya mik'e tsaye yabi bayanta"sbd yana so ya nunama sadam cewa yafishi iko Akanta"suraj ya sauke numfashi yana sakin wani shed'anin murmushi,sbd yadda yaga fuskar dollars da tashin da yayi yabita kawai yabashi Amsar Abinda yajima yana zato Aransa "yaji kuma matuk'ar dad'i"ya tabbatar idan dollars ya mallaki muslima Amatsayin matar Aurensa sai Hjy jamila ta kusa k'aramin hauka"musammun tunda yasan burinta dollars ya Auri malika.......yana isowa bakin k'ofar d'akin yaga tabar key d'in Ajiki"da sauri yajawo k'ofar yasaka key ya rufe yayi tsaye"yana Anan yaji tanata jijjigar k'ofar Amma Arufe "can kuma yaji shiru"securities ya kira ya tambayesu sadam ya tafi?"sbd ya misalta kamanninsa da  irin motarsa  daya gani fake Awaje"sukace yanzun yatafi"sanar  musu yayi karsu koma barinsa shigowa cikin gidan daga yau in har yakoma zuwa"yana kashe wayar ya matsa ya bud'e d'akin"tana zaune k'asa kan carpet tanata sharb'an kuka "sbd ranta yabata shine yazo ya rufeta sbd karta fito suyi mgn da sadam"saidai ta kasa gane miye dalilinsa na Aikata hakan?"tasan dai iya iyawarsa yana kulawa da ita saidai batasan meyasa yake son b'ata mataba....jin motsin ya bud'e k'ofar yasaka ta d'ago kanta idanunta shab'e shab'e da hawaye ta hangesa tsaye fuskarsa bbu Alamar rahama Acikinta"bata dena kukan ba ta mik'e tsaye kawai ta wuto ta

gefensa bata tanka shiba ta fara k'ok'arin rab'ashi ta wuce"da sauri ya tare bakin k'ofar murya bbu Alamar wasa yace sbd bakije wajen shashashan canba shine kike kuka?"wani irin ihu ta saki had'e da gunjin kuka tasaka hannuwanta duka tana turashi daga gabanta"saidai yayi tsaye k'ik'am kamar bashine take turawaba"yadai tsareta da shanyayyun idanuwansa da suka fara canza launi sbd kishi"yanata kallonta kawai"saidai ita ba kallonsa takeyiba"ganin yadda taketa masa ihu yasaka ya fisgota gaba d'aya ta fad'o jikinsa kawai taji ya rungumeta Atsakkiyar faffad'an k'irjinsa "ni yaya ka cikani dan Allah! ta fad'a cikin muryar kuka"bari nayi ki gama motsa jikin naki saina cikaki shiyasa"tayi shiru tanata kiciniyar k'wacewa"wai meyasa bakya jin mgn halimatu?"ya fad'a da wani yanayi Amuryarsa "idan kinaso na barki ki tafi kiyi shiru"da sauri ta dena kukan sai Ajiyar zuciya datake saukewa A jajjere"yaya shine ka rufeni ko?"to meye zakije kiyi masa?"kinsan dai ban son shashanci ko?"yak'are maganar yana cikata"da sauri tayi k'ok'arin tafiya"kije ki wanke fuskarki"batace komai ba ta nufi toilet ,bayan ta wanke ta fito ta samesa zaune saman sofa yana danna waya"zonan! da gudu ta fita daga cikin d'akin "ya girgiza kansa kawai"tashi yayi yarage kayan jikinsa ya watso ruwa" be jimaba Adak'in yafita sbd yayi sallar isha'i"lokacin daya dawo daga masjeed d'in tana kwance kan 3 seeter da Alama har wanka tayi tana jin sallamarsa ta masa banza sbd ba k'aramin haushi yabata d'azun ba"shima yadawo ne sbd yaga kota dena fushin dashi sai yaga Alamar bata dena ba"sai d'aure fuska takeyi"shi kuma jin kansa ya hanashi tankata "kawai saiya wuce dining area yaje yafara dinner"waina ce ta farar shinkafa da miyar taushe"ga gashashshen naman rago da kifi gashashshe"saida yayima cikinsa k'at sannan yatashi yana juyo dariyar muslima itada Eyyah yatab'e baki kawai yayi gaba Abinsa"tare dashan Alwashin Ai gobe zataso ta bishi suje gidan gaisuwa ko?"da tunanin y'ar rigimar tasa yayi shirin kwanciya bacci yana tuna d'azun da zai shiga sashen daddy yanaji Hjy jamila nasanarwa Malika bataje gidan gaisuwar ba wani waje ta tafi ta nunama daddy taje kawai"suna ganinsa sukasha jinin jikinsu"sai yayi d'an murmushi ya gaisheta ya wuce kawai"shidama beson taje"idanma zuwanne yafiso ummi taje"yasan itama kilan gobe zataje"da wannan tunanin bacci me dad'in gaske ya d'aukesa.....washe gari be fito da wuri ba"sai wajen k'arfe 10, sbd da Asuba yajima A online suna mgn da mutanansa game da kasuwancinsa" kuma yanzun yanaso idan yafita yaje office nashi"ga bacin ran Hjy zarah data damesa da kira ta waya bayan ba wani abu me mahinmanci ne yasaka ta kiran nashi ba"yana sanye da suit red colour yayi wani irin sihirtaccen kyau"saidai fuskarsa bbu walwala "yana doso parlourn Eyyah yaji sautin muryarta tana cewa"to Eyyah ba gidan gaisuwar zamujeba nida yaya muslim shiyasa na saka hijab dayazo basai ya jiraniba saimu tafi "d'an murmushin mugunta ya saki yana cije baki ya shigo Anutse yana koma tamke fuska"yaya Ina kwana?"kallonta yayi cikin second 5 kafin ya d'auke kansa yak'i Amsawa duk Eyyah na lura dasu"ba k'aramin shak'a muslima tayiba"tana sanye da riga da siket na Atamfa super me Adon flowers da colour d'in black and purple"tana sanye da hijab tiyebo purple iya gwiwa,wacce taji guga tana d'aukar Ido"bayan ya zauna gefen kujera ya gaida Eyyah"sannan ya wuce sashen Abbie suka gaisa"koda yadawo Lipton kawai yasha yabaro dining area d'in"itadai Eyyah na zaune dama har ranta batason zuwan na muslima.....ganin zai fita yasaka tayi saurin cewa yaya Muslim na taso muje??.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa ban yafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

.....Cike da basarwa dollars ya juyo yad'an kalleta yana fad'in Ina kenan?"yo yaya gidan gaisuwar mana"ban tsara zuwanki Ayau ba"Amma fa harna shirya ko?"banza yamata kamarma be jiba yasa kai yafita yabar mata daddad'an k'amshin turarensa"kuka ta fashe dashi ta kwanta saman kujera harda shashsheka"da mamaki Eyyah ke binta da kallo tare da cewa lallai Abin naki me girmane"indai babban mutum ne kikace zakiyi ta kuka sbd takaicinsa Tofa yanzun kika fara"in ba shirmeba miye Amfanin zuwan naki yau?"tunda munje jiya kin musu gaisuwa kuma har kin yini Acan sai kuma dole kice yau kije....tana cikin maganar Abbie yafito daga cikin parlournsa yana kallon muslima yace"meya faru kuma take ihu haka?"itada babban mutum ne ! sbd yak'i zuwa da ita gidan zaman makokin....ni wlh babu ruwana dashi Abbie ka zama shaida ni ban had'a komai dashi ba"kuma gidan Hjy zan koma"ta fad'a cikin muryar kuka "Eyyah ta d'aure fuska zata yimata mgn"Abbie na murmushi ya girgiza mata kansa Alamar karta yi,kafin yace"to shikenan ba matsala"naji baki had'a komai dashiba"nifa meye kika had'a dani?"kaima ban had'a komai dakai ba ko?"ta fad'a cikin turo baki tana tashi tabar parlourn ta koma d'akin Eyyah..... dollars kuwa dama yasha Alwashin tunda tayi kuka da fushi dashi sbd wani banza saita san ta masa haka "yana driving d'in yana tuna baby face nata da d'an mitsitsin bakinta datake yawan turowa da yima mutane masifa dashi"Ahaka ya iso office yayi Abinda zaiyi kafin ya d'auki hanyar gidan ummah"sbd yau be nemi driver ko body quards nasaba musammun jiya dayaga mutane nata kallonsa gidan gaisuwar"bayan ya iso yayi parking A haraban gidan yafito"Atake mutane suka masa caaa! shi har mamaki yakeyi"sai gaidashi Akeyi da masa gaisuwa"saidai ya Amsa wasu yad'aga musu hannu "Aransa yayi murmushi kawai yana tuna yadda rayuwa ta zama"sai kanada shi kowa keyi dakai"wasuma sun haifesa Amma sbd yanada dukiya dubi yadda suke masa"Acan ya hango suraj Agefe,kusan Atare suka shiga cikin gidan "Anan babban parlourn gidan suka sami ummah itada sauran danginta zaune suna cigaba da karb'an gaisuwa"tunda suka gaisa ta fahimci ba tare da muslima yazoba "saida taga zai tashi tsaye daga duk'iyar da sukayi Agaban ta shida suraj"kafin tace"Ina kabaro muslima yau ko barata zoba ne?"yayi mamakin tambayar ta ummah Amma sai bai nunaba yace "tana gida ,yanzun haka fushi takeyi sbd nace yau barata zoba"be rufe bakiba Amatallahi itama data lura dashi kuma bataga muslima d'in ba tayi saurin cewa yaya Muslim Ina muslima?"tana gida"yabata Amsa Atak'aice yana mik'ewa tsaye suka fita shida suraj"suna fitowa suraj

yace"bakada kirki dollars "Abinda kayiwa sadam jiya ka kyauta?"wani banza kallo ya watso masa kafin yace dani dashi waye naka Acikin mu?"suraj na murmushi cikin tsokana yace shi"banza yamasa yak'i tankasa "yanzun dai kasaka a d'akko muslima tunda kaga Anata tambayarta sbd mugunta shine ka hanata zuwa ko?"hmm? nasan yanzun haka kuka takeyi tanata fushi bana zaton ko nace Aje a d'akkota zata yadda tazo"toka kirata mana"beyi mgn suka wuce wajen zamansu yana k'ok'arin kiranta"saidai harta fara ringing ta tsinke bata d'aukaba"yakoma kira still bata d'auka ba "daga bisani ramadan ya kira yasanar masa komai yakeyi ya Ajiye yaje sashen Eyyah muslima nacan yasanar mata ta fito zai kawota nan gidan gaisuwar"suna gama wayar ya kashe yana tunani"yasan idan ba ramadan d'in yaturaba da wuya ta Amince ta biyo driver yakawota..... muslima kuwa tana ganin kiran nasa ta masa banza tayi kwanciyarta saman bed d'in Eyyah"ba k'aramin haushin dollars tajiba tsakanin jiya da yau"tana kwance tana chats sbd d'eb'e kewa Eyyah ta shigo cikin d'akin ta kalleta tace"kije inji ramadan"toni Eyyah meye zan masa?"ban saniba baza kije bane?"batace komai ba kamar zatayi kuka ta d'auki hijab nata ta saka ta fito rik'e da wayarta Ahannunta...yana tsaye a parlourn yana danna waya "sallamarta da yaji yasaka ya kalleta fuska bbu yabo bbu fallasa yace"yaya ne yace kizo muje na kaiki gidan gaisuwa"ni Allah yaya Ramadan bazan jeba"d'azun....kinada hankali muslima?"koni bana iya kallon tsabar idon yaya na masa musu saike zaki yi?"zaki wuce muje ko saina mammareki?"juyowa tayi taga Eyyah zaune tana kallon su da saurarensu bata tankaba"shi kuma fita yayi"Eyyah kinga yaya Muslim ko?"kiyi hak'uri ki saka takalmi kije yana jiranki"batace komai ba zuciyarta ba dad'i taje ta d'auki plate shoes d'inta ta saka ta fita"Eyyah ta sauke Ajiyar zuciya "Ada da Abbie ya sanar mata ya fahimci babban mutum nason muslima ta d'auka kawaidai yayi hasashe ne Amma yanzun ta yadda sonta yakeyi bedai furta ba"Amma kuma ita bata sonsa"Ayadda ta fahimta "Allah ya zab'a musu mafi Alkhairi"ta fad'a Afili ".....tunda ta shiga motar har suka d'auki hanya suka iso gidan muslima bata tanka yaya ramadan ba sbd shima haushi taji yana bata"kasancewar ta saka face masks a hand bag nata"yana gama parking ta fiddosa ta saka sannan ta fita"cikin nutsuwa take tafiyar tata tamkar me tausayin k'asa"idanuwanta sun k'ara girma ,sunyi d'an ja sbd kukan datayi"tana kallon Ramadan yanufi inda dollars da suraj ke zaune ta tab'e baki ta wuce cikin gidan"dollars yabita da kallo Aransa yace"*my dubulle y'ar rigimata*......kamar yadda yayi Ajiya yauma haka yayi bayan ya fito daga masallaci ya shigo cikin gidan sbd yaga gimbiyar zuciyar tasa taci Abinci"saidai ganin bbu ita Acikin parlourn yasaka ya nufi d'akin baccin umman"Aikuwa yasami muslima tayi d'aid'aiya saman royal bed d'in umma tanata baccinta hankali kwance"ga hijab nata da hand bag nata gefe"d'an kwalin kanta shima na gefen wuyanta da Alama cikin bacci yacire"dogon gashin kanta data d'aure yazubo saman gadon bayanta"ba k'aramin kyau baccin yama taba"besan lokacin daya furta ita kuma yau da y'an bacci tazo?"Eh wlh naga tanata hamma nace tazo ta kwanta"sai yanzun dana shigo nayi sallah naga tayi baccin"cewar ummah dake zaune saman prayer mate"saima Asannan dollars ya lura da ita"sbd tunda ya shigo cikin d'akin Akanta idanununsa suka fara sauka"d'an shafa kansa yayi ya rissinar tare da cewa taci Abinci?"Eh sunci itada Amatallahi"dato ya Amsa ya fita"koda ta farka saida tayi wanka ta maida kayan dake jikinta ta gyara saman bed d'in kafin ta fito parlourn.....da yamma da ummi da siyama da suka zo zasu tafi sai muslima tace zata bisu sbd batama so tabi dollars "Akan idonsa suka fito suka shiga mota"hakan yatabbar masa da cewa ba k'aramin k'ullatarsa yarinyar tayiba Arantaba "......

bayan sallar isha'i yana zaune a parlourn Eyyah yana shan coffee muslima tayi sallama ta shigo"saidai tana ganinsa zaune tayi saurin juyawa tabar parlourn"duk yana lura da ita sai yayi kamar be ganiba"washe garin ranar yakama ranar Ake sadakar ukku"tunda sassafe data je ta gaishe dasu Eyyah bata koma zuwaba sbd bataso taga dollars "tana break fast ya shigo shashen su cikin zazzafan wankansa zai wuce ya gaida daddy"tana ganinsa ta d'aure fuska ta kauda kanta"Malika dake zaune a parlourn tana lura"tana ganin haka tafara iyayi wajen gaida dollars "ya Amsa mata Adak'ile ya wuce"Aikuwa muslima ta dinga b'abb'aka dariya domin ta lura Malika taji kunyar yarfawar daya mata "K ! da ubanwa kike wannan dariyar banzar da kikeyi?" muslima bata fasaba tace da uban wanda ya tsargu"kina nufin ubana kenan?"banza ta mata ta tashi tabar mata parlourn gaba d'aya.......

*3 days a go*

kimanin kwana ukku kenan muslima na wasan y'ar b'uya da dollars"tun yana d'aukar Abin shirmenta ne har Abin yafara damunsa"gashi sunday zai bar k'asar tunda har Abba yayi sati da rasuwa"shi ko bata masa mgn ba,tama bari yadinga ganinta "sau tari bata zuwa inda tasan zata gansa"idan kuma sun had'u zata bar wajen"ko wannan shagwab'ar tata datake masa koyiwa Eyyah duk yayi missing ji "ko jiya dayaje gidan ummah saida ta tambayesa tana Ina?"yace mata tana nan kawai"Acikin kwana 3 zuwa hud'u har yayi y'ar rama"saidai Asafiyar yau daya kama satday da y'ar walwala dollars ya tashi sbd gobe ne ranar bath day d'in muslima"yana so kuma yau ko yaya yasakata farin ciki "tun wajen 10 na safe yabar gidan sai wajen 12 pm yadawo rik'e da wani k'aton cake na musammun dake cikin ledarsa daya saka cikin wani had'ad'd'en kwali"be bari kowa ya d'aukar masaba da kansa ya d'auka yanufi sashen Eyyah dashi ya samu tana kitchen "saidai bbu Alamar muslima na'a shashen,hakan yasa ya wuce sashensu"da nufin yaga ko tana can"sai Akayi sa'a yana shigowa ita kuma tana fitowa daga cikin d'akinta"tana sanye da doguwar riga ta material d'inkin bubu"sai siririn mayafi data yane kanta dashi irin kalar zanen material "tanata k'amshin humrah da body sprays masu dad'i"yazun hannayenta sunji jan lalle datayi jiya"tana ganinsa gabanta yafad'i! ga wani irin bugawa k'irjinta nayi"ba k'aramin kyau k'ananun kayan dake jikinsa taga sun masaba"koma fad'uwa gabanta yayi,musammun dataga yana doso inda take"sai kawai ta tsaya cak! ta jingina Ajikin bango tana satar kallon kabeer da Hjy jamila da suke zaune cikin parlourn suketa kallon dollars da Abinda ke hannunsa"Ada tayi niyar juyawa ta koma Amma sbd ganin mak'iyanta Awajen saita tsaya harya iso"da sauri tace"yaya Ina wuni?"uhmmm! keda ke fushi dani"yak'are maganar yana tsura mata kyawawan idanuwansa"ta sunkuyar dakai "Sam su Hjy jamila da suka kashe kunne suji meye suke fad'a basujiba sbd daga ita harshi k'asa k'asa suke maganar"mik'a mata kwalin cake d'in yayi yana fad'in happy birthday in Advance! d'an ware Ido tayi murmushi na sub'uce mata ta Amsa ta bud'e tana fad'in wow"shidai yana tsaye yabada bayansa yana kallonta"su Hjy jamila basu ganin fuskarsa sai bayansa "tsabar murna muslima bata san lokacin data Ajiye kwalin cake d'in ba tasaki ihun murna ta rungumesa tana fad'in thank you so much my sweet yayanah!......wani irin electric chock dollars yaji Adukkan illahirin sassan jikinsa"sbd wannan karon ne na farko daya bari wata mace ta masa irin wannan rungumar"sbd rungumar me zafice ta shige jikinsa sosai ta mak'alk'alesa tana murna"yamata Alkhairi Arayuwa dayafi wannan Amma Ayau jitakeyi yafi kullum faranta mata"ta d'auka itace kawai tasan gobe ne ranar zagayowar haihuwarta Ashe shima yasani....shidai ya d'an rintse Ido yana sakin d'an tak'aitaccen murmushi na dole sbd

shine kawai yasan meye yakeji Ajikinsa"ko rannan daya rungumeta beji Abinda yajiba Ayau..... innalillahi wa inna ilaihir raju'un! duniya Ina zaki damu?"dama muna jin labari sama sama gashi mun gani Azahiri"Agabana bbu kunya ba tsoron Allah zaki kamasa ki rungume haka?"da sauri muslima tadawo nutsuwarta tsabar farin ciki yasaka bata d'auki Abinda tayiba wani Abu marar kyau"da sauri ta cikasa"shidai yana kallonta batare daya damu da kalaman Hjy jamila daya jisu kaf ba"yasan tunda hassada da k'iyayyarsu takeyi dole ta fassarasu da hakan"kan idonsa muslima ta d'auki cake d'in fuskarta da Alamar rashin jin dad'in maganganun Hjy jamila "gashi ta rasa meyasa taji kunyar ta koma kallonsa?"miye Amfanin ki damu bayan kinsan ba haka bane Aranki?"tattausan muryansa ta katse mata tunani"tad'an kallesa hawaye na ciko idonta tace"dama yaya ko kwanaki ba haka malika ta dinga fad'in irin wa'annan maganganun ba, da cewa har kwana nakeyi wajenka....shiru tayi sbd jin muryar daddy yana fad'in Ina y'ar iskar take?"nina san my friend yaron kirkine itace zata rungumesa ta b'ata mun yaro.....gaban muslima yafad'i ta d'ago kanta ta hango daddy tare da Hjy jamila suna k'ok'arin isowa inda suke tsaye"dollars na tsaye cike da b'acin rai yana tunanin wace irin zuciya ce da Hjy jamila?"ganin isowar daddyn wajen ga muslima tafara kuka yasakashi saurin kallonsa yana girgiza kansa yace"daddy kadena yadda da Abinda za'a sanar maka bayan baka binci kaba"kana nufin k'arya nayi kenan?"cewar Hjy jamila "wani mugun kallo irin na tsana dollars yajefeta dashi ya kauda kai"Adaidai lokacin daddy yace nagaji da mugun halin y'ar iskar yarinyar nan "gara na koreta tun kafin tafara kama mazan layi ta d'akko min mgn"haba daddy! inma laifin me nine keda laifi sbd nine na rungumeta sbd murnan zagayowar ranar haihuwarta"ka dena yadda da duk me kawo maka zuga sbd Ashiga tsakaninka da y'arka"ke kuma wlh kiji tsoron Allah Ina jiye miki ranar tonon Asiri"yak'are maganar yana kama hannun muslima yace"zo muje"kukan munafurci Hjy jamila ta fashe dashi yayinda daddy yakasa mgn"yanzun Alh ka yadda kenan?"tsaki yaja yace"daga yau karki koma sanar mun Abinda ban tambayeki ba daga haka ya wuce samansa ransa Ab'ace.....

suna fitowa yanufi cikin lambun gidan da ita"be cika hannuntaba saida suka iso inda gras carpet yake"sannan yaci kata ya zauna" d'an nesa dashi ta zauna tana Aza kwalin cake d'in saman cinyarta"tafara k'ok'arin share hawayenta....sai kallonta yakeyi yana jin tamkar ya janyota jikinsa ya rungumeta ya rarrasheta"Anutse yafara maganarsa me cike da iya tsara lafazi kamar haka"daga yau komai Hjy jamila zata fad'a Akanki ko Akaina ko kuma Akanmu gaba d'aya bance ki damuba balle harki zubar da hawayenki taji dad'i"ita kuma Malika data cika marar kunya Agabana yaka mata ta fad'i hakan ,dana mata tunin ko ita wacece "saidai lokaci zai bayyanar da hak'ik'anin gaskiya" ita rayuwar mutum ba'a so ta yuyu babu mak'iya! Iya Abinda nasani saida mak'iya Ake samun nassara"shikenan yaya nagode"bece komai ba hankalinsa na wajen wayarsa da sadeeq ke kiransa saidai yarasa meyasa jikinsa yak'i bashi ya d'auki wayar?"saima mik'ewa tsaye yayi sbd yanaso yaje yad'an kwanta tunda ya shawo kan y'ar rigimar tasa"yayaaa! juyowa yayi suka had'a Ido"dama Ina keys d'in shashenka dana d'akinka dake b'angaren su Eyyah??"beyi mgn ba yazaro keys d'in sashensa ya mik'a mata tare da cewa zanje can d'akin na kwanta"idan kingama da can zan baki na shashensu Eyyah d'inko"tunda yanzun kin huce kin dena gudun had'uwa dani "shiru kawai tayi tana Amsar keys d'in sbd bata san meye zatace masa ba"iya Abinda ta sani yafaranta mata ya goge haushinsa data keji Aranta ,shiyasa itama ta zab'i faranta masa Ayau"lura da ta tafi duniyar tunani sai kawai yatafi Abinsa"shida yatafi sbd ya kwanta yayi baccin Amma yakasa baccin"daya rufe Ido

yadda muslima ta rungumesa yake gani"ga b'acin rai da damuwar sharrin da Hjy jamila taso ta musu"ya b'oye mata damuwarsa game da Abin sbd karta damu Amma Abin yab'ata masa rai "shin yanzun yaya zaiyi ya tunkari muslima da zancen irin soyayyar dayake mata?"shi damuwarsa kar tak'i Amincewa ,idan zata Amince bazai damuba zai iya sanar mata"yanaso ya Aureta yabata gata da kulawa had'e da farin ciki"kai yama d'auketa subar k'asar gaba d'aya sai Ammaso Aganta"gaba d'aya sai yaji beson tafiya goben ya barta"yajima yanata juye juye da tunane tunane har k'arfe 1 na rana tayi"hakan yasa yatashi ya shiga wanka ,bayan yafito ya shirya cikin milk d'in jallabiya yafito da nufin yatafi masallaci"A babban parlourn su Eyyah suka had'u"ita zata shigo shi zai fita"had'a Ido sukayi ta sunkuyyar dakai"kin gama ne?"uhmm"to sannunki"canza topic d'in tayi da cewa wancen d'akin Abud'e yake?"ta k'are maganar tana bashi keys d'in "Abud'e yake Amma ki bari ki huta saiki gyara"ya k'are maganar yana Amsar keys d'in "nide bangajiba yaya Muslim zan gyara "kuma dan Allah kasaka Awanke motar can ko?"tayi maganar cikin shagwab'a" Ina zakije?"Anguwa"batada suna?nidai ba driver zaya kainiba.....ganin idan yabiyema sauraron wannan shagwab'ar tata Alwallah d'insa zata iya karyewa sai kawai ya fita Abinsa bece komai ba.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba ko kika siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

........bayan fitar dollars daga cikin parlourn ta wuce d'aki ta sami Eyyah na sallah"hakan yasa ta zauna tana tina Abinda yafaru d'azun,bayan ta idar ta kalleta tace"kukan meye kikayi?"kanta Ak'asa ta shiga sanarwa Eyyah Abinda yafaru"bayan ta gama ta saka mata wani sabon kukan tana fad'in na rasa meyasa mahaifina baya k'aunata sai Aibatani dayake yawanyi koda yaushe Eyyah??"ki dena kuka kinjiko?"in sha Allah kukanki yazo k'arshe "cewar Eyyah cikin jin zafi da rad'ad'in Abinda yafaru"shiru kawai muslima tayi tana mamakin kalaman Eyyah "saidai ranta yabata wani mataki zasu d'auka....Ina babban mutum d'in?"yatafi masallaci inaga"d'akinsa ma zanje na gyara masa"dato kawai Eyyah ta Amsa ita kuma ta tashi ta fita.... dollars koda ya gama sallar kiran gaggawa yasamesa a office"hakan yasa yana dawowa gidan ya wuce sashensa sbd yacanza kaya"tunda yabud'e k'ofar parlourn ya shigo k'amshi ne ke dukan hancinsa irin na turarukan wuta dana Air frishners ga kuma irin nasa k'amshin dake zaune

daram A sashen nasa"komai yayi k'al fas dashi"my dubulle nah tasha Aiki dai sosai"yafad'a da d'an murmushi saman fuskarsa,yana kallon wajen tv stand daya san wajen yayi y'ar k'ura Amma gashi yanzun k'al yana d'aukar Ido"koda yashiga bed room d'inma shima komai gyare k'al"ga kayan gugarsa da aka kawo ta jera masa"harda turaren kaya tasaka masa cikin kayan nasa"saida yafara duba kayan dazai saka ya lura da wasu duwatsu kamar turaren wuta ,saiya d'auka ya shinshina yaji k'amshi "murmushi me fad'i yasaki"tunda yarinyar tafara wayo har taso fara rainashi bata tab'a faranta masa irin yau ba"inama ta d'ore haka"yafad'a Afili yana rufe ward rope d'in "Anutse ya shirya cikin t shirt red da farin wondo  jeans ya Aza pasin cape"kafin ya d'aura Agogon fata fara yasaka takalmi  chukka boot farare"uhmm ! idan Ana sallah ba'a mgn"sosai yafito a young bolonia d'insa "wayoyinsa daketa ruri sun damesa be d'aukaba ya d'auki key d'in wata tsadaddar sabuwar motar daya siya kwana 2 da suka wuce"waccan dayake matuk'ar so yabarma muslima baidai kaiga fad'i ba"sbd yasan duk wanda yaji yabata kyautar motar nera million 80 dole yayi mamaki Amasa wani zato"yanzun yanaso suje ummarah ta maulid dashi da ita da suraj da husnah"yana wannan tunanin ya fita daga cikin d'akin yanata zabga wani irin fitinannan k'amshi....cike da nutsuwa yake tafiyarsa irinta kas'aitattun zaratan mazan da suka Amsa sunansu maza "tun kafin ya Ida isowa mutum biyu cikin body quards nasa suka iso gefensa"beyi musu mgn ba kawai yamik'a musu keys d'in new car d'insa "ba b'ata lokaci Aka kaima babban driver "ya shiga yabata wuta"saida dollars ya gama Amsa wata waya kafin ya shiga back sit da Aka jima da bud'e masa ya zauna.....

zaune suke su ukku kan wasu kujeru Acikin wani club daga gefe"daga gabansu kuma matane mararsa tarbiya keta shan drinks da shisha"wasuma harda kayan maye sukesha"sadeeq ya kalli Adam dake kusa dashi yace"ba'a had'a game dani Atashi 0-1"saidai Atashi 1-1 ko kuma Atashi 0-0" najima Ina jin zafin dollars Araina "na had'a masa gadar zare sau kusan ukku Amma yana tsallakewa"na rasa wane irin jini ne dashi?"kai kwanaki har so nayi da kaina muje wani waje na dab'a masa wuk'a Amma wlh saina kasa sbd ba k'aramin jarumi bane"Adam yatab'e baki had'e da cewa an fad'a maka zai zauna bazai shirya kansa ba ,ya kuma horar da kansa da motsa jiki ba "bayan yanada dukiyar dako shi kansa besan Adadin taba"idan harda zakaji ta tawa daka hak'ura da wannan takun sak'ar da kake so kafara dashi sbd kaine zaka fad'i k'asa warwas "musammun idan yagane kai mak'iyinsane"wlh zai iya b'atar dakai da kowa naka ba'a komai tunda yanada kud'i,kuma yafik....kaga Adam karka mun maganar banza"ko kaima kana daga cikin masu zuwa maulane wajensa?"rai b'ace Adam yace"nafi k'arfin hakan kaima kasani"kaidai ne yaka mata ka Ajiye k'arya da burgan da kake mana kaje kayi maular wajensa"dan nasan ka cire girman kai ka nuna kana son yataimaka maka dan yabaka wata million 10 k'aramin Aikinsa ne"tsaki sadeeq yaja had'e da tashi yabar musu wajen "sbd yasan muddin yaci gaba da zama Awajen zasu iya samun matsala da Adam "batun dollars kuma yasha Alwashin koshi da kansa zai iya kashesa koda an kasheshi beda matsala burunsa Ai yacika....*Allah yarabamu da ciwon hassada*👏🥹

sai yamma likis dollars yanufo cikin gidan "ga gajiya da yunwa daya kwaso"rabonsa da Abinci tun break fast d'in safe"directly b'angaren su Eyyah yayima tsinke"tana zaune tana Azkhar "ga sunnah TV tana kallo"kanta ta d'ago ta Amsa sallamarsa tare da cewa "babban mutum! Eyyah sannu da gida"yauwa kai keda sannu"beyi mgn ba ya Ajiye ledar daya shigo da ita gefen hular muslima dake Ajiye saman 2 seeter "duk Eyyah na lura Amma bata tankaba"bayan ya Ajiye ya wuce dining area yana tunanin k'ilan ko y'ar darun nasa nacan

sashensu"tunda bega Alamar tana Anan ba"Abinciccikan yaduba"tuwon semovita da miyar kuka da taji naman shanu da man shanu"saiga sinasir da miyan kan rago"ga kula shak'e da had'in zobo da yaji cocumber da k'ank'ara"d'an shiru yayi sbd yasan Eyyah bata tab'a had'a masa irin wannan lemon na gargajiya ba,haka kuma bata tab'a yimasa sinasir ba"kamar ya tambayeta kodai bashi Aka Ajiye mawa ba sai kuma ya share"yayi serving d'in kansa yafara cin Abincn Anutse.....nama! A cikin Abinci ko farfesu be cika burge saba Amma yau yaji yamasa dad'i sosai "ko tuwon be ciba yayima cikinsa k'at"bayan ya gama ya goge bakinsa yabaro dining area d'in yana murmushi yace my sweet Eyyah irin wannan zazzafan girki haka me dad'i?"gaskiya bazan miki kishiyaba daga ke babu k'ari"tayi murmushi had'e da cewa babban mutum kenan"to bani bace nayi maka wannan girkin ba"takwarace tayi d'azun bayan sallar Azahar"ni tuwo nayima mijina"ita zaka gode mawa baniba"da zakazo kanamun dad'in baki "indai ka tsofe Agidan bashi kenan ba sai Aba daka sadaka"d'aure fuska yayi yak'i mgn yama bar parlourn ya wuce d'akinsa sbd ya watsa ruwa"saidai gaba d'aya ransa yatafi duniyar tunanin muslima"Ayau yadda yakejin zuciyarsa tamkar ya furta mata yana sonta"saidai k'asan zuciyarsa keta ce masa kul"yayi mamakin yadda ta iya girki haka"sai kuma yatuna tace tayi catering skul "saidai kawai ransa yabashi sbd yadda yafaranta mata Ayau shiyasa itama ta faranta masa"yana wannan tunanin yafara rage kayan jikinsa "saidai daya duba bega towels ba"sai yayi zaton koda ta gyara d'akin ta mayar dasu toilet"hakan yasa yanufi can"ya samesu guda ukku wanke Ashanye"tsura musu Ido kawai yayi yana kallo yana jin tsananin k'aunar yarinyar na karuwa Aransa "*Allah yasa ke rabona ce halimatu* yafad'a yana fara wankansa Anutse yana d'an murmushi da tunani"gaba d'aya sai yaji itama yake son gani"saidai daya tuna gobe zai tafi yabarta duk sai yaji wani iri..... yad'an jima tun daga wajen wankan har zuwa fitowa ya shiryawa"kamar d'azun ma haka jallabiya yasaka ,sai yayi kamar bature ko balarabe"lura da yayi wayarsa na haske yasaka ya matsa yaduba yaga sak'one daga Hjy zarah kamar haka *yallab'ai barka da wannan lokaci! kayi hak'uri da yawan kiranka danakeyi dan Allah ka dinga kulani"bazan b'oye makaba zuciyata ta kamu da matsananciyar soyay*........wani uban dogon tsaki yasaki batare daya Ida karantawaba yayi delete ya goge contact nata bayan yayi blocking. dama ya fahimci sonsa takeyi yabari dai ta furta sai ya d'auki matakin daya dace"yasha Alwashin ko mutanan dake buk'atar temako daya wakilta ta dinga kawosu, bayan ta tabbatar da gaskiyar su  to daga yau yacireta daga wannan matsayin"dama jiyama da dare wata y'ar tasha ta turo masa pics nata bbu kaya tadai b'oye fuskarta"wai idan ta masa su dinga hud'd'a koda bazai biya taba"sosai yaji gaba d'aya tsanar wasu matan"fuskarsa babu walwala yabar d'akin da nufin yaje yaga muslima yatafi masallaci sbd befi mintina 30 magrib tayi ba.....muslima kuwa dollars befi mintina 15 da barin parlourn ba ta shigo da sabon wankanta sbd d'azun ta gaji bacci taje tayi sosai"sai bayan ta tashi ta shirya ta nufo nan"da ledar daya Ajiye Amatsayin tsarabarta ta had'a Ido"sai kawai ta zauna gefen ledar"tana sanye da riga da siket na Atamfa sun kamata sosai"Eyyah ledar waye kuma miye Aciki?"ita ledar zaki tambaya bani ba"turo baki tayi tafara bud'ewa "chacoolates ne da biscuits masu Madara"harda irin wad'anda ta zab'o kwanaki daya mata chopping duk ta gani "nide Eyyah zan  d'auki biscuit guda d'aya"nima ba nawa bane babban mutum naga ya Ajiyesu"sbd haka ba ruwana"nide zan d'auka "kin manta kince ke ba ruwanki dashi kuma baki had'a komai dashiba? haba Eyyah ! dama ba b'atamun rai yayiba,kuma yanzun Aina huce"harfa girki na masa me dad'i kan idonki....tsit tayi sbd ganin shigowarsa datayi cikin parlourn kamar daga sama"sarai yaji duka kalamanta"kamar yayi dariya

saiya gimtse Abarsa"ya fahimci kwanaki kenan tace ba ruwanta dashi yanzun kuma ta huce"yana k'ok'arin zama Eyyah tace"toga babban mutum d'in nan saiki tambayesa yabaki?"meke nan Eyyah?"kinfini sani"k'in mgn tayi ta turo baki tak'i kallon gefen dayake zaune ,sbd bataso yasan tayi zancen Abinda ke cikin ledar yama rainata"yaya Ina wuni?"ta fad'a batare data kallesaba "shi kuwa gaba d'aya ita yake kallo"jin yayi shiru be Amsaba yasaka ta d'ago kanta da nufin ta saci kallonsa Aikuwa suka had'a Ido "da sauri ta kauda kanta"Adaidai lokacin Eyyah ta tashi tabar musu parlourn.....yaya Muslim kanaji na gaisheka shine kak'i Amsawa ko? kuma abu kad'an kace ban iya gaisuwa ba"ya d'auki kusan second 5 kafin yace"idan kinaso na Amsa saiki kalleni ki gaidani ba kina kallon wani wajen ba "meyasa bakya jin mgn ne?"mena yi dan Allah?"bance karki koma yin kuka bane?"saida taji wani iri batace komai ba tana tunanin meyasa ya gane?"ki d'auki tsarabarki dakike tambaya"nifa yaya Muslim ban wani tambayaba"okay bani Abuna tunda bakyaso"babu kyau ai maida kyauta "d'an murmushi kawai yayi bece komai ba"ita kuma tana dai zaune kanta Ak'asa"kin fasa fitar ne?"saifa gobe zamuje sunan yayar jidda data haihu"kikace kinyi fad'a da ita?"to Ai mun shirya"bazaki dena fad'a da mutaneba?"nifa yaya ba wani abu ya had'amu ba sbd yayanta ne"Atake ya had'e rai yana tsareta da mayatattun idanuwansa yace"meye had'inki dashi?"Akunyace tace toba yace yana sonaba"ni kuma bana sonsa"sai waye kike so?"yafad'a cikin wata iriyar muryar da bata san shanshi da itaba"har saida ta d'ago kanta tad'an kallesa ya d'aure fuska "nifa yaya ba kowa"bece komai ba yaci gaba da danna waya"can kuma yace"kin tuna wata yarinya da kuka had'u da ita a office nawa?"wannan sarkin iyayin da tura kai gun maza bbu Aji"da mamaki yadubeta yarasa meyasa bata son zarah?"saidai be tankaba"to yaya naganeta meya faru?"na fasa fad'a miki"ni Allah ka fad'amun"ta fad'a cikin shagwab'a"mik'ewa tsaye yayi yanufi k'ofa tare da cewa gobe in sha  zan koma jirgin k'arfe  12 zan hau"bejira cewar taba yayi ficewarsa yana dariyar kuruciyarta Aransa"yana fita ta d'auki ledar itama ta fita tana jin k'asan ranta kamar kar yatafi"musammun data fahimci daga wajensa sai wajen su Eyyah kawai takejin dad'i Agidan"koda ta shigo sashensu bata kula kowaba ta nufi d'akinta tayi shirin yin sallah sbd ta sami tsarki...sai bayan sallar isha'i dollars yanufo cikin gidan saidai koda yazo sashen Eyyah be samu y'ar darun tasaba"ga tsaraba yamata"kad'an kad'an dayaji motsi zai kalli k'ofa "duk Eyyah na lura dashi"saita tashi ta wuce kitchen ta d'akko Ayaba tasaka A leda ta fito rik'e da ita Ahannunta ta samesa zaune"babban mutum tunda ba wani abun kakeba jeka mik'a ma takwara ta wannan"dato ya Amsa yana kallonta ya wani marketurya yace toni Eyyah Ina nawa?"kaje kadawo tukum"yayi murmushi kawai yafita.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 300 normal grp vip grp 1000
 Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba koki siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj

#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

........koda yafito daga shashen su Eyyah tafiyar yakeyi cikin nutsuwa yana rik'e da ledar da Eyyah tace Abata,da kuma ledar daya mata tsaraba "k'asan zuciyarsa na tunanin tayi bacci ko bata yiba?"yana gab da iza sashen yaji zuciyarsa na wani irin harbawa"Atake ya tuna Abinda yafaru d'azun"d'an d'age kafad'a yayi irin ko Ajikinsa d'in nan da duk yadda za'a fassarasu"kafin ya wuce cikin parlourn gidan....yana shigowa yayi clashing da Malika da muslima suna dambe"Naseem na k'ok'arin rabasu"wata rikitacciyar tsawa yadako musu"ba shiri Malika ta cikata"ita kuma muslima ta d'auketa da wani gigitaccen mari tana huci tace na rama marina"kukan kura malika ta komayi zata fincikota Aguje muslima ta nufi bayan dollars dake tsaye ya had'e rai yana kallonsu"saidai kawai yaji muslima tayi hugging nasa ta baya tana zuro kanta daga gefen damtsan hannunsa tana yiwa Malika gwalo"hakan yabama k'irjinta damar gugar faffad'an bayansa....ba shiri ya rintse Ido sbd wani irin yanayi me girgiza bawa daya tsintsi kansa Aciki "yah rabbih! ya furta Aransa yana saurin bud'e Idonsa ya hango Malika ta haye upstairs tana kuka da Alama k'ara zata kaima daddy"yayinda Naseem ke tsaye yana satar kallon su.....yaya kagani zataje ta sanarwa daddy ko?"ta k'are maganar cikin kukan shagwab'a"da sauri dollars yasaka hannunsa guda yajanye hannayenta data masa zobe dasu"ya tabbar suka k'ara mintina 3 Ahaka komai zai iya faruwa"gashi beso daddy yazo yasamesu Ahaka "da k'yar ya furta bakyajin mgn ko?"bance kidena biye mata ba?"itace fa yaya ta fara janta gaskiya"cewar Naseem"okay idan daddy yazo shiya kamata kama bayani"cewar dollars"saidai be rufe bakiba ya hango daddy na sakko k'asan Malika na biye dashi tana kuka"saida gaban dollars yabuga sbd yadda yaga fuskar daddy....Muslim fita ka bani waje"na lura duk wani iskancin da y'ar banzar yarinyar nan keyi kaine ke d'aure mata gindi"kuma da saka hannunka takeyin komai....dan Allah daddy kajira kaji meya faru"wlh laifin Anty Malika ne....yimun shiru mutumin banza na tambayeka ne?"shiru Naseem yayi ya sunkuyar dakai k'asa"tsabar irin yadda dollars ya hassala kasa mgn yayi"yana dai tsaye k'ik'am be tafinba "yayinda muslima itama take tsaye gefensa gabanta nata fad'uwa"K! zonan"idan ba jikinki ya gaya miki ba bazaki dinga girmama na gaba dake ba"Atake muslima ta tsure ta fara sakin k'aramin kuka ta b'uya bayan dollars"girgiza kansa dollars yayi Ahankali yace"kayi hak'uri daddy karka daketa"ba goyon bayanta nakeyiba Amma ka tsaya Amaka bayanin meya faru?"wai Muslim Ina wasa dakai ne?"bazaka tafiba?"ke kuma bazaki zoba ne?"juyowa yayi ya kalleta cike da tausayi sbd yasan tun tana yarinya tanada tsoron duka"dan uwarki bazaki zoba saina zone?"cewar daddy cikin daka tsawa"tana k'ok'arin tafiya Abbie yaturo k'ofar fuskarsa A murtuke ko sallama beyiba yana kallon daddy yace"sulaiman biyoni zanyi mgn dakai"ke kuma halimatu wuce kije"yana fad'in hakan ya juya ya fita"wata b'oyayyar Ajiyar zuciya dollars ya sauke"jikinsa ya bashi Naseem ne yaje ya sanarwa Abbie sbd ya lura tunda daddy ya disgashi ya fita daga cikin parlourn " yayahhh! yaji siririyar muryarta"juyowa yayi suka had'a Ido "to miye na kuka ?"ya k'are maganar yana kallon cikin parlourn ya lura bbu daddy da malika"daga shi sai muslima ne suka rage "ita dai sunkuyar da kanta k'asa tayi"zoki k'arba ki tafi d'aki "batayi mgn

ba ta matso ta Amshi ledojin da hannu biyu tare da cewa Nagode "beyi mgn ba yana dai kallonta harta nufi k'ofar d'akinta ta bud'e ta shiga"ya sauke numfashi yana tunanin Anya zai jure cigaba da ganin yarinyar cikin irin wannan matsalar??"motsin mutum da yaji yasaka yadawo tunaninsa"kabeer ne ya shigo babu ko sallama sai huci yakeyi"da Alama yana cikin b'acin rai"kallo be ishi dollars ba yajuya ya fita"sbd tun dukan daya masa yadena gaidashi"shi kuma ko Ajikinsa da baya gaidashi"yana fitowa yasami suraj da Abbie da daddy duk suna Atsaye "kafin ya iso wajen su yaji Abbie na fad'in gaba d'aya yaran Jamila idan Aka cire naseem basuda mutunci da tarbiya"surajo ba yayansa bane sbd mace zai shak'esa"har Ina masa mgn yana maidamun shi d'an iska"wlh in bacin marinsa da kayi da Adaren yau ka gama zama da uwarshi"kallonsu kawai dollars keyi yana jin wani irin yanayi na zafin zuciya da fushi na taso masa"idan ya fahimta wato kabeer rashin kunya yaso yayiwa Abbie sai daddy ya maresa"yana wannan tunanin Abbie yace"Allah yakaimu ranar juma'a hukuncin dana yankewa kowa zai fito tunda bakuda mutunci"yana fad'in hakan yayi gaba"suraj na lura da dollars yabiyo bayansa yana fad'in Abokinah kana ciki kenan?"juyowa yayi suka had'a Ido ya tsaya yana kallonsa yace"meya had'aka da wannan yaron harya shak'eka?"yak'are maganar yana huci"wlh Akan husnah nefa! kai kuma shine ka tsaya yaro k'arami yamaka haka bazaka bazar dashi ko fidda masa jini ba? d'an murmushi suraj yayi yace"ban kaika zafin zuciya ba dollars"sannan na barsa ne sbd Abbie da daddy"kasan husnah yakeso niban ma saniba"naga dai kashi biyu muna had'uwa dashi gidansu"shine yau yasanar mata yana sonta"shine ita kuma tace ni takeso"shikenan laifin fa"kawai zan wuce sashen su Ummy nasha coffee muka had'u dashi tamkar wani sa'anshi yasha gabana wai na fita harkan husnah koya b'atar dani"shine naturashi ina gaya masa mgn Abbie ya hango mu yakiramu"shinefa yaxo yayima Abbie rashin kunya sai daddy da suke tsaye Atare ya maresa....wani irin zazzafan huci dollars ya sauke rai b'ace yace"uhmmm! dole na d'auki mataki nima bayan matakin da Abbie d'in zai d'auka"yana fad'in hakan yayi gaba Abinsa.....jiki Asanyaye muslima ta shigo cikin d'akin ta zauna kan carpet ta sauke Ajiyar zuciya tana tunanin yanzun idan da dollars be zoba Abinda zai faru bamai kyau bane"ta kuma tabbatar da Naseem ne yaje yasanarwa Abbie"tabbas naseem da yaya muslim ba k'aramin garkuwa bane gareta cikin gidan "gaba d'aya sai taji fargaban tafiyar tasa gobe da rashin jin dad'i... kiran sadam ne yakatse mata tunaninta kasancewar batada nutsawa saita yamutsa fuska tak'i d'aukar wayar"saima ledojin da dollars yabata ta fara dubawa"Ayaba da kilishi ne sabo yanata tashin k'amshi"tayi shiru tana tunani"Allah sarki yaya Muslim Allah yak'ara bud'i"ta furta cikin jin dad'i tana fara cin Ayabar "saidai shi kilishin ta Ajiyesa zuwa safe zataci"Ayabar ma tacine sbd tana bala'in son kayan marmari.....bayan ta gama shirin kwanciya bacci ta kwanta"saidai damuwa da b'acin rai sun hanata baccin"duk idan ta tuna yadda mahaifinta ke Aibatata sai taji wasu zafafan hawaye na zubo mata "daga k'arshe tashi tayi tayo Alwallah tazo tafara jera nafilfili,tana kuka tana Addu'ar samun mafita ga rayuwarta"da kuma samun jituwa tsakaninta da mahaifinta"sannan tayima mahaifiyarta Addu'ar samun rahama Akabarinta"kafin tayi karatun Alkur'ani me girma "sosai taji zuciyarta tayi wasai sai gashi tafara jin bacci"hakan yasa ta rufe Alkur'anin taje ta kwanta....washe gari misalin karfe 9:47 am"dollars ne zaune Akafaren parlournsa dayaji kayan more rayuwa"tamkar ba'a cikin k'asar Nigeria yakeba"yana sanye da k'ananun kayan da sukayi matuk'ar haskashi"yayi wani irin kyau na musammun "dogayen k'afafuwansa na sark'e "saidai k'wayar idonsa na b'oye cikin eye glass black"sbd gaba d'aya yau baya jin dad'in jikinsa haka yatashi, ko baccin kirki beyi ba Adaren jiya

sbd b'acin ran Abinda yafaru da kuma rungumar da muslima ta masa"wacce gaba d'aya daya tuna Abin shine kawai yasan meye yakeji Ajikinsa"tun Asuba bayan yadawo daga masallaci yaje ya gaidasu Eyyah be koma sashen nasuba"Ayanzun haka yanada niyar yaje ya musu sallama daga nan yaje ya gaida umma suyi sallama saiya tafi Airport "yanata danne danne a laptop dake gabansa a Ajiye saman center table....Ahaka yaji Anturo k'ofar"sautin siririyar muryarta yayi daidai da bugawar zuciyarsa"saida yad'an lumshe idanunsa ya d'ago kansa yad'an kalleta cikin second 5 yana Amsa sallamar can k'asan mak'oshi"tana sanye da riga da siket da suka kamata da mini hijab"Acikin y'an sakanni ya fahimci tayi kuka Adaren jiya kuma da damuwa ta kwana"musammun daya lura da batada walwala"sannan idanunta sun d'an kod'e daga saman eye lashes nata sun kumbura.... Adaidai gefen laptop d'in gabansa ta Ajiye tray d'in hannunta da Eyyah ta shiryo masa Abin break fast"taji shiru be zoba ,kuma tasan yau zai tafi shiyasa ta turo Aka masa yayi karin Anan"tana daga duk'en tace"gashi inji Eyyah ,Ina kwana?.......jin yayi shiru yasaka ta d'an d'ago kanta....meyasa bakya jin mgn ne?"yafad'a in a low voice! saida ta yamutsa fuska had'e da cinno masa d'an mitsitsin bakinta Agaba kafin tace"mena yi kuma yaya muslim?" bance karki koma yin kuka ba?"sunkuyar dakai k'asa tayi idanunta na koma cikowa da wasu sabbin k'wallah d'in tace"idan katafi yaushe zaka dawo?"da d'an mamaki ya kalleta beyi mgn ba"hakan yasa ta mik'e tsaye sbd taji haushi zata tafi"Ina zakije?"kukan datake rik'ewa ta sakar masa"wai meye haka? kinsan dai bana son kuka ko?"zoki zauna ki fad'amun menene?"bakai bane zaka tafi ko?"d'an murmushi ya sub'uce masa"dukda bata ganiba tanama share hawayenta ta koma zama d'an nesa dashi"*halimatuuuuu!*. halinki sai ke "kwanaki fa har murna kikeyi mugu zai tafi sbd ki wala yanzun kuma shine kike rigimar zan tafi?"to yaya bakasan bana jin dad'in zaman gidan ba?nidai wajen Eyyah zan koma gaba d'aya"ban Amince ba"ki cigaba da zuwa kamar yadda kika saba Amma babu zancen zama ki kwana koyin wani Abu "ni kuma ranar friday zan dawo shikenan?"saita nok'e kafad'arta "zoki had'amun ko tea ne nasha kafin na wuce"saiki fad'amun meye kikeso ko kike buk'ata?"

batayi mgn ba ta taso Ahankali zuwa gabansa"shi kuma yana binta da kallon k'asan Ido ta cikin glass d'insa"wanda inda wani ke kallonsu kai tsaye ba'a ce kallonta yakeba"bayan tagama had'a masa tea d'in"ta zuba masa naman rago gashashshe dayaji kayan yaji yanata k'amshi ga ruwa ruwa Ajikinsa sa"Agefe ta  zuba masa yam balls dukta turo masa gabansa"sai kuma ta mik'e tsaye....saurin meye kikeyi ne wai?"yafad'a yana d'aukar cup d'in shayin"batayi mgn ba tad'an zauna ta sunkuyyar dakai tana wasa da zoban Azurfan dake Ayatsanta na hannu"Ahankali tace"yaya muslim dan Allah ka canzamun waya ko? ni bana son waccan yanzun....saida yad'an jima kafin yace"shikenan idan mun fita yanzun sai muje ki zab'a"da murna saman fuskarta ta fara masa godiya"beyi dai mgn ba yana break fast d'insa"yaya zanje kafin ka fito"bazaki mun rakkiya Air port ba?"da harma da gidan ummah zamuje"da murmushi saman fuskarta cikin yarinta tace"zanje pls"shareta yayi yaci gaba da break fast d'insa"bayan ya idar ya mik'e tsaye ya wuce ciki be jimaba yadawo janye da troley d'in kayansa"yayinda keys d'in sashen ke'a hannunsa"muslima na tsaye dai kanta ak'asa saidai taji yace"k'arbi nan"ta d'ago kanta ta Amshi keys d'in sashen "shi dai yanata kallonta yanufi k'ofa ta biyosa Abaya tana gulmar ya rufe Ido da eye glass"mutum biyu ta samu suna jiran fitowar tasa"Aranta tace baya jira saidai ajirashi"har ita kanta cikin ladabi suka gaida ita suna Amsar troley d'in suka nufi parking lot da nufin su jira fitowarsa"Ajere da farko suke tafiyar"saidai daga bisani shi dayake yafita dogon tak'i saiya wuceta"ita kuwa cikin sanyin jiki take tafiyar kamar me tausayin k'asa

"hakan yasa ya rigata Isa shashen su Eyyah"koda ta shigo tsintar sautin lallausan muryansa taji yana fad'in gaskiya Abbie ka koma ja masa kunne"muddin hakan yakoma maimaita kansa Abinda zai faru bame kyau bane"karka damu babban mutum "Allah yabaka sa'a da nassara ya tsareka"yana d'an murmushin gefen baki ya Amsa da Ameen "yana satar kallon mutuniyar tasa data zauna gefen Eyyah"wacce Ayanzun dataji Abinda yakoma faruwa Adaren jiya taji bazata iya bari Hjy jamila taci gaba da rayuwa ita kad'ai da d'anta ba....my sweet Eyyah zan wuce! to babban mutum Allah yatsare yayi maka Albarka "ya Amsa da Ameen ya matso yabduk'a ya rungumeta"tayi murmushi kawai "ganin muslima batada niyar tasowa ta biyosa yasaka harya kai bakin k'ofa ya juyo ya kalleta murya Akausashe yace"kina kiran nace ki taso ne?"ta turo baki tana mik'ewa tsaye tace"Eyyah zan bishi na Amshi sak'o "daga haka ta fita"suka bisu da kallo suna murmushi Atare.....tunda suka shigo motar babu wanda yatanka d'an uwansa"shi yanata Amsa kiran mutane jefi jefi"ita kuma tana gulmar haka masu kud'i suke babu hutu game da waya"any time Amsa ta sukeyi"saidai ta fahimci wannan jin kan nasa harsuma mazan y'an uwansa yimawa yakeyi"ita kanta wayar cikin nutsuwa da Aji yakeyinta ba hayaniya....fitar driver daya gama parking yadawo da ita tunaninta"da sauri ta dubesa yana k'ok'arin fita "yaya Muslim Amma Anan zaka barni ko?"banza ya mata ya had'e rai yafito daga cikin motar "sai bata koma gigin tankashiba tabi bayansa suka nufi cikin gidan....ummah ce kawai da wasu k'ananun yara 3 Acikin parlourn suketa wasa"tana sanye da hijab Ajikinta sai casbaza dake A hannunta tana lazimi"da fara'a saman fuskarta ta Amsa sallamar tasu had'e da cewa Ahhhhhh muslima kece yau Agidan?"Eh ummah Ina kwana?"ta fad'a tana kok'arin duk'awa "yayinda uban gayyar ya zauna kan kujerah"lafiya qlau yasu Eyyah ?" Alhamdulillah"saita kalli dollars murya Amarairaice tace"dan Allah yaya zanje d'akin su Amatallahi"banza yamata yak'i tankata"ummah tace"jeki ku gaisa ko jiya haka tayita yawan tambayarki"da sauri ta tashi tabar parlourn"sai sannan dollars ya gaisheta"ta Amsa tana murmushi tace"Amma Anan zaka bar mana muslima d'in ko?"ah ah ummah islamiya zataje"yak'are maganar Adaidai lokacin da yaransa keta shigowa da kayan Abinci da provisions sunata jibgewa"baka gajiya da hidima had'e da d'awainiya muslim?"Allah ya yimaka Albarka yabaka mace ta gari da zuria d'ayyiba"Allah yakareka daga sharrin mak'iya yajik'an mahaifinka da Alh"cikin jin dad'in Addu'arta ya Amsa da Ameen "yana Ajiye mata rafar y'an 1k guda ukku gabanta"muslim kabar kud'in nan yanzun haka dubu d'ari biyar d'in daka bani ranar sadakar ukku suna nan banyi komai dasuba sbd ba Abinda na nema na rasa"No ummah ki barsu ko taimako ko sadaka kinyi"daga haka yayi shiru sbd ganin shigowar mamy cikin parlourn "Aladabce ya gaida ita ,ta Amsa had'e da masa godiyar d'awainiya"bayan barinta cikin parlourn ya mik'e yana duba wristwatch d'insa yace"ummah bara mu tafi"ita kuma tana can tak'i fitowa"be rufe bakiba muslima da Amatallahi suka shigo cikin parlourn "bayan Amatallahi ta gaidasa sukayi sallama da muslima"ummah na kallonta tace"yayanki yace tafiya zaiyi dake bazai barki Anan ba"ranar friday zanzo Ai ummah"fad'a kanta a sunkuye "to shikenan Allah yakaimu"daga haka sukayi sallama "har cikin ransa Muslim yaji dad'in yadda ummah yanzun take sakema muslima fuska"saidai suna fitowa ta saki kukan shagwab'a ya kalleta be tankataba "saidai yasan data san meye yakeji bazata dinga yimasa shagwab'a irin haka ba bayan be kaiga mallkartaba Amatsayin matarsa....dama yaya kasan bazaka barni Ananba kazo dani?"ko yanzun bata b'aci ba saiki koma"yafad'a fuska Ad'aure yana k'ok'arin shiga mota da Aka bud'e masa"tanata cin magani itama ta shigo ta zauna nesa dashi"be komabi ta kantaba ya jingina bayansa Ajikin kujerar ya lumshe Ido"saida suka iso wajen siyar da wayoyin sannan yafita shi

kad'ai bece ta fitoba sbd ta bashi haushi "Ada yana murna sbd yana zaton tafara damuwa dashi Ashe ba haka bane shirmenta ne....be jimaba yadawo rik'e da ledar da kwalin wayar ke ciki ya Aza mata saman cinyarta batare daya yi mgn ba "saita turo baki kamar zatayi kuka tace"Amma yaya ba zab'a kace zanyiba shine kaje kai d'aya ko?"idan wannan bata miki ba saiki bani kayata"Amma kasan ba kyau maida hannun kyauta ko?"Eh hakane"Amma zaki iya bani sai kiyi istighifari ko?"shiru tayi ta juya masa baya"yad'an girgiza kansa kawai....har suka iso Air port d'in muslima batayi mgn ba "Alokacin kuma 11:35 am"jin motsin bud'e k'ofar yasaka ta juyo suka had'a Ido dashi saiga hawaye"kukan na meye kuma?"tayi shiru kanta ak'asa "ya matso kusa da ita har jikinsu na gugar juna ya kama hannunta guda yasaka mata rafar y'an 1k da ledar da wayar ke ciki"karki damu bazan jimaba zan dawo"yak'are maganar yana cika hannunta yad'ago fuskarta"saita lumshe idanuwanta"ya tsurama kyakykyawar fuskarta Ido"yana jin kamar yayi kissing nata"Ahankali yasaka yatsun hannunsa yafara share mata hawayenta tas"ita dai ta lumshe Ido "*bud'e idon ko dubulle y'ar bak'a?* da sauri ta bud'e idon tana b'ata fuska tace"kai yaya Muslim shine zaka b'atamun suna ko?"by surprise taji ya dafa kafad'arta "k'irjinta yabuga! ta kasa kallon k'wayar idonsa"ki kalleni ki fad'amun hakan mana?"yak'are maganar yana jan karan hancinta "tad'an saci kallonsa"gabanta yafad'i sbd yacire eye glass d'in nasa"ko idonsa ke ciwo ne?"ta fad'a Aranta sbd ganin idanunsa jajir....zan tafi! ya katse mata tunaninta "Agefen kafad'arsa ta kwanto tana sakin k'aramin kuka"ba k'aramin jarumtar danne yanayin daya tsintsi kansa yayiba yad'an shafi bayanta yace"kimun Addu'a kinji nasan An fara kiran sunayen pasingers"Allah yatsare ya saukeku lafiya"ta fad'a Akunyace tana janye jikinta daga nasa"da Ameen yah Amsa yana maida eye glass d'in nasa"kanta Asunkuye gaba d'aya jikinta irin k'amshin jikinsa yakeyi"bance ki dinga fita barkatai ba"su Malika da uwarsu babu ruwanki dasu bayan gaisuwa"to yaya zan kiyaye saika dawo"sosai yaji ta bashi tausayi"saidai shi yafita damuwa da rashinta"yasan sbd yana kulawa da ita Agidan shiyasa bataso yatafi badan sbd wani Abuba"da wannan tunanin yafito daga cikin motar ya kalli driver da body quards nasa dake jiran fitowarsa ya musu Alamar suje kawai"shi kuma mutum guda yabishi da troley d'in kayansa......✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba koki siya kika fitar Allah ya isa banyafe mikiba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

...........tunda driver ya juya Akalar motar suka doshi hanyar gida muslima keta fushi ko tari batayiba Acikin motar har suka iso gida"kai tsaye sashensu Eyyah ta yada zango"yadda Eyyah d'in ta lura da fuskarta bbu walwala yasaka tafara zaton kodai muslima da muslim sun fara soyayya ne Amma su basu sani ba?".....wai Eyyah sai mutum yayita sallama ki masa shiru ko?"Eh nayi shirun, meya hana ki bud'e murya kiyi mgn"tayi shiru ta zauna kan kujerah"Ina zaki da kud'i?"cewar Eyyah tana kallon kud'in da ledar hannunta"yaya ne ya bani"dama Ina son zuwa kasuwa na d'inko sabbin hijabai, na kuma siyo wasu Abubuwan "ya kyauta kin gode"batayi mgn ba saima sannan tafara k'ok'arin zaro kwalin wayar daga cikin ledar"dam ! k'irjinta yabuga dataga wayar k'irar iPhone14 Pro max! Anya Eyyah yana sane yasiyamun wannan wayar kuwa?"sai kuma ta tuna da keys d'in motarsa dataga kud'inta Awaya 80 million suna hannunta be k'arba ba"wayar zatayi nawa ne?"bansan kud'in taba Amma itace waya k'arshen tsada koshi itace hannunsa"kije ki Adana idan baza kiyi Amfani da itaba"idan yadawo kin tambayesa"nide Amfani zanyi da Abuna"kallonta kawai Eyyah tayi batace komai ba "ta tabbatar idan muslim ya mallaki yarinyar sai tafi haka shagwab'ewa sbd tasan k'ara sangartata zaiyi da yimata gata"tana wannan tunanin Muslima ta tashi cike da murna ta nufi sashen su"tunda ta shigo tayi sallama sau biyu bbu wanda ya Amsa"ta kalli Hjy jamila dake zaune kan kujerah ga Naseem k'asa kan carpet Agabanta yayi kneedown,kabeer na tsaye rik'e da belt, d'auke kanta tayi ta wuce d'aki"saidai ranta yabata k'ilan sun gane shine ya sanarwa Abbie Abinda yafaru shine zata hukunta shi"gaba d'aya suka bita da kallo itada kwalin wayar hannunta"mommy iPhone14 Pro max cefa hannun yarinyar can"waye kake ganin zai siya mata inba muslim ba?"wlh in bacin gudun Abinda zai je ya dawo da dare nayi badda kama na d'auke shegiyar wayar balle harta hura hanci A kanta"koni iphone 13 ce nake da ita sai ita banza zata rik'e irin wannan wayar da saika kai wani shege kake rik'eta"shidai naseem na saurarensu be tankaba"yakuma sha Alwashin sanarwa muslima ta b'oye kayanta"Hjy jamila kuwa shiru tayi sbd ganin Naseem na nan"wai kabeer me kake jira dashi ne da bazaka fara jibgarmun d'an iska me kunnan k'ashi ba?"taraka nakeyi dama,kasan kwanaki na rabaka da siyama Amma kak'i ji ko?"na lura y'ar iskar yarinyar nan tamkar ta tsafeka itada muslim "yaron dake gaba dani baya tankamun Amma shine keda mutunci A wajenka sbd baka kishina"kafi sonsu dasu Malika dakuke ciki guda ko?"kiyi hak'uri mommy ni Ina son kowa kawai bak.....dukansa da kabeer ya fara yasaka yayi shiru "tun yana jurewa har yafara ihu"muslima dake cikin d'aki tafara juyo ihunsa "kukan tausayinsa ta saki "tasan ko taje ta basu hak'uri bazasu kyaleshiba"tun tana juyo ihunsa har tadena ji"tayi tagumi tana tunani"can ta sauke Ajiyar zuciya tana fad'in Allah yasa yayan ya Amince"daga haka tafara k'ok'arin kiran layinsa"sai gab da zata tsinke ya d'aga wayar cikin kasalalliyar murya yace hellow !! yaya Muslim! *Uhmm dubulle y'ar baka*"kuka ta sakar masa"kinga tunda bakyason sunan nadena fad'a"nifa yaya ba haka bane "to menene?"ba yaya kabeer bane yaketa dukan naseem be masa komai ba"kuma mommy ce tasaka ya dakesa"shiru yayi yak'i mgn yana tunani k'ilan sun gane shine jiya yaje ya sanarwa Abbie komai daya faru....yaya Muslim dan Allah zan rok'i wata Alfarma wajenka badan na isaba sai dan Allah zaka mun "murmushi yayi marar sauti yadda bazata jiba yace"meye ne?"yaya dan Allah ka fidda Naseem k'asar waje yaje yayi karatunsa koya huta da fitinarsu"ko can inda kake ne ka kaisa (America)"sai yayi karatun kana jin motsinsa"shikenan idan nadawo zan sanarwa da daddy"ihun murna tayi tana yanke wayar.....kafin ta d'auki sabuwar wayar ta saka chargy da

nufin idan ta cika ta maida komai dake a tsohuwar wayarta cikin sabuwar"bayan ta saka chargy d'in ta kwanta bacci"sai bayan sallar Azahar tafarka"saida tafara yin sallah sannan tayi wanka"ta shirya cikin dubai Abaya lemon green"fitowa tayi daga cikin d'akin da nufin taje tayi lunch"tana fitowa ta  hango Hjy jamila ta bud'e warmer d'in Miya tana zuba wani Abu ciki me kama da magani.... innalillahi wa inna ilaihir raju'un! ta fad'a Aranta tana juyawa ta koma ciki"kuka ta fashe dashi Afili tace meye zan miki kisoni mommy?"wace irin tsanace kikamun haka?"kowa yaci Abinci niban ciba shine kika zuba wani mugun abun ciki sbd ki cutar da rayuwata"Aikuwa nagama cin Abincin gidan nan"tana cikin wannan yanayin naseem yaturo k'ofar ya shigo ya murza key"da Ido ta tsaresa tana masa  kallon tambaya"idanunsa sunyi jawur Alamar yasha kuka"Naseem meye ma'anar hakan dakayi?"mgn zamuyi Anty muslima"yafad'a yana zama gefenta"murya can k'asa yace"waye yasiya miki wayar d'anaga  kin shigo da ita d'azun ? babu wani b'oye b'oye tasanar masa sbd ta yadda da Naseem"murmushi me ciwo yasaki yace"dama nasan shine zai siya miki nadai tambayane sbd na tabbatar "to ki d'auki wayarki Anjima ki kaita d'akin Eyyah ki Adana"sbd naji yaya kabeer yace zaizo ya d'auketa ke baki Isa ki rik'e waya me tsada kamar taba "saidai dan Allah karki sanarwa kowa Anty muslima"kinga ko yanzun yadakeni sbd jiya na kira Abbie na sanar masa kunyi fad'a da Anty Malika daddy ya goyi bayanta zai dakeki.....karka damu Naseem babu wanda zaiji"niko kwanama bazan yiba Anan"to ki rufe d'akin,sannan ki d'auki keys d'in motar yaya dake wajenki"sbd gudun kar Asami matsala"duk zanyi naseem "nagode da k'auna da son zumunci dani dakakeyi"Ina jinka kamar uwa d'aya muke dakai d'an uwana"sai ta saka mishi kuka"yamatso ya rungumeta yana share mata hawayenta yana janta da fira"sai gashi ta sake harda yin murmushi"ta rab'a kud'in da dollars yabata zata bashi yasanar mata shima yabashi 50k"batace komai ba ta maida kud'in ta bashi tsohuwar wayarta kyauta"ba k'aramin murna yayiba sbd wayar babbace zatayi 200k sabuwarta"bayan ya Amsa ya bud'e k'ofar d'akin yad'an lek'a yaga bbu kowa a parlourn sannan yafito"ita kuma ta saka hijab ta d'auki keys d'in shashensa dana motarsa ta nufi sashen Eyyah da nufin taje taci Abinci..... Adaren ranar muslima sashen su Eyyah ta kwana"

tun bayan kabeer ya gama dukan naseem Hjy jamila tajashi d'akinta ta bashi spire key tace"cikin dare yaje ya bud'e d'akin muslima ya d'akko mata wayar da keys d'in motar dollars dake wajenta"Abinda yafaru kenan"koda yabud'e be sameta Ad'akin ba"yayi bincike sosai duk ya hargitsa d'akin ya watso mata kaya k'asa da saman bed"Amma bega wayaba da keys d'in mota ba"Atake ransa yabashi Naseem ne dayaji yana maganar zaizo ya sanar mata shine ta gudu"saidai yasha Alwashin bazai masa komai ba zai nunama mommy bega komai ba....Awashe garin ranar data dawo ta d'auki kayan sawarta tazo tasami d'akin Ahaka, ta girgiza kanta tana Addu'ar Allah yaka mata k'arshen Abin.....

*bayan kwana 5*

tunda kabeer ya shiga d'akinta yayi bincike muslima ta dena kwana saidai tazo tayi Abinda yaka mata ta koma shashen su Eyyah "hakama tadena cin Abincin gidan wajen Eyyah take cin Abinci"tsakaninta da Muslim tun ranar data kirashi game da Naseem basu koma yin wayaba"har yau Friday da take tunanin zai dawo"tun jiya ta gyaro sashen sa tas"yau kuma ta tashi da d'okin zuwanta gidan ummah"so takeyi daya dawo bayan sallar la'asar yasaka Akaita"saidai tarasa meyasa tun safe taketa jin fad'uwar gaba? ga wani irin kyau Ayau taga tayi na musammun??"tana cikin yanayin hakan kuma Abba ya sanar Anjima da yamma Abbie

yace"Ataru Aparloun sa za'a yi family meeting"in bacin tasan dole taje data hak'ura da zuwa family meeting d'in tayi tafiyarta gidan ummah......."Atare itada Eyyah suka shiryama uban gayyar Abinciccika masu rai da lafiya"bayan Antaso masallaci Anty habiba da husnah da yaya zainab y'ar Abba me Aure duk sukazo gidan wajen taron family meeting d'in sbd kowa Ansanar masa.... Ab'angaren Hjy jamila kuwa ,tasan tsawon zamanta da daddy kusan shekara 35 sau biyu Aka tab'a yin family meeting a bugaje's house's"saidai yanzun jikinta bata yakeyi kamar babu Alkhairi Awannan taron"Amma zata zuba Ido taga idan Antaru wace uwar za'a yi?....misalin k'arfe 3:11 pm muslima na zaune a parlourn Eyyah "husnah nata yarfa mata kalba k'anana"suna d'an tab'a fira jefi jefi sbd sun kusan idarwa"k'ananun kaya ne riga da wondo Ajikin muslima"sun kamata sosai musammun rigar data matseta sosai"wondon ya fidda shape d'in k'ugunta"saidai tad'an ratayo milk d'in hijab nata daga gefen bayanta ta sauka zuwa har k'ugunta"tayi hakane sbd batasan ko wani namiji ya shigo ba"gaba d'aya yau zafi Akeyi sbd hadarin dake sararin samaniya"shiyasa ta sanya k'ananun kaya"kasancewar tanada yawan jin zafi duk iskan fanka dana AC dake Akwai parlourn be ishetaba saida ta kunnah fanka ta girke ta Ajiye gabanta"gaba d'aya ta zubama wayarta Ido tana chats da k'awarta jidda"yayinda husnah ke mata kalbar tana satar kallon wayar Aranta tana mamaki"sai kuma data tuna da dollars saita cire mamakin domin tasan bayanshi babu wanda zai siyama muslima irin wannan tsadaddar wayar tunda bata kula samari....husnah bata gama wannan tunanin ba "ma'aikatan gidan ,irinsu cleaners da masu bama flowers ruwa suka fara shigowa da manyan ledoji"wani irin mummunan fad'uwa gaban muslima yayi"wanda itama batasan daliliba"ganin Ana shigowa da kayan kawai yasaka ta fahimci dollars yadawo"bata gama wannan tunanin ba taji sautin Amon jarumar muryansa me matuk'ar d'aukar hankalin y'an matan zamani"gaba d'aya husnah ta bishi da kallo tana tasbihi Aranta "kullum idan ta gansa sai tayi Addu'ar Allah ya Ida cire mata sonsa Arai"tasan suraj ya had'u shima"saidai dollars me gaba d'aya ne"idan suraj  na tare dashi ko kyawunsa bata gani.... Atake k'irjin muslima yabuga dataji muryansa "da sauri taja hijab d'in da nufin ta rufe jikinta baki d'aya"saidai dayake hijab d'in sulb'i gareta saita zame.....tunda ya shigo cikin parlourn da bayanta idanuwansa suka farayon  tozali"da wani irin kallo irin na k'asan Ido yake jifar bayanta dashi Atake yaji kasala"husnah dai cika mata gashi tayi ta gaidashi yana k'ok'arin zama kan kujera "gaba d'aya k'amshin turarensa yacika parlourn"yana sanye da suit coffee brown "da sukayi matuk'ar yi masa kyau"sai bayan ya zauna ya Amsa gaisuwar husnah tare da tambayarta Anty habiba"kafin ta bashi Amsa Eyyah ta fito daga cikin kitchen baki washe tana fad'in ga babban mutum ga babban mutum"d'an murmushi yasakar mata beyi mgn ba yana dai kallon mutuniyar tasa datake k'ok'arin saka hijab "Aransa yace"*my world!* kenan! har wanka na miki miye za'a b'oyemun?"gefensa Eyyah ta zauna tana mamakin meye yasakashi yin rama ne?"ga k'asumba ta cika masa fuska....yaya sannu da zuwa! Cewar muslima batare data kallesaba, tadai juyo ta gyara zamanta"bakaji takwara na maka  mgn?"cewar Eyyah"ya mutsa fuska yayi yace"barta Eyyah ba tun d'azun ta ganniba"dariya husnah ta saki"muslima ta mik'e tsaye ranta Ab'ace idanuwanta cike da k'wallah tace"ke kuma sis meye Abin yin wani dariya?"har kalban bana so ki idamun zan tsefe wacce kikayi tun....sai tayi shiru da gudu ta wuce d'akin Eyyah"dollars dai afuska be nuna komai ba"saidai Azuciyarsa beji dad'in kukan nataba beyi zaton zata masa kukaba dabai tsokane taba....babban mutum kaje kaci Abinci ko wankan zaka fara yi ne?"no Eyyah bana jin yunwa zansha fura idan na fito"sosai tayi mamaki sbd be tab'a dawowa ba yak'i cin girkinta"saidai zata bari idan ya nutsu ta tambayesa rashin

lafiya yayine daya zabga irin wannan ramar haka??"motsin tashinsa tsaye yana Amsa waya yasakata binsa da kallo harya b'acewa ganinta"yana wayar harya iso d'akinsa dake Anan sashen nasu Eyyah"tunda yashigo yaketa d'an murmushi Afili yace "na gaji da b'oye soyayyarki danake dako tsawon shekaru da dama halimatu"yak'are maganar yana kwanciya saman luntsumemen bed d'insa ya lumshe Ido batare daya zare takalmin k'afarsa sawu ciki ba"kasancewar gangar jikinsa ne kawai saman bed d'in "ko Ina gwanin kyau Atsabtace"ya d'an bud'e Idonsa yakoma lumshewa Aransa yace"yarinyar nan zansha fama da ita wajen saurin kuka"sai kuma wata zuciyar tace idan baka same taba fa?gabansa yafad'i ya tashi zaune yafara tunanin kodai yasanarwa suraj Anjima koda Akwai wata shawaran dazai bashi game da lamarin ?"sai kuma ya girgiza kansa sbd yatuna dayazo neman shawaransa sbd yana son husnah k'in goyon bayansa yayi....yajima yana sak'a da warwara"har lokacin sallar la'asar yayi duk yana tunani"saida kiran suraj ya shigo wayarsa yaduba Anan ya lura da lokaci"da hanzari ya tashi tsaye yafara rage kayan jikinsa kafin yasaka bathrope yashiga wanka"koda ya fito Anan cikin d'aki yayi sallarsa sbd wasu masallatan duk sun gama sallar"bayan ya idar yad'an shafa creams da turaruka yasaka jallabiya dark brown"yana k'ok'arin fitowa daga cikin d'akin kiran suraj yakoma shigowa cikin wayarsa"oh suraj ka bani da jaraba"irin wannan dogon kira haka"yak'are maganar yana yamutsa fuska ya d'auka beyi mgn ba "wai Abokinah kana Ina?"d'akina! yafad'a Atak'aice"okay kazo inji Abbie,kai kawai Ake jira kowa yataru Anan parlourn sa za'a yi family meeting "tsintar kansa dollars yayi dajin fad'uwar gaba"da k'yar yayi jarumtar cewa gani nan zuwa!.... daga haka ya yanke wayar yanufi parlourn Abbie sbd shi saima yanzun yasan za'a yi wani family meeting d'in.....kusan mutum  yafi Ashirin ne zaune A parlour"Abbie da Eyyah ne kawai zaune kan kujerah Amma harsu daddy duk suna zaune kan carpet"muslima na daga gefen zainab"tasha Alwashin da Angama zata fita ta hau Adaidai ta ta tafi gidan ummah"bazata sanarwa dollars yasaka Akai taba sbd fushi takeyi dashi"tanajin sallamarsa gabanta yafad'i bata san lokacin data d'ago kanta suka had'a Ido dashi ba"Atare k'irjinsu yabuga"harara ta ballah masa had'e da murgud'a masa d'an bakinta "Abin mamaki sai taga ya kasheta da wani tsadaddan murmushin da yayi bala'in yimasa kyau,yana d'auke kansa ya nemi waje gefen suraj da Ramadan ya zauna"Abbie ya bisa da kallo yana fad'in sallu Anal nabiyil Kareem"bayan Angama salatin Abba yayi saurin kallon muslima yace" mamana cika mana da Addu'a "bazata iya musu da Abba ba kanta Ak'asa tashiga yin Addua cikin zak'in murya"daga Abban har muslima d'in da mugun kallo Hjy jamila ke jifarsu duk ummi da Eyyah na lura da ita"bayan Angama Abbie yayi gyaran murya yana fad'in Alhamdulillah!  muna godiya ga Allah d'aya nuna mana zuwan wannan rana me Albarka"muna fatan Allah yajik'an Isma'il da Aysha (mahaifin dollars da mahaifiyar muslima) duk suka Amsa da Ameen,banda Hjy jamila da Malika da kabeer"Abaya Abubuwa sun faru masu kyau da mararsa kyau"Amatsayina na Uba gareku sulaiman da kuma kaka gareku ku yara na yanke hukunci kuma har na zartar Ayau bayan tasowa daga sallar juma'a Anan masallacin Anguwar nan mutane sun shaida d'aurin Auren *yusuf da halimatu* wato Muslim da muslima ...na gaji da ganin babban mutum ba iyali !na zab'a masa halimatu sbd nasan zai rik'eta bisaga Amana"duk lokacin da kuka so zaku tare Abinku"kaima suraj na zab'a maka husnah Amatsayin Abokiyar rayuwarka"An saka ranar Aurenku da ita wata 6 masu zuwa"kabeer da Ramadan inaso kafin wata 6 yacika ku fito da mataye ko kuwa na had'aku Aure da wad'anda na gadama"sai Abu na gaba sulaiman kaima zaka k'ara Aure nanda wata 4 masu zuwa in sha Allah nine zan zab'a maka wacce zaka

Aura"umarni ne ba shawaraba"kai kuma habibu bazance ka k'araba sbd kayi dacen mace ta gari idan kuma kana buk'atar K'arin zaka iya"sai mgn ta k'arshe Naseem nanda sati biyu zai koma America da karatunsa ,babban mutum ne yabiya masa"ke kuma marar mutunci na baki kema wata 6 ki fiddo miji ko kiji labarin Aurenki "yak'are maganar yana kallon Malika da jinta na wucin gadi ya d'auke........✍️

zazzafan sharhi guys😎

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba koki siya kika fitar Allah ya isa banyafeba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq

[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

.........gaba d'aya parlourn tsit yayi"kowa nabin Abbie da kallo"wasu zuciyoyinsu fal farin ciki dajin dad'in wannan Had'i da Abbie yayi"yayinda wasu kad'an daga ciki zuciyoyinsu bak'i k'irin suna tafasa.....tunda yaji kalaman Abbie yake taunar lip nasa na k'asa kamar zai hudashi"saida yaji zafi ya tabbatar da ba mafarki bane yakeyi da gaske ne"saidai Abin yamasa tamkar Almara"ko a mafarki bai tab'a zaton zai samu muslima da sauk'i irin hakaba"d'azun fa yaketa tunanin yadda zai samu mafita Ashe A lokacin tama jima da zama matarsa"tamkar yaje ya rungume Abbie haka yakeji sbd tsananin k'aunar tsohon dayaji tana k'aruwa Aransa "Atake Annuri da farin ciki suka da baibaiye fuskarsa da zuciyarsa....sam wannan ba Adalci bane! kuma ni Ancimun fuska da Akace Alh yak'ara Aure "wato niba mace ta gari bace kenan?kowa yasan kabeer shike son husnah shine za'a bama sur....yimun shiru! daddy yakatse Hjy jamila cikin zafin rai yana cigaba da cewa" kin isa ki nunawa mahaifina Abinda yafi daidai ne?"kuka ta fashe dashi tana kallon su Malika tace ku tashi muje"Naseem kuwa ko Ajikinsa da mommy sbd yasan halinta yaja mata"murna biyu yakeyi zai koma k'asar waje ga kuma murnan Auren muslima da dollars "saidai idan yatuna zai rabu da siyama sai yaji wani iri... shashshekar kukanta yasaka gaba d'aya sauran mutanan dake cikin parlourn binta da kallo"mama nah lafiya?"cewar Abba"nifa Abba yayana ne uwa d'aya uba d'aya haka na d'auke sa,shine kuma zai zama mijina ?ni bana sonsa kuma kunya zanji daz.....kallon da daddy ya watso mata yasaka ta had'iye sauran maganarta"tashi ki bama mutane waje"kar Allah yasa ki soshi d'in"shidai

dollars nata kallonta har Naseem ya matsa kusa da ita yamik'ar da ita tsaye suka fita"da Ido yarakasu har suka fice daga cikin parlourn "ya sauke numfashi yana makama suraj harara dake zungurinsa da k'afa"tunani yakeyi dama Abinda ya guda kenan tun farko, kar tace bata sonsa shiyasa be sanar mata soyayyarsa tun tuniba"yakuma ji dad'in yadda tace ta d'aukesa kamar uwa d'aya uba d'aya"Amma zai nuna mata cewa ba wannan yanzun tsakaninsu ,da kansa zai koya mata yadda zata soshi....my friend yaya dai ko kanada Abin cewa?"banida shi daddy"Abbie nagode sosai da zab'in ka"yafad'a cikin nutsatstsiyar muryansa yana mik'ewa tsaye suka fita shida suraj.....ahhh lallai mutumin kace yau tazo maka Asa'a tunda ka zama Ango ,sai kaje ka cire jallabiyar ka saka shadda yau Akwai hidima fa"d'an murmushi yasaki beyi mgn ba sbd tsabar farin cikin dayake ciki"ada ban yadda da maganarka da kace kanada mataba sai yanzun na Amince"ko yanzun karma ka Amince "k'ilan sai kaganta da baby nah zaka yadda"suraj yadinga dariya yana fad'in kaida ko zancen tarewa da shagalin biki ba'a yiba?"dama Atsarina bana son bidi'a sbd haka babu wani Abinda za'a yi"zan d'auki matata mu tafi"dollars Ai dama tuni na dad'e da fahimtar son muslima kakeyi"Amma kayi hak'uri zamu shawo kanta"sharesa yayi yak'i mgn ya wuce side d'insa dake cikin gidan.....suna fitowa daga cikin parlourn ta k'ara k'arfin kukanta"Naseem beyi mgn ba saida suka iso can cikin lambun gidan suka zauna kan wasu kujeru na hutawa" Ahankali yace"uhmmm Anty muslima na d'auka farin ciki zakiyi sbd kin mallaki yaya Amatsayin mijin Aurenki?"kinga yadda y'an mata ke haukan cewa suna sonsa"kofa Anty Malika tana sonsa Amma baya sonta"kedai nasan zai soki....kaga Naseem ka k'yaleni da zancen wani so"idan har yana sona zai dinga b'atan rai ne? ko yau daya dawo kaga irin disgin daya mun daga na gaidashi"bazan iyaba ni bana sonsa"okay to shikenan kije kici gaba da k'in nasa"yafad'a cikin gatse fuskarsa bbu walwala yamik'e tsaye tana kiran sunansa yamata banza ya tafi"ba k'aramin haushi Naseem yaji ta bashiba"ace kamar yaya Muslim ga kyau , kud'i,jan aji,kwalisa Amma duk tace bata sonsa"lallai sokuwace ita"zai k'yaleta yaga zata sakko ko kuwa tana Akan bakanta na bata sonsa....

uban kuturu yayi kad'an ballan tana na makaho!" Cewar Hjy jamila da tsantsar tashin hankali da razani ke  Acikin k'wayar idonta"tana tsaye sai huci takeyi tamkar kububuwa "ta nuna kanta da d'an yatsa tana fad'in,ni za'a yiwa iskanci da d'iban Albarka"wlh daidai nake da kowa Agidan nan "gaban idona tsohon nan zaici fuskata....dan Allah mommy kiyi shiru musami mafitah"bazan zaunah wannan y'ar iskar yarinyar ta finiba ta dinga d'agan kai da huran hanci itaga matar bolonia"cewar Malika dake kukan b'akin ciki"kabeer yaci gaba da cewa harda wani gulmar Naseem zai tafi America "ni bai burgeniba da kud'in yabashi da shine zamuji dad'i....shiru sukayi sbd shigowar daddy cikin parlourn"gaba d'aya kabeer da Malika suka tashi"suna fita Hjy jamila ta kalli daddy ta fashe da sabon kuka"wai Alh yanzun da gaske Auren zaka k'ara kenan?"sannan Akan idonka zaka bari a Aurama muslim yarinyar nan bayan nasha nasar maka yana son Malika itama tana son....kinga da Allah ya Isa haka! musu ko jayayya kikeso nayi da mahaifina ne?"Aikin gama yariga ya gama, da muslima da Malika duka y'ay'ana ne babu wanda yafi wani A cikinsu"batun Aure muddin yana kan bakansa kinsan sbd ke bazan bujurewa umarnin mahaifinah ba....haka kace?"Eh Ai kinji"yafad'a yana tashi ya wuce samansa..... muslima ce zaune a d'akin Eyyah tanata sharb'an kuka daga Eyyah har Anty habiba babu irin rarrashin da basuyi mataba Amma tak'iji itaba bata son dollars yayanta ne "duk idan tace wai kunya zataji ace mijin tane daga Eyyah har Anty habiba sai sunyi murmushi"ganin tak'i jin rarrashi yasaka suma sukayi biris da ita"Abbie kuwa uffan bece mataba"shidai Abinda

yasani daga ita har muslim d'in gata ya musu"yasan nan gaba kad'an zata soshi..... dollars kuwa cikin farin ciki ya canza kaya zuwa milk d'in sabuwar shadda giznah wacce Akayima Aikin hannu da orange d'in zare"takalmi,hula , Agogo duk orange yasaka"ga hular yad'an kasheta daga gaban goshi ,yad'an gyara zagayayyen k'asumbarsa dake salk'i tana d'aukar Idon me kallo " yau irin k'amshin daya keyi na musammun ne"kasan ransa yana tunanin mutuniyar tasa ko tayi shiru ta hak'ura ko kuwa tana can tana kukan?? oho"Anutse yake tafiyar yana nufowa parking lot yana Amsa waya.....yaya muslim mijin Anty muslima "juyowa yayi suka had'a da Naseem dake kallonsa yana murmushi yace kayi kyau sosai yaya"Allah yasa Alkhairi "saida yagama wayar kafin ya kallesa da d'an murmushi saman fuskarsa kafin yace"Naseem yau nikake zolaya ko?"ba haka bane yaya da gaske ne "tun d'azun nake jiran fitowar ka sbd na maka godiya"naji dad'i zanbar k'asar nan ,nagode Allah yasaka da Alkhairi"Ameen ya Isa haka"Ina ka baro k'awarka taka kuma Antyn ka?"nifa ba ruwana da ita yanzun tunda bata jin shawara "ko mgn bazan koma yima taba sai idan ta Amince da Aurenku"d'an murmushi yasaki domin ya fahimci Naseem na kafa gwabnatinsa wajen muslima"beyi mgn ba kawai ya wuce yayi gaba Abinsa"kasancewar harda wasu daga cikin hadiman gidan suka ziyarci d'aurin Auren"hakan yasa suka dinga yimasa Allah yasa Alkhairi "iya lab'b'ansa kawai yake Amsawa kafin Abud'e masa mota ya shiga"su kansu duk wand'anda ke'a k'ark'ashinsa sun fahimci yau ogan nasu na cikin farin ciki"sbd yawan walwalar da suka gani saman fuskarsa"kai tsaye gidan ummansa suka nufa"k'asan ransa yana fargaban yaya ummah zata d'auki zancen Auren nasa idan ya sanar masa?"shi bema san ta yaya zai soma sanar mata ba?"fatansa Allah yasa tayi farin ciki da Auren,ta kuma saka musu Albarka"da wannan tunanin suka iso.....tun A haraban gidan daya fito daga mota yaketa yima masu gadi kyauta ta musammun harya wuto cikin gidan"Mamy ce zaune a parlourn itada yara"cikin ladabi ya gaisheta kafin ya wuce d'akin umman"tana zaune gefen bed suna vedio call da Usman "fuskarta d'auke da murmushi"jin sallamar dollars yasaka ta d'ago kanta ta kallesa tana Amsawa kafin tace"ka koma kirana daga baya ga yayanku nan ya shigo"daga haka ta katse wayar tana d'an murmushi had'e da binsa da kallo"sbd wani irin kyau na musammun dataga yak'ara yimata"ga murnan ta ganshi da manyan kaya"dama bata son k'in saka kayan Al'ada da bayayi"saidai tayi mamakin yadda ya zabga uwar rama irin haka"saman sofa ya zauna yana d'an murmushi yace"ummah Ina wuni?"na sameku lafiya?"Alhamdulillah Muslim"wai rashin lafiya kayine daka tafi? sunkuyyar dakai yayi yace"uhmm kawai"tayi shiru can tace"Ina kabaro muslima na d'auka koma tare zaku zo da ita? tana can tanata fushi da koke ita bata sona ni yayanta ne bazat....shiru yayi sbd ya manta da yayi sub'utar baki "kallon banganeba ummah ta jefesa dashi"yad'an shafa gemunsa yana koma yin k'asa da murya yace"kiyi hak'uri ummah Abbie ne yau ya d'aura min Aure da ita"ba tare daya shawarci kowaba sai d'azun yasanar mana a family meeting da Akayi", Amamakin sa sai yaji tace"Allah yasa Alkhairi "yad'an kalleta yaga babu damuwa saman fuskarta"kiyi hak'uri ummah wlh babu saka hannuna A Auren kuma....kaga niban ce komai ba muslim"nina haifeka bakai ka haifeni ba"tuni nasan son muslima kakeyi kadai b'oyemun sbd nace ku daidata da Amatallahi"itama muslima d'in nasan zata soka yanzun k'uruciya ke damunta"zancen gaskiya Ada bana sonka da yarinyar"saidai tunda Alh yamun nasiha bayan yagama ya rasu Aranar da kazo ita bayan kun tafi ya rasu"jikina yayi sanyi matuk'a"kuma na dinga tuna Alkhairin mahaifinta da yadda uwarta ta kula dakai sadda jamila ke gallaza maka"sai naga ban kyautaba"Allah yasa Alkhairi yabaku zaman lafiya da zuria ta gari"cikin farin ciki ya Amsa da

Ameen yana jin shifa yau tazo masa Asa'a"yanzun yaushe za'a yi hidimar bikin?"wlh ban saniba ummah"Abbie dai yace duk sadda na tashi mu tare gidana"to shikenan saika fara k'ok'arin had'o kayan lefe ka bata"kodai ba'a yi komai ba Anyi walima sbd neman Albarkan Auren"shidai kansa na'a k'asa yanajin idan ta shine yauma Ace su tare"dole yasamu cikin wata guda ko 40days a Ida Aikin gidansa su koma"may be daga baya ya d'auki kayarsa su tafi honey moon"ungo samun contact nata ma dinga waya"tun jiya Amatallahi ke dokin zuwan nata Ashe Ammata laifi"ta k'are maganar tana mik'a masa wayar"saida ya Amsa kafin yace"to ummah ita basai taje gidan ta kamata ziyara ba"kawai idan ta taho saiki kirani natura Naseem yashigo da ita ciki "ita muslima d'in bazata zoba?"ummah gaskiya fitanta ba yanzun ba"ko islamiya bara taje ba gobe "shiru tayi batace komai ba sai d'an murmushi tana jin dad'in wannan Aure"sbd ta gaji da ganinsa ba iyali ,tana son kafin ta mutu taga jikokinta....gashi ummah bara na tafi"yafad'a yana Ajiye mata wayar yana duba time "zuwa safen zan shigo in sha Allah"be rufe bakiba kiran sadeeq ya shigo cikin wayarsa "d'auka yayi beyi mgn ba"daga d'ayan bangaren sadeeq ya daure yana fad'in Ango Ango!! saidai muji Asama baza'a sanar mana ba?"uhmm haka Abin yazo ya gida?"Alhamdulillah! Ina wani uzurine zan kiraka"yana fad'in hakan yakashe wayar "Atare suka fito tare da ummah sbd ta masa rakkiya"Anan Amatallahi ta gaidashi"sai bayan ya fita tace ummah Ina muslima?"tana murmushi tace"muslima ta zama Amarya b'oyenta muslim keyi"Ayau aka d'aura Auren su"kai Masha Allah! Allah yasa Alkhairi"cewar Mamy cikin nuna jin dad'in ta"yayinda Amatallahi jikinta yayi sanyi"Ayanzun ta Ida yadda itada samun dollars har Abada"fatanta Allah yabata mesonta Acikin manemanta itama tayi Aurenta "daka Auri wanda baya sonka gara ka Auri me sonka"ta jima da zaton shida muslima son juna sukeyi"gashi har sun kaiga mallakar juna Amatsayin ma'aurata.....

Dollars be shigo cikin gidan ba sai bayan sallar isha'i shima sbd yunwar dake damunsa"rabonsa da Abinci tun break fast d'in safe"shiko yunwar ba yaji sbd ba Abincin bane gabansa"sai yanzun yafara jin yunwar sama sama"Addu'a yakeyi Aransa Allah yasa yasamu y'ar darun nasa "Aikuwa yasameta zaune tana cin tuffa"kanta bbu d'an kwali ta wani d'aure fuska "idanuwanta sunyi ja da kumburi sbd kukan data sharb'a"tana jin haushin Eyyah na d'aure mata fuska sbd tace bata son yaya Muslim"hakama Anty habiba da husnah ko sallama basuyi mataba suka tafi"ga Naseem shima fushi yakeyi da ita....gabanta ya fad'i dataji muryanshi yana yin sallama"kan idonsa ta tashi da sauri tabar parlourn "ya girgiza kansa yana Addu'ar Allah yasa taci Abinci"babban mutum! Uhmm Eyyah sannu da gida"yauwa sannunka"yanzun aka maka wani abun ko shima bazaka ciba?"Akamun Abinda yasamu"Ina fatan kin bama matata Abinci taci ta k'oshi "d'aure fuska tayi tace"Ina ruwana da taci ko bataciba?"idan kadamu saika tambayeta"daga haka ta mik'e tsaye ta nufi dining area "shidai be tankaba "bema so sbd tana wannan shirmen suji haushin ta"yana mata kallon k'uruciya ke damunta Amma yasan maganinta"plate d'in naman kaji gashashshe da bowl d'in fruit salad had'e da kwanon fura ta Ajiye masa"Amm Eyyah karki dinga barinta fita saida izinina"kamar Eyyah tayi dariya saita dake ta Amsa dato kawai"Aranta tace bawan Allah shi yana sonta ita kuma ja'ira tana wulak'anci nasan yadda zanma y'ar banza"bayan Eyyah ta wuce d'aki shi kuma yaci gaba dacin Abinsa yana tunanin sahibar tasa"bayan yagama beko bi takan Eyyah ba ya wuce sashensa sbd Agajiye yake....

washe garin ranar yakama satday"kamar ko wane week hakama yau tun 8:30 am muslima data kwana d'akin Eyyah ta shirin zuwa islamiya "dukda tare da Eyyah dame Aikinta suka had'a

break fast Amma Eyyan tak'i tankata"ita yanzun niyarta daga islamiya ta gudu gidan Hjy tunda ba'a sonta Agidan "ba wani break fast d'in kirki tayiba tea ne kawai tasha ta zumbula hijab ta d'auki jakarta ta fito daga cikin d'akin"tana fitowa Eyyah da Abbie dake zaune suka bita da kallo"kinada hankali kuwa halimatu?"cewar Abbie yana kallonta sbd ganin zata fita "menayi ni to?"fita naga zakiyi ne"ko kin nemi izinin babban mutum d'in ne?"nifa Abbie ban tambayesa ko?"ta fad'a cikin shagwab'a tana sakin k'aramin kuka"cak! Dollars dake k'ok'arin shigowa ya lab'e yana murmushi yana jin yadda taketa shagwab'a "ke dallah ki nutsu ko ranki yab'aci"ah ah bita Ahankali "cewar Abbie yana kallon Eyyah"kafin yamaida dubansa ga muslima yace"yusuf shine shugabanki yanzun"saikin bisa ki samu Aljannah kin sani tunda ba jahila bace ke"kije ki gaidasa yana b'angaren sa ki nemi izininsa idan ya Amince saiki je"to Abbie kasanfa halin yaya karfa yadokeni ni tsoro nakeji"Abbie na murmushi shi kansa yasan dole muslim zaisha fama da k'uruciyarta"kije bazai dokeki ba"to Abbie kodai ka kirashi tunda yana jin maganarka"ke kuma bakijin tawa ko?"bafa haka bane"to kije mana"dollars daketa dariyar shirmenta da sauri ya koma inda yafito sbd karta gansa ta fasa zuwa"yasha Alwashin kuma bbu wata islamiyar da zataje"saima ta tayashi sunyi baccin da ciwon mara ya hanashi yayi Adaren jiya.....✍️

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n  2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba koki siya kika fitar Allah ya isa banyafeba

#mommyn fareesa
#dollars
#muslima
#suraj
#Eyyah
#hjy jamilah
#Daddy
#sadeeq
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

........tunda muslima ta doshi hanyar sashen nasa zuciyarta ke harbawa had'e da bugawa"gaba d'aya yau tsintar kanta tayi dajin tsoron shiga shashen nasa"wai yanzun nan ita matar yaya Muslim ce?"saita turo baki ta zaro keys d'in motarsa daga cikin jakarta ta islamiya da nufin ta bashi idan ta shiga"tana isowa bakin k'ofar sashen saida ta harari k'ofar sannan tad'an murd'a handle d'in, sai taga ta bud'e "Ahankali ta d'an lek'a kanta, taga cikin parlourn wayam babu kowa ,saita b'ata fuska kamar ta juya komai ta tuna? oho saita shiga ciki"dollars na tsaye Asaman bene ta glass yana hangota yana d'an murmushi"daga shi sai t shirt me gajeran hannu da wondo 3 quarter "k'afarsa sanye da silipas masu taushi irin na k'asar Amuruka"cikin nutsuwar data zama jinin jikinsa yabaro inda yake tsaye yabud'e k'ofa yafita daga cikin d'akin baccin nasa"yana fitowa idanuwansa sukayi tozali da ita,tana tsaye bakin k'ofar tana shawaran ta shiga kota k'wank'wasa??ta wani tsuke fuska "tana jin ya murd'a k'ofar gabanta yafad'i"tadai dake tad'an zabura tana matsawa baya batare data yadda tama yi gigin kallonsa fuskarsa

ba....Ido yazuba mata yaga kanta Asunkuye tana wasa da yatsun hannunta "saidai ya lura da yadda jikinta ke kirma"beyi mgn ba ya wuce ya zauna kan 3 seeter tare dashan Alwashin bazai mata mgn ba,kuma zaiga bazata tanka shiba haka zata yita tsayuwa"remote d'in TV ya d'auka yafara k'ok'arin kunnah kallo"yayinda k'irjin muslima keta fat fat! kamar zatayi kuka tace"yaya Muslim Ina kwana?cikin deep husky voice d'insa yace" tsayuwar meye kikeyi Anan? yak'are maganar batare daya Amsa gaisuwar tata ba saidai kallonta dayakeyi"wannan karon ba kallon k'asan Ido daya saba jifarta dashi bane" ah ah da fararen kyawawan idanunsa yake kallon nata Azahiri"zonan ki zauna ki fad'amun menene kiketa fushi?"d'an numfashi ta sauke Ahankali ta iso d'an nesa dashi....no zoki zauna Anan "ya nuna kusa dashi"d'ago kanta tayi suka had'a Ido....babu shiri ta d'auke kanta da sauri sbd ganin irin kallon dayake Aiko mata dashi"Atake taji ta daburce had'e dajin jikinta ya mutu"Ad'arare ta zauna gefensa daga can k'arshe "oya fad'amun tura bakin na meye kikeyi?"tayi d'an mamaki sbd be cika yimata mgn fuska Asake irin haka ba"ta d'auka ko shima beson Auren...halimtuuuuuuu! uhmm ,tunanin meye kikeyi?"to yaya Muslim bakai bane baka Amsa gaisuwa taba"kuma wannan Abbie d'in ya hanani zuwa islamiya ko?"murmushinsa ya danne yace"yaushe da yaushe ne kika gaidani ban Amsaba?"saida tad'an b'ata fuska kafin Ashagwab'e tace"ba jiya bane har husnah ta dinga dariya"kuma yanzun ma baka Amsaba"tamkar bazaiyi mgn ba sai kuma taji yace"dama haka aka koya miki gaida miji ne?"da sauri ta kallesa"ya d'age gira "ta kauda kanta"yes haka Akace ki gaisheni kina can nesa dani, Nima Ina nesa dake? uhmmm?tayi shiru"bayan haka Ai bazan Amsa gaisuwar wacce bata sona ba"da safe na Amsa gaisuwar budurwata datake sona! gimtse fuska tayi tak'i mgn"saidai ta rasa meyasa taji zafin kalamansa har fuskarta ta kasa b'oyewa? "shi kuma kallonta yakeyi Aransa yanata cin dariya...can yace"meyasa Abbie ya hanaki zuwa islamiya?"tayi shiru"dake nake mgn"toba cewa yayi saina tambayeka ba"ya kyauta"da kinyi gigin fita ba tare dana saniba dana b'ata miki rai Amarya"ko dayake uwar gidama tunda inada Amaryata ko?"da sauri ta kallesa fuska Atsuke "ya kasheta da murmushi"ta d'auke kanta cikin mamaki "sbd ita bata tab'a ganin yana murmushi ba"tanata cin magani tace"niba uwar gida bace"kuma ni Ina ruwana da Amaryar"?ta k'are maganar tana k'ok'arin tashi sbd ba k'aramin haushi yabata ba"Ina zakije?"islamiya"da izinin waye?"kanta Ak'asa tana share hawayen daba tasan dalilin zuwan nasuba"yad'an girgiza kansa yace"kinsan gwabnati ta hana Aikin banza ko?"islamiya zakije driver saiya kaiki"Amma zauna ki matsamun k'afana na mintina 15 ko nayi bacci saiki tafi.... Amma yaya babu ky..."sai kuma tayi shiru"bakyaji ko my *noory*? noory kuma? ta tambayi kanta"shi kuwa waskewa yayi sbd sunan daya saka mata Azuciyarsa kenan"idan barakiyi ba kije kawai"yafad'a cikin gatse sbd ya gwadata"ta turo baki tak'i tafiya sbd tasan ba kyau k'in bin umarnin miji"badan tasoba ta saci kallonsa ta gansa zaune yana danna waya "k'asa ta sakko tace"to zan fara yimaka"bari nayi ki gama kukan saiki mun"wato had'ani da Eyyah zakije kiyi ko?"salan tace wani abun na miki...nifa bbu ruwana da ita"bece komai ba yad'an kwanta rigingine saman kujerah d'in "ita kuma ta matso tana gulmarsa cikin ranta wai yaje ya kira Amaryar tasa tazo ta masa mana"dama yaje da ita gidansu Amaryar data gane kuranta....sarai ya fahimci zancen zuci takeyi saidai kawai taji yaja karan hancinta da shafar gefen kumatunta"ta d'an sauke numfashi ta sunkuyyar dakai"zoki fara yimun"batace komai ta kalli dogayen santala santalan k'afafuwansa dake sumul jajir kamar na jinjirin da baya taka k'asa"hannunta har kirma yakeyi kamar karta Aza saman k'afafuwan nasa"haka dai ta daure ta fara Aza hannunwan Ahankali....."daga ita harshi wani iri sukaji"musammun ma shi,saida ya rintse Ido"itadai tana

mammatsa masa tana gulmar wai gaba d'aya jikinsa gashi ne"ga wani irin kunyar tab'a masa k'afafuwansa da take ji"itadai Ak'agare take ya sallameta ta fita...bani ruwa! sanyayyar muryarsa ta katse mata tunani "batayi mgn ba ta mik'e tsaye ta nufi wajen k'aramin fridge d'in dake cikin parlourn "yayinda dollars ya juyo yana binta da wani irin kallo yana lumshe idanunsa da suka fara d'an ja"yana ganin zata juyo ya d'auke kansa"Ahankali tace"Ina cup?"kamun haka nan"batayi mgn ba ta iso ta mik'a masa"zaune yatashi ya Amsa"bayan ya b'alle murfin yafara sha ,muslima dake duk'e gabansa ta fara ganin labulayen jikin windows na kad'awa da Alama iskan hadari ne ke busowa"yaya kaga hadari zai taso nide natafi ko?"shareta yayi ya gyara zamansa yana kallon TV "kaji dan Allah?"nanma be tankaba"Aransa yace"yarinyar nan zata kasheni da shagwab'arta"zoki zauna na kira Amaryata ku gaisa"wani yaya Ina ruwana da ita ne?"wlh karma ka had'ani da ita indirji bakinta"inama wannan sarkin shishshigin(Hjy zarah) ?"sarai yasan zarah take nufi Amma sai yayi shiru ,dama tsokanarta kawai yakeso yayi"saidai yayi mamakin yadda taji haushin yayi zancen wata"saidai dama yaji Ana cewa koda mace bata son mijinta tana jin haushin ganinsa da wata"yayyafin da aka fara sama sama yasakashi dawowa tunaninsa"kafin yatashi ya rufe windows ruwan yafara k'arfi"da hanzari ya mik'e tsaye yaje yafara k'ok'arin rufe windows d'in parlourn "yayinda muslima tacika tayi fam itafa batason zaman su waje guda"ga kunyar wai shine mijinta tanaji....tsawar da aka saki yasaka tasaki k'ara had'e da ihu"saidai kawai ta ganta cikin jikin dollars ta cikwikwiye sa tana fad'in wayyo Allah Hjy zan mutu.....in bacin gefen bango suke da babu Abinda zai hana dollars ya fad'i su cube"dama lallab'awa yakeyi da kansa gashi zata koma tayar masa da hankali...yaya nidai ka kaini shashen su Eyyah mana"ta fad'a cikin shagwab'a lokacin da tsawar ta d'an lafa"saidai jm har lokacin jikinta kirma yakeyi"yayinda dollars shagwab'ar tata ta koma saka shi jin wani iri"saidai ya dake yad'an shafa bayanta murya Akasale yace"kin cika tsoro "ki bari ruwan ya tsaya saina rakaki ko?"kafad'arta ta nok'e tasaki kukan shagwab'a "d'aukarta kawai taji yayi kamar y'ar baby"ta saki ihu tana fad'in na shiga ukku yaya ka saukeni "wayyo Allah"be sauketaba saida ya zauna kan kujerah ya zaunar da ita Atsakkiyar cinyoyinsa"gaba d'aya jikinta ya d'auki rawa"dan Allah yaya kayi hak'uri zan tafi wlh"kasa mgn yayi sbd yadda yaga dukta tsorata ta rud'e"meyasa kikeso na barki ki fita cikin ruwa noory?"ko kina so kiyi mura ne?sanyi yakama mun ke?"yafad'a da wata iriyar murya Agefen kunnanta yana sanya fuskarsa Atsakkiyar wuyanta....rintse Ido tayi dukda Akwai hijab Ajikinta Amma numfashin dake fitowa daga hancinsa yana sauka cikin wuyanta "yasaka gaba d'aya jikinta ya mutu....wai dama haka yaya Muslim yake?"ta tambayi kanta tana saka mishi kuka "kinsan Allah koki nutsu ki dena wannan rigimar kona bud'e k'ofar na fiddaki daga cikin parlourn Ayita yin tsawar"shiru tayi saidai Atsorace take ya lura ko numfashin kirki batayi"zobe yamata da hannayensa"ba shiri ta jingina bayanta Ak'irjinsa"zuciyarta na wani irin harbawa"tayi dana sanin zuwa d'akin yafi ak'irga....yaya! menene noory?"ba ruwan ya tsayaba nika tashi muje mana"ki bari su Ida tsayawar mana gaba d'aya "kukan shagwab'a tasaka tana son k'wacewa daga jikinsa"saidai ko motsi bayayi"itace keta juye juye Ajikinsa"data gaji tasaka mishi kuka "ya girgiza kansa sbd har kan nasa yafara ciwo"Ahankali yace"kinyi break fast?"uhmm"bana son k'arya noory"yafad'a yana rik'e da ita da hannu guda "yayinda hannunsa guda ya Aza saman cikinta wai yaduba yaga taci Abinci...nide yaya bana so dan Allah"cak! yatsaya sbd ganin keys d'in motar daya bar mata Amma be sanar mata ba"Ina zakije da wannan keys d'in "nakane yaya Muslim"kinsan Allah na koma jin kincemun wani yaya Muslim d'in gulma saina hukunta wannan d'an mitsitsin bakin naki"kabeer

damu "ga Antyn taka"yafad'a yana kara mata wayar gefen kunnanta "ta wani sha mur kamar yana gabanta"dollars ya dinga yimata dariya"yana ji tanata yima Naseem shagwab'a yana biye mata daga k'arshe ya yanke wayar yace"rabu dashi ki huta"barama na kira Abokinah naji kayan nan dana tura su k'ara cikin kayan lefe sun iso"wai yaya Muslim harda Naseem zamu tafi Nigeria ko?"Eh to idan yasamu hutu ko?idan kuwa tsaka da karatu yake saidai yayi hak'uri "nasan matsalarsa siyama kin dinga had'asu vedio call sunayi"idan mun koma America sati 6 zamuyi hakan kuma yayi daidai da satin bikin"shima Abokinah ya shiga daga ciki kawai"yak'are maganar yana dariyar shakkiyanci"nidai ba ruwana"zaki san ba ruwanki idan su ummah sun ganki d'auke da cikin jikansu"kinga zasu tabbatar Eh Muslim da muslima suna da cikakkiyar lafiya ko? shiru tayi sbd dama babu wanda yasan tanada juna biyu "yayi shiru kawai idan sunje Agansu da Abinsu....yaya dai Mrs dollars bugaje?"harara ta balla masa"yayi murmushi yana dannawa suraj kira"bugu ukku ya d'auka yana fad'in baban soyayya ka manta da mutane! Hmm Ango kasha k'amshi"da sauran lokaci kafin nasha k'amshin nan"yadda kasan na jawo ranar haka nakeji sbd feeling yamun yawa"dollars yadinga b'abb'aka dariya"muslima kuwa duk tanaji ba k'aramin k'ulewa tayi ba"ta lura shima suraj zaiyi fitinah"ita kanta Amatallahi idan sunyi waya zancen datake mata yawan yimata kenan wai sex d'in da zafi?"itafa taga take taken yaya Ramadan kamar bazai bar taba idan an kaita"saidai kawai tace mata ta bari idan sunyi zataji"tana jin sadda suraj ke masa godiyar akwatuna dozin biyu  shak'e da kaya daya tura musu shida Ramadan kowa ya d'auki dozin yakai lefe"bayan sun gama wayar ya kalleta yace "my dubulle y'ar bak'a tashi muje"bazan jeba yaya isihu"ta k'are maganar dariya nacin k'arfinta"yasha mur"kinsan Allah? sai kin san kin kirani da wannan sunan" me k'watarki yau da dare daga wajena sai Allah"dena dariyar tayi tana masa magiya ai shine yafara janta"daga k'arshe tasaka rigimar yatashi su tafi ita ta gaji da zama wajen"mik'ar da ita tsaye yayi yana fad'in wow ji wata fine baby can"Atake ta had'e rai"yasaki murmushi ya sumbaci goshinta "Ahankali yace wuya ko dad'i"samu ko rashi *DOLLARS* na halimatu sa'adiyya ne ita kad'ai har,a Aljannah "Allah yasa sweet heart"ta fad'a cikin jin dad'i "ya kama hannunta suka yi gaba Abinsu......sati guda suka k'ara ak'asar suka koma America Dollars yaci gaba da harkan kasuwancinsa"suna kuma cigaba da zuba soyayya saidai Ace Masha Allah..... Ahaka rayuwar ta cigaba da kasancewa Hjy jamila suna zaman doya da manja itada Hjy naja'atu"wacce cikin k'ank'anun lokaci ta siye daddy,ta hanyar kyautatawa da bashi kulawa had'e da girmama iyayensa"Ayanzun haka idan ba itace keda girkiba zata tafi wajen Eyyah ta mata yini"tsakanin daddy da muslima yanzun Alhamdulillah ,harma kiranta yakeyi idan bata kirashiba"kabeer da Malika kuwa ko gaisuwa bata tab'a had'a su da ummah ba"itama nunawa takeyi bata san dasuba"duk wani Aike idan yatashi Ramadan ko Farooq take Aike"siyama kuwa ta zama d'iyar ummah indai ba'a skul to tana can tayita yimata firan Naseem"ko kuma idan daddy yadawo tayita shagwab'a saiya kira Naseem vedio call ya had'asu su gaisa"hakan yak'ara ma Hjy jamila tsanar yarinyar da k'inta"yanzun haka ta sami lafiya ta warke saidai tafiyarta bata daidaita kamar daba"sannan babban tashin hankalinta yanzun duk wani Asiri nata baya tasiri Akan ummah ko daddy"dukta k'ara lalacewa sbd zafin kishin data sakawa zuciyarta"dan ummah da gayya zata fito yima daddy rakkiya ta dinga yimasa Abubuwa gaban Hjy jamila"idan kuwa Hjy jamila tashiga gaidasa da safe ranar kwanan umman haka zata samu kansa saman cinyoyin umman ko kuma kan ummah saman kafad'arsa "hakan yasa tama dena shiga saita jira saiya fito su gaisa.....

yau juma'a,wanda yayi daidai da gobe ne gagarumin d'aurin Auren gwanayen"gaba d'aya

shirye shirye biki Akeyi "An k'ara k'awata bugaje's houses"sbd wannan biki da yau akeyin dinner gobe d'aurin Aure "Ayau kuma dollars da sahibarsa zasu iso k'asar"tun safe ummah take busy sbd murnan yau shalelen surukar tata zata dawo"ita kanta Eyyah tana cikin farin ciki"tun wancan satin ta Amshi d'inkunan muslima kala 30 da aka bada daga cikin kayan lefenta d'inki"saida Akayi wata biyu ana d'inkunan kafin Agama"wanda dollars ne yace Abayar idan sun dawo saidai tadinga saka Abinta"Ajiya kuma itama Aka gama yimata jeren kayan d'akin"wanda komai daga waje dollars yasiyo yaturo"babu ko sisin daddy"Amma Hjy jamila data samu labari ba k'aramin bak'in ciki tajiba "Azatonta daddy ne yasiya"gashi kayan da aka yima Malika jere ko rabin kyau da tsadar na muslima basuyiba"dukda itama komai na dubai ne Aka mata Amma uwarta ta raina"saidai kuma yau Hjy jamila na cikin farinciki sbd Abu biyu"yau daddy zai dawo wajenta,kuma Ayau takeso ta cika mummunan k'udurinta Akan muslima da dollars "tun jiya kayan Aikin suka zo hannunta"kuma kan kunnanta taji Ance kafin Atafi masallaci zasu dawo"hakan yasa ta tura Malika ta zauna bakin barandar shashen data hangosu tayi mata flashing"bayan ta turata ta fita saita koma d'aki da nufin ta kira Hjy ta bawa ta sanar mata yadda zatayi daidai ne sbd kar Asami Akasi.....bugu ukku Hjy ta bawa ta d'auka tana fad'in ranki yadad'e k'awata uwar gida Agidan Alh sulaiman!wannan tabbas ne k'awata "daga ni ba k'ari"itama wannan banzar lokaci na bata, Amma zamanta yazo k'arshe gidan nan sbd yau kema kinsan burinah zai cika Akanta da kuma wannan shegen d'an nata muslim....cak! daddy dake k'ok'arin shigowa cikin d'akin ya tsaya gabansa na fad'uwa "dama masallacin juma'a zai tafi shine zai bata sak'o koda su dollars sun iso baya nan"sai kawai yayi baya ya lab'e...kina jina k'awata?yanzun haka ga Malika can natura data hangosu tamun mgn zanzo na zuba maganin bakin k'ofar su taka"shi kuma wancan Ai bokan yace"nayi matsi dashi ranar danake da girki ko?okay to shikenan ba matsala"sai kuma tayi dariya tana fad'in, na soma Ace Aikin dazai mun kan muslima Atake ne sai yace sai an wuni An kwana tukum jikin nata zai fara d'oyi mijin yaji ya tsaneta"ke nifa tun yarinyar nan na ciki naso naga bayanta Allah ne beyiba"in baki mantaba ciki nawa na b'ararwa uwarta??tunda na lura Alh yafi son muskima Akan yarana na shiga na fita na saka Aka sanya masa tsanarta Azuciyarsa"kedai bari munyi mgn kar kuma Malika ta kira taji busy"daga haka ta yanke wayar.....✍️

Comments is compolsery 😎😎

Wannan book d'in nakudine idan kina buk'atar siya serious 500 normal grp vip grp 1000
Acc n 2230373842 NABILA ALIYU UBA BANK kituro shaidar biyanki 08100084251

Idan kika karantamun book baki biyani hakk'ina ba koki siya kika fitar Allah ya isa banyafeba
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne!*

.........cikin tsananin tashin hankali had'e da tsantsar mamaki da damuwa daddy yayi saurin yin baya yana jin kansa na juyawa"sai faman murza idanunsa yakeyi sbd yatabbar ba mafarki bane yakeyi"innalillahi wa inna ilaihir raju'un! kalmar daya dinga nana tawa kenan yana nufar cikin parlourn ya zauna kan kujerah 2 seeter dake pasin d'in k'ofar shigowa cikin parlourn "in bacin iskan fanka da sanyin AC da tuni jikinsa ya jik'e da gumi sbd tashin hankalin jin maganganun Hjy jamila"dama wa'annan miyagun halayen nata suka saka kowa ya tsaneta Agidan,

musammun ma iyayensa"biri yayi kama da mutum Ashe itace ta cusa masa tsanar muslima??yarinyar da duk idan yamata cin mutunci daga baya sai yashiga damuwa"dama itace silar zubewar duk cikunan nan da hafsat tayi yin  b'ari a baya??kuma yanzun take son ganin bayan muslima ta rabata da mijinta"shin wace irin shed'aniyar zuciya ce da ita??"jin motsin bud'e k'ofa yasaka gabansa fad'uwa "saidai yayi k'ok'arin danne yanayinsa ya kama danna waya yana satar kallon Hjy jamila da tunda ta fito da cup Ahannunta ta lura dashi gabanta ke fad'uwa"sai kawai ta juya ta koma ciki  d'aki "wato wancan Abin dake cikin cup shine zata zuba musu?? ya tambayi kansa yana tunanin wane irin hukunci yaka mata ya yanke mata?fitowarta daga cikin d'akin yasakashi dawowa tunaninsa "wai Alh ba masallaci zaka je bane?"Eh can zanje kinada sak'o ne? Ah ah naga dai lokaci yayi"ta fad'a tana kok'arin zama gefensa"bece komai ba yaci gaba da danna waya"Ahaka ummah ta sakko k'asan "Tasha gayunta,ga lalle jaa an mata na biki"babu wanda zai kalleta yace ta girmi Hjy jamila "hutu da kula da jikinta datakeyi ya b'oye shekarunta"wani irin bak'in ciki Hjy jamila taji,ga zafin sun b'ata mata Aiki"ga zafin kishin umman"kawai saita mik'e tsaye ta koma d'aki da nufin ta kira Malika ta sanar mata ta zagayo ta window ta Amshi maganin ta zuba daga can waje tunda ita daga nan ba halin ta zuba musu"saidai sau ukku tana kiranta bata d'auka ba"taja tsaki ta Ajiye wayar ta fito daga cikin d'akin"tana fitowa dollars da muslima na shigo cikin parlourn "suna sanye da kaya iri d'aya k'ananu"tsohon cikinta d'an wata biyar ya turo"sunyi matuk'ar kyau da shek'i"fuskokinsu cike da Annuri "ga wani fitinannan k'amshi nasu daya cika parlourn gaba d'aya"yana rik'e da hannunta,ummah bakinta yak'i rufuwa tunda tayi tozali da cikin muslima"dama ranta yabata da wuya Ace batada juna biyu "mik'ewa tsaye tayi tana fad'in ga y'ata ga y'ata"Aikuwa muslima ta rungumeta tana murna"dollars cikin jin dad'i ya nufi wajen daddy suka rungume juna"daga bisani muslima ta cika ummah tana kallon daddy"mama nah lallai zaman k'asashen waje ya Amsheki"to zomu gaisa tunda wajen mamanki kawai kika sani"cewar daddy cikin nuna jin dad'in ganin ta canza ga juna biyu datake d'auke dashi"Akunyace ta iso gefen daddy suka sakashi tsakkiya itada dollars daya wani d'aure fuska"cikin sub'utar baki tace"lahhh yaya muslim fushi kakeyi ummah bata damu dakai ba saini?"ki barni dashi muslima"shi yanzun waye yake ta tashi ne?"daddy ya kallesa yaga suna kallon juna shida muslima yana mata Alamar zasu had'u saita sani"yayi murmushi had'e da cewa ka barsu my friend tun da dai ga daddynka miye na damuwa?"hakane daddy"sai lokacin dollars suka gaisa da ummah ya sanar mata sashen Eyyah suka fara shiga sannan suka yo nan"Hjy jamila kuwa tamkar ta mutu sbd bak'in ciki"lura da kamar ma bbu wanda yasan da zamanta cikin parlourn ya sakata saurin juyawa tabar parlourn"daddy ya duba Agogo yana mik'ewa tsaye yace"my friend muje masjeed idan mun dawo sai ku tafi gidanku?"dato dollars ya Amsa dama yafi muradin hakan "ko kayansu da tsarabansu duk suna cikin mota"dollars ya mik'e tsaye hakan yayi daidai da shigowar siyama Aguje da yunifoam Ajikinta ta fad'a jikin ummah tana cewa ummah Ina yaya Naseem d'in?"lallai siyama mu baki murnan ganinmu?"sai lokacin ta lura dasu",dama taji Ance yau zasu dawo kuma harda Naseem zasu dawo shine dawowarta daga skul kenan ta taho nan taga ko zata gansa"kallon muslima tayi tana murmushi ta kuma kalli dollars da yake mamakin yaushe ta saba da ummah?"saita kwab'e fuska tace"ummah kin gani basuzo da yaya Naseem ba?"karki damu zamuje dake ki gansa idan zamu koma ko sati guda kiyi na mai doki"cewar dollars"ummah na murmushi tace" daka kyauta"ta damu dashi sosai wlh"daddy yace"shima yadamu da ita fin hakan ma"da naga vedio call nasa Tofa nasan fitinar yayi waya da siyama ne

"idan Ina gida na had'asu idan bani gida na k'yalesa"shiru kawai dollars yayi domin ya fahimci da wuya wannan shak'uwar tasu idan bata koma soba"musammun daya san shima shida mutuniyar tasa da haka suka fara"su shak'uwar tasu ta fima haka"yaya muslim! juyowa yayi ya kalleta"saidai ganinsu ummah yasaka ta kasa mgn "my princess bara muje mu dawo ki zauna wajen ummah da wannan sarkin maganar"ya fad'a yana nuna siyama"Adawo Ify muslima ta musu suka fita"suna fita Hjy jamila ta fito fuska washe tana fad'in muslima kune tafe saukar yaushe?"murmushi tayi tace"yanzun Ina wuni?"ah ah bazan Amsaba ki taso muje parlour na mu gaisa mana"murmushi ta koma yi sbd jikinta yabata badan Allah tayi mata hakan ba"tunda take da ita bata tab'a yi mata murmushi ba"karki damu mommy zan shigo Anjima"ummah tashi muje ciki ni yunwa nakeji "ta fad'a cikin shagwab'a"to shikenan muje y'ata "ta fad'a tana janye siyama daga saman cinyarta ta mik'e tsaye"itama muslima ta tashi suka rab'a Hjy jamila dake tsaye suka wuce "tamkar ta bisu da duka haka taji"gashi ta riga ta zuba maganin bakin k'ofar parlourn ta"wai yaya Akayi komai ya cab'e babu sa'a ne wai?"ta fad'a hankali tashe tana koma d'akinta...

suna shigowa cikin had'ad'd'an parlourn ummah ,muslima ta kama murna da yaba tsarin sashen"ummah nata kallonta cike da so da k'auna"domin yadda ta gansu ta fahimci suna matuk'ar zaman lafiya "bayan ta zauna umma ta kalleta tace" meyasa muslima baki bita d'akin taba?"wlh ummah ban yarda da itaba"waccan matar ba imanine da itaba"jikina ya bani kamar idan na bita zata cutar dani"waccan fara'ar data keyi ba har cikin zuciyarta bane"tanada wata manufa", to Alhamdulillah da kika gane"koda kim mayi k'ok'arin binta nima bazan barki ba"Abinda nakeso dake iyakarki dasu sai gaisuwa ko wani Abu nasu bance kici ba"in sha Allah ummah"madallah da fatan ba wata matsala ko?"babu komai"jiya munyi waya da Hjy tacemun ai kina zuwa ku gaisa "Eh hakane tashi kici Abinci sai kiyi sallar ko?"kanta Ak'asa tace "nidai sai yaya muslim yadawo"da murmushi umma tace"nidai dakin k'yale jiran Muslim d'in nan kinci Abinci ba'a son me juna biyu na zama da yunwa"shiru tayi batace komai ba "ummah tace tashi ku shiga ciki kiyi sallah"dato ta Amsa siyama, kuma ta lik'e wajen ummah wai tare zasuyi sallar.....tunda suka tafi masallaci har suka dawo dollars na lura da daddy bashida walwala kamar yana cikin damuwa "sai ransa yabashi kodai sbd Auren yaran ne, musammun Malika daya fahimci cikin family nasu basu san mugun halinta na b'oye ba"kasancewar shida daddy ne kad'ai Amotar "cikin girmamawa yace"daddy dan Allah meke faruwa dakai naga kamar kanada damuwa??"d'an shiru yayi kansa Asunkuye shi kuma dollars yana driving d'in "Ahankali ya shiga fara yi masa bayanin irin miyagun maganganun da yaji Hjy jamila nayi itada k'awarta da Abinda taso ta zubawa muslima ta taka..... Amamakin sa sai yaga dollars ya saki murmushi yana fad'in wannan tsohon Abune daddy"dani dasu Abbie da Anty habiba mun jima da sanin matsafiya ce ita, ta raba tsakaninka da muslima ta saka maka k'iyayyar ta Arai"Amma Alhamdulillah tunda ka gane dama nasan komai jumawa dole wata ran gaskiya zatayi halinta"Amma yanzun kayi hak'uri kabarta zuwa ko kwana 2 da gama biki saika yanke mata hukuncin daya dace"kuma Ayanzun karka sanarwa su Abbie sbd zasu damu"saidai ko idan Abba zaka sanar mawa.... Ajiyar zuciya daddy ya sauke cikin gamsuwa da kalaman dollars yace"haka za'a yi ,dan Allah ka rok'ar mun muslima gafara Muslim ta yafe mun"hak'ik'a naci zalinta ,nak'i sauke nauyinta "komai kaine ke mata"bansan meye zan saka maka dashiba muslim"haba daddy! karka damu"muslima koda ban Aureta ba jinina ce ita"tunda ta rasa mahaifiyarta shikenan tausayinta ya kamani"kuma nasan An shiga tsakaninku da ita ne"ita dama bata k'ullace kaba tasan komai"Ajiyar zuciya ya sauke yanata saka musu Albarka "dollars

Aransa kuwa beyi mamaki ba saidai ya gode ma Allah daya kare su daga sharrin ta"cikin raha suka iso gidan shida daddy"duk bak'i y'an biki na main parlour zaune da wasu friends d'in Malika"sai kallonsa sukeyi"Atake mutumin naku ya had'e rai suka wuce upstairs shida daddy"ummah da wata mata na zaune suna gaisawa suka shigo"ko zama basu yiba dollars yafara y'an kalle kalle sbd yaga Ina noorynsa take?"Iura da hakan yasaka ummah data gama yima daddy sannu da zuwa tace"muslima na d'aki nayi nayi tazo taci Abinci wai saika dawo"ga kuma meyin lalle nan na jira idan ta gama cin Abinci za'a mata"Allah sarki my princess ,mun saba tare muke cin Abinci shiyasa"ya k'are maganar yana nufar d'akin da take ciki"ummah kuma itada daddy suka nufi sashensa.....

cikin sand'a ya turo k'ofar fuskarsa k'unshe da tattausan murmushin daya k'ara k'awata fuskar tasa....muslima na kwance Atsakkiyar luntsumemen gadon ummah"d'an kwalinta na gefe kanta saman pillow"dogon gashin kanta ya zube saman pillows d'in tanata murmushi tana danna waya da Alama chats takeyi kuma yamata dad'i....wuf taji Anyi An fusge wayar"ta d'ago kanta Atsorace tayi tozali da gwanin nata yana jifarta da wani irin mayen kallo"ta turo baki ta juya masa baya "my princess bana hanaki irin wannan kwanciyar ba?"toba kaine ka tsoratani ba"naga hankalinki na wajen waya ne"nida Amatallahi da husnah muke mgn"kice gulmarmu kukeyi ko?"Allah ba haka bane"ya zauna gefenta bayan ta tashi zaune ta Aza kanta gefen kafad'arsa tana fad'in idan munci Abinci zanje Amun lalle da make up na zuwa wajen dinner"hmm! bakiyi sbd niba sai sbd zuwa wajen party ko?"mak'alk'alesa tayi tana masa magiya"ya lumshe Ido sbd jin tana neman sauya masa yanayi"gashi yanzun tunda cikin yafara tsufa bata san yadda dashi...nide yaya muslim tunda kak'i mun mgn shikenan na hak'ura da zuwa wajen dinner d'in "bayan mu ko dinner d'in ba'a yiba ga bi....sai kuma tayi shiru"noory kenan ki Ida fadar Abinda kikeson fad'a mana"Auren mu kinsan yadda yazo, kuma kika yita koke koken bakya sona to shagwalin meye za'a yi?"nima dama banida tsarin yin wata bidia"saidai Ina fatan Allah yasa ki sauka lafiya in sha Allah za'a yi Abinda yafi dinner ma in har Anayi my princess "to Allah ya kaimu"Amma Allah indai bazan jeba kaima bazaka jeba"karki damu duk inda kika saka k'afafuwanki Ina biye"yanzun miye tukwici nah idan mun dawo daga wajen dinner d'in ?"ta turo baki tace"ba madaran ka zan baka ba"sai kuma ta rufe fuska tana dariya"shima dariyar yyi ya mik'ar da ita tsaye yana cewa"meyin lalle na parlour ummah tace zata miki"to shikenan Amma nidai yaya muslim karkayi Nisa nafi son Ina jin motsinka "sarkin kishi! ta ballah masa harara suna fitowa daga cikin d'akin.....saida sukaci suka k'oshi sannan Aka mata zanen lallen bak'i da ja"dollars kuwa sanar mata yayi zasu fita shida suraj, zai turo meyin make up tazo nan ta mata"tunda ya tafi ummah na lura da ita batada walwala, ga yawan kiransa tana tayi ta lura kishi ke damunta"murmushi kawai tayi sbd ba k'aramin burgeta sukeyiba"sai yamma dollars yanufo cikin gidan sbd ganin ya kirata sau ukku Amma tak'i d'auka"yasan halin mutuniyar tasa Akan kishi"shi dariya ma take bashi sbd gani yakeyi yafita kishi"ko dinner d'in nan k'afarsa k'afarta zasuje,kuma sbd ya kama na gida ne shiyasa ya bari suje"ko wanka beyiba tunda suka dawo kayan jikinsa na d'azun ne"suna busy sbd dai shine babban Abokin Ango"kuma tunda suka fita basu mayi mgn da wasu friends d'in Amarya ba"yasan Abinda sahibar tasa kemawa kenan.....muslima na zaune da gownt d'in material silver Ajikinta,sark'a da Agogo da zobba da y'an hannu da takalmi da post duka silver ne Ajikinta "rigar ta bayyana cikin dake jikinta sbd ta kamata"tayi wani irin fitinan nan kyau tamkar bak'ar baturiya ko ba'a merikiya haka tayi"kanta ba d'an kwali ta bari tayi sallar magrib saita nad'a

head nata da kanta"idan sun dawo tayi isha'i saita kwanta"tana ta tunani tunda ta dawo bataga Malika ba da kabeer"itadai ummah na zaune da bak'i tana satar kallonta "Ahaka dollars ya shigo da sallama cikin k'asaitacciyar muryarsa me taushi da kauri"saida taji gabanta yafad'i tak'i kallon inda yake saidai umma ce ta Amsa sallamarsa"tana fad'in sai yanzun kadawo?"Eh umma sannu da gida"yafad'a idanunsa k'yam kan muslima"ummah ta Amsa da yauwa"batare data kallesaba tace yaya sannu da zuwa "be Amsaba sai kallonta da yakeyi"ita kuma saita juyo taga meye yasaka be Amsa ba?"sai taga kallonta yakeyi"saita sunkuyar dakai k'asa "Masha Allah ! my princess kin yi kyau Anya zan yadda kije wajen dinner d'in nan?"umma ta d'aure fuska tana fad'in karma ka fara ,tayi shirinta kaja ta b'ata kwalliyarta "dama kuma kamata laifi ko?"laifin menayi kuma ummah?"ka fini sani"ta k'are maganar suna barin parlourn itada bakinta da sai lokacin ya gaidasu"suna barin parlourn itama tayi k'ok'arin tashi....yasha gabanta ya rungumeta yana sinsinarta yace"haba giwar mata bana fushi bane "wlh muna can muyi nan muyi nan nida suraj duk nagaji ma"da wanka zanje nayi sai kuma naga gara dai nazo naga sarauniyar zuciyata ko ban kyauta bane ?" ta turo baki tana turashi"kinsan Allah zan b'ata miki kwalliyar nan na shanye miki wannan jam bakin kinsan zan iya ko?"nidai ka cikani"pls noory wlh da gaske nakeyi "murmushi ta saki sbd ta tuna Abaya yana kurin rantsuwa cikin mgn baya a tsarinsa"ya sumbaci goshinta da gashin kanta yace"kin yadda ko?"uhmm"to muje gida nayi wanka da sallar magrib saiki tayani na shirya ko?"dato ta Amsa ya cikata ta wuce ciki ta d'auki mayafinta ta fito"ya matso ya Amshi post d'in yace kawo na d'auka miki"batace komai ba ta bashi tanata shagwab'a ya rungumeta jikinsa suka fito"saidai suna fara hawa stars d'in muslima ta rirrik'esa wai Jiri take gani"wanda tayi hakane sbd ganin danda zon y'an mata cike da main parlour sun sha Anko"yanayin yadda tasan dollars tasan dole wata taji ya burgeta"shiyasa tayi wannan kirsar sbd karma ya kalli wata"Aikuwa ya d'auketa suka  sakko yana yimata rad'a waita rik'esa sosai karta fad'i dariya zaiyi idan ta fad'i "saita turo baki ta murd'e masa kunne"yakama dariya suna wucewa"gaba d'aya y'an matan suka bisu da kallo"wad'anda suka sanshi ko suke jin labarinsa suka dinga kallonsu cike da burgewa har suka fita daga cikin parlourn.....

sai wajen k'arfe 11:30 pm na dare suka dawo daga wajen dinner d'in data k'awatu"kai tsaye katafaren bed room muslima Aljannar duniya Anan suka yada zango"da kansa ya musu wanka suka kwanta yafara lalubarta"ba yanda ta iya ta bada kai bori ya hau, sbd tausayinsa takeji"Ayanzun har sati guda tanayi bata bashi kantaba"saidai yau harda kukanta suka rabu sbd ba k'aramar durza yamaba"washe gari da Asubama suna gama sallah ya d'ora daga inda ya tsaya"sai wajen k'arfe 8 na safe,bayan sunyi wanka baccin gajiya ya d'auketa"shi kuma yayi shirin zuwa wajen d'aurin Aure "tsabar yadda ya wanku ko Angunan Albarka"irin kalar shaddar jikinsa ya Ajiye mata gefen bed d'in yafita"da nufin ya sanarwa masu Aikinta da tun kafin su dawo Aka d'aukesu Aiki"cewar kar wanda ya tasheta"idan kuku ya gama girki ya jera ya tafi"bayan yasanar musu yafito parking"tuni driver da body quards nasa ke jiransa yana isowa suka wuce...... k'arfe 12 na rana Aka d'aura Auren sai muce Allah yabada zaman lafiya "....babban Abokin Ango sai bayan sallar Azahar ya nufi gida sbd yaje ya taho da ita bugaje's houses Aci gaba da hidimar yinin biki da ita.....

washe gari da safe Hjy jamila na zaune A main parlourn,masu Aiki nata kimtse kimtse da share share sbd hidimar da Akayi Aka gama"tayi nisa A tunani"sbd tun ranar juma'a ta matsa wannan magani na wajen boka A gabanta Amma daddy be kusance taba"tayi mamaki sbd tasan yanada fitinah",duk ranar kwananta sai yayi Amma beyi ba"kuma jiya data nuna tana son

abun sai yace' ta k'yalesa ya gaji"hasali koma d'akin be kwana ba saima ya dawo parlournsa ya kwanta ya barta Ad'ak'in baccinsa"ranta ya sosu matuk'a"tana cikin wannan tunanin taji muryar Daddy yana cewa masu Aiki sud'an basu waje zasuyi mgn"gabanta yafad'i ! ta kallesa taga yayi bala'in had'e rai"fuskarsa bbu Annuri ko zama beyiba yabita da wani irin raza nan nan kallo yace"Amshi nan"gabanta yafad'i dataga takarda nad'e Ahannunsa"saidai tana k'ok'arin mgn Aka turo k'ofar parlourn da k'arfi"saiga Malika da mijinta sun shigo bbu ko sallama "yana rik'e da hannunta tanata sharb'an kuka" A fusace ya turota gaban iyayen, ta durk'ushe kan carpet"gaban Hjy jamila yakoma fad'uwa....."ga y'ar iskar y'ar ku nan fasik'a na saketa saki ukku"bazan bar nan ba sai An biyani Abinda na kashe na Aurenta sbd bazanyi Asara ba" dana kwanta da ita ban sameta a budurwaba....tsab kalamansa cikin kunnan dollars da muslima dake k'ok'arin shigowa cikin parlourn sbd k'ofar Abud'e take.....✍️

Idan kika karanta mun book baki biyaba kokika siya kika fitar Allah ya Isa banyafe mikiba
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne*

......tsabar damuwa da yadda kalaman taheer suka daki zuciyar daddy kasa mgn yayi ,saidai Ido daya zuba masa daga shi har malikar dake zaune tana rusa kuka"yayinda Hjy jamila ke tsaye tana raba Ido sbd tsananin tashin hankali da rikicewa"daga dollars har muslima kallonsu sukeyi one by one....miye dalilinka na fad'in hakan yaro?"Anya kanada tarbiya da sanin girman na gaba dakai?"koma miye tayi Maka daidai ne kazo har gidansu da irin wannan cin mutuncin??"uhmm daddy kenan? ga y'ar iskar y'ar taku nan ku tambayeta"jiya dana gane batazo mun da martabarta ba saina k'yaleta banyi komai da itaba gata nan ku tambayeta kuji"na d'auka zata kamun hujja ta kare kanta"tunda ba dole sai mace tayi Alfasha zata iya rasa mutuncin taba"saidai banji tace mun komai ba"yau da safe Ina zaune a parlourn sai naga wayarta nata ringing kusan sau biyu"sai na tashi na duba lokacin ta yanke"sai naga tasaka my baby"nayi mamaki"kawai saiga text message ya shigo"dayake nasan pass word nata saina bud'e naga sak'o kamar haka *sannu Amarya! kina can kina holewa ni kin barni ko?"to wlh muddin baki dinga sato jiki kina zuwa Ina hutawa dake ba saina tona miki Asiri*....daidai nan sak'on ya tsaya gabana na fad'uwa sbd ban Amince ba Ina wasi wasi"saida na shiga what's app nata naga tana cikin grps na y'an sex da lesbian"ga chats nasu duk na batsa"bansan lokacin danayi jifa da wayar ba naje na sameta d'aki ta fito daga wanka..."sbd haka wlh sai An biyani kud'ina kona tona mata Asiri kowa yasani....kaiiiiiii! Dollars yakatse sa cikin karaji yana nunasa da yatsa fuska Agimtse  yace"ko hakane koba haka bane ta gama zama dakai kamar yadda kace"kud'i kaine matsiyaci saka  bani acc details naka Abiyaka ko nawa ne tsiyarka"saidai inaso kasani! dole na turaka bayan kanta k'ananun y'an sanda sun casamun kai"sbd naga Alamar bakada tarbiya baka san darajar nagaba da kaiba"in bacin securitys sunsan kai mijinta ne kama Isa ka shigo Anan harkayi wani dabbanci?"ya k'are maganar yana wurgo masa wayarsa key pad"cikin d'ari d'ari da shan jinin jikinsa taheer yace"Million 20 ne tsakanin lefe da Abinda Akayi hidimar biki"yak'are maganar yana d'aukar wayar ya saka acc n d'in ",sbd yadda zuciyarsa ta bushe da tsanar ta gara Abiyasa"saidai kuma k'asan zuciyarsa ya tsorata da kalaman dollars, yasan yanada ikon sakawa Amasa komai ya gadama"Hjy jamila dake tsaye har lokacin ta fashe da kukan bak'in ciki ta zauna durshan ak'asa"Malika kuwa kasa mgn tayi "yayinda daddy ke tsaye dafe da saitin zuciyarsa yana kallon su dollars"muslima kuwa kuka ta kamayi ta shige jikin

dollars "shi kansa dakewa yayi"yasan dama dole wata ran makamancin hakan saiya faru"Amma beso Abin yashafi daddy irin haka ba"mik'a masa wayar yayi,shi kuma yasaka kud'in "Adaidai lokacin securities suka shigo suka ja keyar taheer suka fita"sai lokacin dollars ya kalli daddy yace"kayi hak'uri daddy, zancen gaskiya yaron nan da gaske yafad'a",nasan wacece ita tuni"Amma Azatonta ta d'auka ban sani ba"tana zuwa hotels da club"karka sake ka damu"saidai Amata Addu'ar shiriya "nak'i sanar maka ne sbd wannan matar Alokacin ta Asirceka ba yadda zakayi ba....nice muslim na Asircesa? k'warai! ko nayi k'arya ne?"kina jifar muslima da mummunan kalami ,kina so ki saka daddy ya d'auka ita y'ar iskace ga hukuncin Allah kin ganin kan Malika"muslima na kuka ta d'ago kanta tace" Malika kin tuna ranar da kikace har d'akin yaya Ina zuwa mu kwana muna Aikata Alfasha?"Ashe kece ke Aikatawar bamuba"wlh dake da mahaifiyar ku Allah ya Isa tsakanina daku cutarwar da kuka mun "sanadinki Anzo har gida Ana neman gayama mahaifinmu mgn....jamilah ! ga takardarki na sakeki saki ukku"shekaran jiya naji duk wayar da kukeyi keda Hjy tabawa k'awarki,ki d'auki Malika ki je na yafe miki ita sbd bazan.....tari ya fara sai kuma ya yanke jiki yafad'i sumamme....muslima ta saki ihu Arud'e"dollars yaci kata ya nufi wajen daddy"muslima na ganin hakan ta wuce saman da sauri sbd ta kira ummah....Hjy jamila kuwa tsabar tashin hankali da yadda duniyar tayi mata k'unci kasa mgn tayi"ji takeyi kamar mafarki ne takeyi"Ace ita An saketa y'arta ma haka duk lokaci guda"sannan ita yanzun Ina ita Ina zuwa gidan mahaifinta da sunan zaman zawarci?"gara ta tashi tabar gidan tun kafin daddy ya farka yamata cin mutuncin da yafi haka"ta kalli Malika datake jin mugun haushin Abinda ta Aikata"sbd duk rashin imaninta ta tsani Aikata zina"zaki tashi muje ko kuwa dan ubanki"ta k'are maganar suna tashi suka bar wajen.....ummah da muslima hankali tashe suka iso cikin parlourn "dollars daya gama kiran tanimu driver ya kallesu yace"ummah ku zaunah bara muje nida Abba Asibiti Adubasa karki damu "my princess ki dena kuka yanzun zamu dawo kinji"sunkuyyar dakai tayi"hakan yayi daidai da shigowar su Abbie da Abba"gaba d'aya suka fita dollars na d'auke da daddy"ummah taja hannun muslima suka wuce saman tanata rarrashinta......saida doctors suka d'auki kusan Awa biyu Akan daddy sbd jininsa yakai k'ololuwa wajen hawa"koda Akayi sa'a ya farka bayan Allah ya Isa babu Abinda yake yiwa Hjy jamila, saida aka masa Alluran bacci sannan yayi shiru bacci ya d'aukesa"Abbie ya tambayi ba'a sin meke faruwa da hadda masa kamuwa da hawan jini?"dollars yamasa bayanin komai da harda sakin da aka yiwa Malika da ita uwar Malikar"Abbie yayi murmushi tare da cewa batama gama ganiba"Malika kuma sati guda na bata daya cika tadawo bugaje's houses da zama Ana kula da tarbiyanta"shi kuma taheer kayi hak'uri karka saka Amasa komai Asakesa"laifinsu ne sune suka ja hakan"dato kawai dollars ya Amsa ya mik'e tsaye yafita sbd yana so yayi waya da muslima "dan d'azun yadda take irin wannan kukan yatashi hankalinsa..... Ab'angaren Hjy jamila kuwa kayan sawarta duka ta kwashe da sauran kayan sawar Malika suka nufi gidan kabeer da nufin ya kaisu gidan Malika su kwaso kayan sawarta "dama lefenta yana gida ba'a kaiga kaiwa ba"suna tafe Hjy jamila nata zaginta"ita dai tayi shiru batace komai ba"bayan sun iso gidan kabeer Hjy jamila tafara matsar k'wallah sbd idan yaji matsalarta yatai maka mata...kabeer na zaune shida Amaryarsa a main parlour sun gama break fast d'in da Hjy jamila ta turo d'azun aka musu"kan yarinyar me suna zainab na saman cinyoyinsa da Alama Adaren jiya ya Angwance "sbd sai yauk'i takeyi da shagwab'a yana rarrashinta "saidai tunda taji sallamar mommy ta d'ago kanta ta musu kallo d'aya ta d'auke kanta tana d'aure fuska"ko sallamarsu saidai kabeer ya Amsa da mamaki yana kallonsu"mommy lafiya daiko?"babu lafiya

kabeer"daga ni har Malika muna cikin matsala wlh"ta fad'a tana kok'arin zama kan kujera "batare da zainab ta kallesaba ta mik'e tsaye tana tafiya da d'angyashi ta haye upstairs"Amamakin Hjy jamila bataga damuwar k'in mgn ko gaisheta da matarsa batayi ba Asaman fuskar kabeer"saima gyara zamansa yayi yana fad'in wace irin matsala ce"babu wani b'oye b'oye ta sanar masa komai"yaja tsaki yana yamutsa fuska yace"maganinki kenan Malika"saiki gyara in kuma kink'iya kika kwaso k'anjamau karma ki nuna kin sanni"ke kuma mommy tuni na rabaki da bin bokaye Amma kink'i ji ga Abinda yafaru"sbd haka nidai gaskiya babu ruwana bazan ma daddy mgn yadawo dake ba"sbd dai ba Aure saki ukku ne"wane irin zancen banza kakeyi kabeer?"nida keso kota halin k'ak'a na koma nayi zaman y'ay'an nah"yayi shiru saima ya mik'e tsaye "Malika dake matuk'ar k'ule da shariyar da matarsa ta musu,ga bak'in fatan daya mata idan ta samu k'anjamau"Amasife tace"wai kana nufin kaima tafiya zakayi ka barmu Anan kamar mararsa Aikin yi?"idan ita waccan y'ar iskar marar tarbiya ta tafi bata girmama mahaifiyar kaba kaima haka?"ke wlh koki mun shiru kona tattakaki "meye zatace muku ? bayan kunzo kun katse mana jin dad'i kun takuramu ta hanyar yima sammakon zuwa.....kabeer nice Ayau sbd nazo gidanka na takuraka? Innalillahi wa inna ilaihir raju'un! saita fashe da kuka tana girgiza kanta sbd tuna kalaman Eyyah data tab'a yimata Abaya" *indai duniyace zaki gani kema Ai kin haifa wata ran suruka ce zaki zama*.....wai baby hayaniyar mena ke jine haka?cewar zainab tana daga saman stars d'in bata sakko ba"sai yamutsa fuska takeyi"kasa mgn yayi"taja tsaki tana fad'in gaskiya bana son takura Akan me zakuzi mana tunda sassafe haka?so baby pls ka sallamesu kazo kamun tausa.....uwar data haifekice tausa ! y'ar iska marar kunya"cewar Malika Afusace"zanci ubanki kika koma zaginta wlh"nina ce ki kashe Aurenki balle kizo kina fad'a in fad'a da matata"pls mommy zaku iya tafiya"Hjy jamila batace komai hawaye masu zafi na zubo mata ta  tashi taja hannun Malika suka fito suka shiga mota "Malika taja motar tanata zage zage"yayinda Hjy jamila saidai Ido kawai"domin ta tsorata matuk'a da ganin komai ya cab'e duniyar ta mata k'unci"tunani takeyi tunda take da tata surukar ko d'aga mata murya bata tab'ayi ba"tana dai d'aure mata fuska tak'i gaisheta shima ba kullum ba"idan yakama tana gaisheta"ga Abinda ita tata surukar ta mata harya ninka wanda tayi nin kin banin kin"ga babban tashin hankalinta yanzun babansu ya mutu kuma gidansu na gado ta barma y'an uwanta"matan ubanta ke ciki zaune"ba wani taimaka musu takeyiba"kasancewar mamanta ta jima da rasuwa"kallon Malika tayi tace"muje gidan naki ki kwashe kayanki daga nan muje gidan Hjy tabawa idan gida yaka mata na siya saina siyar da sark'an gold d'ina "dato kawai malika ta Amsa tana jin tausayin kanta dana uwarta"tunda take da dollars be tab'a yin abu taji ya burge taba sai yau da yayima taheer gadagal"ko yaya dai yasan cewa itama tanada gata"kuma iyayenta ba k'ask'an tattu bane ba.....

***************

Rayuwa ta lula tayi nisa,wata ran da dad'i wata ran Asami Akasin hakan"su Hjy jamila Anga rayuwa"tun bayan ta siyar da gold nata ta siyi k'aramin gida ta koma"gashi dama shikenan Abinda take takama dashi ta kuma siyar,satin Malika guda daddy ya Amsheta "kuma ya hana Hjy jamila d'aukar ko tsinke Agidan sai,sai kayan sawa sbd yasan komai shine yasiya"yamata wata irin tsana ko sunanta beson ji"lokacin da Naseem ya sami labari yasha kuka saidai yasan mugun halinta yaja mata"shida yake wata uwa duniya shine yaturo mata dubu d'ari biyar"cikin kud'ad'en da daddy da dollars ke turo masa"wannan kud'i sune tayi ciko tayi furnitures da kujeru"Malika ta siyar da motarta ta siya mata kayan Abinci da freezer LG tana sana'ar siyar da

ruwan sanyi da kunun Aya A, Anguwar da take" tun batayi cikakken sati gudaba ta fara ji Ajikinta"ba fanka , ba Ac,ba kayan kallo,ba cooker gas ,dana girke take girki shima 3kg,ba masu Aiki,komai saidai tayi kota fasa"ga k'afarta ba lafiya sosai gare taba kamar daba"tun safe in ta fara Aikace Aikace sai takai k'arfe 3 na yamma ko k'arfe 4"saidai yanzun da sauk'i ta sami Almajiri"itama sana'ar sbd ta sami Abinda zataci takeyi"wani lokacin tayi ta kuka idan ta tuna daular data bari"kabeer kuwa harma mantawa takeyi dashi Ajerin y'ay'anta"gaba d'aya ko Ajikinsa da halin datake ciki balle ya d'auki wani Abinsa ya taimaka mata dashi"gashi ta fahimci matar daya Aura ta gama dashi sai Abinda tace yakeyi....Afannin Malika da farko taso ta kama umma raini"saida daddy yatasar mata da uk'uba"na sakata Aikace Aikace na gida,bayan ga masu Aiki nan"baya Amsa gaisuwarta ga zagi da tsangwama"sannan tafara nutsuwa ta fahimci ummah sbd Allah take zaune da daddy"gaba d'aya kowa ya tsaneta Amma banda umman"saima nasiha datake yimata"ta saka daddyn yasata islamiya "kuma bata zuwa ko Ina"ya Amsheta wayarta keypad ce kawai yanzun  hannunta"har dollars da muslima suka bar k'asar suma ba ruwansu da ita"Ayanzun data fara zuwa islamiya ta fahimci Abaya harda rashin isasshen ilimin Addini da bata dashi"ya sakata Aikata wasu Abubuwan"da kuma bata dace da kamilalliyar uwa ba"yanzun fatanta daddy ya barta ta fara Aiki kodan sbd ta in ganta rayuwar Hjy jamila da yanzun ta zama Abin tausayi....Asashen tsintsayen soyayya wato muslim da muslima"ba'a cewa komai dasu da suraj da husnah dasu Ramadan"soyayya kawai Ake zubawa"bayan bikin su da sati guda suka koma America "dukda su Eyyah sunso ya barta nan sbd cikinta yafara tsufa"ba kunya muslima ta nuna son bin mijinta takeyi"shi kansa yafi son ya tafi  k'afarsa k'afarta"yasan idan ya barta Anan kishinta bazai bari hankalinta ya kwanta ba"lokacin da suka iso America suka sami naseem cikin damuwar Abinda ya faru da uwarsa"rarrashinsa dollars yayi ya nuna masa yayi Addu'ar Allah yasa haka shine sanadin gyaruwar kura kuranta"kuma in sha Allah nan gaba da kansa zai siya mata gida ta koma"ba k'aramin dad'i Naseem ya jiba"ya rok'i muslima gafaran ta yafema mommynsa"tayi murmushi me ciwo sbd Ana barin halal ko dan kunya"Naseem ya b'ata da Hjy jamila dasu Malika sbd muslima"kodan sbd darajarsa zata iya yafe mata"Atake tace ta yafe mata"shima dollars yace" Abinda tayi masa Abaya ya yafe mata "sbd murna har kukan farin ciki Naseem ya rungumesu yana yi.....

kimanin watan su ukku kenan da dawowa America basu waiwayi gida ba"sai faman waya Eyyah da Abbie keyi sbd cikin muslima ya shiga watan haihuwa "shidai dollars saidai yace zasu zo"Amma beda niyar zuwa yafiso ta haihu nan Akula da ita da babyn sai bayan tayi 40 days sai yakawota Nigeria"hakan yasa Aka yima Eyyah biza suka zo itada Ramadan da siyama"sbd hutu sukeyi"Aranar tsabar murna kamar Naseem yayi kuka"siyama taga ya mata wata irin canzawa sbd har gemu yafara"sai surutu take zuba masa"daga k'arshe ya d'auketa suka fita sbd shima yazama d'an gari yasan wurare.....

Ayau kwanan Eyyah 4 kenan da zuwanta America itada siyama da ramadan"kusan kullum sai sunyi sama itada mutananta sbd batada ikon ganin muslima tayi Abu tace ta dena sbd lafiyar jikinta data babyn"shikenan dollars saiya goyi bayan muslima"gashi ta hanasu kwana d'aki guda Amma k'ememe dollars yak'i bari"dayaga tayi bacci zaije ya d'akko muslima yamaida ita d'akinsa "kuma baya sarara mata"shiyasa Asifiyar yau ta tashi da nak'uda "dukda ranta yabata fitinar dollars ce ta tado mata nak'udar"Abinka dame baki ta fara raki"Arikice suka nufi Asibiti da ita"saidai fa koda suka iso dollars yak'i fita daga cikin labour room"da yake turawa ne

basu wani damuba"Eyyah ce dai kawai keta masa fad'a yafito "yak'i kulata",ga hannunsa muslima ta rik'e tanata raki "sai rarrashinta yakeyi yana cewa tayi Addu'a"gaba d'aya shida bashine ke nak'udar ba Amma yafita rikicewa"da yake Allah ya kawota da sauk'i ko mintina 15 bata yiba Adak'in haihuwar ta santalo k'atuwar y'ar ta jajir me kama da ita"saidai ta d'akko farin mahaifinta da tsayinsa......✍️

Guys kunyi y'a 💃💃💃

mu had'e last page da dare in sha Allah

Idan kika karanta baki biyaba  kokika siya kika fitar Allah ya Isa ban yafe mikiba
[7/7, 13:04] Buhainat😁: *Littafin kud'i ne*

..... Alhmdllh! Alhmdllh!! kalmar da dollars keta faman furtawa kenan cikin tsananin farin ciki yana bin muslima da kallon tausayi"k'asan zuciyarsa yana koma jin tsananin k'aunar mahaifiyarsa da tausayinta"tabbas dole Ayabama mata"duk meson ya gama da duniya lafiya dole yabi iyaye musammun ma uwa"ya Ayyana hakan Azuciyarsa yana ta kallonta"matsawa yayi ya shafi fuskarta ta;d'an bud'e Ido tana sauke numfashin gajiya"sannu my princess"ta turo baki tare da cewa ni babu ruwana dakai da babyn da wannan Naseem d'in "wai uncle Naseem d'in kike fushi dashi sbd Addu'ar sa taci?"tayi shiru sbd wata iriyar kunyarsa ma takeji"lura da hakan yasaka ya dinga yimata dariya yana satar kallon likitocin na shirya babyn me kama da uwarta"Aransa yace"k'ilanma har tsiwar saita d'akko"ya kalleta yaga idonta Arufe"my dubulle kin biyani da kika haifi me kama dake"next time sai ki haifi me kama dani ko? ya fad'a k'asa k'asa yana kanne mata Ido"itadai bata tan kaba "tanaji wata doctor tace ya fita A kimtsa su"kuma babyn sai sun tafi da ita Ammata gwaje gwaje sbd gano Ai nahin tanada isasshiyar lafiya"be musaba ya fito baki washe"ko Eyyah bata tambayaba fuskarsa kawai data kallah tasan An sauka lpy" meye ta samu?"baby girl ce"Masha Allah! Alhamdulillah! ta fad'a tana mik'a masa wayarta tace"fiddobmun number d'in Alh...Adaidai lokacin Naseem da Ramadan da siyama suka iso gabansu "Naseem na sab'e da siyama" An haihu ne yaya?"suka tambaya Atare "Eh baby girl Aka samu....be rufe bakiba Naseem yayi ihu ya rungume siyama dake hannunsa"gaba d'aya sukayi dariya"Eyyah ta hararesu tana Amsar wayar ta fara k'ok'arin kiran Abbie "yayinda dollars y afara kiran suraj da Hjy yabsanar musu"yasan indai Eyyah ta sanarwa Abbie su umma dasu daddy zasuji suma....cikin k'ank'anun lokaci dangi ,y'an uwansa Abokan Arzik'i suka sami labarin haihuwar muslima"har dollars yakoma gida shida su Naseem suka shirya suka dawo ba'a barsu sukaga muslima da babyn ba sbd Anata binciken lafiyarsu"ko wanka sune suka yima babyn da uwar babyn"Eyyah dai nata mita wai zuwanta beyi Amfani ba"kuma saita canza musu wani wanka na Asali "sannan dollars yayi gaggawar nema masu biza nanda kwana 2 zasu koma Nigeria sai tayi 40 days ta dawo"bece komai ba sbd shima yafiso Ayi hidimar suna can"tunda ba'a yi hidimar biki ba yaka mata kowa yanzun yasan yana cikin farin ciki da samun wannan babbar kyauta da Allah ya masa"sai yamma Aka fito dasu zuwa d'akin hutu"dukda Acan ma inda suke "sun mata Alluran samun k'arfin jiki dana samun bacci"kasancewar dama dollars yabsaka Anyi order d'in Abinciccika irin na Nigeria babu b'ata lokaci Eyyah ta had'a mata tea me kauri ta loda mata Abinci me yawa"shidai dollars da Naseem da Ramadan na zaune

suna santin babyn da fisalta kamaninta kamar wasu k'ananun yara "ba k'aramin dariya suka bama Eyyah ba ta dai sharesu"muslima kuwa tak'i ma kallon dollars sbd kunyarsa takeji"k'asan zuciyarta tana kuma tunanin dama haka Akeji idan za'a haihu?"ni kuma nace taki da sauk'i tazo....my dubulke y'ar baka duk kece zaki cinye wannan Abincin?"ta b'ata rai tana kallon Eyyah kamar zatayi kuka tace Eyyah kin ganshi ko?"kunfi kusa takwara "ni Ina ruwana?"nazo na shiga tsakanin ku naji kunya daga baya"Abinci da yake mgn idan baki ciba y'arsa Ai bazata samu ruwan mama ba"dama kamar nasan kilbibin da zaku mun "sai cikin kayana na taho da gero tiya guda surfaffe"sai garin kunun tsamiya"idan zan koma Anjima zan damo miki kunun kanwa"gobe kuma na daka geron na dama miki farin kunu"nidai Eyyah dakin hak'ura dasu kunu d'in nan kin barta tunda ga tea nan"dallah rufemin baki kaima shine uwarka tasha data haifeka "itama shine uwarta tasha data haifeta"shiru dollars yayi yak'i tankata "muslima dai bata saka musu baki ba"sbd dama jiya sunyi waya da ummah tace" idan ta haihu kome Eyyah ta bata umarni  tayi kar tayi musu ta Aikata.....bayan ta gama cin Abincin Eyyah ta takura saida suka shiga bath room ta koma  gasheta sosai"sai gashi taji dad'in jikinta"bayan sun fito ta Amshi babyn A hannun Naseem tace su fita muslima zata shirya"saidai dollars beda niyar tashi sai kallon mutuniyar tasa yakeyi"Eyyah ta kallesa tace"sannu isihu isasshe! kana jira sai nace ka tashi ka fita ne?"muslima ta dinga b'abb'aka dariya"noory wlh kin san halina na fiki iya mugunta"kibar ganin dan ga wannan Eyyah d'in ko gabanta zan iya yimiki Abinda naso"murmushi Eyyah tayi batace musu komai ba"muslima ta masa gwalo"ya mik'e tsaye yana murmushi ya nufeta"ta saki ihu tana fad'in Eyyah kin ganshi ko?"wlh babban mutum ka fita idona na rufe"wace irin fitsara ke damun ku?"wlh koka fita kona b'ata maka rai"bece komai ba yabi muslima da kallon daya haifar mata dajin kasala yana furta zamu had'u dake dubulle y'ar bak'a"ya fad'a dariya na sub'uce masa "ta saki kukan shagwab'a"yanzun takwara kin hai
hunma ba zaki dena wannan shagwab'ar ba?" Ah ah Eyyah ki k'yalemun mata tamun shagwab'arta ai bake tayi mawa ba"juyowa Eyyah tayi ta masa dakk'uwa ya fita yana dariya....sai wajen k'arfe 5:11 Eyyah ta fito daga cikin d'akin ta iso reception ta samesu su hud'u zaune"dollars na vedio call da suraj yana dariya"sbd manyan maganganun da suraj d'in keta cab'owa"wai yanzun dollars maraya ne babu shi bbu zuwa garin maji dad'i sai muslima tayi 40 days.....babban mutum kuzo ku kaini gida nayi wanka na damo mata kunun"Naseem tashi kuje ka kaita"ke siyama zauna yadawo"ihu siyama tayi ta rik'e gefen rigar Naseem"kaga nidai muje da ita bana son fitinah "cewar Eyyah"dollars beyi mgn ba bayan sun wuce ya makama suraj harara yana fad'in kaga tsohuwar can dake takuramun ta tafi bara naje wajen noory ko kissing tamun"yana fad'in hakan ya yanke wayar ya kalli Ramadan da yayi k'asa da murya suna waya da matarsa Amatallahi" bara naje nadawo"kansa kawai ya gyad'a masa shi kuma yamik'e tsaye yanufi d'akin"muslima na zaune rungume da babyn tanata kallonta"kyakykyawar gaske"ita kanta Azuciyarta cewa takeyi da fara ce ita ba k'aramin kyau zatayi ba"saidai dukda tana bak'ar ta godema Allah"dama Allah baya had'ama mutum duka"yarinyar sai tayi kamar y'ar turawa,ga kyau ga gashi ga tsayi....ta shagala da kallon yarinyar uban gayyar ya shigo ya rufe k'ofar "saida taji k'irjinta ya buga data gansa"su noory me jego ko?"kai kuma Angon jego ko?"ta k'are maganar yana zama gefenta ya Amshi babyn"saita kwanto Ajikinsa ta saki kukan shagwab'a"menene ko Eyyah ce?"Eh mana"kinga yanzun tace mu koma Nigeria?uhmm Amma yaya sai nayi 40 days zamu dawo tare ko?ah ah noory"hak'uri zakiyi ko week end nazo nan na dinga yi"nafiso Antynmu (babyn) ta taso da komai irin na y'an k'asar mu"inaga gaskiya daga

